IDAN KAYA YA GAJI..

GAMMO MA YA GAJI

DAGA ALKALAMIN BADI'AT IBRAHIM MRS BUKHARI B4B GIDAN KAMSHI

MARUBUCIYAR LITTAFIN SHANONO DA KAILAN KU.

LITTAFI NA ƊAYA

SHAFI NA FARKO.

ƊANƊANO

Da sunan Allah mai rahama mai jin ƙai

Godiya ta tabbata ga Allah sarkin da babu irinshi daya bani damar sake fitowa a cikin wannan tafiyar mai rikitarwa. Masoya barkanku da jumuri

Godiya ga Ubangijina daya faɗaɗa ƙwaƙwalwata.

Godiya ga Ubangijina daya tausasa alƙalamina.

Na sadaukar da littafin ga Dr Zarah'u umar shohuwar gwamandiyar mata ta hisba, kuma Malama a jami'ar Bayero dake Kano. Kuma shohuwar kwamishiniyar matan jihar Kano. Mamallakiyar makarantar gyaran Aure dake dai jihar  ta Kano.

Edit with WPS Office

JIHAR JIGAWAN DUTSE:.

Jigawa wani sassa ne na kasar arewa maso yammacin najeriya. Hausawa sune mafi rinjaye a jihar sannan akwai Fulani, mangawa,badawa,da ngizimawa waɗanda yarukan kanuri ne. Mafi yawancinsu suna zaunene a ƙananun hukumomin  Birniwa, birnin kudu.

Tattaunawar samar da jigawa ya gudanane ƙarƙashin  jagorancin malam inuwa Dutse

Tsohon Kwamishinan noma da albarkatun ƙasa a tsuhuwar kano ( wanda ya haɗa da jihohin kano da jigawa ta yanzu)

Zamanin Alhaji Abdu bako.

An soma shi ne a ta farko_farkon shekarar 1980 (Agusta) lokacin mulkin soja na shugaba Ibrahim Babangida Badamasi. Duk da cewar an samu nasarar yin kiraye_kirayen a samar da jihohi, akasarin kananun hukumomin da aka gabatar da su a farkon rahoton samar da jihar an kawar da su aka kuma ɓullo da sababbi. Wasu yankunan da aka barsu sun haɗa da Albasu, ajingi,wudil,Sumaila, kachako,Takai. Kaɗan ne daga cikin waɗanda suka tayar da hankalin samar da jihar a zahiri a cikin sabuwar duniya ( jihar jigawa tarin Allah, a taken gama gari ga jihar

Faɗin ƙasa da yawan jama'ar jihar jigawa

Jihar jigawa tana da faɗin kasa kimanin murabba'in kilomita dubu ashirin da uku da ɗari da hamsin da huɗu. Sannan tana ɗauke da jama'a kimanin miliyan biyu da dubu ɗari takwas da ashirin da tara da ɗari tara da ashirin da tara ( ƙidayar yawan jama'a a shekara ta dubu ɗaya da ɗari tara da casa'in da ɗaya.

SHIMFIDA

SABUWA:.

Edit with WPS Office

Misalin ƙarfe biyun daren ranar asabar, goma ga watan Agusta watan marka_markan ruwa kenan. Kamar yadda aka saba yau kwananmu uku cir ana ruwa, yayi ƙarfi kana ayi irin masu yif_yif ɗinnan afumangai .  A nan jihar Jigawan Dutse A wannan daren ruwan ya shallake tunanin mai karatu wani irin ruwa mai ƙara haɗe da wata iriyar iska akeyi, ga ƙanƙara dake ta ragargazan kwanukan jama'a, sannan  ba ma iyakar Jigawa bane kaɗai ruwan ba, garuruwa da dama na Arewa a cikin ruwan suke muna jin labarai a TV da rediyo, ruwan yayi ɓarna sosai, har ambaliya ruwan yayi a garin Jos cikin wata unguwa can tudun osi, asakamakon wani rafi dake wajajen ƴan tukwane daya cika, an yi asarar rayuka da dama, ruwa ya tafi da gidaje da mutane da dama, nasan ba zaku kasa tuna shekarar ba ko? A al'ada da ɗabi'ar mutane sukance in ana ruwa anfi samun bacci mai daɗi da nishaɗi, wanda yake cike da mafarkai masu daɗi ɗauke da yanayi mai burgewa. Wanda ni a wannan lokacin tsaye nake a ɗakina ina aikin kai kawo yadda kuka san soja a filin daga, gara ma su aikin kuɗinsu suke yi. Minti_minti ina ɗaga kaina in kalli agogon dake manne a bangon ɗakin  nawa domin sanin haƙiƙanin lokaci. Sannan ina matsawa bakin taga in buɗe labule inga ko zan ga shigowar motar Babangida. Amma shiru, kafin ruwan ya tsananta wajajen sha biyun dare na yi karambanin kiran layinshi. Yanayin da ya sani dana sani kenan, ɗaga wayar akayi ba tare da ance komai ba, ina jiyo nishin Babangida tare da wata macen tabbacin suna gudanar da mu'amalar banza. Na kirane bai san ya ɗauki wayar ba, a_a yana sane ya ɗauka domin ya ninka mun azabar da yake bama ruhina, a_a ita karuwar da yake tare da'itane ta ɗauki wayar su suka barma kansu sani, ni dai babu guiwa na zare wayar a kunnena sabida abinda nake jiyo ma kunnuwana Babangida yana wani irin mugun sambatu na fitar hayyaci, da wani irin gurnanin da ni da nake a matsayin matarshi ma bansan ya iyasu ba kun dai gane. Na kirashi ne in sanar mishi irin zazzaɓin dake damuna matsananci, ba abun in fita ba kuma zargin daya saba ya hau kaina ko kuma ya haukace dan kishi, ashe rabon zanji wannan tashin hankalin ne.

Hawayen dake zubowa daga guraben idanuna na share, na haɗiyi wani yawu mai ɗaci da kauri, na lumshe runannun idanuna ihun Babangida da sambatunshi suna tai mun amsa kuwa. Wai in tambayeku dama haka maza suke ne, ko kuwa nice dai banyi sa'a bane?.

Ko da yake bani kaɗai bace banyi sa'a ba. Da yawa _yawan mazan wannan ƙarnin da muke cik zinace_zinace suka sanya a gabansu sai dai wanda Allah yasa yafi ƙarfin zuchiyarshi. Kai Ina cikin tsaka mai wuyar fita, ina cikin nadama, baƙin cikin kasancewata matar Babangida tur da namijin da baya iya killace kanshi ga iya kar halalinshi, tur da mazinatan maza masu irin halin bunsuranci irin na Babangida, Tur da Babangida.

Bakin taga na dawo na yaye labulen da kyau, na nutsu bil haƙƙi zubar ruwannan a makeken tsakar gidan kawai nake kallo, da yadda ruwan yake gudu, da kuma yadda ya lalata shukokin fulawa da aka daddasa a gidan domin ƙawa. Gidane na alfarma amman a wajena bashi da wani amfani ko misƙala zarratin.

Karfe ukun dare dot sai naji wayata tayi ƙara a zabure na duba kasancewar wayar na riƙe a

Edit with WPS Office

hannuna.

Ganin sunan Maigogul akan tangaran ɗin wayar sai na tsinci kaina da faɗuwar gaba, nasan dole dai wani mummunan abunne ya faru, dan a gidanmu munanan abubbuwa suna yawan faruwa, in da sabo ma mun riga da mun saba. Iyai kuwa ina ɗagawa sai naji muryar Rakiya a madadin inji ta Maigogul.

"Lolo kina jina" Lolo shine sunan da ake kirana dashi a gidanmu, da ƙawayena na duniya. Sabuwa kuma sunan da gama gari ke kirana dashi kenan, da kuma dangin Babangida ma haka, da ƙawayena na makaranta dan da Sabuwa nake amfani a makaranta, shine a jikin katin ɗan ƙasana ma.

Ta faɗa da ƙarfi kasancewar ita dama Rakiya haka take magana gatsal_gatsal kamar rubar zawo.

Ina jinki Rakiya lafiya da wannan muƙu_muƙun daren?"

"Ina fa lafiya kin ganmu a gidan Labbai ɗan gidan da uban naku yake taƙama dashi ya rushe abunki da ginin biskit ginin laka. To gamu nan dai a gidan Labbai  tare da su Sa'ada da Qamriyya ragowar basa gidan abun ma ya faru, Uzairu zuchiyata ne da Maigogul suka kawo mu wajen Labbai. Kinga babu abunda muka ɗauka ruwanma har gidansu Malam Tanko duk ya haɗa ya narka, gidaje da yawa duk sun rufta. To gidanma yayi ƙarko irin ruwan da ake zabgawa a wannan damuna ta bana da yawa yake. Har gidajen bulo da bulo ma sun rushe. Ɗaiɗaikun gidajene a unguwar basu rusheba, in basu rusheba zaki tadda kwanon gidan ya yaye. Ita kanta Labbai kwanon ɗakinta ya yaye kin ganmu a cikin ruwa a takure wallahi. Kujerunta duk sun tsotsi ruwa"

Idanuna na runtse dama yaya lafiyar kura ballantana tayi hauka. Bayan na sauke ajjiyar zuchiya sai nace

To Rakiya gobe da sassafe zan shigo gidan in sha Allah. Kun faɗa ma su Ramatu da Adama suma?"

"Duk an sanarma kowa dama kece ƙarshe, su kuma waɗancan ai na faɗa miki sun tafi yawon barbaɗa acan dama zasu kwana basu san me ake ciki ba. Sai in sun dawo idanunsu ya gane musu"

Ina jiyo Maigogul yana cewa.

"Ki bar ce musu sun tafi yawo barbaɗa Rakiya ina faɗa miki, ki kiyayeni kar mu raba abun faɗe a gidan surukai da daddarennan"

Ai kuwa Rakiya ta dira a wuyan Maigogul da hayaniya haya_haya, sai faɗi in faɗa suke yi. Nasan ba abun kunya bane a wajensu ace a gaban mijin Labbai ɗin suke wannan rikicin ba. Dan baƙin ciki da takaici sai kawai na datse wayata kawai, tare da dafe kaina daya ƙara tsananta  ciwo.

Edit with WPS Office

Rayuwata cike take da badaƙala iri daban daban da sannu zaku fahimci komai, amman gaba da baya a cikin rayuwata babu dama_Dama. Ba gidan uban ba, ba gidan mijin ba. Lulawa nayi cikin tunani rayuwata ta baya har lokaci ya shura sosai ba tare dana sani ba.

Wayata ce ta ƙara yin ruri a karo na biyu, Adama ce ke kirana yata ce ɗakinmu ɗaya da'ita, itace ta biyu a gidanmu. A ɗakinmu akwai mata tara cib maza huɗu. Sama shine babba obarol, sai Adama, sai Ramatu, sannan Gaza, sannan Labbai, sai  Uzairu zuchiyata, sai Salaha, sai ni, sai Sadiya sannan Magazin, sai Halima, Sa'ada, sai Autarmu Aisha.. A ɗakin kishiyar Rakiya  Hauwa tana da yara mata takwas sai maza biyu  Ma'aru da Masa'udu. Mu rai ashirin da uku cib mahaifinmu Maigogul ya haifa. Bakin gadona na samu na zauna tare da ɗaukar wayar"

"Lolo Rakiya sun kiraki wai gida ya rushe ko?"

Ajjiyar zuchiya na sauke kana nace.

Yanzu na gama wayar ma dasu"

Cikin hargagi da faɗa take cemun.

"Wai kinji shegen mijin Labbai da fa wai yaƙi fita ya bar ɗakin yana gado, sai ita Labbai ɗince ta fito. Da ƙyar Labbai ta lallaɓashi yana kumbure_kumbure ya yarda ya fita, kuma kwanukan ɗakinta duk sun yaye ma a cikin ruwa fa suke . Wannan wanne irin iskanci ne ɗan abu ta kazan...." Ta ɗebo zagi ta dinga ɗurawa dai, dama mijin Labbai ba ƙaramin tatacce bane. Uhm nayi shiru ina ruwa ina zagin gada, dan ta fanni da dama mijin Labbai yafi Babangida mutunci babu haɗi.

Adama in dai  Badaru ne ai ba yau ya soma wannan du da gwa ɗin ba. Yanzu dai gobe da sassafe zanje can gidan musan me za'ayi."

"Me za'ayi ko kuma gobe zaki je ki kwasosu su dawo gidanki da zama kafin a samu a gyara musu nasu gidan. Duk da ba zuchiya mazan gidan suke dashi ba, koma ince a ina zamu tsintosu ma. Su kuma ƴan matan gidan nasan sisinsu zai yi wuya su iya bayarwa kema kinsan rayuwar gidan namu nafsi_nafsi ce tunda sai ka fita ka nema zaka samu kaci. A haka Maigogul ya gina mu. Nima fama nake yi. Ɗakin kishiyoyina duk kwanukan sun yaye. Kin gansu fa a ɗakina suna kwance suna bacci da bataliyar yaranmu"

Kunji wata sabuwa.

Idanuna na lumshe na soma tunanin taya zan kwaso bataliyar gidanmu in kawota nan gidana su zauna? Bama wannan ba in ce ma Babangida kuma me, zaman me kuma zasu yi, kishiyata dake bin diddigina kuma sai ta samu labarin da take son samu a kaina a ɓagas? Dan ko Rakiya saita ɓarar mun da galan_ galan na asirina da  Hamida ta jima tana son ta samu labari akai. Harda ƙarin labari akan sauran ƴan uwana, duk da wannan su zasu fallasa ma kansu da kansu.

Ai ba shiri na miƙe tsaye a lokacin ruwan da akeyi ya sassauto sosai kasancewar lokacin karfe

Edit with WPS Office

biyar tayi harda minti ashirin anata kiraye_kirayen sallar asuba.

Ta taga na hango tsakar gidan babu Babangida babu motarshi tabbas acan ya kwana, ko a gidan karuwai ko a club tare da ƴaƴan iska irinshi.

Kwafa nayi kawai jikina da mugun sanyi na faɗa banɗaki na ɗauro alwala nazo nayi Sallah. Nayi shiru akan sallaya inata tubkewa yana warwarewa. Ni yanzu yaya zanyi da su Maigogul, zamansu dani ba abu bane da zai haifar da ɗa mai ido ba. Ko Babangida ya yarda Malama Babba mahaifiyarshi ba zata taɓa yarda ba, balle ma ko sama da ƙasa ma zata haɗe Babangida bazai yarda ba tabb. To a cikin ƴan uwana wanda muke ciki ɗaya da waɗanda muke ƴan uba ni banga gidan wacce zasu je su zauna ba, dama_ dama gidan Layuza itace mai ɗaki ɗaya estira nasan uwarta da ƙannenta zata kwasa. To mu dai a ƴan ɗakinmu nice kaɗai nake da waje da zan iya ajjiyesu, amman akwai gaggarumar matsala. Ni ba kuɗi ba balle ince ko haya zan kama musu tunda kusan nice mai kuɗin kab familin, gashi yau da suna a gidan abokiyar zamana Hamida ta haihu yau za'ayi sunan gida zai ɗinke da baƙin nesa dan ba ƴar gari bace, kuma na fuskanci ƴar dangice sosai, la'akari da sanda aka aurota irin jama'ar da suka rakota, da kuma lokacin da ta haifi ɗanta na fari, itama kuma bata da aiki sai zuwa garinsu biki ko suna har mamaki Babangida yake bani yadda yake suntirin kaita garinsu sha'ani saɓani ni da tun da mu kai aure bai taɓa takawa ya je gidanmu ba, har wani ciwo da Rakiya tayi aka cire rai ma da'ita wallahi Babangida bai je ba, kwananmu ma talatin da uku a asibiti, ya buɗi baki yace mun ya mai jiki ma mitsiyaci ya kasa. Shima gidansu gidan yawane, ga ƴan garinsu da suke da zumunci da son zuwa sha'ani yau dai gidan zai kasance a ɗinke. Gori da habaici ni kuma saita ALLAH. Gashi ni ba abun in kulle ɓarayina in bar gidan har sai na tabbatar an gama sunan ba.

Da waɗannan tunane_tunanen daba fissheni zasu yi ba na miƙe na fito falona tare da nufar ɗakin yara. Zazzaɓine sosai a jikina dan jikina har rawa_rawa yake yi mun.

Mardiyya na zaune a kan sallaya ɗiyata ta fari kenan ƴar shekara goma sha huɗu da haihuwa, sai dai in kuka ganta zaku ɗauka tayi irin sha bakwai ɗinnan. Gaɓa_gaɓan jiki gareta sosai, ga nonuwa a ƙirjinta har mamaki nake yi, gata a dire kamarta ɗaya sak da ubanta barinma bakinsu."

Mardiyya kaddai su Aminu basu tashi sun yi sallah ba?" Na tambayeta ina kakkafeta da ido.

Cikin tsari da kwainane irin na gadon gidansu Babangida take tsaramun yadda akayi, bari kuji me tace"

"Aminu yaƙi tashi, Adɗa'u kuma fitsari yayi a kwance, ita kuma Malama zazzaɓi take yi"

Malama Autata kenan, wacce taci sunan mahaifiyar Babangida sai yayi mata alkunya da Malama. Sunan da sai da akayi rikici bayan an saka shi, dan ita mahaifiyarshi bani taso in haifi wacce zata ci gajiyar sunan nata ba sabida ƙiyayya.

Shigowa nayi na zauna a kan gadon nasu mardiyya na taɓa jikin Malama ai kuwa kau da zazzaɓi. Ba shiri na tallafota jikina, to ita irin yarannanne masu shegen shagwaɓar tsiya da yima ciwo kuka ( kamar Abdullahi na) ai wai dana tallafota sai ta sau kuka. Kukanta ne ya tashi Aminu da

Edit with WPS Office

Aɗɗa'u a bacci. Gadonsu daban suma su biyu.

"Ummi tun da daddare wannan yarinyar take ta mana kukan banza"

Cewar Aminu mai bin Mardiyya"

"Ka wuce kaje kayi alwala kayi Sallah. Ummi bakinshi baki ji wari ba"

Cewar Mardiyya data tashi tsaye tana naɗe sallayarta.

Aminu ya doka mata harara ya fita zuwa banɗakinsu da ƙofarshi ke jikin ɗakin nasu. Shi kuma Aɗɗaku na dubeshi nace.

Sannu makaka na hanaka shan ruwan dare baka ji Aɗɗa'u balle jiya an sha ruwa, mardiyya in Aminu ya fito ki taimakama Aɗɗa'u yayi  wanka. Ita kuma uwar masu gida zan mata a bayan gidana, zata ma rakani gida, zaki je umman masu gida?"

Na tambayeta ina shafa bayanta ƙaunar yaran da tausayinsu  na huda duk wata tsoka ta jikina. Mardiyya ce ta shiga aikin dungurema Aɗɗa'u kai ni dai na suri Malama na kaita ɗakina na yi mata wanka jikinta da zafi rau gashi bani da magani, kuɗin hannuna iyakar kuɗin da zanyi na mota ne in je gida.

Wanka na shiga nayi zuchiyata babu daɗi ga ciwo na cina, saida nayi kuka sosai a banɗakin kafin na fito

Mardiyya na tarar a ɗakin tana shafa ma Malama mai, Aɗɗa'u kuma yana batun yinwa acici kenan mala'ikun tauna. Kai na girgiza na wuce wajen sib ɗina na zaro doguwar rigar kanti da mayafinta a tare. Dana juyo na kalli Aɗɗa'u yasan sauran ba shiri ya fice. Ina zaune a gaban wadrop ina shafa maina na Queen Elizabeth muka jiyo dirin motar Babangida. Wani ƙududune ya tokaremun wuyana, ihunshi na jiya ya bijiromun. Agogo na kalla ƙarfe shida na safe, na dawo da idona kan Mardiyya da Malama. Mardiyya ita ke buɗe ma Babangida get a duk sanda zai fita ko zai dawo. Komai dare.

Kur nake kallonsu a zahiri a baɗini kuma basu nake kallo ba, bafa a cikin hayyacina nake ba rayuwar kawai akeyi.

Toh fa kunji wannan salon. Na faɗa muku akwai bambanci wannan ɗanɗanone ci gabansi zai soma zuwa muku zuwa bayan Sallah da yardar Allah da misalin karfe takwas na dare in sha Allah.

Ku dai ku shirya kuma ku gyara zamanku wannan tafiyar ta bambanta da sauran.

Nagode sosai da ƙaunarku a gareni.

Edit with WPS Office

Masu son magana dani kai tsaye ga link na group ɗina ku shiga domin kasancewa danu.

IDAN KAYA YA GAJI.....

GAMMO MA YA GAJI

MALLAKAR BADI'AT IBRAHIM MRS BUKHARI B4B GIDAN KAMSHI

LITTAFI NA ƊAYA

SHAFI NA BIYU.

"Ummi! Ummi"

Ashe mardiyya ta daɗe tana kiran sunana wallahi banji ba, wai ashe har sun iso gabana ban sani ba. Hmm Namiji tuwon ƙaya miyar allura. A sanyaye cikin wata iriyar murya nace.

Mardiyya ki kama Malama kuje ki bata tea, zan kawo miki nera hamsin a siyo mata parasitamol ki bata.

Ni zan je gidane amman ba daɗewa zanyi ba."

Bana son ma in ji me take son cewa. A sanyaye ta kama hannun Malama zasu fita, sai suka bani tausayi sabida a halin yanzu bana iya shiga cikinsu ma muyi wasanmu da dariyarmu kamar yadda muka saba, dafa har wasan carabke muke yi dasu, harda wasan ɓuya. Amman ubansu ya hautsina mun ƙwaƙwalwa da rayuwa ma.

Mardiyya"

na ambaci sunanta. Ta juyo ta kalleni.

Gidanmu ne ya rushe jiya da daddare shine zanje in gansu suna gidan Labbai."

"Allah sarki ummi, to yanzu ummi a gidan Anty Labbai zasu zauna har a gyara musu?" Ni dai nace.

Ban sani ba tukunna, ki kula mun da gida ki yi gyare_gyare duk wanda yazo nema na kice bananan. Ku saka sababbin kayanku da Babanku ya ɗinka muku na cin suna"

Na dai faɗa mata duk abinda ya dace taja hannun Malama suka  fita. Idanu na runtse hawayen da nake ta tarewa suka zubo a guje. Wayata da Adama ta shiga kirane yasa na miƙe ba shiri na

Edit with WPS Office

saka riga na yane kaina da mayafin rigar, daidai wayar Adama ta kuma shigowa. Da sauri na ɗaga.

"Lolo wai baki fito bane? Nifa ina gidan tuntuni. Ɗakin Labbai kinga ruwa itama anata kwarfewa da kofi dai yanzu"

Ban fito ba yanzu zan fito nima"

Carab sai Maigogul ya amshe wayar yace dani.

"Lolona in zaki tawo ki tawo mana da ɗan abincin da zamu ci, nan wajan Labbai babu komai sai ɓeraye a ɗakinta, ƴan uwanki kuma basu dawo ba balle mu samu abun lasawa"

Ya ƙarashe magana yana dariyar da ta zame mishi ɗabi'a a duk ƙarshen magana, ko na faɗa ko na lumana.

To maigogul"

Kaɗai na iya cewa na ajjiye wayar na fita da sauri. Ina fita Babangida na tsaye a bakin ƙofa hannunshi riƙe da labule yana magana da Aminu. Wato bazai ma shigo ba yake nufi, ai shikenan .Ganina ne yasa ya dubeni. Buɗar bakinshi yace

"Sabuwa ga kayan miyannan ku fito ku gyara ke da Mardiyya kafin maƙota su shigo su kama muku. Su Sa'a da Rauda ma suna hanya"

Kuri nayi mishi da idanu ina dubanshi, shima kasaƙe yake kallona. Sama da ƙasa Allah bai bani ikon ce mishi komai ba. Wani ƙududune ya tokare mun maƙoshina kawai. Ji nakr kamar in ɗura mishi zaggi ko zuchiyata zata rage raɗaɗi.

"Ya ina magana dan bura'ubanci kin kakkafeni da idanu kina kallona ia idandunanki na fitsara? Ko da yake ba'a baku tarbiyya ba, in banda haka ya ina magana a gaban yara zaki yi mun banza? Ko da yake masu ba da tarbiyyar suma..."

Sai yayi shiru yana hararata. Hawayen idona na mayar, na dubi yarana na sake kallonshi. Da ƙyar na danne zuchiyata nace dashi.

To gashi dama kai nake jira ka shigo inaso zanje gidane wani abunne ya faru, amman bazan fi awa ɗaya ba zan dawo sabida abincin sunan, Mardiyya zata soma gyara kayan miyan"

Ai ina wuta ya saka ni daga faɗar haka, sai ya shigo ya soma mun tashanci. Mardiyya kuma ta tattare kan ƙannen nata suka shige ciki, inda sabo Babangida ya saba da tozartani yarana na gani. Shi yasa da sunga ya shigo suke tashi sum_sum subar ni daga ni sai shi.

Ya daɗe a tsaye a kaina yana zagina ta uwa ta uba har da lakace mun hanci.

"Dama a gidanku ai kullum sai wani abun ya faru, wannan ba sabon abu bane. Bazai wuce ace kuje ku harhaɗa kuɗi ayi belin Rakiya a ofishin ƴan sanda ba ai. Ya ana suna zaki kaɗa ƙafarki ki

Edit with WPS Office

fice yawon ɓel_ɓel ɗin da kika saba. Sabida bakya son ganin dangina ko? Kila ma wanine yake jiranki a hotel ko? Shine ni zaki ma ƙarya kice zaki je gidanku."

Shi dama ɗan iska a kullum kallon kowa ɗan iskane yake ma kowa.

Babangida bashi dai da aiki sai zarge_zarge. Baya ƙaunar ince zan fita sabida yasan irin  abinda yake shukawa a wajen shi yasa yake tsoron kada shima a shuka mishi.

Idanuna cike da ƙwalla a lokaci guda kuma ina murmushi na dubeshi nace.

Kura tayi lafiya Babangida. Da dane wallahi Allah kafin ka sauke yatsa na karya maka, kasan na fika iskanci Yar balaja'u ce ni cikakkiya wallahi kaima ka sani. Batun kayan miyan suna kuma Mardiyya zata gyara. In kuma dole sai ni ɗin sai a jirani na dawo daga lalurata"

Ina gama fadar haka na yi wucewata kitchen ɗina dake falon na ɗaura babbar tukunya da ruwa.

Hakan fa bai mishi ba sai gashi ya shigo kitchen ɗin yana kiran sunana.

"Wai ke Sabuwa ubanme kika taka, ni kike cema zaki karya mun yatsa, harda wani kura tayi lafiya an faɗa miki ko wanne gida irin gidanku ne da zan kasa ladabtar da rashin mutuncinki? Kura ta jima batai lafiyaba dan ubanta. Tunda nake ban taɓa ji ko a tarihi irin gidanku ba taron marasa mutunci,gayyar na ayya, gayyar na yadada. Ni dai Allah yana gani bazan dena nadamar saninki da nayi ba wallahi.

Ya buga tsaki ya fita fu ya barni da ƙamshin turarenshi da bazan mance da ranar dana soma shaƙa ba. Har ya fice bai dena zage_zage ba.

Harna gama farar taliyarnan ina tsaye a kitchen ina jijjiga na damuwa da takaicin rayuwata ma baki ɗaya, gami da nadamar sanin Babangida da nake yi kuma zanci gaba da dana sani abadan. Mardiyya ce ta shigo tace.

"Ummi kin yi baƙi suna falo"

Na dubeta nace.

Babanku fa?"

"Ya shiga ɗakinshi"

To tsane mun taliyarnan ki zuba mun a waccan ƙatuwar kular, ki ɗiba muku naku in zaku ci, sannan ki dumama mun miyar tumatur ɗincan ina zuwa"

Da sauri na fita falon na samu wasu mata su biyu kamar ƴa da uwane a yanayin dai kamanninsu. Da gani akwai gari a hannunsu.

Sannunku dai da zuwa, ina kwananku?"

Na faɗa ina zama a kujera. Babbar tace.

Edit with WPS Office

"Lafiya lau Sabuwa. Dama Naja ce tayo mana kwatance wajenki shine nace bari mu zo. Kinga wannan ƴata ce gata sunanta Hafsa wallahi Sabuwa kishiya ce ta hanata sukuni sam a gidanta mijinma wata biyu kenan baya shiga ɗakinta. Shine Naja tace mu zo wajenki dan aikin ki kamar yankan wuƙane akwai biyan buƙata"

Kallonsu nayi tsab da gani masu dashi ne. Murmushin mugunta nayi tare da cewa.

To a gaskiya sai dai ku dawo zuwa gobe dan yanzu haka unguwa zan fita sa'a ma kuka ci kuka same ni. Gobe da rana sai ku dawo. Ai ta sha kuruminta kunzo gindin maganin, da kishiyar da mijin duk saita danne wuyansu."

Na ƙarashe maganar ina jijjiga kaina.

murnace ta cikasu sosai , suka zaro nera dubu biyu suka bani, dan ko ban yi aiki ba ganina kawai ka faɗi matsalarka dubu biyun zaka ajjiye. Sun fita suna murna, nima nayi kitchen ina jin dubu biyun kamar miliyan

Nasan kuna da tambayoyi  da kuke son ku yi ko? Hahahahh

Hmm mu je dai zuwa wai mahaukaci ya hau kura. Zan bambance muku zare da abawa.

Kular abuncin na zura a leda irin kulannance mai hannu wannan doguwar mai abun miya a ciki, a ciki taliya biyun dana dafa aka zuba. A gurguje na shiga ciki na ɗauko jakata da wayata na fito na ba mardiyya nera ɗari kuɗin maganin Malama.

Ina fita tsakar gida Rauda da Yaya Sa'a suna shigowa, Babangida kuma fitowarshi kenan ya isa wajensu suna tsaye. Ga tiƙa_tiƙan raguna har biyu a ɗaure,ga kayan miya kwando kusan uku, ga mai, ga nama cikin babbar baƙar leda sai ɗigar jini yake yi, ga manyan tukwanen girki da babban murhu.

Yaya Sa'a data kalleni sai ta watsar. Ni ko banma san ta na yi ba dan na riga dana saba da wulaƙancin dangin miji. Miji ya darajaka ma ya kake iyawa dasu, balle ya nuna ma duniya rashin darajarka. Mun fi shekara guda bama ko ga miciji da Yaya Sa'a  Dama dama Rauda jifa_jifa mu kan gaisa. Dana fahimci  jijji da kan nasu na dangin miji yana ka sai nazo na wuce su daga su har Babangidan ban ko kallesu ba.

"Aikin banza in banda ƙaddara muna ƴaƴan malamai uwa da uba me zai kaimu haɗa haula da irin wannan baragurbin."

Cewar Yaya Sa'a kenan. Tutuyarsu kenan daga su har Babangidan su ƴaƴan malamai ne ciki da waje. Sai rashin mutunci fal ciki, da abubbuwan da in aka tona kare ba zai ci ba. Gara ma mu ta wani fannin. Ni dai nasa kaina kawai. Tib_tib_tib na jiyo gudun Babangida a bayana. Ban aune ba ya sha gabana.

"Meye wannan a ƙatuwar leda zaki fice mun dashi a gida? Sannan sabida rashin mutunci kina ganin Yaya Sa'a ko ki gaishesu ko da yake babu wannan tarbiyyar. Uhmai dallah bani in gani sai

Edit with WPS Office

ki kafe mutun da idandunanki na fitsara"

Yasa hannu ya fisge ledar hannuna. Idanuna na lumshe abubbuwane da yawa suke bijiromun da Babangida yayi maganar idandunana. Babangida Baban soyayya bawan soyayya ammafa ada banda yanzu da nake ganinshi tamkar dodo, ɗan kyanshi da gayenshi da yake ji dashi ko burgeni basa yi, ni bana ma gani sai wataran in Hamida ta fito tsakar gida tana kurantashi tare  da gwarzantashi  in zai fita.

"Dafaffen abinci dai kullum in zaki je gida sai kin dafa him kin kai musu tunda dai dama ba'a saba girki ba sai dai ko wacce ta suri ƙwanonta. Allah wadaran.."

Sai yayi shiru sakamakon wayarshi da take ruri. Ledar ya sakarmun, ya zaro wayar a aljihunshi yana murmusawa tare da jan gemunshi irin na mayaudaran maza masu siye mata da kalaman yaudara masu shegen daɗi da tsaiwa a rai.

Ledar nasa hannu na ɗauka na fita da sauri daga gidan. Ga sabon hadari sai haɗuwa yake yi. Wata iskar ƴanci na shaƙa ga gida iyaka gida da kyau da yalwa. Ga miji iya miji na nuna ma sa'a amman fa Babangida yafi kunama dafi, tamkar ɗanyar guba haka yake, marmarine shi daga nesa

Ba mummuna bane shi, farine ba irin sol ɗinnan ba,yana da hanci da ido sosai, ƙirar jikinshi daidai da misalin da hankali zai ɗauka, ƴan gidansu maza da mata suna da tsayi masha Allah.

Babangida ya ƙware wajen iya tattausan lafazi da tarairayar mace sosai, in dai yana soyayya da mace sai ta jita tamkar sarauniyar matan duniya. gashi ya iya ɗaukar wankan manyan kaya dan baya ta'amali da ƙananun kaya a iyakar sanin mutane dashi. Sai dai a bayan fage har tiri kwata da riga amules sawa yake yi.

A gidansu dai shine na uku a ɗakinsu, kuma shine na uku a kuɗi ma sana'ar Baban bola yake yi yana da kamfaninshi da suke niƙa robobin da suke siya, suna da motar ɗibar kaya zuwa Lagos,mutane sama da talatin ke aiki a ƙarƙashinshi.

Wannan gidan da muke ciki bamu fi wata biyu da dawowa ba sabon gidane dal, ko maƙota bamu gama sabo dasu ba. A ranar da muka tare a sabon gida Babangida ya yage amaryarshi Farida a kwali ma'ana tare da Amarya muka tare rana ɗaya. Ni ƴan uwana na tayani jera kaya da maƙotanmu na tshohon layinmu. Hamida ma haka danginta sunzo daga garinsu. Amarya ma danginta sunata mata jere muka zama mu uku a wajen Babangida. Allah kar ya nuna mana abinda bazai wuce ba, kar mu shiga da zurfi a cikin waiwaye zaku ji komai.

Ina isa titi na tari abun hawa zuwa unguwar kargo wacce anan unguwar gidanmu yake.

Ni dai tunda na zauna a ɗan sahu na dafe kaina na shiga aikin tunani har muka iso bakin unguwarmu.

Saukowa nayi na ciri kuɗi na biya mai ɗan sahu na suri ledata na ratsa cikin unguwar.

Edit with WPS Office

Unguwace ta talakawa irin geto ɗinnan ce mai ɗauke da cinyayyun gidaje gajiyayyu wahalallu. Kunsan dai a irin waɗannan unguwannin tarbiyya tayi ƙaranci sosai.

Ina tafe ina ganin irin barnar da ruwa yayi a unguwar har gidan Aminiyata wacce bani da tamkarta ruwa ya yaye musu kwanon gidansu baki ɗaya, gidansu yana kallon gidanmu. Namu gidan kuwa gabaki ɗaya ginin ya sauka komai ya rushe ga suturu facaca a cikin filin gidan da tukwane. To gida biyu ne tsakanin gidanmu da gidan da Labbai take aure a ƙofar gidan su Labbai ɗin na hango Gaza da Uzairu Zuchiyata da Adama a tsaye suna tattaunawa.

Sannunku Gaza yaushe rabon da in saka a idanuna?" Na faɗa ina ɗan murmushi.

"Cau cau cau babbar yarinya Sabuwa mai sabon aiki, kaga shegiyar gyaɗa da ƴaƴan kanya a lafiya dai"

Ya haɗe hannayenshi irinna ƴan daba da mafarauta.

Gaza wa nane ɗakinmu ɗaya na faɗa muku jiya riƙaƙƙen ɗan dabane fitinannen gaske na ƙin ƙarawa. Baya zama a gida mu kammu bamu isa mun san makwancinshi ba, babu me number wayarshi, akwai dai wani lungu da nanne fadarshi ɗauke da matasa masu shaye_shaye. Kusan kullum a guje_guje yake tsakaninshi da ƴan sanda baya rabo da laifi. In gangar siyasa kuwa ta kaɗa bama ko iya sa Gaza a idanunmu. Ƴan siyasa na amfani da irinsu Gaza sosai a tafiyar mulkinsu. Sai dai kash da sun gama kamfen anci zaɓe suka fita da fitarsu shikenan za'ayi watsin ruwan tsarki dasu sai wani zaɓen kuma.

Adama tace.

"Kin ganmu tun ɗazu muna magana da su Gaza akan wannan lamarin ne Lolo. Itafa  Layuza tun tuni tazo cikin gidannan su Karima take jira su dawo daga yawon iskancin da suka fita tun daren jiya ta kwashesu zuwa gidanta" Gaza ya dubeni da muryarshi irinta riƙakkun ƴan daba yace dani.

"Kin gane ne Lolo? Dole eh ki tafi da su Rakiya su samu su zauna a gidanki kafin eh Dattijo yasan ya zai. Tunda ai ya san manyan mutane ƙila su ɗan taimaka mishi. Danni wallahi yadda Dattijonnan ya sake ni a titi harna rayu na gane duniya da ƴanci wallahi bazan iya taimaka mishi ba ban eh rufe ku ba. Tun ina yaro ɗan shekara bakwai nake ciyar da kaina fa, sisina bazai gani ba . Taya ma ba zamu lalace ba wai?"

Kafin muyi magana sai ga wata dalleliyar farar mota ta tsaya a gefe daura damu. Aisha ce kame a gaban motar da wani Dattijo sai cingam take ci cakal_cakal irinna ballagazayen mata marasa kamun kai ɗinnan.

"Ah wannan ai Alhaji  Jabiru ne, ku jira ina zuwa"

Gaza ya tafi cikin tafiyarshi mai kama da tsalle zance ko yaya? Bansan yadda zan kwatanta muku ba dai irin ta ƴan iska to.

"Ah Alhaji Jabiru kai a lafiya dai. Kanwata an dawo kenan?" Aisha tace.

Edit with WPS Office

"Gaza wallahi na dawo ya rayuwa to? Bari in ƙarasa wajen su Lolo"

Nan ta baroshi ta nufo mu.

"Gaza me kake yi a layinnan a ina kasan Aisha kuma?"

Dariya yayi yace.

"Kaga wancan rushasshen gidan gidanmu ne a gaban idona aka haifi Aisha uwarmu ɗaya ubanmu ma haka ai. Ashe kaima kana ɗan leƙowa eh Alhaji?"

Dariya suka yi tare da tafawa.

"Baka da dama Gaza bari in baka na sigari dai yanzu"

Nera dubu biyar ya tafa mishi Gaza ya dawo wajenmu muka shiga cikin gidan.

Muna shiga cikin gidan muka tadda maigogul a zaune akan turmi yana gyaran fuska da ƙaton madubinshi, ga matan gidansu Labbai ko wacce tana aikinta na yau da kullum. Igiyoyin gidan shaƙe da shanyar tsadaddun shaddojin Maigogul da ruwa ya musu aiki.

Yana ganina ya yashe bakinshi har haƙoran makkanshi sama da ƙasa farare suka bayyana dan Maigogul kab cikin ƴaƴanshi yafi ji dani kuma tamu tafi zuwa ɗaya.

Layuza ce ta fito daga ɗakin Labbai ita da Uwarta Hauwa zasu tafi. a yatsine cike da wulaƙanci tace.

"Lolo har kin zo ashe?"

Wallahi kuwa nazo nima in tattare kan su Rakiya su koma gidana.

Cikin gatse nace.

Ga abinci Hauwa ba zaku ci kafin ku tafi ba?" Na tambaya ina kakkafesu da idona. Maigogul ne ya mike tsaye ya fisge ledar abincin.

"Ko lauma Hauwa bata isa taci ba a cikin abincinnan. Ba gidan Layuza zata je ba sa ci acan." Layuza tace.

"Sha kuruminka Maigogul bama ta so, akwai abinci na can yana jiranta. Hauwa muje kinji"

"Shinkafa da mai da yaji ba?"

Inji Maigogul

Tsaki Hauwa tayi ta bi bayan Layuza suka fice tana faɗin.

"Aikin banza aikin hofi abincin banza abincin hofi. Ai duk wanda ya san Lolo yasan ba jin daɗin auren take yi ba. Allah yasa suje su ɓallo mata auren muga ta ƙaryar ana auren mai kuɗi."

Edit with WPS Office

Gaza yayi carab yace.

"Hattara dai Hauwa. Ki iya bakin ki akan wannan furuci naki. Baƙin ciki yayi katutu a gidannan. Ai Lolo bata hana yaranki Auren mai kuɗi ba. Saki ai ba akanta aka soma ba in ma ya sakota zawarawa nawa ne a ɗakin ki ƴaƴan iska"

Tsaki Hauwa tayi suka fice. Dama nasan bata isa ta tanka ma Gaza ba.

Dariya kawai nayi na shige ɗakin Labbai. Maigogul na tarar yana ta zuzzuba taliya a robobi Rakiya tana zaune ta buga tagumi, Labbai na gefe a rakuɓe. Ɗakin duk ruwa. Caɓal_caɓal

Hannu Gaza ya sa zai ɗau roba ɗaya na taliya. Maigogul yayi sauri ya riƙe robar gam Gaza ma ya riƙe robar.

"Dattijo cika robar nan tunda dai ba da kudinka aka girka ba" Cikin hargagi Maigogul yace.

"Ai ba kai aka kawo ma ba. Yaushe rabon da mu saka ka ma a idanunmu. Ka cika robarnan ko in maka kafirin duka"

Rakiya tace.

"Mai zai zo yayi gida duk tarin yinwa da tsiya. Mu kanmu zaman ƙaddara dai muke yi zaman gaibu"

Kallonta Maigogul ya tsaya yana yi, Gaza ya samu ya fincike abincin yayi waje.

Ai kuwa Maigogul sai ya dira a wuyan Rakiya, mu dai fa muna tsaye ko wajen zama babu a ɗakin tsabar tsukuku ga ruwa. Idanuna na lumshe kawai da wacce damuwa ni kam zanji. A haka zamu tafi gidana su Rakiya na irin wannan sa'insar da suka saba da Maigogul, a haka zan tafi dasu Aisha suna fita suje su kwana a waje, ko kuma suje su yi dare a waje?"

Sallama da shigowar Rahama ne ya katse mun tunanina.

"Rahama kunga mu jenku daga waje ɗakin bazai ɗauke mu ba."

Dukkanmu muka fito waje Labbai ta shinfiɗa mana ƙatuwar tabarma muka zazzauna Uzairu zuchiyata dai tunda ya suri robar taliya shima ya sulale ya gudu. Maigogul yana cin abinci yana magana damu.

"Yanzu Lolo tunda gaki bari mu kammala cin abincin ai sai mu ɗunguma muje. Ke Labbai in su Momi sun dawo sai ki sanar musu muna gidan Lolo. Hauwa na wajen Layuza"

Da sauri na ɗago na dubi Maigogul, na dubi Rakiya, na sake waigowa na dubi su Adama da duk sai zuba nomar abinci suke yi a yinwace.

Maigogul har da kai zamu tafi dama?"

Na tambaya har zuchiyata na tsalle"

Edit with WPS Office

"Lolo a titi kike son in kwana ni koko ya kike son in yi da raina in ban biku ba? Tare dani za'a tafi kinga Allah ya rufa mana asiri sai ku yi karo_karo a ganganɗa a gyara gidan ba Shikenan bane. Ai mun auna arzikima tunda dai gidanki akwai waje wadatacce da zai ishemu, ai ayi komai a hankalima ba gaugawa. Itama Layuza ta tattare kan ƙannenta ba shikenan banene?"

Lallai Hauwa tayi gaskiya watan mutuwar aurena ya tsaya, Aurena ya mutu ya gama, dan a rashin mutunci irin na Babangida da rashin ganin girma da darajar su Maigogul da yake yi, ba abun mamaki bane ya fatattakomu daga ni har su ɗin ba  Haushe ma mahaifiyarshi zata yarda, mu da take kallonmu gabaki ɗaya a matsayin mummunar ƙaddara, ko kuma ince ala ƙakai, dama tace mu kaskane. Buɗar bakin Adama tace.

"Ni kam bani da wani kuɗin karo_karo Maigogul a ɗofane nake a gidana, abincin kirki bana samu. Sai dai ƴan matan gidan da zaurawan gidan tunda ƙasar a hannunsu take, mu kam muna ƙunshe wama zai baka. Rahama ko ba haka ba?"

Sai da Rahama ta haɗiye taliyar data cika a bakinta kana tace.

"Hmmm in ana sallah ba'a magana Adama. Kwanana bakwai cib bamu ɗaura abinci ba kinji nace wallahi, naga Gaza a waje yana cin taliya sai a mishi magana ya tattaro kan su   Ma'aru, da Sama suma. Ko Allah zai sa a samu kuɗi a hannunsu.

Ni dai ina zaune akaita tattaunawa, hankalina ma baya kansu na lula duniyar tunani. Kafin su kammala cin abincin sai ga Zuwaira, da Sadiya sun shigo ko wacce daban daban.

"Ke Sadiya ku kirawo samarin naku a waya su zo su kaimu gidan Lolo. Ke zuwaira Uwarki na gidan Layuza can zaki je"

Sadiya ta zaro wayarta a jakarta mai tsada ta rangaɗama saurayita waya, cikin abinda baifi minti goma sha biyar ba sai ga kira ya iso.

Harda Labbai duk muka haɗu muka tarkata muka fito ƙofar gida. Dake motar siyana ce duk ta ɗauke mu Sadiya tana maƙale a gaban mota. Muna tafe Maigogul yana hira da Saurayin Sadiya sune harda dariya. Sha'ani dai na rashin girma da daraja. Ni dai inata tubkewa ina warwarewa, su Adama kuma sai hirarsu suke yi da Rakiya hankali kwance har Allah ya iso damu unguwarmu. Muna shawo kwanar gidanmu sai muka ga motar ɗiban kaya a ƙofar gidan ƴan uwan Farida Amarya suna ta kwashe kaya Babangida ya saketa dama ko da Hamida ta haihu Farida bata gidan.

"Lolo wa Babangida ya saka kuma? Yaro sai kace mai bakin iyaye, daga aure sai saki. Anya kuwa ba aljanun auri saki bane suka aure shiba kuwa? Abun yayi yawa da anyi motsi sai saki, da anyi motsi sai aure Ko da yake kowa yaga dama_dama akace sai ya dama."

Ya karashe maganar yana taɓe bakinshi tare da ɗaga kafaɗa halamun ko a jikinshi.

Farida ya saka Amarya"

Edit with WPS Office

Iyakar abunda nace musu kenan a mugun sanyaye, saurayin Sadiya ya ajjiye mu muka shiga gidan ɗu.

Ga hadari baƙi ƙirin garin sai lumshi yake yi. Gari

Yayi irin duhunnan na hadari. Karfe goman safe ne amman yadda karin ya koma tamkar irin dab magriba ɗinnan.

Ga wata iska mai daɗi da take kaɗawa mai ɗan sanyi _sanyin ruwa a cikinta.

Ruwan daf yake da sakkowa.

WANNAN SHI AKE KIRA DANKARI SUNAN KARE A LAHIRA.

https://chat.whatsapp.com/IUKFTeuI76p2VaAvQ5nk0U

IDAN KAYA YA GAJI...

GAMMO MA YA GAJI

BADI'AT IBRAHIM MRS BUKHARI B4B GIDAN KAMSHI

BABIN FARKO

SHAFI NA UKU

*NA SADAUKAR DA WANNAN SHAFIN ZUWA GA MATAN CIKIN TASKAR BADIAT*

*RANKU SHI DAƊE MATAN GABAN GOSHI DA GIRMAN KUJERUNKU, DA GIRMAN SIFIKUNKU ( KU KAƊAI ZAKU GANE WANNAN YAREN) NA KARYA MUKU ƊANKWALI*🫡

Edit with WPS Office

Ina mika saƙon gaisuwa da dukkan masoyana masu bibiyar rubutuna.

Allah ya nufeni da sake fitowa a wata sabuwar tafiya mai ɗauke da sabon salon da nasan zai ilmantar, zai faɗakar.

Haƙiƙa fitowata ta tabbatarmun da yadda ku kai kewar rubutuna.

Nagode ƙwarai da wannan soyayyar ta fisabilillahi da kuke yi mun.

Masu cewa na tuƙe duk wata basirata a cikin littafin Iyabo mai suna NAMA YA DAHU ROMO ƊANYE gareku nasan saƙona zai isa gareku.

Ku bibiyi wannan littafin zaku gane cewar ita baiwa daga rabbil izzati take. Mutum kuma bai isa ya nema ma kanshi ɗaukaka ba madamar ba Allah bane yaso ya ɗaukakashi ba. Nasan in kuka bibiyeni zaku kane Allah ɗaya ne, kuma zaku gane baiwa baiwace Nagode da soyayyarku ga labarin Iyabo.

*Bincike ya nuna sama da mutune miliyon goma sha biyar ke shan muyagun ƙwayoyi a najeriya.

Hakan kuma ya jawo asarar rayuka, taɓarɓarewar tarbiyya. Ya habɓaka fitinu da manyan lefuka a arewacin najeriya dama ƙasar baki ɗaya.

Tun kafin zama ya gagaremu mu koma bacci da ido ɗaya a buɗe. Lokaci yayi da zamu haɗa ƙarfi da ƙarfe domin mu taimaka ma hukumar yaƙi da sha da fataucin miyagun ƙwayoyi.

Dan ganin mun kawar da wannan ta'asa dake shirin zame mana ruwan dare.

Shaye_shaye annobace ga al'umma.

Wannan saƙone daga hukumar yaƙi da sha da fataucin miyagun ƙwayoyi wato ( NDLIA)

Edit with WPS Office

Har ƴan uwansu Babangida na Ringim sun zo tsakar gidannan cike, ga maƙota suma anata aikin suna. Wasu na soyar kaji, yayin da wasu suke yanka kayan lambu su karas da kabeji, wasu na wanke shinkafa, wasu na zuba zoɓo da lafiyayyen kunun gyaɗa a leda dai. Aiki suke yi ka'in da na in ga kiɗa na tasowa daga ɗakin Hamida mata nata mamin ɗin waƙar sunusi Anu mai taken cakwala daɗi.

Ga kuma dangin Farida sunata fito da kayan ɗaki ashe harda ma Faridan aka zo ɗibar kayan. Ni dai illahirin kunna duk ta kamani. Tsorona Allah tsorona kada Maigogul da Rakiya su tsinkani a gaban dangin miji, da dangin kishiya.

Mardiyya ce ta hangomu ta tawo a mugun guje zuwa wajen Maigogul, ni kuma wajen ajiye motar Babangida na kalla motar bata wajen da dukkan alamu baya cikin gidan. Ajjiyar zuchiya na sauke.

Haka wallahi muka ratso tsakar gidannan muka zo muka ratsasu, Su Rahama ne sukai musu sannunsu da aiki, ni kuwa sanin ko na gaishesu ba zasu amsaba ne yasa ban ma soma ba ga kunya haɗe da fargaba fal ruhina.  Rakiya kuma ta tsaya gaisawa dasu, Sa'a sai wani fuskewa take yi ita kuwa Rakiya ko a jikinta sai washe bakinta take yi. Ina jiyo wata murya tana faɗin.

"Wannan gona_gonan ƙaton fa da aka wuce dashi ciki bako gaisuwa fa, Sa'a shi kuma waye? Sannan duk wannan bataliyar daga ina" Ina tsaye a lokacin muna gaisawa da Alawiyya ƴar ɗakin su Mashi ƙannen Babangida na ɗayan ɗakin da sune kaɗai muke mutunci. Sai naji Sa'a tace.

"Baban Sabuwane shima sunan yazo abun mamaki anzo cin abinci. Sauran kuma duk cikinsu ɗaya Ƴaƴane dashi far sai rashin tarbiyya fal cikinsu. In banda abun kunya ina uban Ƴa da zuwa sunan kishiyar Ƴarshi?"

Mardiyya taja su Rakiya zuwa wajena ni da Adama da Ramatu kuma nace musu su zo su rakani wajen maijegon su gaisa.

"A_a Lolo ki bari ki ɗau wanka mana zuwa anjima ba sai mu shiga ba tasan kinfi ƙarfinta. Mu dai mu tsaya mu taya su aiki tunda naga aikin yayi musu yawa"

Cewar Adama da taci ɗamara da hijabinta ta ƙarasa wajensu Alawuyya tasa hannu a yankan kabeji.

Mu kuma muka shiga aikin taya masu wankin shinkafa. Masu ɗibar kaya kuma suka gama ɗibar kayansu suka fice a gidan tare da bango get suna zage_zage. Lamarin daya tunzura dangin Babangida suka fita suka bisu waje nan rikici ya ɓalle da zagi in zaga. A guje Maigogul ya fice waje wai yaje raba faɗa da ƙyar Labbai ta jawo hannunshi suka koma ciki. Kunji ko ya soma ya

Edit with WPS Office

da girman.

Muna aikinnan ina tuno lokacin haihuwar Aminu irin tozartani da Babangida yayi ko haƙiƙa bai ma Aminu ba sai daga baya Sadiya ta yi mishi da kuɗinta. Malama ma albarkacin mai sunanta taci shi yasa ta fita zakka ita kaɗaice Babangida yaima haƙiƙa a cikin yarana, Mardiyya Baba Malam ne yayi mata. Kuma ita kaɗaice ta saka suturar da Babangida ya siya mata kab yaran haka na haifesu tsiya_tsiya babu suturar arziki. Bayan mun gama zuba shinkafar a tukwane uku, biyu jallof ce ɗayar tukunyar soyayyar shinkafa ce taji hanta da kayan lambu, aka gama kosulo nan muka wanke hannayenmu muka wuce ciki Sa'a ta bi mu da hararar tsana. Harda faɗin.

"Allah wadaran naka dai ya lalace. Babangida ya jajiɓo mana jaraba muna Yaƴan malamai gaba da baya. Amman jibi irin surukan daya ɗebo mana"

Adama tace.

"Kuma dole aka karɓi ƙaddara ba. Sa'a ke dai kinji kunya wallahi bakya ƙaunar a zauna lafiya na rasa uban abinda Lolo ta tare miki a duniyarnan ta maliki yaumuldini."

Hannun Adama na ja muka shige dan nasan daga haka yaƙi tsab zai iya tashi. Ni kuma wallahi na gaji da masifa da bala'i.

Su Rakiya suna falo sun yi baje_baje Maigogul yasa mardiyya ta ƙure musu fankar sama. Su Sadiya sun yi wata iriyar kwanciyar rashin kamun kai, Sadiya na waya tana ta dariya,  Aisha kuma ba mai yawan  magana bace ita dai ku barta da daddanna waya. Labbai tana zaune a kan kafet tana canja tashar setilat. Su Adama da muka shigo tare duk suka nemi waje suka zauna sai sake santin gidanmu suke yi, irin kyau da haɗuwarshi. Ni ko a wajena bashi da maraba da kurkuku dan matsi da uƙuba.

"Lolo kuna ta aikin suna ko? Kin ganmu muna ta shan fanka ƴaƴa mata masu daɗi. Yanzu da ba dan ke ba bansan ma ina zamu dosa ba. Su waɗancan maza mazan in banda shaye_shaye babu abinda suka saka a gaba, da neme_neman matan banza irinsu Uzairu zuchiyata kenan. Kina gani wannan abun daya afku ko a kwalar rigarsu yaushe ma rabon da mu saka su a idanunmu ga Rakiya nan, Rakiya ko suna leƙowa in bana nan?"

Rakiya tace.

"Oo_oo basa zuwa, rannan dai ƴan sanda sun rako Ma'aru a guje ya tsallake katanga ya fice. Da kake batun shaye,_shaye ai dole su sha nima da zan samu sha zanyi ko zan rage nauyin zuchiya kaine ai silar komai . Neme _ nemen mata da kake danganta Uzairu Zuchiyata dashi ai faɗe kake yi tunda dai kamar kumbo kamar gatanta" Maigogul ya taɓe bakinshi yace.

"To kinga ni bani ma da labari. Uwarshi Hauwa kuma ba faɗa mun zata yi ba. Babu mamaki ma yana hannun hukumane tunda kwana biyu shiru. Sannan Lolo ki jama Rakiya kunne a gidan surukai muke ta fita idandunana in rufe tana yawan zagin sana'ata. Kuma wannan sana'ar da ita jama'a suke ganin darajata, sana'ar da take ta ɗaga darajata."

Edit with WPS Office

Ni dai waje na samu na zauna kawai. Na ba Rakiya haƙuri dan ta shaƙa sosai so take ta fesar.

Na dubi Mardiyya nace.

Mardiyya ki ja su Aminu kuje ku shirya ku fita cikin dangin ubanku maza. Rakiya ni zanje in yi wanka. Kafin maƙota su soma shigowa"

Wuce wa nayi ɗakina su Sadiya da su Adama duk suka biyo ni ɗu zuwa ciki zazzaɓi sai sake sakkomun yake yi. Mardiyya kuma ta ja su Aminu, muka bar Rakiya da Maigogul a falo suna kallo. Sabida tsabar damuwa ni ko tambayar jikin Malama ban ba.

Banɗaki na faɗa, su kuma duk suka zube a gado suka buɗe babin hirarsu hankali kwance anata musu da ɗaga murya. A banɗaki naci kukana na ƙoshi dama dai kuka a banɗaki ya zamemun tamkar Sallah biyar a rana, rana bata fitowa ta faɗi ban yi kuka ba duk kwanan duniya. Ni kam na shiga uku me zance da Babangida wai in yazo yaga su Rakiya?'"

Fitowa nayi cikin rashin kuzari  na tadda Rakiya tana zaune itama a bakin gado tana magana dasu Adama.

Rakiya ina kika baro Maigogul?" Na tambayeta ina kallonta.

"Yanzu ya fita an kirashi a waya, yace dai sai zuwa dare zai dawo in dai ubanku ne ƙila ma sai gobe zaki sake ganinshi. Shegun yan matan dai da yake harka dasu ɗinnan ai ba barinshi zasu yi ya huta ba. Da kai magana ya hau zaginka yace sana'arshi ce kowa da hanyar cin abincinshi. Yanzu shekaranjiya waccan fa wasu tsofaffin zaurawa daya kwaso mana su sai da suka kwana biyar anan ɗaki tare damu a cunkushen haka, sai da suka gama abinda ya kawosu suka sallameshi da kuɗin aikinshi suka tafi ko  sisi bai iya kashewa a gidan ba sai ma kuɗin ɗinkinshi daya biya. Yanzun ma fa wallahi kamar wasu baƙin matan yayi ƙila ki gansu tare dasu ma balle yaga yalwar waje. To ya zaka yi kuskure dai an riga da an yishi tun daga tushe, kuma dai aka ce bawa baya wuce ƙaddararshi ko?."

Ban sake cewa uffan ba ni dai, nasan ma yau zamu tarkata dukka mu bar gidan kowa ya huta. Sib na buɗe na zaro atampata super mai ruwan ganye sabuwace fil dan ban taɓa sakawa ba, yana daga cikin kayan da akayi  mun lokacin sunan Malama Aisha ce ta ƙarbo mun a shagon saurayinta. Tunda aka ɗinko ban taɓa sakawa ba ban nutsu ba balle in saka. Ranar sunan Malama kuma abubbuwan da suka faru ba su bani damar yin kwalliya ba dan ko wanka abun mamaki ban ba.

Kayan na saka na saka fashion sarƙata itama mai ruwan ganye abunka da farar mace sai kalar ta haskani. Duk wannan abun da nake yi zuchiyata ɗaci take yi, kuma ina tsoro da fargabar kar Maigogul ya kawo mun matan da yake aiki dasu gida, kar ya ƙara tozartani bisa tozarcin da tun asali shi  ya zame mana tsani. Banso yin wata kwalliya ba amman Aisha sai da ta matsa mun ta rangaɗamun kwalliya mai kyau ta zamani, Sadiya ta fasheni da turarenta data ciro a jaka. Ina gaban sib ina ciro atampar novo da nake son in ƙara da sabulu in kaima Hamida. Rakiya tace.

Edit with WPS Office

"Ni fa Lolo yinwa nake ji sosai kinga fa azahar ta kunno kai amman ba'a kawo abincin sunan ba har yanzu"

Labbai tace.

"Shiru nayi kar in yi magana ace na fiye ci shi yasa. Tun ɗazu fa cikina ke ƙugi"

Sai da su kai maganar abinci na tuna ni rabona da abinci tun jiya da rana, dan da daddare baƙin cikin da Babangida ya ƙunsamun kafin ya tafi yawon barbaɗarshi bai bani damar sanya komai a cikina ba. Ɗazu a gidan Labbai taliyar wasa na dinga yi da'ita a hannuna har dai suka cinye.

To bari muje Mardiyya zata kawo. Labbai kuzo muje shashen mai jegon ku yi mata barka. Naji ma kamar ƴan uwanta sun ƙaraso"

Dani da su Labbai muka fito, su Aisha ma mun barosu suna shirin yin wanka wai fita zasu yi. Duk kayayyakina suka ciro shi zasu saka.

Tsakar gidan maƙil da jama'a a gaskiya dangin Babangida sun yi ma Hamida kara sosai ita dai suna sonta gaskiya. Ga danginta suma sun iso sai kaca_kaca akeyi, anata cin abinci a tsakar gida, har falon maijegon duk abinci ake ta ci. Hadarin daya haɗu yanata washewa sai dai garin da sanyi kasancewar babu rana.

Gaggaisawa mu ka yi da ƴan uwanta.

Hamidan tana ciki ne?"

Na tambayi Yayarta Hajara tsohuwar mara mutunci ake faɗa muku.

"Tana ciki ki shiga tana ɗakinta da ƙawayenta"

To. Adama mu janku ko?"

Muka ratsa mutane dake ta faman cin abinci muka shiga uwarɗakin mai jego, wannan shine shigata Uwarɗakinta na uku. Amman a sabon gida wannan shine shigata uwarɗakinta na farko. Gadonta da labulayenta fararene sol, sai ƙaramin kafet mai ruwan jinin kare, takalma da jakunkunanta suna ajjiye a ma'ajiyarsu jingim dan Babangida ba ƙaramin lefe yayi mata ba gaskiya. Maijego na naɗe a gado ta ci adon swiss lace ɗinta ɗinkin doguwar riga wuyan rigarnan yasha surfani, kai ya ɗau kitso, hannu da ƙafa kuwa ya ɗau ƙunshi tayi kyau babu ƙarya itama tana da kyawunta daidai misali baƙace irin bakinnan mai kyau wanda ko fari bazai nuna mata komai ba.

Maijego sannu ya taro. Ina wuninku bayin Allah?" Na faɗi tare da ɗakko ma Adama jaririyar. A yatsine ta amsa mun halinta ne dan sai mu fi wata cir bama ko ga miciji ma, ko tsakar gida bata fitowa ko a gidanmu na da balle kuma da muka dawo wannan mai tsarin komanka a ciki.

"Maijego irin albarka yaya taron?"

Edit with WPS Office

Cewar Adama, kunsan me? Yi tayi kamar bata ji ba ma wallahi sai ta shiga magana da Rahina aminiyarta. Labbai ce tace.

"Mejego ana gaisuwa baki ji bane ko yaya?" Sai ta juyo wai.

"Ai kaina ya ɗau zafi ina wuninku?"

Suka amsa mata ni dai ina tsaye. Ledar hannuna na miƙa mata aminiyarta Rahina ce tace.

"Angode maman Mardiyya"

Ai babu komai. Mu janku Adama"

Adama ta ajjiye musu jaririyarsu muka fice karab a kunnena najiyo tsakin Hamida. A raina nace.

Allah ya kiyaye kishi akan wanda baya kishin kanshi kenan. Iska na wahal da mai kayan kara in dai Babangida ne yarinya. In kin yi kishi dani ki yi yaya da karuwanshi  wanda dani dake bamu san adadinsu ba kuma dasu ake raba mana abunda kike kishi akai?"

Haka muka sake ratsewa muka koma ɓarayina, ni ko ƙyallin su Aɗɗa'u ban gani ba. Har zamu sha kwanar ɓarayina sai muka hango Gaza da Amina  ƙawata suna tawowa harda ƙaramin kare a hannun Gaza. Jikinnan nashi duƙun_duƙun gashi a cake yana tafe kamar faɗa dan masifa. Amman dake shi ɗan uwa duk lalacewarshi kana son abunka cikin fara'a na tarbesu. Cike da cije baki Gaza ya kalle ni ya kalli gidan yace.

"Bura uba Lolo gaskiya Babangida ya ƙera gida. Lolo kece a cikin wannan daular, kam bu. Yarinya Allah ya kashe ya baki Sabuwa mai sabon aiki sai babbar yarinya sai dake ƙanwata.

Ɗan uwa abun wuya. Duk damuwar da nake ciki da cunkushewar zuchiyata sai da Gaza ya sani dariya. Adama tace.

"Amina ina ke kuwa kika tsinto Gaza har ya rakoki?" Da dariya Amina tace.

"Wallahi a  cikin  adaidaita sahu muka haɗu, to shine ma yake labarta mun gida daya rushe abun bai yi daɗi ba. Wallahi muma gidanmu bango ɗaya na ɗakina ya rufta. Ai jiyan da daddaren ma na kira Lolo inaga tayi bacci, a lokacin abun ya faru".

Ai wannan ruwan yayi ɓarna ƙawata kuma naga kiranki abubbuwanne sai a hankali gashi mun wayi gari da hidimar suna. Ku muje daga ciki, Gaza karyarka ce ta haihu kake yawo da kuikuyo?" Gaza yayi taga_taga yayi baya ya dubeni yace.

"Ke wannan ne kare jinjirin zaki ne fa"

Dariya muka tuntsure dashi muka shiga dukkanmu dai. A cake yake ƙila idanunshi jinjirin zakin yake gani.

Ni kitchen ma na ja Labbai da Amina  muka shiga muka tsaida sanwar jallof dan ba lallai a bamu

Edit with WPS Office

abincin da zai ishemu  ba gaskiya in ma fa an bamu ɗin kenan.

"Lolo kun yi waya da ƴar shuwa kuwa gidansu itama fa ya kwanon ya yaye duk da nasan dole kin sani?"

Murmushi na ƙaƙaro a ƙoƙarina na birne damuwata a idanun Amina nace da'ita.

Kinsan Allah ba mui waya ba Amina. Da naje gida naga gidan nasu a yaye  kuma muna shigowa na faɗa aikin abincin suna. Bari in kirata na san ma sai ta zazzageni"

Amina dai tana ta mun dariya na ɗaga wayata na kira ƴar shuwa ai kuwa ringing biyu ta ɗauki wayar.

"Ƴar iska sai yanzu kika ga damar kirana, ko dai suna ne yasa kan ki ya ɗau zafine da har aka kasa mun jaje?"

Da dariyata nace.

Wane ni ƙawata abubbuwane kawai sukai mun yawa. Ga batun rushewar gida, naje na ɗakko su Rakiya suna nan tare dani ma, ga Amina ma tazo sunan ƙawarki Hamida" Dariya tayi tace.

"Allah ya isa ƙawarki dai ku da kuke raba miji. To ya sunan munci burin zuwa ai Allah bai yi ba. Yanzu haka muna hanyar Maiduguri ni da su Mama. Ke dai in muka sauka zan kiraki akwai labari mai zafi kifin ya shiga cikin koma kuma kifin babbane ga maiko labari ya faɗa dai a taƙaice. Ki gaishe mun da Amina da su Rakiya, ki isarmun da jajena wajensu"

Da haka mu kai sallama na ajjiye wayar ina dariya ina fatan Allah ya ɓullo ma da Yar shuwa wani mijin ta yi aurenta ta huta zawarci babu daɗi.

Duk da dai naji tace ta samu wani.

Har abincin dai dana ɗaura ya kusan nuna kafin Hamida tasa aka aiko da abincin suna sai kun ganshi, babu nama, zoɓon ma bamu samu ba sai kunun gyaɗa shima fa leda shida aka saka mana. To dake abincin da yawa muka girka sai bamma damu ba aka zuzzuba kowa yaci hatta maƙotanmu waɗanda suka shigo domin ni jallof ɗin da muka girka muka zuba musu.

Gaza dai yana gama cin abinci yace.

"Rakiya ni kam zanje ana kirana a area ya kamata inje. Lolo zan wuce ɗan bam na abun hawa mana dana hayaƙi"

Nera ɗari biyu na miƙa mishi yayi mana sallama ya fice.

Haka dai wunin sunan ya kasance da yamma lis Amina da maƙotanmu, da su Adama  duk suka tafi gidan ya rage daga ni sai Rakiya, sai su Mardiyya su Sadiya tuni suka fice gantalin da suka saba Maigogul dama shi tunda ya fita bai dawo ba.

Edit with WPS Office

Ko motsi naji sai gabana ya yanke ya faɗi sai in zaci Babangida zai shigo, ni wallahi bansan ta yadda zantare shi da batunan ba.

"Lolo yarinyarnan jikinta fa da zafi sosai fa kinji. Malama jeki uwarki ta taɓa jikinki taji" Ko data taso ma kafin ta iso wajena ta faɗi ƙasa sunammiya. Da mugun sauri mu ka yi kanta ni da Rakiya Mardiyya ta ɗebo ruwa da gudu aka yayyafa mata ta farfaɗo sai dai ko idanu bata iya ƙibtawa.

Rakiya na shiga ukuna."

"A_a maza ɗauko mayafinki mu kaita asibiti maza"

Da gudu na shiga ɗaki na ɗakko mayafi da zanin goyo na ɗamare Malama a bayana.

Mardiyya ku kula da gidan, in Babanku ya dawo ki faɗa mishi munje asibiti zan ma kirashi. In Maigogul ko su Sadiya sun dawo ki sanar musu.

A gurguje muka fice dan sai sanƙarewa Malama take yi. Ko da isanmu babban asibiti kai tsaye aka bamu gado a ward ɗin yara. Ina zaune a kan gadon tare da Malama Rakiya na tsaye a gefe sai ga likita ya shigo. Kallon kallone ya shiga tsakanina dashi, gabana ya yanke ya faɗi. Take wasu kifiyoyin suka soma sossokemun Zuchiyata, saurin sauke kaina nayi ƙasa babu shi. Shi kuma yayi murmushinnan nashi na asali kawai tare da girgiza kai ya shiga duba Malama dake kwance a jikina.

"Lolo kin kira Babangida kin faɗa mishi halin da yarinyarnan take ciki kuwa?"

A_a  Rakiya ban kirashi ba tukunna zan kirashi"

Na bata amsa ina dafe da kaina.

Ina ɗagowa idanunmu suka sake gaurayewa. Murmushi ya sake sakar mun tare da kashe mun idanunshi ɗaya. Saurin kawar da kai na kuma yi gabana na sake tsananta bugu, tunani na neman mayar dani baya. Jinin Malama ya ja ya fita daga ɗakin ba tare da ya kalleni ba.

Ajjiyar zuchiya na sauke kawai. Na ciro wayata a jakata ina laluben number Babangida.

BABANGIDA:.

Mu tara gobe in Allah ya kaimu da rai da lafiya

https://chat.whatsapp.com/IUKFTeuI76p2VaAvQ5nk0U

Edit with WPS Office

https://chat.whatsapp.com/IUKFTeuI76p2VaAvQ5nk0U

IDAN KAYA YA GAJI...

GAMMO MA YA GAJI

BADI'AT IBRAHIM MRS BUKHARI B4B GIDAN KAMSHI

LITTAFI NA FARKO

SHAFI NA HUƊU

*WANNAN SHAFIN NA MUTUM BIYU NE SAI YADDA SUKA YI DASHI*

HAJARA ALIYU ( MAMANMU)

KHADIJA MAIDOKI ( MASOYIYA)

Bincike ya nuna sama da mutune   miliyon goma sha biyar ke shan muyagun ƙwayoyi a najeriya.

Hakan kuma ya jawo asarar rayuka, taɓarɓarewar tarbiyya. Ya habbaka fitinu da manyan lefuka a arewacin najeriya dama ƙasar baki ɗaya.

Tun kafin zama ya gagaremu mu koma bacci da ido ɗaya a buɗe. Lokaci yayi da zamu haɗa ƙarfi da ƙarfe domin mu taimaka ma hukumar yaki da sha da fataucin miyagun ƙwayoyi.

Edit with WPS Office

Dan ganin mun kawar da wannan ta'asa dake shirin zame mana ruwan dare.

Shaye_shaye annobace ga al'umma.

Wannan saƙone daga hukumar yaki da sha da fataucin miyagun ƙwayoyi wato ( NDLEA)

BABANGIDA:.

Tun safe daya fice a gidan kamfani ya nufa ya ɗan taɓa aiyuka tare da sanya idanu akan lamarin aikin dai haka. Ya kuma gana da wasu baki da suke son za'a kai musu kayan baban bola zuwa jihar Lagos.

Da misalin ƙarfe biyu Hamida ta aiko ƙannenta da abincin suna zuwa kamfani, domin shi akaima wannan soyayyar shinkafar. Ma'aikata aka ci aka sha tare da yima oga adda'ar Allah ya raya abinda aka samu.

Zuwa bayan la'asar kamar yadda ya zame ma Babangida al'adar tashin shi daga aiki, yau ɗinma ana sallah ya fice kai tsaye zuwa unguwar Zai gidan iyayenshi, a nan bakin titin shiga unguwar majalisar zaman gulma da yi da mata da maza ta su Babangida take, wanda  duk sanda ya baro wajen aiki kai tsaye nan yake zuwa, kuma basu suke barin wajen ba sai wajajen goman dare zuwa sha ɗaya.

Majalisace ta magidanta mafi yawansu ma'aikatan gwamnatine, sai ƴan kasuwa ƴan tsirari. A wannan majalisar daga mai mata biyu sai mai mata uku, huɗu amman babu mai mata ɗaya, wannan dalilin yasa kullum wannan majalisar a cikin tattauna matsalolin matansu suke, harma da matsalolin matan unguwa da maƙotansu dama matan da suke zuwa gibtawa. Matan unguwar Zai suna kuka sosai da irin mugun sa idon da ƴan wannan majalisa suke yi musu. Ƴan mata kuma masu neman mazajen Aure idanu rufe basu da aiki sai zuwa gibtawa ko zasu dace. Wasu daga ciki sun dace an auresu, yayin da wasu kuma aka mayar dasu karuwan gida. ( Hattara iyaye mu riƙa lura da sanya idanu sosai akan ƴaƴanmu musamman mata) A wannan majalisar suke samun guragun shawarwari daga ƙwaƙwale mabambanta.

Isowar Babangida wannan majalisa yasa suka soma mishi dariya ana gwarzantashi, shima da dariyar ya ƙaraso kan kafet ɗin da suke zazzaune anata shan shayi ga mai shadda ya kawo musu shadda da yaduna na siyarwa.

"Wai menene ya faru ne kuke ta dariya tun tsaiwar motata?" Babangida ya tambayi abokanshi.

Jamo yace.

"Babu komai ai kasan in kazo ko babu komai zaka jijjiga majalisar da hira, dama kai da Sani, da

Edit with WPS Office

Mustapha ne gwanayen samo labari to shi  Sani ya tafi semina Abuja. Mustapha kuma kasan kaine ƙwarin guiwar hirarshi"

Kofin shayi ya ɗauka ya tsiyiyo gahawa daga butar shayin dake ɗaure akan gaushi a gabansu. Sai da ya ɗan kurɓa ziwit_ ziwit kafin yace.

"Hmmm akwai babban labari. Ai bayan na fito a gida ban jima ba sai ga wayar Hamida take sanarmun dangin Farida sun zo ɗibar kaya. Kar kuji yadda raina yayi mun fari fat. Sai dai fa sun takali su Yaya Sa'a da rigima sosai Hamida tace mun har ƙofar gidan sai da ta cika da magulmatan unguwa fa kasan mu hausawa muna da matsalar gulma sosai. To ɗazu  da yammannan Farida ta turo mun da sakamon tes da tayi tana ɗauke da juna biyu wata biyu. Abun bai mum daɗi ba sam har dalilin hakan yasa naji da ba dan inna gama da mace na gama da'itaba kenan na rufe shafinta, to da Farida na mayar da'ita ɗakinta gaskiya"

Amiru ya tuntsire da dariya yace.

"Haba dai yau kai da kan ka kake maganar kome Babangida Kacigari? ( Babangida Kacigari gari shine sunan da abokanshi ke kiranshi dashi) Ai ka rabu dasu kawai ta haihun ta gama shayar da abinda ta haifa yaro a karboshi a jefa shi cikin ƴan uwanshi kawai. Ka rufe babin wata Farida kar ka ba damu mana, kaifa kake ɗoramu a hanyar in an shanye mangwaro yada ƙwallon akeyi a huta. Balle Farida data aikata maka laifi mai girma."

Nan kowa ya shiga tofa albarkacin bakinshi, da suka rufe wannan maganar sai suka shiga hirar matansu na gida. Wacce tayi ba daidai ba ayi ca a kanta, wacce ta burge miji kuma a yaba mata, a_a wance tafi wance iya samfuri_samfuri na kwanciyar Aure dai haka wannan majalisar take a kullum. Daf magriba aka aiko da farfesun kaza daga gidan Babangida Kacigari na suna da yasa akayi musamman domin ya fita kunyar abokanshi. Tunda haka akeyi ga duk wanda matarshi ta haihu za'a aiko abincin suna cikin kuloli na alfarma na ƴan ƙarya.

Amiru kuma a gidanshi aka fito da lafiyayyen tuwon shinkafa miyar kabewa taji ɗanyen kifi, da zoɓo mai kyau.  Sai da su ka sallaci magriba a masallacin ƙofar gidansu Babangida Kacigari, ko ince haɗe yake da gidansu, wanda yake hannun mahaifinshi, da makarantar da ake koyarwa da safe ta matan Aure, da daddare zuwa bayan isha ta magidanta. Duk haɗe suke da gidan nasu Babangida kacigari.

Bayan sun idar da Sallah Babangida ya ƙarasa wajen mahaifinshi dake shirin fita a masallacin.

"Baba Malam barka da dare"

Babangida ya faɗa a ɗarare dan shi a wajen mahaifinsu kullum mai laifine a wajen Malama Babba ne kawai yake ƴantacce. Mahaifinsu  Baba Malam mutumne mai tsantsanin duniya sosai, Dattijone managarci, mai nagartattun halaye. Malamine na addini maza na zuwa ɗaukar karatu a gabanshi, kuma yana da makarantarshi babba wacce take jikin masallacinshi sunan makarantar KHAIFA NAHYA ARABIC SENTA bugu da ƙari yana koyar da almajirai karatun tsangaya, almajiran da suke makarantarshi zasu kai guda ɗari in ƙirgawa za'ayi. Abun sha'awa

Edit with WPS Office

da burgewa a da wasu daga cikin ɗalibanshine ke malinta a wannan makarantar. Da Allah ya ba Baba Malam ƴaƴa sai ya ɗaurasu a harkar karatun addini domin su gajeshi kuma ko bayan babu shi su riƙe wannan makaranta mai ɗumbun tarihi da kyau. Iyakar mazan gidanne kaɗai su kai karatun boko iyaka sakandare, amman su Yaya Sa'a basu taɓa zama a ajin boko ba. Allah ya cika ma Baba Malam  burinshi tun da ranshi kab yaranshi suke koyarwa a wannan makaranta maza da mata kuma duk muƙaminka dokar gidance dole ka karantar. Mazan kasancewar da rana suna wajen ƙwadago sai suka zaɓi makarantar dare ta magidanta. Matan kuma aka barsu da mata ƴan uwansu suke koyar dasu da safe. Baba Malam bai bar yaranshi a haka ba duk wata yana biyan ko wanne yaro albashi duk kudinka kuma dole ka karɓa.

Matanshi biyu Malama Saratu wacce ake kira Malama Babba itace uwargidan Baba Malam da su kai Aure tun ladan loma Allah ya azurtata da yara goma cib biyar maza biyar mata. Akwai Sa'a Akwai Kudidi, Maryam, Murjanatu, sai Hafsatu, a mata kenan a maza kuma akwai Babangida, akwai Mustapha wanda ake kira da Wawo shine babba oba rol a maza akwai Umar akwai Usman.

Sai matarshi ta biyu Malama Nasara wacce ake kira da Malama Karama Allah ya azurtata da yara takwas biyar mata uku maza.

Aisha'Alawiyya, Hadiza, Amina, Rauda. Mazan kuma akwai Jibrilu, Akwai Mashi sai Idirisa wanda ya kasance shine autan duka gidan.

Ta ɓangaren iyaye mata babu haɗin  kai, ko wacce ta janye yaranta a jiki, ba dai kaji sirrin wannan ɗakin acan ɗakin ba, kowa ya adana sirrinshi. Amman babu faɗa ko gaba, ko kuma wata bayyanarnar fitina a tsakankanin iyayen Mata da ƴaƴan gidan. Ko wanne na girmama matar Babanshi dan Baba Malam  mutunme tsayayye sosai a kan ahalinshi, kuma sun kurɓi tarbiyya daidai misali, sai dai da yawa ana ƙorafi akan wasu daga cikin gidan suna wasu ɗabi'u da bai dace ace ƴaƴan malamai gaba da baya na yi ba. Musamman Babangida da sunanshi yayi ƙaurin gaske, irin ƙaurin da yasa ya fita zakka acikin  ahalin dan shine yaro na farko daya kunyata Baba Malam  a idanun duniya shine abunda ya tsayama wannan dattijo a rai ƙyam.

Wannan kenan

Baba Malam  ya dubi Babangida da kyau yace.

"Dama ina nemanka saura ka gudu daga makaranta kamar yadda kayi jiya, na shiga ina faɗa uwarka ta kareka."

Babangida ya sosa kai yana tsoron Allah yana tsoron abinda zaisa mahaifinshi yace yana son Magana dashi.

"Zan zo Baba Malam inna gama koyar da ɗalibai kayi haƙuri"

Ya faɗa cikin ƙan da Kai. Baba Malam baice mishi komai ba yayi shigewarshi cikin gida, ajjiyar zuchiya Babangida ya sauke ya kaɗa kanshi ya koma majalisa wajen cin tuwo dan duk ranar

Edit with WPS Office

girkin Hannatu Uwargidan Amiru Babangida zagewa yake yi yaci abinci ya ƙoshi. A kab majalisar an yi ittifaƙin babu matar da ta kai Hannatu iya girki musamman miyar tuwo, da dama suke sawa ayi girki a fito dashi aci ana hirar nishaɗi. Wacce bata iya girkin ba tasha caccaka, wacce ta iya a yabeta. Bayan sun kammala cin tuwonnan sai su kai sallar isha daga haka Babangida ya nufi hanyar cikin gida dan yanason ganawa da malama  Babba kafin ya amsa kiran Baba Malam ko zata bashi satar amsa. Yana shiga gidan kiran Sabuwa yana shigowa wayarshi. Ko da ya ciro wayar a ajjihunshi yaga sunanta Cus kamar yadda yayi sebin number sai ya ja dogon tsaki ya mayar da wayar ajjihu.

A gurguje ya shiga falon Malama tana zaune a kafet ita da Umar autanta suna cin funkaso da miyar taushe sai ƙamshin man shanu ke tashi.

Waje ya samu ya zauna kusa da Umar yasa hannu a kwanon kafin yace.

"Malama ina wuni ya gida?" Murmushi tayi dan itafa a kaf yaranta tafi son Babangida kasancewarshi mai sunan mahaifintane.

"Lafiya lau Babana Yaya aikin da kuma masu suna?"

"Malama ni kam Baba Malam ne yace zai yi magana dani tun jiya, to ni gaskiya ina gama koyarwa dana sallami ɗalibaina na gudu. To yauma ya tare ni da maganar" Yana gama magana yasa funkason a bakin shi yana amsa gaisuwar Umar duk lokaci guda.

"Ai kuwa akan hakan hadda ni sai da ya ɓatan mun. Duk da nayi ƙoƙarin kareka amman Malam bai saurareni ba"

Idanu ya firfito dashi waje yace.

"To akan me yake nema na Malama ? Kinsan ni kullum mai laifine a gidannan." Murmushi malama Babba tayi kawai tace.

"Tashi kaje ka gama koyarwar Malam baya so ana barin ɗalibai suna jira.In kuka gama ganawa da malam sai kazo mu yi magana danni bansan akan me yake nemanka ba. Ba wayarka aketa kira ba ne Baba?"

"Wannan wawuyar yarinyarce take ta wani kirana. Nifa wallahi Malama albarkacin  Baba Malam kawai take ci na gaji wallahi an takureni da yawa fa gaskiya"

Ya miƙe ya fice yana maganganu. Malama Babba ta girgiza kai tace.

"Allah ya shirya mun Babana. Da kake cewa ka gaji ai tsuntsun da ya ja ruwa shi ruwa kan doka duk wanda yasai rariya yasan zata zub da ruwa. Umar ƙaro mana miya duk kun bi kun shanye"

Babangida yana aji yana karɓan hadda daga ɗalibanshi  Sabuwa ta dameshi da kira ya kashe wayarma baki ɗayanta. Karfe tara makaranta ta tashi bayan ya tsaya sun gaisa da ƙanne da yayye sai ya nufi turakar Baba Malam ya same shi yana shan fura mara nono tun da suka taso

Edit with WPS Office

bai taɓa ganin ranar da Baba Malam ya fasa shan fura ba sai rana ɗaya tak ranar da ahalin gidan basu isa sun mance da'ita ba. Su Malama da kansu suke daka mishi fura bai yarda an ba ƴan aiki ba.

Malama ƙarama tana gefenshi tana duba littafin nahawu Babangida ya nemi waje ya zauna ya gaishesu cike da ladabi. A taƙaice Malam ya amsa kafin yayi gyaran murya irin ta manya yace.

"Wato Babangida labarin sakin Farida matarka ya iso mun sarai duk da kai ka kasa sanarmun haka ma mahaifiyarku sai Sa'a na taka na bi har ɗakin mijinta shine take sanar mini halin da ake ciki. Babangida ita kuma Farida me tayi maka ka saketa?"

Kanshi a ƙasa kamar mutumin ƙwarai yace.

"Malam wallahi Farida yarinyace marar tarbiyya kamata nayi tana barbaɗamun asiri a cikin abinci shine na sauwaƙe mata. Kuma wall....."

"Dakata ya isheni haka nace mutumin banza da har kake kiran wata mara tarbiyya"

Baba Malam ya ɗaga hannu ya dakatar da Babangida. Dole ya haɗiye ragowar maganarshi. Baba Malam ya jima yana kallonshi kafin daga bisani yace.

"Kabi duniya a sannu Babangida. Ka tuna Allah ya baka ƴaƴa matannan ina guje maka ranar da zaka ɗanɗani wani ɗaci a matsayinka na uba. Ban taɓa yi maka baki ba kuma bazan yi ba. Amman ka sani alhaki kuikuyone, sharri tamkar haushin kare ne bayan mai shi yake bi.

Ɗazu na je can kasuwa wajen mahaifin ita Faridar na bashi haƙuri Alhamdulillah mun samu fahimta. Amman ya shaida mun Farida juna biyu gareta. To ni da na roƙi alfarmar su bani Farida in dawo maka da'ita ta zauna a ɗakinta har zuwa lokacin da zata haihu iddarka ta sauka a kanta. Mahaifinta yaƙi yadda ya faɗi munanan kaifafan maganganu akan ɗabi'arka a lokacin da suke bincike. To ita kuma yarinyar ta kafe tace in ba kai ba mutuwa zata yi. Wannan shine wautar da ƴaƴanmu suke yi a wannan  zamanin kenan a kan maza sai mace ta lahanta kanta sai kace ance mata dole sai da ɗa namiji zata rayu. To da duk so da zunzurutun ƙaunar data nuna maka ka kasa yin haƙuri da'ita mutumin kawai" Malama ƙarama da ta ga Baba Malam ya fusata da yawa sai ta saka baki.

"A dai yi haƙuri Malam in dai da yadda za'ayi shi ya mayar da'ita ɗakinta ai yafi ace wata ya kuma aurowa yana ƙara rushe martaba da darajar sunan gidansu."

"A_a Karama kar mu yi haka dake ai Babangida na daɗe da cire hannuna akan sha'aninshi musamman sha'anin  matanshi. Ubanshi Manga da yake shigewa gaba wajen nema mishi auren baice ya dawo da yarinyar ba, ai kinga ni bazance ya dawo da'ita ba. Ya dai ji tsoron Allah kawai"

Baba Malam ya jima yana ma Babangida faɗa kafin ya sake shi. Tsabar jagulewar da Babangida yayi ko cikin gida bai shiga ba kai tsaye motarshi ya shiga ya nufi gida. Karar sigari ya ɗakko a dash bot ya kunna yana sha a hankali yana lumshe idanunshi da suka ƙanƙance mishi.

Edit with WPS Office

SABUWA:.

A sanyaye na sauke wayar tawa a kunnena Rakiya tace.

"Yaya dai Lolo ko bai ɗauka bane?"

Bai ɗauka ba Rakiya dama bai fiye ɗaukar wayata ba nifa..."

"Ya isa Lolo ki gode ma Allah a hakan. Domin baki rasa sha ba, baki rasa ci ba, baki rasa sutura ba, yaranku suna karatu. Nifa a gidan ubanki du na rasa, ke dai ki ci gaba da gani kamar ba kya gani, kici gaba da ji kamar ba kya ji kawai. Jibi gidanki, jibi yaranki da shi kanshi mijin da kike Aure a kab ƴan uwanki babu wanda yayi dace kamarki fa"

Shiru nayi ina āuna kalaman Rakiya ina jinjina kaina da ke sake yi mun nauyi.

Wajajen bayan isha'i sai ga Sadiya ta karaso dan tun ɗazu na kira wayarta na sanar mata halin da ake ciki.

Tana ƙarasowa Likitan shima ya shigo shi da wata nurse hannunta riƙe da ruwa. Suna ƙarasowa ya jona ma Malama ruwannan a hannunta kana ya dubeni.

"Ayi ƙoƙarin bata abinci taci zamu yi mata allura kuma allurar tana da ƙarfi. Baban yarinyar bai san halin da yarinyar take ciki bane?"

Yayi maganar cikin kakkafeni da idanunshi.

Bai sani ba tukunna, amman zan kirashi in faɗa mishi. Amman meke damunta?"

Na tambaya cike da son jin amsarshi. Sadiya ce ta ƙarasa kan gadon ta ciro abinci a cikin roba tayi zaman bama Malama. Ni kuma na dawo da hankalina zuwa wajen Likita, shima hankalinshi a kaina.

"Ki same ni a office akwai bayanin da zan yi miki, sannan ku yi ƙoƙarin biyan kuɗin gado dan sun yi muku mutunci ma."

A sanyaye na bi bayanshi kaina na yi mun matsanancin ciwo kamar zai tsage gida biyu.

Tunani cike da kaina muka isa ofishin likita ya nuna mun kujera na zauna shima ya zauna.

Bayan tsowon kamar minti Biyar haka ni shiru, shi shiru sai ƙaran fitar iskar bututun sanyaya waje dake fitowa a hankali, can naji yace.

"Ashe rai kan ga rai Sabuwa? Tuni na yanke ƙauna da sake sanyaki a idanuna sai gashi yau Allah ya haɗamu. Sai dai banji daɗin yadda naga kin lalace kin fita hayyacinki kamar ba Sabuwar dana

Edit with WPS Office

sani ba ƴar gaye gwanar iyayi da wanka ba. Meke faruwa dake Sabuwa?" Ya ƙarashe maganar cikin haɗa lumfashi da fitowar kalmar ƙarshe.

Murmushi nayi kawai nace.

Khalid kenan ai rayuwa babu wanda bata ladabtarwa ciki har da Sabuwa"

Dariya yayi kawai ya miƙo mun wata takadda nasa hannu na karɓa.

"Alluran da muke buƙata kenan. Dattijuwar da kuke tare mahaifiyarki ce ne?"

Idanuna na lumshe nace.

Me ke damun yarinyar Khalid? Ka ajjiye tambayoyinka domin babu amfanin da za su yi maka daga ni har kai ɗin. Meke damun ƴata?"

"Allah ya baki haƙuri Sabuwa. Na fahimci kin mance dani sam a rayuwarki, ni inacan wata ƙasar zuchiyata da tunanina na tattare waje ɗaya naki ne ke kaɗai Sabuwa, ke ashe kinma mance da Khalid ɗinki hmm. Nimoniya ne yake damun yarinyar kuma cutar tayi tsanani sosai a jikinta, muna kan bincike amman a asibiti kika haifeta, sannan anyi mata allurorin riga kafin da ake yima yara?"

Idanuna na lumshe hawaye suka zubo mun a guje bansan sanda na fashe da kuka ba wallahi"

Na daɗe sosai ina rera kukan baƙin ciki da tuno a irin halin ma dana haifo Malaman yarinyar da ko awo ban taɓa zuwa ba a cikinta ma. Ga kuma wani babban miki da Khalid ya fama mun shi a zuchiyata.

Miƙewa nayi na fita daga ofishin kawai na dawo ward na yi zamana da takadda a hannu. Nazo na tarar su Rakiya suna cin abinci Malama tana kwance tana baccinta ƙarin ruwa na shiga jikinta.

Sai mun tara gobe in Allah ya nuna mana.

Mrs Bukhari ce

https://chat.whatsapp.com/IUKFTeuI76p2VaAvQ5nk0U

Edit with WPS Office

IDAN KAI YA GAJI...

GAMMO MA YA GAJI

BADI'AT IBRAHIM MRS BUKHARI B4B GIDAN KAMSHI

Wa.me/2348179523215

BABI NA FARKO

SHAFI NA BIYAR

Bincike ya nuna sama da mutune   miliyon goma sha biyar ke shan muyagun ƙwayoyi a najeriya.

Hakan kuma ya jawo asarar rayuka, taɓarɓarewar tarbiyya. Ya haɓɓaka fitinu da manyan lefuka a arewacin najeriya dama ƙasar baki ɗaya.

Tun kafin zama ya gagaremu mu koma bacci da ido ɗaya a buɗe. Lokaci yayi da zamu haɗa ƙarfi da ƙarfe domin mu taimaka ma hukumar yaƙi da sha da fataucin miyagun ƙwayoyi.

Dan ganin mun kawar da wannan ta'asa dake shirin zame mana ruwan dare.

Shaye_shaye annobace ga al'umma.

Wannan saƙone daga hukumar yaƙi da sha da fataucin miyagun ƙwayoyi wato ( NDLEA)

BABANGIDA:.

Motarshi na shan kwanar unguwarsu ya hango wata mota a dai_dai ƙofar get ɗin shiga gidanshi hakan yayi dai_dai da fitowar Mardiyya daga cikin motar kenan ta shige gida da ƙatuwar leda

Edit with WPS Office

niƙi_niƙi a hannunta. Sai da birkin Babangida ya ƙwace mishi zare idanu yayi yana kallon motar ya kalli ƙofar gidanshi.

"Tadi Mardiyya take  ko me, a gidana ƴata kuma? Lallai Sabuwa an yi mara mutunci makwaɗaiciyar banza da wofi daga ita har Mardiyyan yau ba zasu kwana lafiya ba. A gidana Yata take shiga bayan mota tayi taɗi bama gaban mota ba? Sale_salin yaron mutane ya kwantar da'ita a bayan mota yayi abinda ranshi yake so da'ita hmmm lallai."

Cikin sauri ya karaso ƙofar gidan maimakon yayi hon mai motar yayi gaba a_a dake rigimar yake so sai ya parka a bayan motar ya fito daga motarshi ya doshi wannan mota bai baƙin gilashi. Yana zuwa ba sai yasa hannu ya ɓalle murfin motar ta wajen zaman direba ba.

Kai ya dafe da ganin abun mamaki. Aisha ce zaune ɗare_ɗare akan cinyar matuƙin motar suna aikata aikin da alkalamina bazai iya rubutawa ba.

Mai makon Babangida yayi saurin sakin murfin motar a_a sai ya ƙura musu idanu suma shi suke kallo har Aisha ta sauka a cinyar saurayinta Babangida bai saki murfin motar ba saima shaidan dake ƙawata mishi surar Aishan dan ya ga abinda bai kamata ya gani ba. Wani irin abune yaji yana fusgarshi game da ƙirjin Aisha daya gani. Gata fara sol kamar Sabuwa, duk da kab yaran gidansu Sabuwa fararene tas wanke hannu ka taɓa.

"Lafiya Malam zaka buɗe ma mutane murfin mota kazo kayi tsaye. Baby ko kin san shi ne?" Ya juya yana kallon Aisha data haɗe rai a rainace, cikin rashin kunya tace.

"Mijin yata ne Sabuwa. Amman bansan dalilin zuwanshi nan wajen ba." Babangida yayi gyaran murya cikin tacewa a bariki, yawu ya haɗiya muƙut na sha'awar Aisha, da ƙyar yayi yaƙi da zuchiyarshi ya dubi saurayin Aisha yace.

"Kai ka rasa kuɗin hotel da zaka kama ka kai yarinyar taka sai dai ka danneta a mota? Amman dai an ji kunya, a haka dai kamar ɗan iskan gaske ashe ba haka ba. Ke kuma irin talakawan samarin da kike bi kenan ko?"

Yayi maganar idanunshi na kan ƙirjin Aisha sai lumshe idanu yake yi. Dariya saurayin Aisha yayi kawai ya ture Babangida ya rufe motarshi garam Babangida yana tsaye yana zage _zage Aisha ta fito a motar ta shige gida tare da doko get garam. Kafin ya gama mamaki sai ga Halima itama mota ta sauketa ta fito daga motarnan cikin riga da siket na atampa amman ɗinkin banza ƙirjinta duk a waje babu ko ɗankwali a kanta sai wani yalolon mayafi data ɗaura a kanta gashinta duk a waje, tsagun siket ɗinta ta baya kuwa ba'a ma magana. Taga Babangida sarai amman bata nuna tasan yans tsaye a wajen ba. Shi kuwa Babangida har ta ƙule ta rufo get  bai ɗauke kanshi daga kallonta ba, ƙaran figar mota da saurayin Aisha yayi ne ya dawo da Babangida daga hayyacinshi.

Har ya shiga motarshi mamakin to me ya kawo ƙannen Sabuwa da daddarennan gidanshi haka yake yi

Edit with WPS Office

Hon ya danna da ƙarfi ya lumshe idanu yana jiran Mardiyya tazo ta bude mishi get ɗin. Itace mai buɗe mishi get duk dare sai dai in ya wuce sha biyun dare sai Sabuwa ta fanshi yarinyar.

Bai buɗe idanunshi ba har sai da yaji ta buɗe get ɗin tukunna. A guje cike da haushi ya shiga gidan, kai tsaye inda yake ajjiye motarshi ya ƙarasa. Ta tagar uwarɗakin Sabuwa yake jiyo kiɗa da inuwar rawa. Kur yayi yana kallon inuwar matan a labule yana mamakin to uban me yaran gidansu Sabuwa suke yi a gidanshi da daddare, harda tara samari, da kunna mishi kiɗa a gidanshi? A zafafe ya fito ya kira Mardiyya da zafin murya. Yarinyar a ɗarare ta iso gabanshi tana zuwa ya kifa mata mari saida bakinta ya fashe.

"Dan uwarki me kike je yi cikin motar da naga kin fito?"

Jikinta sai ya kama rawa tana dafe da kunci ga hawaye ya haɗe da jini tace.

"Anty Aisha ce dama tace in zo in rakata."

Tsugunnowa yayi kamar yadda take a tsugunne ya kamo haɓarta yana rarraba idanunshi a kanta.

"Me kika ga sun yi da kika shiga motar dan uwarki?"

"Babu komai wallahi Baba"

Kunnenta ya kama du biyun ya murɗe yace.

"Duk ranar da na kuma ganinki a cikin motar wani sai kin gane kuranki. Ita Sabuwa tana ina da har ta barki kika bita. Alhalin tasan halin Yan gidansu sarai?"

"Ta kai Malama Asibiti tun da yamma, har suma malama tayi"

Kunnenta ya sake ya miƙe ya barta a wajen, ɓarayin inda turakarshi take yayi bai nufi ɓarayin Hamida ba dan yana jiyo shewar ƴan uwanta.

Yana shiga ɗakin ya faɗa banɗaki yayo wanka ya fito daidai wayarshi na ruri. Ganin number mai kiran ne yasa ya saki murmushi yayi wuf ya ɗauka nan suka shiga aike ma da juna kalamai marasa daɗi da rashin ɗa'a har hotunanshi da matarshi kaɗai ya kamata ta ganshi a yanayin sai da ya tuttura mata ta manhajar WhatsApp itama nan ta shiga aiko mishi da nata a kan doguwar kujera ya zauna yana kallon waɗannan hotunan yana lumshe idanunshi kasala na sakko mishi da wata iriyar buƙatuwa sosai. Dama Aisha ta riga ta kunna shi tun a waje.

Yana cikin wannan yanayin Hamida ta ƙaraso ta shigo cike da sallama da fara'a ɗauke a fuskarta. Shima da fara'ar ya tarbeta tare da miƙo mata hannayenshi halamar tazo gareshi.

Kallo ɗaya tayi mishi ta gane a halin da yake ciki ai kuwa tana shiga jikinshi ya soma fice mata a hayyacinshi sai da ta raɗa mishi.

"Habibi karfa ka mance bani ce da kai ba, kuma jego nake yi"

Edit with WPS Office

Jin hakan yasa ya ƙanƙameta tsam a jikinshi yanata sauke ajjiyar zuchiya a ƙoƙarinshi na mallakar kanshi. Ɗagowa yayi ya zuba mata idanu.

"Ya na ganka kai kaɗai ina matar taka ka barka?"

"Wai Sabuwa tana can asibiti Malama babu lafiya waccan wawuyar yarinyarce take faɗa mun, ɗazu dai ina makaranta naga kiran uwar sabida haka zanje in same su a asibitin inji me ake ciki"

Agogon dake manne a ɗakin ta kallo goma har da kwata duk da dai wannan ai ba dare bane a wajenshi shi da yake fin haka a waje musamman in Sabuwa ce dashi.

"To sai ka dawo. Kaga fa ni da nake gidan bata iya sanarmun da halin da ake ciki ba, kuma bata turo Mardiyya ta faɗa mun ba. Ni bansan wanne irin zama matarka take shirin tsara mana ba dani da yarana ba. Yanzu sabida Allah hakan ya dace kenan? Ko ƴan uwana a tsaitsaye suka shigo ita da yayyenta suka gaisa a taro fa, bayan an gama girkin suna ma kenan fa ni kam Habibi ya kamata kayi mata magana "

Shafa wuyanta yayi yana ƙanƙance idanunshi yace.

"Tsari da yanayin zamantakewarku ya kusan daidaita da izinin Allah lokaci yayi ki kwantar da hankalinki Tawan. Yanzu dai bari inje asibitin inga halin da ƴata take ciki ni sai na dawo ko, kice da su Goggo ina musu barka da zuwa da safe zan shigo in duba ku"

Tashi tayi ta fita tana mishi a dawo lafiya. Tana fita ya miƙe ya shirya tsab ya kulle ɓarayinshi ya fito yana karkaɗa keyn mota.

Hango Aisha yayi a bakin get tana buɗe ƙaramar ƙofar a tunaninshi ma ko Sabuwa ce ta dawo daga asibiti cike da tsantsar mamaki ya ga Maigogul ya shigo yana magana da Aisha.

"Wai lafiya kuwa nake ta ganin ƴan uwan Sabuwa harda Maigogul ko dai Malama mutuwa tayi ne to in mutuwar ma tayi sai uban Sabuwa yazo gidannan?" A zuchiyarshi yake wannan maganar har ya isa bakin motarshi dan banza yayi da Maigogul kamar ma bai ji sanda yake ambaton sunanshi ba.

Sauri_sauri gudu_gudu Maigogul ya ƙaraso bakin motar Babangida a lokacin har ya buɗe motar ya shiga yana mamaki ƙoƙarin kiran wayar Sabuwa yake yi ya jiyo maganar Maigogul a kanshi.

"Babangida fita zaka yi ne?" Ya tambaya yana ɗan dariyar rashin kamun kai. Babangida bai kalleshi ba yace.

"Fita zanyi. Amman lafiya dai ko na ganka a darennan ko wani abunne ya faru?" Yayi tambayar yana kakkafe Maigogul da idanu tamkar ba sirikinshi ba. Jira yake yaji abinda zaice mishi kawai sabida ba ƙaramin ɓacin rai yake ciki ba.

"O_o_o_o babu komai wallahi. Lolo ba tai maka bayanin abinda ya faru da gidanmu bane?'

Baki ya taɓe tare da girgiza kai halamar

Edit with WPS Office

a_a. Ko bakinshi bai buɗe ba.

Tsaiwa Maigogul ya gyara ya shiga yi mishi bayanin komai.

"To shine nace mu mu dawo wajen Lolo mu zauna kafin Allah ya ɓullo mana da yadda za'ayi. Ita Hauwa da yaran ɗakinta suna gidan Layuza kaji dai halin da muke ciki. Sai a taya mu da adda'a a matsayinku na malamai magada annabawa. Kuma muna buƙatar ka taimaka mana dan Allah Babangida dama dai kasan halin da muke ciki a gidan"

Bari in barka kar in cika ka da surutu"

Wuce wa yayi zuwa cikin gidan.

Tsabar mamaki kasa magana Babangida yayi. Shiru yayi yana auna rashin hankalin Sabuwa da iyayenta. Shine zai riƙesu a gidanshi ya ciyar dasu bayan ƴarsu da yake ciyarwa Aure da zaman ƙaddarar da take yi ma ya gaji ga ƙarin iyayenta da Yan gidansu ma. Tabb lallai kuwa zai aikata abinda Baba Malam zai yi fishi dashi fiye da fishin da yake yi dashi a yanzu. Dama tuni turarshi ta kai bango da zama da Sabuwa. Albarkacin Baba Malam kawai take ci tun farko ma. A yanzu kam abinds zai faru ya daɗe bai faru ba"

Motar ya ja fuuu sabida tsabaragen fishin zuchiya yau ko hon bai yi dan Mardiyya tazo ta bude mishi get ba da kanshi ya buɗe ya fice, bai damu da kasancewar gidanshi da zai kwana a buɗe ba.

Sigari ya kunna yana sha yana murmusawa dan mamakin Sabuwa da iyayenta shima kuwa zai basu mamaki wallahi . Sumy ya kira a waya ringing ɗaya biyu ta ɗaga.

"Jarumin jarumai ina kwance cike da kewarka"

Murmushi yayi mata mai sanyi saida ya ja sigari ya busar kana yace.

"Ina hanyar gidanki ki tanadar mun ruwan wanka kafin in ƙaraso."

Ihu tayi sosai na murna.

"Shikenan sai ka iso ina maraba da zuwanka. Zaka samu tarba mai kyau ta yanda sai ka mance da tsamayen matanka, duk da kaƙi yarda mu yi aure"

Dariya yayi mata kawai yace.

"Sumy uwar ƙorafi, in ban zo ba kice na barki ke kaɗai. In nace miki ina hanya ma sai ƙorafi ko? Ai kinsan ina sonki fiye da matan nawa, kuma matsayinki ai yafi nasu kece ma kike haɗa kan ki dasu. Kulawar da nake baki ai su basa samu."

Nan dai suka balle da hirar masha,a, daya isa gidan Sumy kuwa suka dulmiya cikin aikin ɓarna. ( Sumy irin ƴan matannanne da suke baro garinsu da zummar yin aiki a wani garin ko kuma yin karatu. Tana da iyaye ammam su suna ganin tamkar tarbiyyar da suka bata ya isa su barta zuwa

Edit with WPS Office

wani garin yin aiki. Iyayenmu na yanzu damuwarsu kawai a turo musu da kuɗi. Sumy tana da ɗaki ciki da falo cike da kayan alatu tana da rikakkun ƴan bariki da suke ɗaukar nauyin ci, sha, suturarta, kayan kwalliyarta da duk buƙatar rayuwarta. Ta gayyato duk wanda taso yazo su kwana suna aikin ɓarna.Amman asali dai Babangida shi ya lalata mata rayuwa tun tana karatu bata soma aiki ba ya rabota da ɗakunan kwanan dalibai. Ya kama mata haya a wajen makaranta, ya zuba mata kayan more rayuwa, shi yake ɗaukar nauyin komai nata tamkar matarshi ta sunnah haka ya mayar da'ita. A taƙaice dai Sumy daduron Babangida ce. In garin yayi mishi zafi gidanta yake zuwa ya yada zango sai yafi sati guda ma.

Kalubalene a garemu iyaye wallahi Allah zai tambayemu akan ababen kiwon daya bamu. Mu ji tsoron Allah dan mu iyaye muna da ruwa da tsaki wajen lalacewar tarbiyyar yaranmu. Kuna da saninku da tunaninku akan son duniya zaku mayar da ƴarku mai zaman kanta muji tsoron Allah)

Washegari

SABUWA:.

Yadda naga darennan haka naga rana, nurse tazo har sau biyu tana tambayata ko na siyo allurar ina ce mata ban samu Babangida a waya bane.

"To dan Allah ayi ƙoƙari kar ya wuce gobe ku siya, sannan maganar kuɗin gado ma iyakar alfarmar da zamu yi muku ta gobe ce, Allah ya bata lafiya"

Ni dai ina zaune shiru, Rakiya tana kan kujerar roba tana ta baccinta, Sadiya kuwa taran dare ta bar asibitin abinta. Tunda muka zo ko ruwa na kasa kurɓa a haka har garin Allah ya waye Malama jikin nata muka wayi gari ya tsananta sosai. Ina idar da sallah na miƙe tsaye.

Rakiya zanje can gida in samu Babangida tunda kinga baya ɗaukar wayata kuma kona tura su Aisha ba saurarensu zai yi ba yanzu zan dawo."

Ban jira amsar da zata bani ba nayi ficewata daga asibitin kai tsaye gida na nufa.

A tsakar gida na tadda dangin Hamida suna ta hidimar suyan ragon suna. Maigogul da su Mardiyya ma suna ƙofar ɗakina Maigogul yana wanke bakinshi da buta a gabanshi kamar alwala yake yi ido na ganin ido, gashi dangin Hamida na shigo na samu sai kallon inda Maigogul yake suke yi.

Take raina ya sosu na karaso wajensu.

Edit with WPS Office

Haba Maigogul dan Allah nan fa gidan sirikinka ne kaga ina da kishiya kuma ba zaman dadi muke yi ba, ya zaka zo kana Alwala a tsakar gida da safe haka. Ga bayan gida a ɗaki ka baro?"

Na ƙarashe faɗe ina sake kallon su Hamida.

"Ungo naki ƴar nema. Sai me dan a gidan siriki nake nifa na haifa mishi ke. Maganar kishiya Lolo Alwala fa nake yi makara nayi sanyin waje da katifa yasa bamma san inda nake ba. Aɗɗa'u kin ganshi nan shine ya tasheni. To meye laifi dan na fito. Koko dai iyakata kike son nuna mini ne sabida munzo gidanki kin bamu mafaka?" Duk wannan maganganun da yake yi dangin Hamida suna jiyo mu. Shima yana maganar yana kallonsu.

Ni dai bance mishi komai ba ganin yaran sai kallona suke yi.

"Ummi ya jikin Malama?"

Na dubi yaran nawa take hawaye ya kawo a idanuna da ƙyar cikin jarumta na ƙaƙaro murmushi nace.

Jikinta da sauƙi gado ma aka bamu."

Maigogul daya kammala alwalar sai muka shiga daga ciki mardiyya ta shinfiɗa mishi dadduma a gefe ya ta da kabbarar Sallah.

Wai ina su Aisha ko dai basu kwana a gidan bane?"

Na tambaya Aɗɗa'u yace

"Suna ɗakin ki suna bacci Ummi. Dan Allah ummi zaki kai ni inga Malama?"

Aɗɗa'u ya faɗa a mugun marairaice dama Malama mutuniyarshi ce tasu tazo ɗaya duk da babu wuya ya maketa.

A_a aɗɗa'u ka manta zaku je islamiyya ne yau? Jiya ma da baku je ba ai kunsan sabida suna da za'ayine. Mardiyya in kuka je Islamiyya kya sanar ma Baba Malam an kwantar damu a asibiti. Babanku jiya bai dawo bane?"

Mardiyya tace.

"Ya dawo Ummi harma ya mareni kinga bakina yadda ya fashe. Sabida Anty Aisha tace in rakata zance. Amman da safe da muka tashi bamu ga motarshi ba'

Kai kawai na gyaɗa nama rasa me zance. Karfi da yaji dai Babangida yana son ya dena kwana sam a gidan duk ranar girkina, yana wajen ƴan iska abokanshi ƴan iska a Club anata holewa kenan.  shi yasa ya kasa ɗaga wayata ma hmmm."

"Lolo ita Rakiya kika bari tare da Malaman. To ke ɗin me kika dawo yi, naga ko abinci kike buƙata ai Babangida  zai kai muku ba sai kinzo ba ko?"

Edit with WPS Office

Abu nazo ɗauka Maigogul amma yanzu zan komá"

Da haka na miƙe na shiga ɗakina, su Aisha suna kwance sun naɗe a bargo ga ac sun babbaka ɗakin yayi mugun sanyi.

Gaban sib na ƙarasa na buɗe wallahi bansan me nake nema ba bani da ko sisi na sani, kuma bana son in sake kiran Babangida sannan bazan haɗashi da Baba Malam ba.

Wasu hawayene suka gangaromun nayi saurin sharewa daidai lokacin da wayata ta shiga ruri Naja'atu ce. Da sauri na ɗaga tare da adda'ar Allah yasa kuɗina da nake binta zata bani. Ilai kuwa ina ɗagawa tace dani.

"Sabuwa a gurguje nasa mijina ya tura miki dubu ashirin cikon wancan aikin. Akwai ƙanwata ma zan rakota wajenki dan itama tana fuskantar wulaƙancin rijalu. Sannan akwai maƙotana dana turo sunce mun dai sun zo kince su dawo washegari da rana to Mamance aka wayi gari ba lafiya da zaran ta warke zan kawosu ma da kaina"

Murmushi nayi naji wani sanyi a raina.

To shikenan Naja'atu babu damuwa Allah ya kawo ki. Tunda dai kikai aiki da magungunan shikenan babu wata matsala dai ko?"

"Wallahi babu, duk fa abinda nace yayi mini yi mun yake yi jikinshi na rawa. Ai babu abinda zance dake sai godiya nikam, na dinga turo miki mata kenan"

Da haka mu kai sallama na kashe wayar tawa ai kuwa kuɗin sun shigo wallahi. Wani farin cikin samun wannan kuɗi ya lulluɓeni sib ɗin na rufe na juya na fita, su Aisha sunata gwartin asara.

A kitchen na tadda Mardiyya tana aikin suyar ƙwai

Ga farfesun kayan ciki tana girkawa.

Mardiyya me yasa kika taɓa kayan cikinnan kinsan fa na Babanku ne ko?"

Kallona tayi tace.

"Maigogul ne ya buɗe deeprizer ya ciro yace in dafa mishi. Ummi ga abincinku na gama zaki tafi dashi?"

Basket ɗin da take muƙo mun na karɓa.

Mardiyya zan tafi, ku yi shirin Islamiyya dan Allah. Kar ki manta ki sanar ma Baba Malam halin da Malama take ciki. Kuma ki nutsu ki kula da kan ki, ban yarda su  Aisha su jaki ko'ina ba nima. In Babanku ya kuma ganinki abin bazai yi miki kyau ba ni na tafi"

Da haka na fito yaran suna biye dani suna mun adawo lafiya. Har zuwa wannan lokacin dangin Hamida suna tsakar gida anata suyan nama ko ina ya karaɗe da ƙamshi har waje.

Edit with WPS Office

A waje na hango Maigogul da maza maƙotanmu yana ta gaisawa da jama'a yana labarta musu ai mahaifinane ga abinda ya faru ga abinda ya faru yasa suka dawo wajena. Dama in basu zubar mun da ɗan mutuncin da nake lallaɓawa ba ai ba su bane. Ta ƙasan layinmu na sulale na gudu dan takaici. Ina zuwa asibiti na biya kuɗin gado na siyo allurar da aka rubuta mana wata nurse tazo tayi mata lokacin ina kan gadon ina bata tea tana sha. Magungunan da zata haɗiya ta miƙo mun.

"Gashi da zaran ta gama cin abincin ki bata waɗannan magungunan tasha ko? Allah ya ƙara sauƙi in akwai wata matsalar zaki iya nemanmu"

Tayi mana sallama ta ƙarasa gadon dake kusa damu. Ita yarinyar tunda na dawo take kuka har zuwa lokacin da nurse ta isa gabansu bata dena kukan ba Maman duk ta rikice  da ganin mahaifiyar da mahaifin yarinyar da tun jiya yake wajen yana kula da uwar da ƴar a ruɗe suke da ciwon ƴar tasu.

Kaga mazan arziki maza ƴan Aljannah dama ba'a riga an zama ɗaya ba dole akwai bayin Allah masu tausayi da ƙaunar ahalinsu.

Ajjiyar zuchiya na sauke dai kawai. Nasa Malama ta sha magani tayi bacci sannan na sakko kusa da Rakiya nima na zuba tea na yagi biredi wainar ƙwan kuwa Rakiya ta kusan cinyewa ganin yadda wainar ƙwan take mata daɗi sai na bar mata nawa ina ɗan kurɓar tean a hankali.

"Wallahi Lolo ki gode ma Allah nifa a tunanina ko Babangida dukanki zai yi kullum in kikai la'akari da gidanku da tsattson da kika fito, da yadda akayi auren ma ba zaki ɗauki damuwar duniya ki ɗaura ma kanki ba kita rama irin wannan ba. Jibi tea kakkaura ga wainar ƙwai mai kauri naji harda kifi fa a cikin ƙwan. Wallahi Allah a cikin ƴan uwanki da wata zata samu rabin gatan da kike samu zata yi maraba dashi ko da kullum sai an daketa ne. Ki duba Labbai irin yinwar da take ciki suturar arziki ba dai ki gani a jikinta ba, jibi Adama sai a kwana nawa ba'a ɗaura tukunya a gidansu ba, duk da wannan baƙin talaucin kuma ga iskancin maza gana kishiyoyi kullum a cikin gori take. Dubi yaran ɗakin Hauwa Layuza ce dama_dama fa. Ni dai ki nutsu ki riƙe aurenki kina ganin rayuwar da ƙannenki suke yi. Dole ce fa take sasu fita in basu fita ba yinwa da baƙin talaucin ubanku ne zai kashesu a banza. Kuma a matsayinsu na mata suna da lalurori da dama da suke son ayi musu, in basu fita sun nema ba wa zai musu. Maigogul dai ya yar da zuchiyarshi kare ya tsinyeta me akeyi da namiji irin Maigogul Lolo?"

Hmmm kawai nace take na shiga zurfin tunani ƙwaƙwalwata na hasko mun rayuwar shekara goma sha biyar baya. Idanuna na lumshe kawai zuchiyata na yi mun wani irin ɗaci da zafi tamkar zata tarwatse.

Wajajen goman safe sai ga Adama ita da Labbai sun ƙaraso. Ko dana kalli Labbai sai naga halamun taci kuka ta ƙoshi a fuskarta da idanunta.

"Rakiya Bara'u fa uwarshi tasa ya saki Labbai wajen biyun daren jiya mitsiyaci. Dama meye a auren Bara'u in ba jar azaba ba"

Edit with WPS Office

Sai mun haɗu gobe

Ranar asabar da Lahadi ba posting sai zuwa monday in sha ALLAH

MRS BUKHARI B4B GIDAN KAMSHI

https://chat.whatsapp.com/IUKFTeul76p2VaAvQ5nk0U

IDAN KAYA YA GAJI.....

GAMMO MA YA GAJI

BADI'AT IBRAHIM MRS BUKHARI B4B GIDAN KAMSHI

LITTAFI NA FARKO

SHAFI NA SHIDA

Wa.me/2348179523215

Bincike ya nuna sama da mutune miliyon goma sha biyar ke shan muyagun ƙwayoyi a najeriya.

Edit with WPS Office

Hakan kuma ya jawo asarar rayuka, taɓarɓarewar tarbiyya. Ya habɓaka fitinu da manyan lefuka a arewacin najeriya dama ƙasar baki ɗaya.

Tun kafin zama ya gagaremu mu koma bacci da ido ɗaya a buɗe. Lokaci yayi da zamu haɗa ƙarfi da ƙarfe domin mu taimaka ma hukumar yaƙi da sha da fataucin miyagun ƙwayoyi.

Dan ganin mun kawar da wannan ta'asa dake shirin zame mana ruwan dare.

Shaye_shaye annobace ga al'umma.

Wannan saƙone daga hukumar yaƙi da sha da fataucin miyagun ƙwayoyi wato ( NDLEA)

Babangida:.

Yana kwance yayi rashe_rashe a gadon matar da ba tashi ba yanata baccinshi hankali kwance.

Sumy ce ta ta shigo daga falo tayi ado tayi kyau jikinta da gidan sai ƙamshi yake yi. A kan gadon ta zauna ta soma yima Babangida tafiyar tsutsa a gadon bayanshi. A hankali ya buɗe idanunshi suka haɗa da Sumy ya sakar mata murmushi tare da damƙe hannunta.

"To Sarki kaje ka yi wanka na haɗa maka ruwan wanka karin kumallo yana falo yana jiranka kuma"

Noƙe kafaɗa yayi yace.

"Yau ba za'a taya ni cuɗe bayan bane, me kike nufi?"

Hannunta biyu ta haɗe tace.

Edit with WPS Office

"Ina neman afuwarka  taso muje in cuɗe kayana. In wanke abuna tas"

Hakan kuwa akayi Sumy ita ta cuɗe Babangida kamar yadda ta saba a duk ranar da ya kwana a gidanta. Bayan ya fito ya tsaya gaban sib ɓangaren da kayanshi na gidan suke ya ciro farar shadda mai guntun hannu da baƙin takalmi mai yatsa, sai da ya kintsa tsab ya fito  ya sameta a falo tana haɗa mishi tea a kofin faɗi ka mutu (mug) ga wani lafiyayyen farfesun kayan ciki wanda tun asuba ta ɗaura a tukunyar dafa abubbuwa masu tauri wai ko me sunanta da turanci na dai mance. Amman kun ganeta na san. Ga biredi mai laushi ta ajjiye mishi a gabanshi yana ci suna hira.

"Dama kayan cikinnan bai ƙare ba Sarauniya?"

Dariya tayi tace.

"Iyakarshi kenan wannan. Kayan abincina ma duk ya ƙare sai sabuluna da maina sun yi ƙasa sosai"

Sai da ya kurbi  tea  ziwit_ziwit  kana yace.

"To babu matsala zan tura miki kuɗin sai ki siyo duk abinda kike buƙata."

Yana tsaka da magana kiran Hamida ya shigo wayarshi, wayar ya duba ya juyo ya dubi Sumy. Wuf ta ɗauke kanta a kanshi ta haɗe girar sama data ƙasa kunji fa ƙarfin hali irin na matan bariki. Wayar ya mayar ajjihu yaci gaba da karyawarshi, itama ganin ya ajjiye wayar yasa taci gaba da yi mishi hira har ya gama karyawa. Ta goge mishi takalminshi harda fesa mishi turare, su kai sallama akan tayi abincin dare dashi yana sa ran zai dawo"

Sai da ya shiga motarshi ya kira layin Hamida ruri biyu ta ɗauka.

"Baby wai a asibitin ka kwana dama? Na shiga barayinka na ganshi a kulle jikin yarinyar ya tsananta ne? Dan ɗazu uwar ta zo gida amman ko su Goggo bata iya gaisarwa ba" idanu ya lumshe yace.

"A can na kwana sabida yanayin jikin nata da asussuba na shigo gida wanka kawai nayi na sake kaya na koma, Lokacin gaskiya baku tashi ba shi yasa ma ban kiraki ba. Amman yanzu ma zan ƙaraso gidan kinsan fa bamu gaisa dasu Goggo ba" Murmushi tayi mishi tace.

"Ai kuwa Inna sai ƙorafi ma take yi wai baka shigo ba, sai da na faɗa mata yarinya ce babu lafiya. Amman ni kam Habibi in tambayeka mana?"

"Ina saurarenki"

"Naga ƴan uwan Maman Aminu harda mahaifinta, kuma naga kamar kwana ma suka yi a gidan. Dan abun kunya ido na ganin ido ya fito yana alwala a tsakar gida. Maman Aminu tayi mishi magana ya shiga zaginta. Kuma ya fita waje yana ta gaisawa da jama'a."

Wani ƙududun baƙin cikine ya tokare wuyan Babangida jin labarin da Hamida take labarta mishi.

Edit with WPS Office

Da ƙyar ya haɗiye yawu tare da magana cikin murya mai kauri ta cikar mazantaka.

"Hmmm zasu bar gidan yau ɗinnan dolensu wallahi, zan haɗa harda Sabuwan in koresu dan bazan zauna su zubar mun da mutunci a unguwa ba wallahi. Malama zata zo zuwa anjima ita da Yaya sa'a.

Wani irin daɗine ya haɗu ya dabaibaye zuchiyar Hamida shikenan burinta ya kusan ciki gida da miji zasu zama nata mallakinta ita kaɗai. Ai sai ta ƙara da cewa.

"Abun babu daraja naga mahaifin nata baida nutsuwa sam Baka ga yadda yake guje_guje dasu Aɗɗa'u ba har faɗuwa yayi rim a ƙasa fa yaran sukaita mishi dariya. Yanzu ni kaga su Goggo inata roƙonsu ko kwana ɗaya su ƙara amman sun ƙi dan Abbanmu kwana ɗaya ya basu izinin yi yace ba za'azo gidan siriki a shantake ba yanzu haka kai suke jira ku gaisa su tafi."

"Hmmm ku da gidanku yake gidan tarbiyya kenan. Gani nan a hanyar zuwa su jirani dan Allah fa"

Da haka su kai sallama bai zarme ko ina ba ya wuce asibiti dan ya duba jikin Malama."

SABUWA:.

"Ai gara ma da mitsiyacin ya sake ki ko Allah zai kawo miki wanda ya fishi. Ina roƙon Allah ya baki irin gidan Lolo"

Cewar Rakiya kenan. Adama tayi carab tace.

"Nima tun muna hanya nake rarrashinta da auren Badaru ba gara zawarcin ba? Ai zawarawa su suke ci yanzu. Wallahi Zaliha yarinyar Auwalu mijinmu da aurenta ya mutu ba kuga yadda manyan motoci ke sunturi a kanta ba. Kuma da in kuka ga ɗakin Zaliha kamar kitchen ɗin ƙazama. Yanzu ko ta yi bilicin  ta zama fara sol kamar jini zai fito a jikinta"

Rakiya tace.

"Kunji ba. Ni wallahi gaba ta kaimu ma da ya sakota ina wani arziki a auren Badaru in banda ƙaddarar dole data haɗa abun. Mitsiyaciyar ai ita ta jama kanta duk abinda ya faru, sai ki riƙe ya zama miki darasi a tafiyar zawarcinki, in kika tsaya kula irinsu Badaru to wallahi zafin talauci da baƙin cikin ɗa namijine ajalinki ƴar iskar kawai. Me ake da talauci wai? Ku dubeni yadda na lalace ɗan ƙyan nawa da hasken nawa duk ya dishashe. Ubanku bashi da aiki sai ɗaura mana baƙin ciki da takaici amman ƙaddara ta riƙe mu muna zaune. Ni wallahi dama ni aka saka."

Edit with WPS Office

Ni dai nayi kasaƙe ina ji sunata tattaunawa dai. Labbai sai wani farin ciki take yi itafa tayi Firi. Zama suka yi suka zuzzuba tea da biredi suna kan sha sai ga Maigogul da Aisha, Sadiya, da Rahama sun shigo ɗakin hannun Sadiya riƙe da filas ɗin abinci.

"Adama ashe kun zo, ai da tambaya muka iso ɗakin wayar Lolo taƙi shiga, Sadiya kuma dan iskanci wai bata riƙe lambar ward ɗin ba." Rakiya tace.

"Maigogul kaga wai ɗan iskan yaronnan Badaru ya saki Labbai kuma wai cikin tsakar dare fa"

Rakiya na taɓa da take ta faman ɗaga murya ga mutane a ward ɗin kuma ba'a fiye son hayaniya ba. Dakuwa tayi mun kafin tayi magana wata ma'aikaciyar jinya tazo ta koresu waje ya rage ni kaɗai a ɗakin su kuma suka ce mun zasu zauna a waje in ina buƙatar wani abun sai in kira ɗaya daga cikinsu.

Har ga Allah ni da zasu tafi in dena ganinsu da nafi so, amman hannunka baya ruɓewa ka yanke ka yar. Su nan zumunci suka nuna mun da suka ɗungumo suka tawo. Ina cikin wannan tunanin ma Sai ga Gaza da shi da  Magazin ana kiranshi da magazin ne sabida duk wani labari mai kyau ko mara kyau a bakinshi ake ji, shine tsuliyar duniya. Yafi shekara guda a gidan gyaran hali sakamakon kamashi da saida miyagun ƙwayoyi da akayi. Tabbas sana'arshi kenan dan har a gida a tsakar gida yana zama ya ƙuƙƙullah kayan sana'arshi.

Magazin yaushe kayi firi ikon Allah?"

Dariya yayi mun da muryarshi irin ta masu shaye_shaye sosai yace.

"Gamu Allah yayi mun sake shaƙar iskar ƴanci. Kinsan akace an ɗauremu ɗaurin rai da rai, mune ɓata gari mune ƴan iskan gari da dai soki burutsunsu. To gamu dai mun dawo zamu ɗaura sana'armu daga inda muka tsaya labarin yadda akayi na fito kuma ki basar. Ya naga kin wani rame ne kin yi duhu ko kece babu lafiyane, ko dai ɗan akuyan mijinkine in sa a faffarɗe mun shi. Na faɗa miki in na shiga fadama mu kan haɗu a cikin ruwa wajen kamun kifi fa"

Gaza ya dafa shi yace.

"Yaro nutsu a asibiti muke kaga sai kallonmu ake yi. Lolo ya jikin eh ita Malama ɗinne?"

Hmm jikinta da sauƙi kaga bacci take yi. Kun ga su Maigogul a waje ko?"

"E mun gansu, kinsan halin Fada ko da ya ga magazin sai ya hau tsine mishi bayan duk dattin ƙwaƙwalwar shi ya ja mana"

Yana cikin faɗin haka sai ga Maigogul ya shigo shi da Babangida. Ya ji abinda Gaza yake faɗi sabida Allah ko dan ganin idon Babangida da kuma asibiti da muke ba sai yayi shiru ba? Sai ya farma Gaza da zagi yana kiranshi da mashayi.

"Hattara Fada wallahi kar ka sake zagina eh. Ai duk halin da muka tsinci kanmu a ciki kaine silar komai. Ka haifemu ka sakar ma duniya mu ya ba zamu lalace ba ya ba zaka ga ba daidai ba?

Edit with WPS Office

Mune bin kwararo_kwararo neman abinda zamu saka a bakinmu wai sunan muna da iyaye. Iyayen arziki na saka yaransu a makaranta su killacesu su basu tarbiyya. Mu sai dai da zaran gari ya waye a koro mu waje ace mu shiga duniya. Babu arabi babu boko, babu ci babu sha ka haifemu rai nawa  babu abinda ka iya tsinana mana shin in bamu zama ƴan iska marasa ji ba me kake so mu zama. Ina ji ina gani ƙannena na yawon ɓel_ɓel ce maka akayi daɗi muke ji? Ciwon a zuchiyata da cikin jikina yake. Zan hanasu nemama kansu rayuwa mai kyaune. Me kake so ne?  mun zama marasa ji kamar yadda kuka so ai. Al'umma su guje mu su aibantamu, kuma da ku ka taɓarɓara tarbiyyarmu ku hantaremu ku zagemu bakwa son mu raɓe ku. Shin wai baku taɓa zama kunyi tunanin muma bama son kanmu a haka bane? Ai mana adalci dan ALLAH."

Da kuka Gaza ya ƙarashe maganarshi. Abinda zaisa Gaza yayi kuka lallai babbane. Maigogul kuwa da duka ya rufe Gaza da magazin da yake ta yi mishi kallon banza tun shigowarshi. Ina hawaye zuchiyata na yi kamar zata faɗo ƙasa muka haɗa idanu da Babangida da yake mun murmushin dana yi imanin na takaicine. Ma'aikatan kiwon lafiya ne da sikuruti suka zo suka kori su Gaza daga asibitin. Magazin yazo wucewa ta gaban Babangida , harfa ya wuce ya dawo.

"Dena kallona dan uwarka ko in tsiyaye maka idanun kallon matan bariki. Kasanni wallahi babu kyau babu daɗi. In maye ya manta Uwar  Ƴa bata manta ba."

Da sauri Babangida ya kau da kai dan yasan karon babu daɗi. Maigogul ya fice yana sake zagin su Gaza da suka fice suna zage_zage.

"Kunji kunya ku kam Sabuwa. Jibi yadda wanki yake zagin ubanki. Tur da wannan rayuwa ta gidanku. Wallahi ban taɓa jin labarin irin gidanku ba ko da a hikayoyine. Iyayenki da fanɗararrun ƙannenki da kika tarkato mun zuwa gidana kuma wannan zaki karɓi sakamakonki a hannunki sai inga ko a bakin  kwatar unguwarku zaku dinga kwana. Muniyar banza"

Nera dubu ashirin ya jefo mun kan cinyata ya juya ya fita cikin ɓacin rai marar misaltuwa. Saka kaina nayi a tsakankanin cinyoyina na fashe da wani irin kuka na fitar hayyaci. Na daɗe sosai ina rera wannan kukan. Kirjina da kaina sunyi wani irin mugun nauyi. Ni da kaina na rarrashi kaina da kaina. Idanuna a rufe ina jujjuya kalaman Gaza wallahi dukkan abinda ya faɗi gaskiya ne Maigogul da Rakiya dai idanunsu ya rufe ba zasu karɓi wannan gaskiyar bane kawai. Oh mu kuma haka ƙaddara tayi damu.

Kiran Yar shuwa daya shigo wayata ne yasa na ji zuchiyata ta ɗan sassauta a wajenta kaɗai nake jin sanyi take bina da kalamai masu daɗi. Ina roƙon Allah ya bata miji nagartacce.

Ɗaga wayar nayi na saisaita muryata.

Kawata sai yau kika kirani? To bazance nayi fishi ba tunda nima ban kira ba. Kinga ƴarki Malama ce babu lafiya muna asibiti ma"

Yar shuwa ta sauke ajjiyar zuchiya tace.

"Wai ke Lolo muryarki kullum a cikin damuwa kike ne? Ya kamata ai ki saba da halin Babangida

Edit with WPS Office

zuwa yanzu ko? shekara goma sha kina cikin abu ɗaya. Ni shawarar da zan baki kiyi watsi da ɗan banza kawai ki daure kiyi ta harkokin da suke gabanki ya fiye miki. Kinsan fa ko wanne bawa da kalar ƙaddararshi"

Hawayene ya kuma silalomun a kuncina na cije leɓena na ƙasa cike da takaici nace.

Ƴar shuwa ba zaki gane bane. Duk macen da take fuskantar irin abinda nake fuskanta a gidan aure ce kaɗai zata ji irin raɗaɗin da nake ji. Ko ba wannan ba matsalolin cikin gidanmu ma kaɗai wallahi sun isa su hallakani har lahira. Yanzu Gaza, da Maigogul, da Babangida suka haɗu a asibiti suka cunkusamun sabon baƙin ciki. Kinsan Allah ji nake kamar in kashe kaina uban kowa ya huta"

Dariya tayi tace.

"Haba dai ai duk wahalar rayuwa tafi mutuwa. Ke dai sai haƙuri kawai. Kinga fa Aurena saura sati biyu in faɗa miki komata ta kamo babban kifi, kuma na sarƙe mishi wuya ta yadda bai isa ya kubce mun ba. To ya sammacenine ko ince su Mama ne suka sa ya fito faka_faka dan wallahi ban shirya ba ni.

To a Maiduguri dai za'a ɗaura auren nasan zai yi wahala Babangida ya barki kizo biki ko ƙawas,?"

Duk damuwar da nake ciki sai na nemeta na rasa wallahi. Shekara nawa ƴar shuwa tana zawarci sai yanzu dai Allah ya kawo mijin. Lallai wannan miji zaiga lele dan ƴar shuwa ta haɗu ta ko wanne ɓangare ta iya kula da namiji sosai kun dai san shuwa wajen mallakar miji.

Kai ƙawata mijin ƙarfen kice ya iso? Abun daɗin kuma a ƙanƙanin lokaci ba'a ja lokaci ba. Kawata ai dole ayi bikinnan dani. Zan yi iya ƙoƙarina Babangida ya barni in zo ai mune ƙirjin bikin ko bai barni bama zanzo dan ko sama da ƙasa zata haɗe bazai barni ba ni na sani."  Dariya muka saka dukkanmu nace.

Kawata amman ni bansan labarin wannan na hannun ƙarfen ba. A ina kuka haɗu ko dai shine wanda ya kawo ki rannan gidana da uba uban shopping?"

"Ai kuwa shine ƙawas. Ni bama wani son shi nake yi ba nagartarshi ce tasa zan aureshi kuma ni nafi son namiji son shi yafi nawa to a taƙaice dai hankalina ya nutsu dashi. Amman gaskiya wasa nake yi miki babu wani biki auren sirri nake son mu yi sabida kema kinsan muna da masassada shi yasa ma a Maiduguri za'a ɗaura suren. Sabida shima auren sirrin yake so a yadda ya faɗa mun matanshi in suka sani ba zasu bari ayi bikin lafiya ba kinsan kishi na mata. To ni kuma dake a matse nake saina mika wuya duk da naji tsoro sosai da yake faɗa mun gida ɗaya zai haɗemu da matanshi. Kawata kinsan kishiyace ta fitar dani a gidana na farko ki taya ni da adda'a, kuma ki buga mun ƙasa mu ga ko abun da haske nasan aikin ki yankan wuƙane"

Dariya nayi nace

Edit with WPS Office

Kema kinsan ta wannan ɓangaren baki da matsala. Ina da magungunan da zaki yi amfani dasu a ranar da kika tare in dai kika yi amfani dashi, gaskiya ya zama miki nama ƙawata"

Nan mu kaita hira mu shiga ta nan mu ɓulle tacan har saida damuwata rabi ta baje kafin mu kai sallama da'ita. Ina ajjiye wayar sai ga kiran Malama mahaifiyarsu Babangida. Gabana sai da ya yanke ya faɗi dana naga kiran ƙila akan zamansu Rakiya ne, dama dai nasan za'a rina. Malama bata taɓa kiran wayata haka siddan ba. Cikin dakiya na ɗauki wayar,  kafin fa ince wani abun tace.

"To maras kunya gani a gidan naku kizo ki same ni yanzu. Yanzu Babangida ya shigo yake faɗa mun kina asibiti yarinya ba lafiya. Ki tawo yanzu ki same ni"

A sanyaye nace da'ita

To"

Kit ta kashe wayarta, ni kuma nayi murmushi kawai na sauka na fita na tarar da su Sadiya sai hira suke duk sun cika ma mutane kunne.

Rakiya ki zauna a wajen Malama zanje gida mahaifiyar Babangida tana nema na tace in zo yánzu."

Maigogul ya kalleni da kyau kafin yace.

"Maza jeki duk abinda zata ce kice tayi haƙuri. Lolo bana son abinda zai barroki da wannan daular kuma muma wallahi babu inda zamu je har sai na samu yadda na gina ko ɗaki ɗayane duk mu je mu gwamutsa, ko ba gaskiya ba Rakiya?" Rakiya tace.

"Sosai kuwa dan tatsuniyar gizo bata wuce ta ƙoƙi. Dubi yadda shi kanshi Babangidan yazo ya wuce mu fuu kamar bai san Allah yayo ruwan tsaronmu ba babu ko gaisuwa fa." Maigogul yayi magana yana mai zazzare idanu yace.

"Ni da nayi mishi bayanin iffitalin daya faɗa mana ma. Har na gama magana ɗan tahalikinnan baice mun uffan ba, sai dai nine na bashi waje. Lolo jeki kar mu tsareki, nima yanzu zan tafi akwai meeting da aka gayyaceni zan yi dare sosai, ƙila ma sai zuwa gobe in Allah ya amince zan dawo"

Da jan ƙafa ni dai na fita titi. Kai tsaye na samu abun hawa har ruwa ƙofar gida.

Abinda na gani na mamakine yasa ni buɗe baki. Kunsan wai me na gani?"

Nima zan so kuji abinda Sabuwa ta gani

Wannan rikita_rikita da yawa take

Edit with WPS Office

Sai Allah ya kaimu monday in sha ALLAH zamu ci gaba

Ayi weekend lafiya.

Nagode sosai

MRS BUKHARI B4B GIDAN KAMSHI

IDAN KAYA YA GAJI....

GAMMO MA YA GAJI

BADI'AT IBRAHIM MRS BUKHARI B4B GIDAN KAMSHI

LITTAFI NA FARKO

SHAFI NA BAKWAI

OGA YACE YAYI HAKURI AYI MUKU POSTING

Ina manyan mata masu capacityn  suke?  ku fito lambarku ce ta fito.

Yar uwa turaren wuta kike nema nau'ika daban_daban masu musulmin ƙamshi da kama muhallu? Ba itacen banza masu sanya gida ƙauri da hayaki kamar an kunna taohuwar bespa ba.

Matso gasu MRS  BUKHARI B4B GIDAN KAMSHI nazo miki da duk abinda kike buƙata na ƙamshi. Kama daga turarukan wuta irin na gidan alfarma. Zuwa humrori iri daban daban masu musulmin ƙamshi da riƙe jiki.

Bugu da ƙari muna da turarukan kaya, na fesawa dana turara kaya.

Muna da kulaccam nau'i daban daban masu gyara jiki da lausasa  fata mata, ga kuma ƙamshi

Edit with WPS Office

mai inganci.

Muna da turarukan tsugunno na musamman masu sirri Hajiyata

Muna da room freshener iri_iri

Muna da mopping mix masu kama waje.

Akwai turarukan kafet dana kujeru.

Sannan akwai box _ box  setika na Hajiyoyi masu ƙyallin goshi.

Muna da Amarya package.

Muna da uwargida package

Muna da maijego package

Muna bayar da sari ko a ƙasar waje kike, muna tura kaya

Saudiyya

Nijar

Ghana

Camaron

A duk ƙasar da kike kayanmu zai iso miki cikin aminci da yardar Allah.

Hajiya akwai Humrar matan aure wannan ta musamman ce.

Duk wani abu da kika sani na ƙamshi babu irin wanda bamu dashi a kamfaninmu.

Muna da turaruka designer na maza da mata wanda kamfaninmu ke bugawa Hajiya babu inda zaki je ki ci karo da mai irin ƙamshinki.

MRS BUKHARI B4B GIDAN KAMSHI TAZO MUKU DA DUK ABINDA KUKE SO NA KAMSHI HAJIYA.

KUNSAN KANURI MUNE KAMSHI DAMU AKE KOYI

SIYAN NAGARI MAIDA KUDI

MUNA MARABA DA MASU SIYAN ƊAYA KO SARI.

LAMBAR DA ZA'A SAMENI KAI TSAYE ITACE.

Wa.me/2348179523215

Edit with WPS Office

SAI NA JIKU

Mota ce a kofar gidanmu shaƙe dam da kayan Amarya. Da ganin kayan Amaryar amaryace irin masu darajarnan wacce ta fito a babban gida. Mata da maza sai sauke kaya akeyi. Illahirin mamaki niko ya kamani ashe bani kaɗai ba wallahi matan unguwa sai leke suke yi suna zunɗe, ai dole suyi yaushe muka dawo unguwar da har Babangida zai sake aure ga Farida daya saka har yaushe aka kwashe kayanta ni Sabuwa? Kai kawai na girgiza na shige cikin gidan, ashe banga komai ba matane suka zo sosai masu jere kusan rai ashirin gasunan a tsakar gida wasu na daga ciki na waje na miƙa ma na ciki kaya.

In da ranka kasha kallo, ni dai da sallamata na shiga ɗakin Hamida na tarar da Malama tare da Sa'a. Hamida na gefe tana shayarwa idanunta sun koma kamar garwashin wuta, ga akwati ƙanana turoli guda biyu ɗaya baƙi ɗaya ja. Ai dole taci kuka masu ƙyallin goshi ƴan gaban goshin oga ba.

Babu wanda ya amsa sallamata dama banyi dan su amsa ba. Na nemi waje na Zauna.

Ina kwana Malama ya jikin girma?"

Nan ma shiru tana dai riƙe da haɓarta tana watso mun kallon wulaƙanci. Shiru nayi ban sake cewa da kowa uffan ba inata haɗiyar yawu tare da  ja da saukar nunfashi. Har Malama ta ƙaraci shiruntа kana tace.

"Ga akwatin faɗar kishiyanan ke ɗaya Hamida ɗaya auren ma an riga da an ɗaura, duk da ba da zummar ɗaurin auren aka tafi ba sadaki da tsaida rana kawai aka je ayi to basu dawo ba sai da aka ɗaura. Wannan kayan ba Babangida bane yayi muku a matsayin faɗar kishiya ba ita yarinyar da ya aura itace tayi muku da guminta. Ni nama taba ganin yarinyar arziki kamarta ƴar albarka. Yanzu ne dai Babangida zai yi aure duk mai sa hannu a auri sakin da yake yi da yardar Allah alkadarinshi ya karshe daga wannan Babangida ya dena saki in sha ALLAH. Bayan itama wata zata shigo ku zama huɗu kenan kiji in faɗa miki.

Murmushi nayi sosai ina kallon akwatin ina kallon Malama duk a lokaci guda. Ni ba yau  aka saba yi mun haka ba, in yana zama jiki to ni yama  zama maina wallahi.

Allah ya sanya alkhairi yasa in ta shigo sai dai mutuwa ta raba. Zan iya tafiya na bar marar lafiya a asibiti?"

Sa'a tace.

"Ameen in da gaske kike yi. A wannan karon asirinki bazai yi tasiri ba dan yarinya ƴar malamai ce itama kamar yadda muke ƴaƴan malamai gaba da baya iyayenta malamai ne. Hamida kece zamu ba haƙuri ki yi haquri da kishiyar da akayi miki bagatatan. Kema kinsan muna sonki da

Edit with WPS Office

Babangida kuma muna yinki. Sai dai hakan bazai sa Babangida na son ƙarin aure mu hanashi ba. Amman mu dangin Babangida muna yinki"

Murmushin na kuma yi dan faɗan da yafi ƙarfinka wasa kake mayar dashi. Ita dai Hamida kasa daurewa tayi ta hau shesshekar kuka tana faɗin ita sam ba'ai mata adalci ba. Wallahi rarrashinta sukai ta yi kamar wacce jaki ya nana da ƙasa. Malama ta dawo da dubanta kaina tace.

"Magana ta biyu shine. Iyayenki da fetsararrun ƙannenki da yayyenki da suka tare a gidannan sabida abun kunya gaba kuka bashi ba baya ba. Yau ba sai gobe ba kamar yadda  nazo basa nan in kika koma ki sanar musu kar wanda ya tako cikin gidan ɗana. Wallahi Allah in suka dawo kema Sabuwa zamu yar da ƙwallon mangwaro mu huta da ƙuda ko da hakan na nufin Malam zai tsine ma kininshi ne akan ki. Ku babu kunya a tattare da lamarinku sabida iyayenki mutanen banza ne sai su zo su tare a cikin gidannan har da mahaifinki ma wanda a samfurin rashin ɗa'a da rashin ta'ido babu irin samfurin da mu bamu ganshi ba shine sabida lalacewar ta kai lalacewa zai biyosu gosai_gosai. In maye ya manta uwar ɗa ba zata mance ba. Yadda ya tozarta sunan haularmu a lokacin da muke roƙonshi ya ƙiya. Muma dole ya fice a gidannan ko da a titi zasu kwana. Kema kuma ki sani zaki bisu muddin suka dawo cikin gidannan yau ɗinnan suka kwana. Na gama maganata tashi ki fice Mun dan yadda nake ƙin mutuwata haka nake ƙin ki, kuma wallahi abadan bazan taɓa jin sonki ba ko abinda kika haifa ba."

Miƙewa nayi kawai zuchiyata na garbawa har ga Allah kuma har cikin raina ji nake kamar in dura ma Malama ashariya in silleta soso da sabulu kafin in fita in tabbatar mata da rashin tarbiyyar gidanmu. Amman babu komai akwai lokaci. Kuma tasan ba kanwar lasa bace Sabuwa ruwane ya doki babban zakara.

Akwatin na ɗauki bakin na ja na fita ina ganin duhu_duhu, ance raba arne da makami ibadane da ba dan haka ba babu abinda zanyi da wannan akwatin. Ashe goga naku yana cikin gidan yayi uwa yayi makarɓiya a cikin maza dangin Amarya ƴan jere. Haɗa idanu muka yi dashi yana riƙe da ƙaton kwalin gado irin na italiyan ɗinnan, ai na faɗa muku Amaryar gaskiya ƴar masu dashi ce da ganin kayan da aka danƙara mata. Ashe harda abokan Babangidan duk sun saje anata aikin lada dasu. To aikin lada mana namiji tuwon ƙaya miyar allura kenan. Ka ci ka sossoke, ka ƙi ci ka mutu dan yinwa.

Kaina na kaɗa kawai na bi ƙofar ɓarayina ina share hawayen da wallahi bansan na menene ba. Ɓarayin a share tas Mardiyya akwaita da ƙoƙari sosai. Key nasa na buɗe ɗakin na shiga falonma a gyare tsab har da ƙamshin turaren kajiji da yake shine turaren wutana da'iman.  Kuma dake ingantaccene wanda ya fito daga hannun Mrs Bukhari B4B GIDAN KAMSHI ram ya kama ɗakin ko wacce kusurwa ƙamshin turaren ke tashi. Akan kureja na zube na saki kuka wiwi ina dafe da kaina da nake ji kamar zai fashe.

Ni yanzu yaya zanyi da su Maigogul? Dan ba ƙaramin aikin Malama bane tayi musu tujara ta tozartasu har waje ba. Maigogul kuma da Rakiya ba ƙyaleta zasu yi ba abubbuwane zasu kuma damalmalewa tarihi ya kuma maimaita kanshi dama karon babu dadi. Wata zuchiyar tace ki

Edit with WPS Office

siyar da kayan ɗakin ki ko haya ne ki kama musu su koma...

Idanuna na lumshe dana tuno mahaifin Babangida ne yayi mun kayan ɗakin babu ko sisin kwabonmu a dukkan kayan katakon dake ɗakina.

Wata zuchiyar tace ki ɗauki ɗan kunnen zinaren Malama ko na Mardiyya ki siyar ki basu kuɗin su gina gidansu.

Tuno hakan da nayi yasa na zabura da sauri, ba shiri na koma na zauna daɓar wallahi jirine ya yar dani na jima irin jimawar da zata baku mamaki, na rasa suma nayi ne, ko kuma a hayyacina na fita bazan iya cewa ba. Kunga dai lissafin ai da safe nazo gidan ko? Bani na san inda kaina yake ba sai azahar da ƙyar na tashi kuzarina yayi nauyi sosai wani jiri nake ji sosai. Sallah na soma yi kamar kullum na dinga kuka a gaban mahaliccina, kunga ban iya wasu addu'o'i ba sai na hausa kawai, kullum adda'ata itace Allah ya kawo mun ƙarshen wannan al'amarin. Banɗaki na faɗa nayo wanka na sake kaya na fito kai tsaye zuwa ɗakin Babangida domin in ɗauki ɗan kunnen gold ɗim Mardiyya. Ina jawo durowar waɗannan ɗan kunnaye suka ce ɗauke mu inda kika ajjiye. Babu komai a wajen sai tarin tarkacen Babangida kawai. Nayi imanin Babangida ne ya ɗauke waɗannan ɗankunnayen dan babu wani mahalukin da yasan ɗankunnayen a wajen suke, wani irin ajjiya akayi musu ta yadda wanda ya ajjiyene kaɗai zai san inda ya ajjiye.

Jikina na rawa na fito ina harhaɗa hanya. Wayata ce naji tana ta faman ruri a jakata dana yasar a falo. Babu karsashi a jikina na ƙarasa na zaro wayar Baba Malam ne yake kirana.

Assalamu alaikum Baba Malam barka da rana"

Na faɗa a hankali babu ƙarfi a jikina sam.

"Lafiya Sabuwa, Yaya mai jikin kuma duk da dai gani a asibitin nafi minti arba'in. Maigogul yace mun kinje gida sakamakon kiran gaggawa daga wajan Malama ko?"

Ya tambayeni muryar Dattijon mai cike da haiba.

E hakane. Yanzu ma nayi wanka inaso zan yi girki ne in dawo"

"Ashsha ba sai kin yi girki ba Sabuwa ga abinci nan na sa an girka mun tawo dashi. Kizo asibitin ki sameni kinji Sabuwa?"

Ya faɗa da sigar tausayi. Hawayen daya gama wanke fuskata na share.

To Baba Malam ganinan zuwa"

Sallama mu ka yi na datse wayar na ɗauki mayafina na saka tare da ɗaukar jakata na kulle ɗakina na fice a gidan. Masu jere har sun gama kamar ma ba'aiba.

A barandar da ake zama na tarar da Baba Malam da Malama ƙarama  ga abinci sun kawo shinkafa da miya, Maigogul yana zaune yana ci an mishi tsoro da plate. Labbai kuma tana kan zuba wa a plate, Rakiya tana ciki tare da Malama. Su Sadiya kuwa tunda ban gansu ba  su nasan

Edit with WPS Office

sun shiga gari

A tsanake na iso kan tabarmar na zauna ina ɗigar hawaye na gaishe da Baba Malam da Malama ƙarama. Maigogul kuwa ya samu waje sai zaro zance yake yi da abinda ya dace aji da wanda ma bai dace din ba duk faɗe yake yi hankalinshi kuma kwance. In yaso ma saiya cika abinci a baki zai shiga magana. Labari yake ba Baba Malam akan abinda ya faru dashi da su Gaza ɗazu.

Buɗar bakin Malam yace.

"Ai ɗan yau ka haifeshi ne baka haifi halinshi ba duk irinsu Babangidan kenan fa.

Sabuwa ashe kuma abinda ya faru kenan gidanku ya rushe baki sanar mun ba, da kin sanar mun ai da ba sai Maigogul sun dawo gidanki da zama ba tunda hakan ba dacewa bace, sannan a wajen mata sai ya iya zama abun faɗe. Yayi mun bayani akwai gidana ƙarami ne sosai mai ɗaki biyu falle_falle na basu su je su zauna zuwa lokacin da Allah zai hore ya gyara nashin. Sai dai ayi haƙuri gidan ƙaramine dama na haya ne anan cikin unguwarmu yake."

Ai sai na fashe da kuka mai gunji inata godiya. Ban sanar mishi bane sabida wani dalili mai ƙarfi.

"Ai Malam babu komai mun gode sosai. Ko can ɗinma nawan ai ɗaki biyu ne falle_falle a haka tsawon shekaru muke zaune, a haka duk akaita haifo su Labbai .  To Kasan yanayin rayuwar wallahi ko mun koma bamu da abinda zamu dafa, sannan katifunmu har yanzu basu bushe ba, amman wannan babu matsala zamu ari katifar Labbai Kaga Labbai nan jiya cikin dare mijin ya sakota wani nauyin ya ƙara hawa kaina. Ga yara maza kana dasu amman marasa imani ko sun samu kuɗin sun gwammace su yi shaye_shaye dashi. In suka nemo rigima suka gudu azo a naɗe ni ko uwar tasu"

Baba Malam yace.

"Assha Maigogul ai ba'a aibata yara haka. A bisu da adda'a kawai. Zan sa a aiko muku da masara da ƴar shinkafa da zaku yi amfani dashi na kwana biyu."

Illahirin kunya ce tasa wallahi na kasa tsaida kukan nawa ma. Malama ƙarama ita kanta gani nayi tana jinjina kanta tana ma Maigogul kallon da bai dace ba.

Hannu yasa a aljuhu ya ciro nera dubu goma tim ya miƙo mun. Hannuna da jikina na rawar baƙin ciki na amsa.

Allah ya saka da Alkhairi "

"Ameen Sabuwa ki dena kuka babu komai ba'a cewa haƙurin mutum ya ƙare. Wata rana sai labari. Naji labarin Babangida ya sake jajiɓo Aure  har Kawunshi ya shige mishi gaba. Sabuwa bansan komai a kai ba hatta gyatumarshi ɓoye mun tayi. Ki yi haquri ki daɗa akan wanda kike yi. In dai Babangida ne kina zaune zaki ji labari ya saketa"

Babu komai Baba Malam Allah ya sanya alkhairi."

Edit with WPS Office

"Ameen Sabuwa. Maigogul in ka shirya sai mu tafi in kai ka gidan in danƙa maka ɗan mabuɗin ai"

Maigogul dake ta danna shinkafa da miya shi da Labbai. Sai da ya cika shinkafa a baki fa sai yace.

"To Malam shinkafarce tayi mun daɗi taji mai  ga zaƙin nama cau ke Labbai ƙaro mun in yi maza in ci mu tafi"

Dariya Baba Malam kawai yayi amman fa da gani kasan na baƙin cikine zallah.  Shima Maigogul dariyar yake yi. Haka Labbai ta sake yi mishi tsoro da abincin ya share tas yasha ruwa.

"Lolo bari muje. Kya faɗa ma Rakiya duk yadda ake ciki. Malam muje"

Malam yana gaba Maigogul na biye dashi malum_malum ɗinshi nata cika da iska. Ya ɗau wanka wallahi a wankanshi zaku yi tunanin ya juyama sama da miliyoyi  baya, alhalin ko duba daya bai juya mata baya ba. Kuɗinshi kab a suturu masu tsada yake ƙararwa, dan hatta takalmi baya saka na dubu hamsin, ko agogonshi ai yafi ƙarfin dubu hamsin. Ga ƙamshi da kullum a cikin shi yake ga gogul da'iman a manne a fararen idanunshi.  Malama ƙarama na biye dasu a baya. Ni kuma ina bin diddigin takunsu Maigogul ne kaɗai baya tafiya irinta Dattijai masu kamala, tafe yake baya kallon gabanshi, shine kallon nan shine kallon can. Kai na girgiza na juyo da kaina ina sauke ajjiyar zuchiya.

"Gaskiya Lolo wallahi ki gode ma Allah kin yi sa,ar uban miji. Kiga a baya abubbuwan da suka faffaru, da irin turjiyar da Maigogul yayi musu. Amman gida sukutum fa ya bamu aro,  ji abinci lafiyayye miyar taji mai ga naman kaza. Wato Lolo kiyi haƙuri mijinki ɗan iska ne lamba ɗaya motsi ɗaya aure, motsi ɗaya saki."

Dariya kawai nayi mata nace.

Labbai kenan. Allah dai yasa mu cinye jarabawa"

"Lolo a cikin ni'ima fa kike, kici abinda kike so, ki kwana a waje mai kyau, ga yaranki na karatunsu har islamiyya, yaranki mata har ɗankunne daham garesu fa.

Lolo wato naga aya a gidan Bara'u, naga makircin uwar miji. Ke dai Allah ya sa mu a danshinku"

Miƙewa nayi nace

Bari in shiga wajen Rakiya"

"Abuncin fa Lolo? Kizo ki zauna kici"

Labbai bakina babu ɗanɗano, ke dai ina zuwa"

Anan na barta tana ta ƙara abinci tana mishi cin Allah tsine uwar mai ƙarya. Waya na samu Rakiya tana yi da ƙanwarta dake Aure a mahaifarsu su ƴan  Kano ne ƙaramar hukumar Bebeji,

Edit with WPS Office

iyayensu sun jima sosai da rasuwa, sai dai tarin dangi masu yawa. Amman Rakiya su huɗu Babansu ya haifa. Haruna shine babba, sai Bashar, Rakiya, Indo. Su dukka suna Bebeji Rakiya ce ƙaddara ta fito da'ita birni.

"Ke dai ki bari Indo rayuwarce sai haƙuri. Sakinnan fa ya zama ruwan dare, zaurawa nawa ne a gabana jiya mijin Labbai ya sakota. Hauwa duk yaranta zaurawane, kinga naki ai da sauƙi. Mu kammu fa ni da Hauwa bamu da bambanci da zawarawan dan Maigogul dai bana ɗaukarshi a miji."

Indo daga cikin wayar tace.

"Mu fa Yaya kinsan zawarci a ƙauye ba kamar a birni ba. Shi yasa nake son Tsaharen ta tawo wajenku ta zauna ko Allah zai sa ta samu miji"

Kai na girgiza kawai a raina nace.

Ta samu miji ko ta faɗa yawon banza dai"

Rakiya tace.

"To ta dai dakata tukunna tunda yanzu na sanar miki halin da muke ciki a gidan ƴarki Sabuwa muke zaune. In Maigogul ya gyara mana inda zamu zauna Indo zan kiraki sai ki turo tsaharen ko aikin wanke_wanke a nemar mata."

Indo tace.

"Shikenan Yaya kya gaishe da yaran duka. Inaima Sabuwa ya mai jiki sai anjima"

Rakiya ta kashe wayar tana tsaki. Malama na kalla jikin  nata da sauƙi idanunta biyu tana wasa da warwaron hannunta sai dai idanunta ya faɗa sosai. Murmushi tayi mun da taga inata ƙare mata kallo.

Kanta na shafa.

Malama yaya jikin naki?"

"Da sauƙi ummi. Ummi ina Aɗɗa'u?"

Dariya nayi mata kana nace.

Suna islamiyya shima yace in gaisheki da jiki. Harda su Mardiyya da Aminu ma. Rakiya kinci abincinne?"

Rakiya ta kalleni tace.

"Banci komai ba tun safe dana karya. Kun haɗu da uban mijinki da kishiyar shaiɗaniyar uwar mijinki? Sun zo sun duba mu har kishiyar uwar mijinki ta bani dubu biyu. Yanzu ƴan kayi nayi suka kirani akwai wani kayan Amarya da auren ya mutu ko zan siya. Can nake son zuwa in gano

Edit with WPS Office

kayan in sun yi in nemo dillalai su siya in fita da fitata"

Na tsani wannan sana'ar ta Kayi nayi da Rakiya ta nace ma sabida haɗari da cakwakiyar dake cikinta dan wataran in rikici ya ɓarko har Ofishin ƴan sanda sau nawa muka yo belin Rakiya, har kwana tasha yi a sel. Amman kuma bamu da ikon hanata wannan sana'ar ko dan abinda za'a samu a gagganɗa a rufa ma kai asiri.

Labarta mata batun gida da Baba Malam ya ara musu nayi. Da labarin auren da Babangida yayi."

"Wannan siriki yana sonki Lolo. Ai mun gode muma sai mun fi so mu bar gidanki dole ce ta sa muka je. To a gaskiya na fasa zuwa ganin kayan ma zan zauna a gama komai tukunna. Shi kuwa mijinki in bai kiyaye ba watarana sai ya auro mai kofato. Ke dai karma ki damu kan ki, ke kinga a gidan ubanki yadda ake zawarci ai tunda Allah yayi miki gyaɗar dogo to ki samama kan ki lafiya tayar da hankali da kishi bama naki bane. Bari in je nima inci abinci ke kuma ki zauna da Malama "

Har ta yi nisa ta dawo.

"Af Lolo wani likita wai Dr Khalid yazo har sau biyu nemanki bai same ki ba. Yace in kin dawo ki sameshi a ofishinshi. Harma dai nayi mishi koke akan rushewar gidanmu. Kinsan Allah Lolo dubu arba'in ya kirgo ya bani kai wannan yaro kwai kirki a hakanma yana ta bani hakuri wai iyakar ko kash ɗin da yake hannunshi kenan. Amman yace zai baki saƙo ki kawo mana"

Kika faɗa mishi gidanmu ya rushe?. Wai dan Allah Rakiya me yasa kuke haka ke da Maigogul ne?"

"Kinci ubanki Nuru ka ga mun ƴar iskar yarinya marar tausayi ƴar abu ta kazan.."

Yowa kaina tayi kamar zata dake ni nayi sauri na kare fuskata da hannayena dan ba abun mamaki bane Rakiya ta kile ni ba.

"In kara jin bakin ki"

Ta wuce fu ajjiyar zuchiya na sauke ni dai.

Zuwa yamma lis Maigogul ya zo ya ɗauki Rakiya da Labbai suka tafi can gidan ya rage sai ni kaɗai a asibiti ina zaune nayi tagumi ga shinkafa da miya a gabana na zuba zanci amma na kasa ci. Kawai naga anja kujera an zauna a gabana Khalid ne ashe. Kur ya zuba mun idanunshi ni kuma na ɗauki cokali na soma cinkusa abincin a bakina.

"Sabuwa yarinyarnan bata da Babane wai?"

Da sauri na juyo har cokali na faɗuwa a hannuna. Malama irin yarannanne masu wayo da yawa ai kuwa carab tace dashi

"Ina da Baba sunanshi Babangida ko Ummi?"

Edit with WPS Office

Idanuna na runtse ganin hankalina ya tashi sai Khalid ya basar ya shiga hira da Malama. Wayata dake gabana ya ɗauka ya daddanna lambarshi ya kira wayar tashi, ya ajjiye mun tawa  a gabana yana mun wani karuwan kallo har yana lashe laɓɓanshi.

Har ya ƙule ban dena kallon hanyar da ya bi ba, haka kamshinshi ma yana wajen daram.

"Ummi wanene wannan?"

Ba shiri na juyo ina murmushi na ɗauki lokalina saida na ciko da shinkafa kana nace.

Saurayin Sadiya ne. Yaya jikin naki?"

Tace dani da sauƙi, hira na shiga yi mata inayi inacin abincina har itama ta ƙara abincin. Sai ga waya ta shigo wayata da sabuwar lamba, ina ɗagawa naji yace.

"Sabuwa ta Khalid. Har abada bazan mance dake ba domin kece soyayyata ta farko. Da sonki zuchiyata ta buɗe. Na so muyi maganganu na yaushe gamo, amman na fahimci ƴarki na da tsananin wayo. Ki saka ma lambata suna, na biya kuɗin asibitin ƴata tunda ubanta bai damu da'ita ba. Gobe zasu baku sallama. In kin je gida kin nutsu zan kiraki. Ina sonki har abada. Kuma ki saka a ranki Khalid ya dawo gadan_gadan"

Kit ya kashe wayarshi. Illahirin mamaki yasa na dinga kallon wayar ina jin jinjina kaina.

Wata sabuwa in ji ɗan caca.

Mrs Bukhari

Mu tara gobe in Allah ya nuna mana

Bincike ya nuna sama da mutune   miliyon goma sha biyar ke shan muyagun ƙwayoyi a najeriya.

Hakan kuma ya jawo asarar rayuka, taɓarɓarewar tarbiyya. Ya haɓɓaka fitinu da manyan lefuka a arewacin najeriya dama ƙasar baki ɗaya.

Tun kafin zama ya gagaremu mu koma bacci da ido ɗaya a buɗe. Lokaci yayi da zamu haɗa ƙarfi da ƙarfe domin mu taimaka ma hukumar yaƙi da sha da fataucin miyagun ƙwayoyi.

Edit with WPS Office

Dan ganin mun kawar da wannan ta'asa dake shirin zame mana ruwan dare.

Shaye_shaye annobace ga al'umma.

Wannan saƙone daga hukumar yaki da sha da fataucin miyagun ƙwayoyi wato ( NDLEA)

IDAN KAYA YA GAJI...

GAMMO MA YA GAJI

BADIAT IBRAHIM MRS BUKHARI B4B GIDAN KAMSHI CE

LITTAFI NA FARKO

SHAFI NA TAKWAS

Ina manyan mata masu capacityn suke? ku fito lambarku ce ta fito.

Yar uwa turaren wuta kike nema nau'ika daban_daban masu musulmin ƙamshi da kama muhallu? Ba itacen banza masu sanya gida ƙauri da hayaki kamar an kunna taohuwar bespa ba.

Matso gasu MRS BUKHARI B4B GIDAN KAMSHI nazo miki da duk abinda kike buƙata na ƙamshi. Kama daga turarukan wuta irin na gidan alfarma. Zuwa humrori iri daban daban masu musulmin ƙamshi da riƙe jiki.

Bugu da ƙari muna da turarukan kaya, na fesawa dana turara kaya.

Muna da kulaccam nau'i daban daban masu gyara jiki da lausasa fata mata, ga kuma ƙamshi mai inganci.

Muna da turarukan tsugunno na musamman masu sirri Hajiyata

Muna da room freshener iri_iri

Muna da mopping mix masu kama waje.

Edit with WPS Office

Akwai turarukan kafet dana kujeru.

Sannan akwai box _ box  setika na Hajiyoyi masu ƙyallin goshi.

Muna da Amarya package.

Muna da uwargida package

Muna da maijego package

Muna bayar da sari ko a ƙasar waje kike, muna tura kaya

Saudiyya

Nijar

Ghana

Camaron

A duk ƙasar da kike kayanmu zai iso miki cikin aminci da yardar Allah.

Hajiya akwai Humrar matan aure wannan ta musamman ce.

Duk wani abu da kika sani na ƙamshi babu irin wanda bamu dashi a kamfaninmu.

Muna da turaruka designer na maza da mata wanda kamfaninmu ke bugawa Hajiya babu inda zaki je ki ci karo da mai irin ƙamshinki.

MRS BUKHARI B4B GIDAN KAMSHI TAZO MUKU DA DUK ABINDA KUKE SO NA KAMSHI HAJIYA.

KUNSAN KANURI MUNE KAMSHI DAMU AKE KOYI

SIYAN NAGARI MAIDA KUDI

MUNA MARABA DA MASU SIYAN ƊAYA KO SARI.

LAMBAR DA ZA'A SAMENI KAI TSAYE ITACE.

Wa.me/2348179523215

SAI NA JIKU

Edit with WPS Office

Wayar na riƙe a hannuna ina mamaki.

Gaga_gaga haka muka wayi gari sassafe aka turo almajiran gidansu Babangida da kayan karin kumallo lafiyayye wanda nasan dai  Baba malam ne yasa a aiko. Babu fa wanda yazo ya duba jikin malama babu wanda ya kirawoni a waya sai Alawiyya yarinyar malama ƙarama.

Misalin ƙarfe takwas da masu karbar aiki suka zo sai aka bamu sallama tare da magunguna da dokokin yadda zan kula da lafiyar Malama.

Ina kan tattare kayanmu sai ga Labbai Maigogul ya turo mini ita.

Tare muka tafi gida, a tsakar gida muka tarar da Babangida daga shi sai gajeren wando yana wankin mota. Yana yi yana mamin ɗin waƙar ɗan anace. Kamar bai ganmu ba haka yayi har yana watso ruwa yana samun mu.

"Abba mun dawo"

Cewar Malama uwar ƙukafacin ubanta kenan. Kallon yarinyar yayi yace.

"Zo uwata tafi ta kowa maza tawo"

Labbai ta saki hannun Malama tare da gaishe da Babangida.

"Uhm sannu ko?"

Shine amsar da ya ba Labbai ni kam ai harna isa bakin ƙofar ɗakina inata faman kiciniyar buɗe ƙofata.

Ina buɗewa na shiga da sallama na nemi waje na zauna ina murmushi. Labbai ta biyo bayana ta zauna tace.

"Kishiyarki tana cikin gidannan wai ita bata fitowa ne, ni kullum nazo har in gama wunina bana ganinta?"

Ajjiyar zuchiya na sauke kawai nace.

Bata fitowa sai da dalili mai ƙarfi. Yanzu dai Labbai ki sama mana abinda zamu ci bari in watsa ruwa inzo ki bani labarin sabon gidanku"

Labbai tayi kitchen ni kuma nayi uwarɗakina, na watsa ruwa na ɗan ji daɗin  jikina amman fa

Edit with WPS Office

zuchiyata babu daɗi. Doguwar rigar yadi mai sauƙi na saka na murza kwalli a idanuna ko mai ban shafa ba na fito. Na tarar da Naja da wannan matar data kawo ƴartannan.

Naja kune? Sannunku da zuwa"

Waje na samu na zauna muka gaggaisa wannan matar tace.

"Tun ranar da muka bar wajenki nake kwance ciwon ƙafa ya matsa mun. To ita kuma yarinya ta matsa sabida tana cikin damuwa sosai, shine dai yau nace bari mu rarrafo. Wata biyu miji baya shiga ɗakinta ga kishiya ta matsa mata. Da safennan wai kishiyar ta ɗebo wanki tace tayi mata bayan ta gama wankin asussubar fari shine tazo ta same ni"

Kai na girgiza ina mamakin sha'anin mata da mazan ma. Duk wani lalacewar mace ko da Namiji kuke gani a gaban matsalar akwai macce a bayanshi wanda kai tsaye zance ita ke rura wutar matsaltsalun. Ai mu dai mata akwaimu da shegiyar mugunta, gamu da son kai.

Allah ya kyauta. Komai yazo ƙarshe kuzo mu shiga daga ciki"

Na jasu zuwa ɗakin yara muka zazzauna, carbi na zaro a hannun ƙofa na saka wani turare a hannuna na murza tare da carbin kana na watsar a ƙasa nace.

Ɗauki ɗaya"

Hannuta naga har rawa yake yi ta ɗauki ɗaya. Sai ga Labbai da wayata a hannunta.

"Lolo ƴar shuwa na kiranki"

Da sauri na amshi wayar na ɗauka.

"Kawata ya jikin ƴar tawa? Kinga ban kiraku ba kaine ya ɗau zafi. Ke maganin mallaka nake so ki bani ta yadda zan baza mulkina a gidan, dan ya sanar dani matanshi basa jin magana. Yaushe zan aiko Umar ya zo ya karɓomun jibi zai shigo Maiduguri?"

Kawata in mallaka kike so kin samu kinsan Allah zaki baza tabarmarki kiyi tsiyarki. Gobe da yamma yazo ya karɓa miki zan kwana aiki akan baƙin buzu, zanyi duk yadda zaki samu mijinki a hannunki. Zuwa anjima mu yi magana ina da baƙin da nake ma aiki"

Wayar na kashe, Hafsat ta miƙi mun carbin na kama inda ta ɗauka. Na kirga daga sha biyu zuwa inda ta ɗauka. Kai na girgiza ina dariya kawai. Cabir na kuma yarwa nace.

Sake ɗauka maza"

Ta sake ɗauka ta miƙo mun na ƙirga.

"Baƙin farraƙu akayi mata ita da mijin. Kuma kishiyarta ce tayi mata. Aikin nata fa babbane Hajiya kun tanadi kuɗi dai ko? Aikin na buƙatar a zubar da jini ma'ana sai an yi yanka"

"Kuɗi babu matsala kamar nawa ake buƙata. Ɗan kunnenta nasa ta siyar dan a nema mata

Edit with WPS Office

magani. Daga baya inta samu kan mijin zata mayar da ɗankunnen a hankali tunda mijin nasu mai yi ne"

Kai na gyaɗa nace.

Ku ajjiye dubu talatin a soma mata aiki.

Ina zuwa"

Fita nayi da sauri falon duk ya kaure da ƙamshin jallof ɗin manja. Kitchen ɗin na shiga na ɗauki gora da Mardiyya ke tarawa tana yawan yin zoɓo na cika da ruwa, durowa na buɗe na ɗakko gora cike da ruwan rubutu na tsiyaya a ruwan na rufe na jijjiga"

"Wai Lolo ba zaki bar wannan sabgar ba har yanzu? Ina jiye miki ranar da mijinki, ko dangin mijinki, ko kishiyoyinki zasu san halin da kike ciki. Ki dai tuno da abinda ya faru da Maigogul a shekarun baya. Tunda har kika ga Maigogul duk san kudinshi ya rabu da harkar tsubbu, kema ya kamata ki bari tunda wanda ya koyar dake ma yayi saranda"

Labbai wallahi inaso in bari nima. Matanne suke sake jefani ruwa. Su kuma maza kullum a cikin cusguna mana suke. Zan dena watarana, kuma babu wanda zai san inayin wannan sabgar"

Ficewa nayi na koma ɗakin, na mika mata gorar nace.

"Ki dinga zuba mishi a cikin ruwan wankanshi, ko girki zaki yi ki tabbatar kin ɗiga wannan ruwan. Gobe da yamma ki dawo zan baki magunguna.

Naja rakiya kawai kika yi ne ko akwai wata matsalar ne"

"Babu matsala sabuwa. Nakosu nayi daman"

Nan mu kai sallama suka fita nima na koma kitchen wajen Labbai. Anan na samu Malama tana tsaye tana shan yogot, ga kuɗi a hannuna ni kuma cunbus.

"Lallai wannan sana'ar tana kai muku fa Lolo. Yanzu mata ukune suka baki duk wannan kuɗin?"

Idanu na ƙibta mata sabida Malama wayo gareta. Na dauke zancan da tambayarta sabon waje"

"Baki ga gidan ba mai kyau Lolo. Adama ta basu tabarma, ni kuma Maigogul yasa an ɗakko katifata an jefarma da Rakiya. Hauwa ma ƴaƴanta dai sun sai mata kafet katifarce dai Layuza tace zata kawo musu yau. To sai bin ɗaki kuma jiya maigogul a ɗakin Hauwa yake, su Sa'ada suka ɗungumo muka kwana tare. Wallahi Allah Lolo jiya ban bacci ba sabida tsabar matsi, duk wannan ɗan sanyi_sanyin da akeyi zafi jiya kamar zai kashemu. Ga tusa da Rakiya tai ta bango mana dama kin santa. A hakan ma Aisha da Qamriyya bafa su kwana a gidan ba. Shi yasa nake faɗa miki duk tsiya zaman gidannan rufin asirinkine. Kinsan fa in kika bar gidannan dole sai dai in rayuwar baya zaki koma ko? Yau fa ban ko karya ba sai ruwa nasha sabida banda kuɗi. Hauwa jiya ta ɗaura tukunya uban mijinki ya ba Maigogul shinkafa da garin dawa. Tayi tuwon harda dumame, data dumama ita da maigogul ne kaɗai suka cinye tuwon da safe dama haka

Edit with WPS Office

suka saba. Zawarawan gidan kuma duk sukai wanka suka fice, ni zama zanyi a gidan yinwa ta kashe ni? Dole na ce bari inzo wajenki a asibiti. Wallahi kwana ɗaya da nayi a gida tuni naji na gaji, cikin dare har zan kira Badaru in bashi haƙuri. Sai maƙocinmu gidan Malam Habu sai ga kira ya turo yara sun kirani. Ɗan tahalikinnan wai sona yake yi zai cikace ta huɗu dani da zaran na kammala idda in mishi magana. Wallahi aurenshi zan Lolo."

Zaro idanuna nayi waje nace.

Lallai Labbai zawarcinne har ya kaɗaki da kike tunanin auren malam Habu. Mutumin da matanshi har waje yake rakosu da gudu, madokine fa"

Labbai tace.

"Hmm wallahi Lolo na sani. Kinsan daga gidanmu ma muna jiyo dukan da yake ma matanshi. To wa zai zo ya aureka duk wanda yazo ƴan unguwa zasu kai gulma sai dai kiga bazawarinki ya gudu. Baga su Sa'ada nan shekara nawa a gida ba. Ni  kuma yawon ɓel_ɓel ɗinnan a halin yanzu bansan ma ta inda zan soma ba. Zan dai duba in gani"

Ato ki dai duba wallahi. In kika aureshi zaki ci ɗan karen duka wallahi"

Dariya muka yi duka. Jallof din shinkafar na dahuwa Labbai ta zuzzuba mana muka fito falo, ragowar muka juye a kula in su Mardiyya sun dawo sa ci.

Muna cin abincin muna kallon tashar arewa 24 a lokacin farkon tashar kenan. Suna kan yin shirin gari ya waye.

Malama maza ci abincinki ki sha magani Labbai ta miki wanka ki kwanta ko?"

"Ummi zani makaranta nima?"

A_a tukunna dai sai jikinki ya warware tukunna"

Muna kan cin abincin muka jiyo sallamar Hamida. Ta shigo hannunta riƙe da leda baƙa jaririyarta na bayanta, yaronta  Usama na biye da'ita.

Ashe yau za'ayi ruwa harda ƙanƙara yau nice Hamida ta shigo ɗakina? Allah mai iko bari muji da wacce tazo, banza bata kai zobo kasuwa ilai kuwa. Sai cewa tayi.

"Maman Aminu yaya jikin na Malama ashe an sallamoku banma sani ba sai da naga Malama Babansu ya shigo da'ita ɓarayina."

Waje naga ta nema a kujera ta zauna suna gaisawa da Labbai, da ganin idanunta taci kuka ta ƙoshi.

Jikin Malama da sauƙi. Labbai dan Allah tunda kin gama cin abincin ki ma Malama wanka ta saka kayan sanyi naga garin ya rufe sosai ga sanyi"

Edit with WPS Office

"Maman Aminu dama nazo ne mu yi wata magana muhimmiya dake dan Allah in babu damuwa"

Ta faɗa muryarta na rawa halamar karaya. Labbai ta miƙe tare da jan hannun Malama zuwa ɗakinsu. Hankalina na miƙa ma Hamida.

Ina saurarenki Hamida, ina fatan kuma lafiya?"

Sai kawai ta fashe mun da kuka. Ni wallahi dariya ma ta bani, kuma saina raina wayonta duk da dai yarinyace ƙarama sai iya shege fal cikinta. Ban hanata kuka ba, bance uffan ba har dai tayi shiru a karan_kankin_kanta.

"A kan batun auren Babansu Aminu ne dama na wannan matar da akace ita tayi mana akwati dan wulaƙanci."

Murmushi nayi kawai na gyara zamana.

Ina dai jinki Hamida. Me kike so to?"

"So nake mu haɗe kanmu mu hana Baban Aminu kwanciyar hankali dashi da bazawarar da zai kawo mana. Yace satin sama zata tare akwai abubbuwan da bata kammala ba"

Dariya ce ta kuɓuce mun. Sororo Hamida ta kalleni.

"Au ke dariya ma na baki? Jiya kwana yayi yana waya da'ita fa kuma a gabana, bata shigo gidan ba ma kenan ina ga ta shigo kuma. Ni wallahi da ba dan jego nake yi ba da gidanmu zan koma. Amman inaso ki bani haɗin kai mu haɗe mata kai ta yadda zaman gidannan bazai taɓa yi mata daɗi ba."

To naji abinda ya kawo ki Hamida. Amman ni in Babangida zai auro biyu a rana ɗaya ya haɗe mu mu koma mu huɗu wallahi ko a jikina. Shi yaji zai iya tunda ni dai ba a kaina zasu zauna ba. Kema ina shawartarki in dai kina so ki tsugunna akan ƴaƴanki to kibi a hankali. Kafin zuwanki wasu sun tafi, sai da aka fitar da mace kika samu ɗaki."

Shiru tayi kawai ranta na lura ba ƙaramin ɓaci yayi ba. Tashi tayi tsaye ta ajjiye mun ledar naman suna da yajin daddawa ta ja yaronta suka fice. Tana fita aka ɓalle da ruwa kamar da bakin ƙwarya. Ledar data ajjiye mun na buɗe naman sunane tsoka biyu sai ƙashi guda uku raƙau_raƙau da ɗan ƙullin yajin daddawa haka. Miƙewa nayi na koma ɗakina na rurrufe tagogi, na fito na shiga ɗakin Babangida na rurrufe tagogin ɗakin. Daga haka na shiga gyaran ɗakin, na wanke banɗakin na sauya zanin gado, na yi goge_gogen komai da komai. Burner na kunna na turaren wuta kafin na fito.

A bakin gadona na zauna na jawo akwatin faɗar kishiya da akayi mana na buɗe. Atampopine datsa_datsa guda uku, leshi ɗaya, sai shadda ɗaya. Takalmi da jaka ɗaya, sai kayan kwalliya, ɗankunne da sarka ɗaya, ɗan diras da bireziya ɗaɗɗaya, sai mai da turare. Ina cikin duba kayan Labbai suka shigo ita da Malama ta saka mata  kayan sanyi sosai.

Edit with WPS Office

Magungunan tasha kuwa?"

"Tasha harda kuka"

Dariya nayi mata.

Ƴar baɗo bata son magani dama. Hau gado ki kwanta abinki sanyi"

"Duk wannan kayan na faɗar kishiyarne? Lallai wannan kishiya ta bambanta da sauran kishiyoyin da suka shuɗe. Naji fa duk maganar da kishiyarki ta kawo miki. Kuma kinyi mun daidai. Ni gani nake yi so take ta ɓalle miki auren shine ta bullo miki da wannan dabarar. Jikina a mace nace.

Allah ya kyauta kawai Labbai. Ai Babangida yayi nisa baya jin kira"

Hirarmu mu kai ta yi ta zumunci, ruwannan akaita zuga shi bashi ya tsaya ba sai wajajen la'asar. A hakanma garin sake dunɗewa yayi kamar dare wani irin baƙin hadari ne yake sake haɗuwa. A haka yaran suka dawo suka tarar mun dawo nan suka shiga murnar ganinmu. Ana yin sallar la'asar ruwannan ya sake ɓallewa da wani irin mugun ƙarfi ko ina ya ɗauki sanyi. Yaran sai nace su je su kwanta kawai yau dai babu batun zuwa islamiyya kenan. Kitchen na shiga na soma hidimar girkin dare. Tuwon semo na tuƙa miyar Egusi mai naman rago, sai ruwan bunu dana dafa mai citta na cika filas. Bani na gama ba sai bayan magriba, a lokacin ruwan ya soma sassautawa babu laifi. Mardiyya nasa ta cika gawayi a kaso ta kunna da lede, duk da ko'ina a rufe yake ruf hakan bai hana sanyi surnanowa ba, duk dani da yaran mun yi wanka mun saka suwaito. Cikin ƙanƙanin lokaci gaushin ya ruru rijis na ɗakko kasko na saka a tsakiyar ɗakin na ɗauki kajiji biyu na watsa akai. Sai na zuba ma kowa abincinshi, Malama kam sai a baki na bata dan jikin ya ɗan tashi mata kunsan ciwone da baya shiri da sanyi sam.

"Lolo ni Kam Allah _Allah nake ruwannan ya ɗauke in gudu kar mijinki yazo ya rutsani a gidannan yayi wata fassarar daban."

Ina cikin zurfin tunanine na juyo maganar Labbai. Juyowa nayi na kalleta, na sake kallon su Mardiyya da suka kunna tocila suna aikinsu na makaranta, suna yi suna dariyarsu nace.

In dai Babangida ne ba lallai ya dawo gidan bama ruwa akeyi sosai. Ki jira yara su gama karatu sai kije ki kwana a ɗakinsu gobe kya koma, nima goben nake son zuwa in ga gidan."

Ai kuwa hakan akayi, su Mardiyya na gama aikin makaranta su kai Sallah sai suka tafi ɗakinsu.

Ni dai ina zaune an barni da kirgen agogo.

Babangida ba shi ya shigo ba sai ɗayan dare. Lema na ɗauka naje na buɗe mishi get ya shigo na rufe. Da gudu ya fito a mota yayi asalin turakarshi a guje dan har izuwa wannan lokacin ruwa ake zugawa.

Ɗaki na shiga na jera komai a basket na ɗauka na sake fitowa zuwa turaka. Na tura ƙofar baya ciki sai halamar wanka a banɗaki. Basket ɗin na ajjiye na koma dan ɗakko filas ɗin tea in kuma

Edit with WPS Office

taso Labbai ta rufe ƙofa dan duk ranar da Babangida ya wuce turakarshi yana nufin acan zai kwana wacce take da girki kuma sai taje ta sameshi. Ɗaki na shiga sake kayan jikina zuwa rigar bacci mai kauri data dace da yanayin, na sanya hula a kaina dan rabona da kitso ya daɗe ni da duk sati ada sai na sabunta kitsona. Ammam a yanzu damuwa da matsalolin gidan Babangida sawa yake in mance da kaina.

Labbai na taso ta rufe ƙofa ni kuma na fito na nufi ɓarayin Babangida. Ina murɗa ƙofar na jita a garƙame ga muryarshi raɗau ina jiyowa yana soyewa a waya sai ragargazo kalaman ƙauna yake yi. A hankali na shiga buga kofar funfurunfus Babangida yaki buɗe ƙofar sai dariya yake yi a waya. Hawayen daya zubo a kumatuna na share na bar ƙofar turakar jikina a sanyaye. Kamar ance in kalli ɓarayin Hamida sai kuwa na ganta ta taga tana leƙena. Murmusawa kawai nayi na wuce nawa ɓarayin na bubbuga ƙofa Labbai tazo ta buɗe mun tana tambayata ko lafiya.

Babu damuwa kiyi haƙuri inata tasoki, je kiyi kwanciyarki sai da safe mayi magana"

Ɗakina na wuce na zauna a tsakiyar gado ina tambayar kaina

Shin a haka zan ci gaba da rayuwar ƙasƙanci a cikin gidannan, wai meye ma amfaninane a cikin gidan in aka ɗauke kula da yarana da nake yi? Anya kuwa zan iya ci gaba da irin wannan rayuwar ace miji sai ya jingineni na fin watanni sai sanda yaga damar yin mu'amular Aure da kai yake yi. Gashi duk wani wulaƙanci da cin kashinshi a kaina yake sauka.

Yaya makomar yarana zata kasance in na kasa jure wannan uƙubar?"

Wata zuchiyar tace.

"Ki sadaukar da dukkan rayuwarki domin walwala da farin cikin yaranki. Kar ki sake kiyi fatali da rayuwarsu kamar yadda iyayenki suka yi fatali da taku rayuwar.

Wata zuchiyar tace.

"Ki kashe kan ki a banza. In ƙasa ta rufe miki idanu ai Shikenan komai ya ƙare."

Kwanciya nayi ina kuka mai gunji da haka bacci ya ɗaukeni har izuwa asuba.

Ina fitowa falo naga yarana suna Sallah sai naji zuchiyata ta yi wasai_wasai.

Haka dai harna sallamesu suka tafi makaranta, abincin kari kuwa ban yi da Babangida ba tun asuba ya ja motarshi ya bar gidan kuma dama banyi niyyar yo dashi ba. Kwano na samu na zuba ma Labbai doya da kwan da muka soya nace ta kaima Rakiya in na tambaya aka barni zasu ganni.

Da yamma bayan yara sun dawo daga makaranta har sun shirya sun tafi islamiyya sai ga Umar ƙanin ƴar shuwa, sako na bashi ya tafi. Hafsatu ma tazo da yamma lis lokacin ina hidimar kaɗa miyar kuka ta karɓi nata maganin.

Gaga_gaga. Haka al'amura suka ci gaba da cakuɗawa ni dai har na fice a girki Babangida bai

Edit with WPS Office

bani damar keɓewa dani ba, yana dai amshe abincinshi yaci ya ƙoshi.

Ranar da Hamida ta amshi girki goma dai_dai motar Babangida ta shigo gidan dake ƴar gaban goshi ce ita ƴan gatan miji waɗanda miji baya son ganinsu da wata damuwar.

Washegari har gaban mota naje na samu Babangida yana ba Hamida kuɗi, wai kuɗin dinki.

Inaso zanje gidane dama dan Allah"

"Kije ai bazan hana ki zuwa gida ba. Sai naji labarin ashe Baba Malam ne ya ba su Rakiya aron gida suka dawo layinmu? Hmm Allah ya tseratar da samarin layin da lalacewa dan naga Gaza ya soma yawo da kare a unguwa" kallon Hamida nayi sai naga dariya take yi mun.

Nera ɗari biyar kuɗin mota cib ya miƙo mun nasa hannu na karɓa na barsu a inda na same su.

A gurguje na shirya na fice a gidan dan na sanar ma da Mardiyya su wuto gida su sameni sai suci abinci su saka kayan islamiyya su wuce tunda yanzu duk layi ɗaya muke. Abinci na girka cikin kula jallof dib manja da bushasshen kifi nayi na fice abuna zuwa gida.

Da sallama na shiga na tarar gidan a hautsine Rakiya da Hauwa suna faɗansu da suka saba. Maigogul yana kwance akan tabarma yana waya hankalinshi kwance ko a jikinshi fa. Babu kowa a gidan sai Uzairu zuchiyata dake zaune yana goge kaushin ƙafarshi. Ga dai karnuka kusan guda biyar a cikin wani ƙaton keji ashe akan karnukan ake wannan dambarwa. Maigogul yana ganin shigowata yayi sauri ya amshe kular hannuna. Hauwa ta harareni daga ni har maigogul ɗin.

"Ni dai na faɗa miki wallahi baku isa dan surukinnine ya ara mana gida ba kice zaki mana mulkin mallaka ba. Waɗannan karnukan ina amfaninsu sun hana mu sukuni, jiya babu wanda ya runtsa a gidannan sabida haushin su." Rakiya tace.

"Baƙin cikin Lolo shine zai yi sanadinki dai Hauwa kinji kunya hassada da ƴar cikin ki, yarinyar da ke kika yanke mata cibi. Lolo ta zame miki gagaragasarki, tafi ƙarfinki da ke da kaf zawarawan ɗakinki. Ta riga ta zama tauraruwa a cikin gidannan kinsan kab gidan itace Allah ya duba ya bata gidan hutu da jin daɗi, ya bata miji ɗan gidan malamai"

Dariya Hauwa tayi harda shewa ta buga cinyarta tace.

"Waye baisan waye Babangida kacigari ba a kaf faɗin garinnan? Yaudarar kanku kuke yi da bamu san meye silar auren bane da saiki faɗi haka Rakiya. Amman ai kowa ya san a ina aka haɗu yaya ma tafiyar ta faro. Ai ko makawo ya shafa fuskar Lolo yasan a cikin tashin hankali take.

Ni dai zamana nayi a kusa da Maigogul muka ci gaba da kallonsu, Uzairu Zuchiyata kuwa sai dariya yake yi. Ya gama kwaskwarimarshi ya shige ɗaki ya sako kaya. Ya ɗau gaye zaku rantse da Allah irin yaran masu dashi ɗinnanne shi yasa ya zama ƙwararre wajen yaudarar zukatan mata.

Edit with WPS Office

Uzairu zuchiyata irin wannan wanka haka sai ina?"

Na tambayeshi. Yana dariya da ƙwanbo yace.

"Kinsan mun dawo sabuwar unguwa shine nake ɗan zagayawa muna ƙarema ƴan matan layin kallo. Kinsan ni mayen mata ne"

Dariya mu ka yi dukkanmu, Maigogul yace.

"Haka dai ka iya. Ajjihu babu sisi babu aikin fari balle na baƙi sai jar yaudara kasa a gaba"

Dariya ya saka kawai ya girgiza kai yayi ficewarshi yana takawa ɗaiɗai, ƙafarshi ya lailayeta da mai kaushin ya kwanta kamar ma babu.

Gidanmu gidan daɗi, gidan takaici.

Su Rakiya sai da suka yi ya ishesu sanan ta same mu akan tabarmar ta zauna.

"Lolo ya jikin Malama?"

Jiki da sauƙi Rakiya. Dan Allah ki dena kula Hauwa kuna wannan hayaniyar har maƙota su gane ku daga dawowarku."

"Kinsan Hauwa sai da wuta. Shi yasa na silleta soso da sabulu tunda ba sirikanta bane suka ara mana gidan ba. Tana rigar alfarmata bata isa ta yi mun na ƙyaleta ba."

"Haka kika iya. Dallah ɗakko kwano ki zuba mun abinci inci dama yinwa nake ji dumamen da naci bai isheni ba"

Cewar Maigogul kenan.

"Yaushe zai isheka ka kashe zuchiyarka. Ko ka samu kuɗin baka iya tsinana mana komai sai siyan sutura. Ai kaine silar duk abinda ya faru, da ka kula da hakkin dake wuyan ka yaushe rayuwar yaranka zata lalace haka. Gida sai kace gidan magajiyar karuwai yara duk babu wani nagari wannan masifar dame tayi kama ne haba ni wallahi na gaji ka sake ni in huta. Wallahi ka sake ni me kuɗi kana ji kana gani zan aura, ƙila ma daga cikin iyayen gidanka"

To nan faɗa ya dawo tsakanin Rakiya da Maigogul dole haka ya fice a gidan ya barmu yana zage_zage manya_manya kamar ba babba ba. Rakiya fa bata kyaleshi ba har zaure ta bishi tana mishi ele. Ni wallahi shi yasa bana son zuwa ganin gida ma sam.

Da ɗaya da ɗaya yaran da manyan gidan suka dawo. Da akayi azahar saina shirya na ɗauki Aisha nace taimun rakiya gidansu Babangida.

Makaranta muka soma shiga Malam kuwa yana cikin ofishinshi a zaune. Su Sa'a da su Alawiyya suna aji suna bama ɗalibai matan aure karatu.

Ofishin Baba Malam muka shiga da sallama.

Edit with WPS Office

MRS BUKHARI B4B GIDAN KAMSHI

Mu tara gobe in Allah ya kaimu

Bincike ya nuna sama da mutune   miliyon goma sha biyar ke shan muyagun ƙwayoyi a najeriya.

Hakan kuma ya jawo asarar rayuka, taɓarɓarewar tarbiyya. Ya haɓɓaka fitinu da manyan lefuka a arewacin najeriya dama ƙasar baki ɗaya.

Tun kafin zama ya gagaremu mu koma bacci da ido ɗaya a buɗe. Lokaci yayi da zamu haɗa ƙarfi da ƙarfe domin mu taimaka ma hukumar yaƙi da sha da fataucin miyagun ƙwayoyi.

Dan ganin mun kawar da wannan ta'asa dake shirin zame mana ruwan dare.

Shaye_shaye annobace ga al'umma.

Wannan saƙone daga hukumar yaƙi da sha da fataucin miyagun ƙwayoyi wato ( NDLEA)

https://chat.whatsapp.com/IUKFTeuI76p2VaAvQ5nk0U

IDAN KAYA YA GAJI....

GAMMO MA YA GAJI

BADIAT IBRAHIM MRS BUKHARI B4B GIDAN KAMSHI

LITTAFI NA FARKO

SHAFI NA TARA:.

Edit with WPS Office

Ina manyan mata masu capacityn  suke?  ku fito lambarku ce ta fito.

Yar uwa turaren wuta kike nema nau'ika daban_daban masu musulmin ƙamshi da kama muhallu? Ba itacen banza masu sanya gida ƙauri da hayaki kamar an kunna taohuwar bespa ba.

Matso gasu MRS  BUKHARI B4B GIDAN KAMSHI nazo miki da duk abinda kike buƙata na ƙamshi. Kama daga turarukan wuta irin na gidan alfarma. Zuwa humrori iri daban daban masu musulmin ƙamshi da riƙe jiki.

Bugu da ƙari muna da turarukan kaya, na fesawa dana turara kaya.

Muna da kulaccam nau'i daban daban masu gyara jiki da lausasa  fata mata, ga kuma ƙamshi mai inganci.

Muna da turarukan tsugunno na musamman masu sirri Hajiyata

Muna da room freshener iri_iri

Muna da mopping mix masu kama waje.

Akwai turarukan kafet dana kujeru.

Sannan akwai box _ box  setika na Hajiyoyi masu ƙyallin goshi.

Muna da Amarya package.

Muna da uwargida package

Muna da maijego package

Muna bayar da sari ko a ƙasar waje kike, muna tura kaya

Saudiyya

Nijar

Ghana

Camaron

A duk ƙasar da kike kayanmu zai iso miki cikin aminci da yardar Allah.

Hajiya akwai Humrar matan aure wannan ta musamman ce.

Edit with WPS Office

Duk wani abu da kika sani na ƙamshi babu irin wanda bamu dashi a kamfaninmu.

Muna da turaruka designer na maza da mata wanda kamfaninmu ke bugawa Hajiya babu inda zaki je ki ci karo da mai irin ƙamshinki.

MRS BUKHARI B4B GIDAN KAMSHI TAZO MUKU DA DUK ABINDA KUKE SO NA KAMSHI HAJIYA.

KUNSAN KANURI MUNE KAMSHI DAMU AKE KOYI

SIYAN NAGARI MAIDA KUDI

MUNA MARABA DA MASU SIYAN ƊAYA KO SARI.

LAMBAR DA ZA'A SAMENI KAI TSAYE ITACE.

Wa.me/2348179523215

SAI NA JIKU

Yana zaune a kujera ga tarin littattafai a gabanshi, da wata mata da yake magana da'ita.

Har ƙasa na tsugunna na gaisheshi.

Ya amsani da fara'arshi. Aisha kuwa a tsaye riƙe da ƙugu ta gaisheshi ga cingam tana taunawa kamar tsohuwar karuwa.

"To iyakar maganata kenan baiwar Allah. Kije ki yi tunani da kyau kafin kice zaki shigar da ƙara kotu. Ko babu komai ai kun haifi yara kuma ana gudun abinda za'a shafa ma  Haula baƙin fenti. Ki koma aji nayi baƙuwa matar Babangida ce tazo"

Wannan matar tace.

"Shikenan Malam Nagode. Laa dama wannan ce matar Mu'allim? Allah sarki"

Edit with WPS Office

Gaisawa muka yi da'ita.

Ta yi mishi sallama ta fita. Ya nuna mun kujera yace.

"Sabuwa zauna naji daɗin zuwanki. Ita ƙanwar taki ta jira a waje"

Fuu Aisha ta fice cikin ƙunƙuni na tsiwa. Kai kawai ya girgiza yace.

"Yaya jikin Malama ta warware ko? Sannan ana kulawa da'ita kinga akwai sanyi sosai a gari kasancewar ruwa da ake ta samu. Kuma lalurarta bata son sanyi ko wasan ruwa."

Jikinta da sauki yau tabi ƴan uwan zuwa makaranta ma. Ai tana ta son zuwa islamiyya ma"

Dariya yayi irin ta dattijai yace.

"Malama ai akwaita da ƙoƙari babu laifi. Mardiyya dai kina saka mata idanu yadda ya kamata ko Sabuwa? Ke kinsan komai dole tana buƙatar kulawa ta musamman. Macace kuma kinsan halin uban nata, shi sharri ɗan aike ne a kullum ina faɗa muku a kula ayi adda'a sosai"

A kunyace nace.

Ina kulawa sosai Baba Malam."

"To_to Shikenan. Sai batun bikin ita yarinyar da Babangida ya auro, an faɗa miki za'ayi taron biki na famili ai ko? Dan naga Malama Babba ta aika can gidan naku da angon bikin, wajen abokiyar zaman naki an baki naki dai ko?"

Mamakine ya cika ni. Au wannan karon har wani taro za'ayine na musamman harda anko, sai kace yau Babangida ya saba auro mata? Lallai wannan Amarya komai nata na musamman ne"

A_a banma san da bikin ba gaskiya. Amman ƙila ko inna koma Hamida zata sanar mun, ko shi Babangidan ban dai sani ba"

Dariya yayi ya miƙe tsaye.

"Ki jirani ina zuwa"

Yasa kai ya fita, a lokacin ne na samu zarafin zubar da hawayen da in ya zubo nake ɗan samun sauƙin cunkushewar zuchiya."

Ina zaune ina tunanin rayuwa da irin yadda rayuwa take tamaule dani, da yadda duniya taimun atishawar tsaki. Nasan kuna da tarin tambayoyi amman dai mu je a hankali zaku ji komai.

Ina cikin rabe ɗayan biyu Baba Malam ya shigo da leda a hannunshi ya miƙo mun ledar. Yasa hannu a ajjihu ya zaro nera dubu goma ya ajjiye mun.

"Ankon bikin kenan. Kuɗin kuma ki yi ɗinki dashi. Ranar asabar zasu yi taron bikin a gidan ƙanina Manga ki shirya kamar yadda Hamida zata je kema ayi dake. amarya lahadi zata tare

Edit with WPS Office

Sannan nasihar da zan miki shine ki ƙara haƙuri akan wanda kike yi Sabuwa. Da sannu Babangida zai yi dana sanin duk abinda yake aikatawa. Domin lefinshi yafi yawa a kan duk abinda suke hange shi da mahaifiyarshi. Ke da Babangida babu rabuwa ƙaddararku a manne take data juna. Ke dai ƴaƴanki mata ki kula dasu sosai. Tashi kije ki gaishe da iyayenki mata, shi mahaifinki muna haɗuwa dashi a masallaci"

Ina hawaye na fita a ofishin Baba Malam. Na tadda Aisha a zaune a baranda tana waye_waye da ƴan iskan samari. Ganina ne yasa ta miƙe muka fito. Kuɗin da Baba Malam ya bani na cusa a jakata

Aisha ungo kayannan maza kaima Rakiya ta ajjiye mun. Sai ki dawo mu shiga cikin gidan su Babangida "

Ledar ta fisga tana wata ƴar iskar dariya a waya.

Sabida damuwa  bansan A'isha har taje ta dawo ba, sai da ta zungureni na yi firgigit na juyo.

Kin dawo ne?"

"Ke ko meye yake damunki Lolo. Har naje na dawo baki ma sani ba ikon Allah. Na shiga gida na tarar Gaza ya saki karnuka a tsakar gida yana musu wanka. Su Rakiya duk suna ɗaki dasu Sa'ada karnukan mafaɗatane nima yowa su kai kaina saida yayi musu magana suka koma"

Baki na taɓe na sauke wawuyar ajjiyar zuchiya muka shiga barandar almajiran gidansu Babangida, muka ratsa zauren gidan allunan almajirai da buhun kayansu yafi hamsin. Take zuchiyata ta shiga tsalle a cikin jikina tunanina yana hautsine yayi gaba yayi baya. Inna tuno zuwanmu gidannan na farko ni da Maigogul, da haɗuwata da dangin Babangida na farko. Zuchiyata tana kwana biyu a hautsine bata dawo daidai ba, sabida rikice_rikicen da suka afku da yawa suke.

A hankali jiki a mace na wuce zaure na farko, muka shige zaure na biyu har dai muka ƙarasa tsakar gidan su Babangida. Almajiran gidan, daga masu shara sai masu wanke_wanke, da masu wanki. Tsakar gidan babu kowa a ciki ko wacce tana ɗakinta mazan gidan dake manya ne ko wanne ya fita nema. Ɗakin malama ƙarama muka soma shiga tunda shine na farko, kullum ma shi muke soma shiga.

Tana tsaye a gaban kwabarta tana gyara littattafai ta amsa sallamarmu. Ɗakin tsab dashi gwanin kyau.

"Sabuwa kece a tafe?"

Wallahi nice. Ina wuni?"

Ta amsa babu yabo babu fallasa tace.

"Lafiya lau ya jikin Malama?"

Edit with WPS Office

Na ɗan ƙaƙaro murmushin dole.

Ta warware tana makaranta"

"Ashe kuma iyayenki sun dawo layinnan Malam ya basu gida kafin su gyara nasu. Ince dai an soma gyaran can asalin gidan naku ko?"

Gabana ya faɗi ras. Aisha na kalla naga tana taɓe baki, na dawo da kallona wajen malama ƙarama nce.

Tukunna dai, amman zasu gyara ba da jimawa ba"

"Allah yasa. Dan nan ɗin haya akeyi ana karɓar kuɗin. Ni dama hayar suka biya kinga sai su zauna a tsanake ko na shekara biyu ne sai su biya"

Ni dai na kasa cewa uffan yawu ma da kyar na haɗiye balle har in iya sarrafa harshe wajen kalami. Malama ƙarama ma  ta yaɓo mun magana balle malama Babba da kullum dama a cikin yaɓa mun magana ita take.

Da ƙyar guiyoyina suka iya ɗaukar gangar jikina muka fito. Aisha dai muna fitowa tayi hanyar waje fuu ta barni ƙafafuna na rawa na kasa saka takalmi. Tsugunnawa nayi na yayimi takalman na shige ɓangaren Malama Babba shima ƙal dashi. Tana bakin ƙofarta a zaune tana tsince alkama, ga alaiyawo da wuka a kan babban tiran silver. Muna haɗa idanu ta zabga mini uwar harara harda sakar tsaki.

"Aikin banza ni bansan abinda yake kawo ki gidannan ba, tunda Malam shi ke ɗaure miki gindi ai sai ku dinga haɗuwa kuna gaisawa a waje dashi ba sai kin shigo ba. Kab gidannan babu mai ƙaunar haɗa idanu dake sai shi Malam ɗin da yake ganin ci  gaba da riƙe aurenki shine abinda yake dai_ dai. Ko da yake na manta ballagazin ubanki ya dawo layinnan kin ɗaura ɗambar shigowa layin kenan. Jeki abinki nagode ba sai kin karaso ba."

Kunsan ance iyaye iyayene, duk laifin da suke aikatawa ba zaka so a aibantasu a gaban idanunka ba, tunda ba kai ka zaɓa ma kan ka su ba. Kuma Maigogul ya cancanci a kirashi da abinda yafi ballagazi ma, amman shi cin fuska babu daɗi. Kuma wallahi ina mutuwar son shi a yadda yaken. Shima ya fifitani cikin Yaƴanshi.

Da bi bango na fito a barayin. Ina zuwa zaure ganina ya ɗauke ɗib nake jin wani irin mugun jiri da wani irin ciwon kai. Yib na faɗi cikin allunan dake zauren.

Ni dai farkawa nayi na ganni a kan katifa Maigogul yana shafa mun ruwan rubutu, gasu Adama, su Ramatu, da su Labbai, harda Uzairu Zuchiyata sun yi mun rumfa duk ƴan ɗakinmu.

"Lolo kin farka oh Allah mun gode maka."

Cewar Rakiya kenan da take tsaye da mafifici a hannunta ta nai mun fifita.

Meya faru dani Maigogul?"

Edit with WPS Office

Kafin ya bani amsa na tuno da abinda yai mun silar shiga wannan halin dana shiga. Wannan shine karo na huɗu ina faɗawa irin wannan hayanin.

"O_o_o_o bamu sani ba. Almajirin gidan su Babangida aka turo wai mu zo mu ɗauki ƴarmu ta sume a zaure. Lolo a tsakiyar alluna naje na sameki jikinki duk ya kuje, ni da Uzairu Zuchiyata ne muka yi kai da ƙafa muka kawo ki gida. Kinfi awa biyar a wannan halin da kike ciki. Har su Aɗɗa'u sun dawo boko sun wuce islamiyya. Da dai naga abin yaƙi ci yaƙi cinyewa shine nayi tattaki naje na sanar ma uban mijinki halin da kike ciki. Kinga rubutu ya bani yace in kawo miki. In ta kama na asibiti ma muje dai"

Maigogul ne yake wannan bayanin. Idanuna a lumshe inata hawaye. Rahma tace.

"Sannu Lolo dama baki da lafiya ne kika tawo gida, ko wani abunne ya faru dake a gidansu Babangidan dan nasan uwarshi ba ƙaramar marar mutunci bace"

Adama ta cabke da cewa.

"Ke baki ji ke A'isha tace ba? Tun a ɗakin kishiyar uwar aka soma zubo mana habaici. Ni naga ba mu muka roƙi Malam ya bamu gidannan ba. In abun zai zama rikici ai sai su tashi a gidan kawai"

Hauwa ce ta yi shewa daga tsakar gida tace.

"Ayi dai mu gani in tusa zata hura wuta. Gida ya cika da taron yara marasa zuchiyar da ko haya ba zasu iya kamama iyayensu ba. Ai gori yanzu aka soma saima anzo an yi fatali da kayanmu waje tukunna"

Maigogul ya fita jikinshi har yana rawa suka shiga hautsinawa.

Rakiya zan nema muku ko gidan hayane dan Allah ku..."

"Kul kika ƙarashe dan ubanki. Ya Allah ya rufa mana asiri ku zaku tona mana asiri. A wanne irin gidan haya zamu zauna ba tare da an koremu ba. Ga Adama ga Ramatu ga Uzairu zuchiyata sune manya zasu tuna lokacin da muke yawon haya kafin ubanku ya sai mana wancan ruɓaɓɓen gidan irin korarmu da aka dingayi a unguwa_ unguwa Wai zamu lalata musu tarbiyyar yara ke abubbuwa iri_iri. Ai baƙin ciki sai dai ya kashe surukarki babu inda zamu je. Dama kuɗi kuka haɗa kuka tayar mana da gini ko na lakanne a mayar"

Ni dai ina kwance jiri ma nake yi a kwancen. Abincin dana kawo shi Labbai ta zubo ta miƙo mun.

Ba Uzairu Zuchiyata bazan iya sa komai a bakina ba. Kaina kamar zai tarwatse. Maigogul yana tsakar gida suna faɗi in faɗe da Hauwa, itama muguwar mafaɗaciyace ni banma taɓa ganin Hauwa mara faɗa ba. Rahma tace.

"Lolo wallahi ke daɗine yayi miki yawa. Ke nifa in nice a gidan aure irin naki ko me za'ayi mun bazan ma damu ba. Wallahi da yau zan fito in auru da tuni na baro gidan auren na sauya miji ko zan dinga samun abinci sau uku. Sai da mu ka ci uban dambe dashi fa akan nera ɗari biyu ta

Edit with WPS Office

daya sa hannu ya sata. Shi bai bani ba ban isa in yi ajjiya ba sai ya sace. Yara kowacce ta shiga yawon banza dan su samu abinda zasu ci ba arabi babu bokon kamar mu dai, ke Allah ya rufa miki asiri jibi makarantar da yaranki suke zuwa fa, ga islamiyya, Mardiyya har ta kusan sauke Qur'ani sukutum"

Adama tace"

"Nima hakan fa take. Ko jiya sai da mu kai zagi in zaga ni da Shehulle wan Babansu Fatima . Ba dama mu yi shanya sai yazo ya zuge mana ya baza tashi shanyar dan iskanci. Ni kuma jiya yana gama bazawa na zo na zubar dasu duk a kwata shine fa faɗa wallahi har waje ido na kusan ƙwaƙwule mishi ma. Duk fa a takure muke kece kaɗai kikai dace. Dan tsangwamar dangin miji sai me. Ba kya toshe kunnenki wanda ya nemi matsa miki ki nuna mishi ke tsohuwar ƴar daba ce. Oh Lolo wanne irin rashin mutunci da neman magana ne baki yi ba. Dama fa a gidannan daga Gaza, sai magazin, sai Uzairu zuchiyata sai ke a jawo magana. Tunda mu sanda mu kai zamaninmu ba'a magana.

Aisha tace.

"Gara ku mu auren muke so mu sake abu yaci tura ga dai tarin zaurawa ga hidima iyakar yi amman da ance a fito suke guduwa. In lokacin sanyi yayi wallahi ba kullum mutum yake iya bacci ba"

Wannan tace wannan _wannan tace wannan. Uzairu  zuchiyata dai yana ta cin abinci yana waƙarshi hankali kwance ga wani ƙaton takalmi mai tsada a ƙafarshi. Shi dai babu ta inda ya baro Maigogul ta fannin gayu. Rakiya kuma tana gefe can tana cintar shinkafa.

Wannan damuwoyin su suke sake kassaramun kuzarina. Nayi lamo a katifa ina sauke numfashi da jawo shi da kyar Rakiya tace.

"Ku harhado mai taro mai sisi ayo cefane mu ɗaura girki. Ku kuke daka ta Lolo dadine yayi mata yawa. Rannan fa da Labbai ta kwana a gidan doya da kwai cikin kwano ta soyo ta aiko mana dashi. Mu muga haka mana a gidannan. Wallahi bamu taɓa soya doya da ƙwai a cikin gidannan ba, sai dai ka cire kuɗi ka siya ko kuma in kun fita ku tawo mana da tsarabarta."

Haka kowa ya dinga saka ɗan abinda yake dashi, nera ashirin Uzairu Zuchiyata ya saka Adama kam bata sa ba.

"Ni ko sisi banda shi, a ƙafa na tawo kuma a ƙafa zan koma"

Aisha miƙo mun jakata gata can na hangota"

Ta saka hannu ta miƙo mun na zaro dubu uku na miƙa ma Rakiya, na ba  Rahma dubu ɗaya Adama dubu guda.

"Ni fa Lolo bani da ko na katin da zan kira budurwata a waya. Ke ƴar ɗari da zan saka mu yi free call cikin dare bani da'ita fa."

Edit with WPS Office

"A haka zaka ƙare ko tausayinmu baka ji. Jibi takalmi da suturar jikinka masu tsada kai da ubanka babu abinda kuka sani sai sanya suturu masu tsada kuyi ta ƙwambo. Nera ashirin ka saka kuɗin cefane, in kuma aka girka kafi uban kowa ci"

Cewar Rakiya. Uzairu zuchiyata yayi dariya yace.

"Rakiya ki kwantar da hankalinki ke da kinsan da ƴar gidan wa muke soyayya a waya ko?  da ba ma zaki ce haka ba. A 2go muka haɗu. Ta mato a kaina. Wallahi hotunana data gani cewa tayi amman mun haɗa jini da larabawa, ko bararoji ko, taga yaro mai hanci da dara_daran idanu Wallahi duk tabi ta rikice Uzairu Zuchiyata dai kullum take ambato. Ku dake a arha kuke ganina shi yasa duk kuka rainani"

Su Adama suka saka dariya. Ni kuma na girgiza kaina dake ciwo kawai.

"Labbai zo ki je kiyo mana cefane maza hadarine sosai a garin kar ruwa ya sakko bamu da cefane a hannu."

Lissafama Labbai akayi duk abinda ake bukata ta fita taje siyowa. Na miƙa ma Uzairu Zuchiyata ɗari biyar ya dinga godiya ya saka kai ya fice.

Maigogul ne ya shigo yana zagin Hauwa.

"Ai Hauwa shegen baƙin haline da'ita"

Shi dai bai kulata ba. Akwatin kayanshi ya buɗe ya sake feffesa turarenshi mai tsada ya gyara tsaiwar hularshi.

"Lolo nasan kafin in dawo kin tafi. Ki yi ta haƙuri kuma a dinga gode ma Allah ko. Rakiya ni na fita"

Kafin ya fice ta tare ƙofar.

"Baka bayar da kuɗin cefane ba ka sake feshe jikinka da turare zaka fice ƙila ma sai gobe zan ganka"

Dariya yayi mata yace.

"Ga yara mata riɗa_ riɗa masu ƙira a c

Jikinsu a rasa yadda za'ayi ayi cefane sai ni na bayar haihuwa ba zata yi mun rana ba kenan har abada? Gafara bani hanya kar kuci abincin dan kuna ganina a gidanne ma"

Ya tureta ya fita. Ai dawa Allah ya haɗata ta hau faɗa tana ɗaga murya. Ni dai sai dafe kaina nayi na yi saurin rufe idanuna. Matar data kawo mata wata tsohuwar randar siyarwa ce ta katse bambamin da take yi ta fita  harkar kasuwancinta.

Sai da na huta sosai jirin ya ɗan sassauto mun kafin na rama sallar azahar nayi la'asar. Sai ga

Edit with WPS Office

ruwan sama ya ɓalle wajajen biyar na yamma ne lokacin. A guje Rakiya ta shigo da kurfo ɗin girkinta dake kan tire ta ajjiye a dokin ƙofa.

"Rahma maza je ki sake ma karnukannan tamfol kafin Gaza yazo yaita tijara akan an bar mishi karnuka sun jiƙe dan yafi son karnukanshi sama da mu, ku kuma ku taso ku jera kayan ruwa, baku da aiki sai danna waya"

Ko wacce ta tashi tayi abinda Rakiya ta saka ta, ni dai ina zaune nayi zurfi a tubani maganganun malama Babba sai yawo yake yi mini a kaina, da maganar Malama ƙarama da tace dama haya su Rakiya suke biya. Gashi ni bani da komai da zan iya siyarwa in soma yi musu gini a hankali. Ɗan harkar tsubbun da nake yi kwana biyu abubbuwan sun ja baya a da sai mata goma su zo a rana amman a lokacin dake a geto eriya nake, yanzu kuma bama kowa ya sanni ba, a can ko na kafu sosai da yawa kuma basusan ina muka dawo ba ma sai ɗaiɗaiku.

An daɗe sosai anata zuga ruwa fa, har bayan isha, kusan mu shida a katifa ana taɓa hira da shewa da musu, hakanne yasa numfashina da yake mun tauri ya ɗan sassauta, a faranti ɗaya Rakiya ta miƙo mana wata caɓaɓbiyar jallof ɗin shinkafar hausa, loma biyu nayi dan in sa albarka na bar musu in naje gida ko tea na sha, dan suma ba isarsu zata yi ba. Wajajen tara ruwan ya dakata ni dasu Adama duk muka miƙe muka soma shirin tafiya kuma. Na zaro jakata da ledar atampata.

"Wai atampar menene uban mijinki ya baki ne Lolo?"

Cewar Rakiya data zuba mini idanu.

Angon bikin Babangida ne, wai zasu yi taron famili shine aka fitar da ango. Labbai zan shigo ranar asabar sai muje tare"

"A_a nice dai zanzo in ɗan zaɓi atampa mai kyau a kayanki in saka. Kinga kayan nawa duk sun lalace babu na fita taro"

Murmushi nayi kawai dan ba yau bane farau, har su Adama in zasu yi wani sha'anin gidana suke zuwa su ari kaya, duk da jikin mu ba ɗaya ba, amman ina da manyan ɗinkuna masu bubu sosai shi suke ara ko abayoyina.

A tare muka fito har da su Labbai ɗin. Muna fitowa sai ga Malam Habu wai dama yaro yake nema ya miƙa ma Labbai ledar tsire. Kunji fa tun daga unguwarmu can ya tawo da ɗan ƙunshin ledarshi.

"Wai Halima Labbai soyayyya take yi da Malam Habu ko sulhu zai yi mata da Badaru ne?"

Dariya Aisha da Halima suka saka.

"Wanne sulhu da Badaru? Shi yake son ya ɗauka. Ai kullum sai ya kira wayarta, shi yake bata ma kuɗin karyawa fa, idda kawai yake jira ta gama a shafa fatiha"

Edit with WPS Office

"Tabbb lallai malam Habu wato maza basu da kunya. To duk da dai madokine amman da yawon banza gara a rarrafa tayi auren. Labbai ce zata yi maganinshi ƙila ma tasa matanshi su yi firi a duka." Na dubi Adama nace.

Kenan kema kina so ta aureshin wai?" Halima ce tace.

"In ma bata aureshi ba wallahi sai dai tabi sahun mu. Muma fa ba daɗin abinda muke yi muke ji ba. Yinwa da fitar da kanka a kunya kesa dole kabi maxan ka samu kuɗinka na ƙashin kan ka, daidai da sabulu fa kai zaka siya ma kan ka, suma iyayen da kai suka dogara. Ki barta tayi aurenta in ma maziga sun barshi ya aureta kenan ai"

Haka dai Labbai ta same mu a hanya. Muna zuwa kofar gidansu Babangida yaran suka fito muka haɗu mukai titi.

Majalisar su Babangida a batse take tun daga nesa muke jiyo hayaniyar su anata cin uban musu. Babangida shine a tsaye yana ta kaɗa hannu yana musu bayani.

Wucewarmu yasa wasu munafukan abokanshi suka nuna mishi mu, gabaki ɗaya kallo ya dawo kanmu yuu bafa su dena kallonmu ba har saida ni da yara mu ka hau abin hawa muka bar wajen, na bar su Adama suna tarar nasu ita da Rahama hanyarsu ɗaya sai am sauke Adama za'a wuce da Rahama

MRS BUKHARI.

Mu tara gobe in Allah ya kaimu

Bincike ya nuna sama da mutune   miliyon goma sha biyar ke shan muyagun ƙwayoyi a najeriya.

Hakan kuma ya jawo asarar rayuka, taɓarɓarewar tarbiyya. Ya haɓɓaka fitinu da manyan lefuka a arewacin najeriya dama ƙasar baki ɗaya.

Tun kafin zama ya gagaremu mu koma bacci da ido ɗaya a buɗe. Lokaci yayi da zamu haɗa ƙarfi da ƙarfe domin mu taimaka ma hukumar yaki da sha da fataucin miyagun ƙwayoyi.

Dan ganin mun kawar da wannan ta'asa dake shirin zame mana ruwan dare.

Shaye_shaye annobace ga al'umma.

Wannan saƙone daga hukumar yaki da sha da fataucin miyagun ƙwayoyi wato ( NDLEA)

Edit with WPS Office

IDAN KAYA YA GAJI...

GAMMO MA YA GAJI

BADIAT IBRAHIM MRS BUKHARI B4B GIDAN KAMSHI

LITTAFI NA FARKO

SHAFI NA GOMA.

Ina manyan mata masu capacityn suke? ku fito lambarku ce ta fito.

Yar uwa turaren wuta kike nema nau'ika daban_daban masu musulmin ƙamshi da kama muhallu? Ba itacen banza masu sanya gida ƙauri da hayaki kamar an kunna taohuwar bespa ba.

Matso gasu MRS BUKHARI B4B GIDAN KAMSHI nazo miki da duk abinda kike buƙata na ƙamshi. Kama daga turarukan wuta irin na gidan alfarma. Zuwa humrori iri daban daban masu musulmin ƙamshi da riƙe jiki.

Bugu da ƙari muna da turarukan kaya, na fesawa dana turara kaya.

Muna da kulaccam nau'i daban daban masu gyara jiki da lausasa fata mata, ga kuma ƙamshi mai inganci.

Muna da turarukan tsugunno na musamman masu sirri Hajiyata

Muna da room freshener iri_iri

Muna da mopping mix masu kama waje.

Akwai turarukan kafet dana kujeru.

Sannan akwai box _ box setika na Hajiyoyi masu ƙyallin goshi.

Muna da Amarya package.

Muna da uwargida package

Muna da maijego package

Edit with WPS Office

Muna bayar da sari ko a ƙasar waje kike, muna tura kaya

Saudiyya

Nijar

Ghana

Camaron

A duk ƙasar da kike kayanmu zai iso miki cikin aminci da yardar Allah.

Hajiya akwai Humrar matan aure wannan ta musamman ce.

Duk wani abu da kika sani na ƙamshi babu irin wanda bamu dashi a kamfaninmu.

Muna da turaruka designer na maza da mata wanda kamfaninmu ke bugawa Hajiya babu inda zaki je ki ci karo da mai irin ƙamshinki.

MRS BUKHARI B4B GIDAN KAMSHI TAZO MUKU DA DUK ABINDA KUKE SO NA KAMSHI HAJIYA.

KUNSAN KANURI MUNE KAMSHI DAMU AKE KOYI

SIYAN NAGARI MAIDA KUDI

MUNA MARABA DA MASU SIYAN ƊAYA KO SARI.

LAMBAR DA ZA'A SAMENI KAI TSAYE ITACE.

Wa.me/2348179523215

SAI NA JIKU

Muna zaune a cikin bus Mardiyya tace.

"Umma wai ranar asabar za'ayi taron bikin Babanmu. Ummi auren ya kuma yi?"

Na dubi yarinyar nayi murmushi nace.

Aure ya sake yi Mardiyya ai ba haramun bane. Nasan da taron kinga ankon nawa ma an bani"

Edit with WPS Office

Na nuna ma yaran a ƙoƙarina na ganin na kawar da tunaninsu. Ai kuwa Mardiyya ta karɓi ledar ta buɗe.

"Aɗɗa'u irinta sak muka gani Goggo Sa'a na miƙa ma mamansu Jamila ɗazu ko?" Aɗɗa'u yace.

"Irinta sak. Ummi muma za'ayi mana ankon?"

Dariya Mardiyya da Aminu suka yi mishi. Malama tayi lamo a jikina na ƙanƙameta dan ba karamin sanyi ake busawa ba

Atampar za'ayi maka sai kace Toye yaron Iyabo?"

Dariya suka kara yi mishi, shi kuma ya haɗe rai harda cuno baki. Aminu uban ƴan son girma yasa hannu bub ya bige bakin nashi. Shikenan ya saki kuka.

Sannu ragon maza dan ya bige maka baki shine zaka yi kuka? Shi yasa a makaranta ma sa'anninka suke saka kuka. Kar ka zama rago kaji? So nake ka zama jarumin gaske. Irin jaruman da ake tsoron karo dasu"

Hakan da nace yasa ya share hawayenshi yaci gaba da dariya a cikin ƴan uwanshi.

In na dubi yarana a nutse sai inji kwanciyar hankali, damuwa da ƙuncin da nake ciki a gidan mahaifinsu sai inji kamar zan iya jurewa. In na sake tuno baƙar rayuwar da ahalina suke ciki sai inji kamar zan iya jure duk wulaƙancin Babangida. Amman fa zan mutu da wuri cikin ciwon takaicin ɗa namiji matsawar zuchiyata taci gaba da kunshe waɗannan abubbuwan to wata rana sai dai a wayi gari a ganni a mace zuchiyata tayi bindiga damm ta fashe."

"Ummi mun kawo layinmu, kwandasta akwai nanan"

Na jiyo muryar yaran. Saba Malama nayi a baya dan yayyafine ma ya dawo sai dai babu karfi na miƙa ma mai motar kuɗinshi muka kama hanya gudu_gudu.

Muna shiga ɗaki nace da su Mardiyya su je su kwanta dan nasan dama sai sunci tuwon dare suke dawowa gida. Mardiyya ta karɓi malama sukai mun sai da safe.

Ni kuma kitchen na nufa na ɗaura ruwa a ƙaramar tukunya na jefa ƙwai guda ɗaya. Ina taran ruwa a butar dafa shayi na jiyo wayata na ruri da sauri na fito. A tunanina ma ko daga gidane sai naga baƙuwar lamba, kamar bazan ɗauka ba sai dai kuma na ɗauka.

"Ranki shi daɗe. Kinji ban kiraki ba,nayi tsammanin zaki kirani ai ko. To ya daren?"

Ɗaki na tafi da sauri.

Khalid mai kake so ne, ina da aure fa kuma ai nasan kana da labari a wajen abokanka"

Dariya yayi yace.

"Tabbas ina da labari, ga ƴarki ma na gani. Amman ai nasan auren bazai hana mu mu'amala ba,

Edit with WPS Office

ko da ma yayane. Lokacin da za'a aramun a cikin na oga ai bashi da yawa. Kuma na fahimci kina buƙatar mai kwantar miki da hankalinki wanda zai baki kulawa ta musamman. Kwanana nawa da yi miki magana a WhatsApp amman baki ma buɗe ba. Sai dai nayi katari da hotunan kyawawan yaranki"

Ajjiyar zuchiya na sauke na kashe wayar ba tare da nace komai ba. Kashe wayar nayi baki ɗaya na cillar akan gado na fita.

Ina komawa kitchen na samu ruwan sada ɗaura yanata tafasa indomi taliyar yara na dafa babba guda ɗaya na cika albasa sosai, na juye a roba na ɓare dafaffen ƙwaina na ɗaura a kai. Na dafa ruwan bunu na tafi falo. Tv na kunna na zauna sosai a ƙasa ina cin abincina ina kallo. Bana ma ko fahimtar me akeyi a tvn. Falon na shiga ƙarema kallo duk wanda zai shigo zai yi tunanin mamallakiyar falonnan bata da wata matsala da zata iya damunta a rayuwa. Amman ni masu zaune a gidan kurkuku ma sun fini sakewa da walwala.

Hon ɗin motar Babangida na jiyo kafin in kai ga tashi Mardiyya har ta fito da kayan bacci a jikinta taje ta buɗe mishi ta dawo. Rufe ƙofar falon nayi na tafi ɗakina. Bayan na fito wanka naji ana bubbuga ƙofar ɓarayina kamar za'a jijjigeta kafin in yinƙura na soma jiyo muryar Babangida yana kiran sunana.

"Sabuwa, ke Sabuwa wannan wanne iskancinne zaki kulleni a waje. Daga ni sai tawul a ƙirjina na fita na zare mishi sakatar muka haɗa idanu.

"Dan iskanci da wulaƙanci ni da gidana zaki rufe mun ƙofa ki barni a waje sai kace buta. Sabida dai ke baki da tarbiyya ko?"

Kallonshi nayi nace.

To ai bansan zaka shigo ba, kaga bazan bar ƙofata a buɗe ba ai"

Harara ya doka mun yace.

"Kina nufin baki san kece da girki ba kome? Gashi a yinwace na dawo ina son cin jallof ɗin shinkafa da bushasshen kifi"

Agogo na kalla sha ɗaya saura.

Amman ni banyi girki ba naje gida, kuma shinkafa yanzu ai dare yayi ko. Sannan da kake maganar girkinane ni ina zan sani sabgogi sun sha kaina?"

Shigowa yayi ciki yace.

"Ni nace kije gida ki zauna ne? Kuma da kike cewa baki yi girki ba ai wannan ruwanki ko? ni dai na faɗa miki abinda nake son ci ina jiranki a ciki. Aikin banza aikin wofi. Ko sabgogin uban meye suka sha kanta owo sai kace wata haɗaɗɗiya Cus kawai"

Wucewarshi yayi cikin ɗakinshi yana mita. Kai na girgiza kawai burin Babangida ya wulakantani

Edit with WPS Office

kawai, wannan kalmar ta Cus da yake faɗamun, ko ya kirani da'ita tana mugun ƙona mun rai. Haka na shiga ɓuruntu a kitchen sai da na kai mintin arba'in a kitchen na gama girkin na zubo mishi a plate na rufe da wani plate ɗin na saka gorar ruwa, kofi, cokali duk a tire na nufi ɗakin da sallama.

Video call yake yi da mace hankali a kwance. Ganin na shigone ya sake gyara kwanciya yana zubo mata kalaman yaudara. A teburin dake gaban gadon na ajjiye tiren ina haɗiɗiye yawu. Duk fa yadda mace take da tsanar mijinta bata son taji shi da wata maccen ko da kishiyarta ce, balle budurwa a waje kuma irin su Babangida da basa soyayya haka kurum sai da laluben jikin mace.

Ɗakina na koma na saka kayan bacci na muttsuka humra na kwanta ina jin wani irin baƙin ciki da takaici. Idanuna a rufe ya turo ƙofar ya leƙo"

"Kizo Cus "

Iyakar abinda yace dani kenan ya juya da waya a kunnenshi. Miƙewa nayi a hankali na fito na koma ɗakin. Yana tsaye sai kai komo yake yi a tsakar ɗakin ina shigowa ya zabura ya juyo. Jikinshi har rawa yake yi na rashin mutunci yace.

"Sabida baki da hankali baki san meye miji ba ni kika zubo ma abinci a plate kamar almajiri. Shikenan ban kai darajar da zaki zubo mun abinci a kula ɗebi da kanka ba dan wulaƙanci da bura'ubanci. Hamida da sauran matan dana sake su kullum a cikin sake mun kuloli da plate da su cokula suke. Amman ke kuwa kullum bakya sauya salo, yanzu ma a plate kamar yadda kuke zuba ma almajirai haka kika zuba mun. Duk da ba'a kawo ki da ko tainke ba Baba Malam ne yayi miki komai. Yayi ne ba sabida ke ko ƴan gidanku ba saboda ni yayi  in zaki je gidanku ai naga a kula ɗirkekiya kike zuba musu abinci ko? Sai nine ban kai ba yau."

Da mamaki nake kallonshi zuchiyata na tunzurani inajin kamar in dira a wuyanshi, ko kuma in lailayo ashariya in danƙara mishi. Da ƙyar na mallaki kaina dan yanzu na dena biye mishi muna raba abun faɗe. Kafin in kai ga magana yace.

"Dallah rufa mun baki ki kwashe abincinnan ki zubo mun shi a kula in ɗiba da kaina. A majalisa matan abokai kuloli na alfarma, plate na alfarma amman banda ke iyakar abinda kika sani shine in zaki gida ki debe mun abinci ki girka cikin babbar kula ki kai musu ai taci an samu na gwamnati."

Abincin na ɗauka na fita na barshi yana buyaginshi

Kula na ɗauko a sama na juye abincin nasa mishi wani plate  na koma mishi da abincin. Yana zaune a kujera.

"Wato sabida raini ina cikin magana kika fice sabida kin rainani Ko. Dan na saki aikine kike ganin ke wata ce. Na  fasa cin abincin bana cikin usulubin da zan iya cin wani abinci kuma"

Duk yadda na kai da dannewa sai da Babangida ya tunzurani.

Edit with WPS Office

Babangida wai me kake nema danine, me yasa har yanzu ka kasa yadda ka rungumi ƙaddararka ne?

Na faɗa ina hadiye zuchiya. Gabana ya ƙaraso yana lakace mun hanci.

"Masifa da jar jaraba nake nemanki dashi. Kaddara da kike maganarta har abada bazan mance da fentin da kukai mun ke da Maigogul ba. Kun haɗu ke dashi kun rabani da nawa uban korar kare yayi mun ya jefo mun jakar kayana tsakiyar unguwa nima yasa gardawanshi suka jefoni. Akan ki sai da mahaifiyata ta shiga halin da har gaba da abada ba zamu mance ba"

To ka sake ni da kai da  da'ita ku huta mana wannan jar azabar da kake yi mun tayi yawa. Kuma ka sani ai kai da kan ka ka shafa ma kanka baƙin fenti ba Sabuwa ba."

A zafafe nayi maganar ina zubar da hawaye cike da ɗaga murya yayo kaina kamar zai dokeni.

"Na faffasa miki baki ƴar iska mara kunya kawai"

Wallahi Allah duk sanda hannunka ya sake taɓa lafiyar jikina ko wallahi sai ka gane kurenka zaka san lallai tabbas ƴar daba ka auro kamar yadda kake faɗe, kasan karon babu daɗi kaima ka sani. Bar ganin nayi sanyi ganin damanane ba sabida wannan hargagin naka ba. Kuma zan haɗaka da magazin yai mun maganinka. Babangida na gaji da kai na tsani komai daya danganceka wallahi. Ka sake ni ka huta in huta na roƙeka"

Na faɗa tare da fashewa da kuka mai gunji, tura ta kaini bango na lura hauka Babangida yake so nayi.

Murmushi yayi na mugunta yace.

"Mutu ka raba kenan takalmin kaza. Kema kinsan in ba dan burki da aka ja mun ba, kuma ina ganin daraja da kimar mahaifana bana fatan abinda zai sa mahaifiyata ta bar ɗakinta na aure a sanadinki. Kinsan da tuni na sauke wannan kayan mai nauyi. Amman ga gidannan ki ci gaba da zama farin ciki da kwanciyar hankali kin rasashi har  gaba da abada. Yadda ganinki ke fama mun mikin zuchiyata, kema haka zaki zauna kiyita ƙunsam baƙin cikin Babangida Kaci gari"

Kafin in yi magana yasa hannu ya riƙo kafaduna ya jefa ni kan gadonshi ya bi kaina.

Ban yi yinƙurin yin bige_bige ba dan nasan a banza zan sake azabtar da kaina ne kawai, dan Babangida in ya danneni bana iya numfashi mai kyau, in nace zan kwace tabbas zan iya amman zan jijji ciwo kafin in iya kwacewa, sannan a wannan lokacin babu ƙarfi sam a jikina. Kamar mayinwacin zaki a kullum Babangida yake zama a lokacin da muke tarayya dashi. Murzata yake yi ainun dan duk ran da ya damƙeni ina ɗanɗana kuɗata. Ta'amali yake da ƙwayoyin bature masu ƙara ƙarfi da kuzari sosai, shine shan kofi na maza duk wani magani in dai na bature ne Babangida na shan shi. Hawaye bai dena zuba a idanuna ba har ya gama kiɗanshi da rawarshi ya sauka yana mayar da numfashi. Take bacci mai nauyi ya ɗebeshi na jar azaba. Mafi akasarin lokuta da irin wannan sigar ɗiban albarkan Babangida yake neman hakkinshi a wajena, sai afi

Edit with WPS Office

wata uku bai nemeni ko sau ɗaya ba. Duk ranar da ya tashi neman nawa hakan zaiyi mun. Ina cike da zafin zuchiya tare da tunanin rayuwata ta baya, a wannan daren nayi kuka har sai da idanuna suka dena zubar da hawaye dan masifa bacci yayi awon gaba dani a nan ɗakin, bacci mai cike da zafin zuchiya dana ruhi, da gangar jiki. Bani na farka ba sai da asuba. Ko dana buɗe idanuna ni kaɗaice a ɗakin Babangida baya nan. A banɗakinshi nayi wankan Sallah na fito. Rigar baccina na zura na fice. Kai tsaye na koma ɗakina sai da nayi sallah kafin naje na taso yara Malama jikinta da zafi kau jikin ya rikice sosai.

Mardiyya maza ku shirya ki dafa muku tea ki soya muku doya dole zamu koma asibiti da malama bazai wuce ruwa da sanyin da akayi jiya bane ya tayar mata da ciwonta ba. Akwai kuma jallof ɗin shinkafa in ita kuke so yanzu na saka a firgi"

A tare da yaran muka fita, su suka wuce makaranta ni na wuce asibiti dan Babangida baya ma cikin gidan sam kuma na kira wayarshi yaƙi ɗauka bazan kashe ƴata da kaina ba sai dai yayi duk abinda zai yi na dai san zansha faɗa da zarge_zargenshi daya saba.

Bamu daɗe ba muka samu shiga ganin likita kasancewar mune na bakwai a layi. Ina shiga ɗakin naga ashe Khalid ne a zaune. Nima da ƙyar nake tafiya sabida jiri da ciwon kai, kafin ya bani izinin zama na zauna dan jiri ne naji yana shirin kayar dani.

Shiru Khalid yayi kawai yana kallona fuskata a kumbure take sosai, kaina tamkar zai tarwatse mun sai wani motsi tsakiyar kan nawa yake yi kamar irin tsutsotsi na mun yawonnan

"Yarinyar kika kawo ko kanki? Ni likitan yarane sai dai bari in kira Dr Binta tazo ta duba mun ke"

Kici kicin kiran waya ya shiga yi na dakatar dashi ta hanyar ɗaga mishi hannu.

Yarinyace na kawo jikinta ya tashi, jiya taje islamiyya acan ruwan ya tareta, kuma ruwan ya ɗan taɓata a hanyar dawowarmu gida".

Kallona yayi yace.

"To amman ke kan ki ai babu lafiya a tattare fa dake, gashi fuskarkar ki ta kumbura sosai."

Idanuna na runtse na tsani yayi magana ma wallahi ƙara tunzura zuchiyata yake yi. Lura da hakan da yayi ne yasa ya kirawo Malama ya ɗaurata a gado ya soma binciken lafiyarta.

"Tana kan shan magungunan nata a kan lokaci?"

E tana sha"

"Okay kina saka mata kayan sanyi sosai dai ko?"

Kai na ɗaga halamar E.

"To ta haƙura da makarantar har sai ta warware ta gama shan magungunan nata. A kiyaye kar ruwa ya sake dukanta."

Edit with WPS Office

Waya yayi sai ga wata nos ta shigo, ya ce.

"Rose ki tafi da wannan yarinyar ki siyo mata biskit da viju a waje ko?"

Wacce ya kira da Rose tace.

"Okay Dr ( to likita)

Ta ja hannun Malama suka fice da sauri Khalid ya zo ya zauna a teburin dake gaban kujerata ban aune ba naji hannunshi a wuyana, ɗumin jikina da ɗumi da taushin hannunshi suka ratsani, da sauri na kauce.

Ka bari Khalid ba abinda ya kawo ni asibitinnan kenan ba"

Baice dani komai ba ya kira waya, sai ji nayi yana.

"Dr Binta ina da marar lafiya a ofishina dan Allah ki yi maza ki zo ki duba mun ita ba zata iya zuwa ofishinki bane"

Ya ɗan yi shiru can yace.

"To Shikenan nagode sai kin shigo"

Ya kashe wayar ya dubeni.

"Na kira za'azo a duba mun ke. Naga kina wasa da lafiyarki, Sabuwa ki sani a duk halin da kike ciki ai gangancine wasa da lafiyarki. Ko babu komai in kina da lafiyarki komai zai zame miki mai sauƙi sosai lafiya darajarta tafi ta komai a duniya,kar kice zaki yi mun musu. Nasan damuwarki bazai wuce akan mu maza bane. Ki ji da kyau mafi akasarinmu muna morar lafiyar jikin macene, daga lokacin da ciwo zai far mata daga lokacin muke zuƙe jikinmu daga gareta, bance dukkan maza ba fa amman dan ko ni Khalid bana cikinsu. Ki sani lafiyarki tana da matuƙar mahimmanci a wajena inaso ki saka a ranki bazan iya barinki a cikin yanayin damuwa bama balle na ciwo uhm?"

Bance mishi komai ba dan haƙiƙa bani da lafiya ciwo ya daɗe yana cina. Amman a nawa tunanin ciwon bana asibiti bane ciwon rayuwa a gidan Babangida ke damuna.

Da sallama wata likita ƴar gaye ta shigo sai ƙamshin turare take yi. Irin kallon da naga suna jefa ma juna ita da Khalid tabbas akwai alaƙa mai ƙarfi a tsakaninsu.

"Kin ganta a galabaice take sosai, ki dubata anan dan Allah, sabida in san abinda ke damunta"

Kallonta ta dawo dashi gareni tace.

"Baiwar Allah mu ƙarasa daga ciki ko?"

Miƙewa na yi na bita cikin wani ɗan lungu da aka rufe da labule, karamin gado ta nuna mun na hau a hankali ta soma gwaje_gwajenta cikin ƙarewa da sanin makamar aiki, ta ɗebi jinina harda

Edit with WPS Office

fitsarina ma.

"Ki kwanta ki jirani, naga kamar kina jin jiri ma ko?"

Kai kawai na gyaɗa mata, ta girgiza kanta ta fita.

Ina kwance ina kallon saman dakin ɗin asibitin wayata dake cikin jaka ta shiga ruri, a hankali na mike ina ƙoƙarin janyo jakar Khalid ya shigo ya zuge jakar ya ciro wayar.

"Babangida"

Khalid ya faɗi take ƙirjina ya ba da bugu mai ƙarfi, wayar ya miƙo mun nasa hannu na karɓa tare da karawa a kunnena bayan na ɗauka.

"Gidan uwar wa kika je tun safe gashi har sha biyu na shirin wucewa baki dawo ba. Na aika gidanku ance baki zo ba. Ko kuwa baƙo kika yi kika kaishi zangon baki domun kinsan har gaba da abada bazan taɓa yadda dake ba ko?"

Khalid na kalla shima ni yake kallo.

" Ba magana nake yi ba dan bura'ubanci shine kikai kunnen uwar shegu dani, ko kuwa shi ɗan iskanne ya hanaki kiyi magana ne, ai naji ma kamar a hands free kika saka ni ko?"

Malama na kai asibiti ciwonta ya tashi ne sabida jiya ruwa ya taɓata"

"Ba dole ciwon yarinya ya tashi ba kin saka gantali a gabanki kece bini _bini zuwa gida ko uwar me akeyi a gidan oho. Kin mayar dani mai kudin banza kenan shi yasa ma kika bari ruwan ya daketa yaushe_yausshe aka sallamota daga asibiti nayi asarar kuɗina. Wai Sabuwa kina cikin hayyacinki kuwa, ko dai har yanzu kina ɗan zuƙe_zuƙene? Kika sake ƙarfe ɗaya tayi miki a waje wallahi wallahi zaki sani. Sannan ai kinsan halina zansa aimun bincike in ba asibitin kika je ba kema kinsan sauran"

Yana gama bambaminshi ya datse wayarshi. Abinda yake yi ma yaran mutanene baya so ayi mishi, shi yasa yake zafafa kishinshi musamman akan fita unguwar mace. Hawayene suke shirin zubo mun ganin Khalid yasa na kanne na koma nayi kwanciyata. Minti ashirin sai ga Dr Binta ta dawo, a lokacin ni kaɗaice a keɓaɓɓen wajen.

"Malama menene sunanki?"

Sunana Sabuwa?"

"Okay Sabuwa kina jin yawan ciwon kai haka, ko jiri, ko kuma kiji kamar iskar da kike shaƙa tayi ma huhunki ƙaranci?"

Mamaki nayi data lissafo abubuwan da nake jinsu a jikina.

E inaji duk abinda kika lissafo ɗinnan, harma da fin hakan inaji"

Edit with WPS Office

Kallona take yi daga cikin tabarau ɗin idanunta.

"Ok yanzu dai zuwa ranar monday ki dawo, zan baki katina da kin shigo asibitin ki kirani ki yo sammako amma. Sannan shawarar da zan baki ki dena matsantama ƙwaƙwalwarki wajen aikin tunani, kina ƙuntata zuchiyarki tare da nauyayata. Akwai gwaje_gwaje da zan sake miki bisa ka'idar aikinmu in sha Allah a wannan gwaji na biyunne zan samu tabbacin abinda ke asalin damun naki. Ga katin nawa akwai lambar wayata a jiki"

Hannu nasa na karɓa nayi mata godiya na sakko. A kan cinyar Khalid nazo na samu Malama ya zuba mata farfesun naman kaza yana bata a baki.

"Dr har kun gama, menene matsalar?"

"Mun gama amman ba duka ba ranar monday zata shigo in sake sabunta gwaje_gwajen da nayi mata"

"Batun magani ba'a buƙata kenan tunda binciken bai kammalu ba ko?"

Ya tambayeta. Ta bashi amsa da cewa.

"E sai zuwa monday ɗin in tazo muka sabunta gwaje_gwajen sai mu ɗaurata akan magani"

Miƙewa yayi tsaye yace.

"Mu je in kai ku gida Sabuwa"

Fita Dr Binta tayi daga ɗakin na cabke hannun malama nace.

Ka barshi mungode"

Na saka kai na fice ina jin wani jiri na ɗebeni. Ina shiga gida Lokacin ɗaya saura kwata ajjiyar zuchiya na sauke dani da Malama duk kusan a kwance muka wuni, Khalid ko ya doshi kiran waya yana nacin tambayar yaya jikin nawa? Tun ina ɗauka ince da sauƙi har na kashe wayata baki ɗayanta.

Sai wajajen bayan la'asar na ɗan ji dama lokacin har yara sun dawo boko sun shirya sun wuce islamiyya.

Ganin shida saura kwata yasa na miƙe dan ɗaura mana sanwar dare. Bansan Babangida me yake son ci ba shi a ƙa'idarshi dole shi zai faɗi abinda yake son ci. Dole na kunna wayata na kira bai ɗauka ba, sai na ajjiye mai sako.

_me za'a girka da daddare?_

Shikenan iyakar abinda na rubuta. Ko minti biyu ban yi da turawa ba ya bani amsa da.

Sakwara da miyar ɗanyen kifi ( cat fish) yake nufi ɗanyen  kifi tarwaɗa.

Edit with WPS Office

Ga ba lafiya ita dakan sakwara ba ga rago ba. Haka na fere doyarnan na ɗaura a wuta na ɗakko kifina a firji yayi ƙanƙara na wanke na ɗaura tare da tsaida sanwata tsab. Ina kitchen na jiyo sallamar Hamida tana falo a zaune.

Hamida kece ashe kike sallama?'

Na tambayeta babu yabo babu fallasa.

Itama ranta babu daɗi sam.

"Nice ai ɗazu nazo na tarar ɓarayin naki a kulle"

Ayya ya akayi to?'

Muskutawa tayi tace.

"Yanzu muna ji muna gani Amaryar Babansu Aminu zata tare a gidannan? Wai kinga irin shirin bikin da Malama Babba take shirin yi kuwa? Nifa har gulma na jiyo a majiya mai ƙarfi wai har saniya shi uban gayyar ya siya duk na taron bikin da za'ayi ne.

Kuma wallahi ance bazawar sai tatikarshi kuɗaɗe take yi mu ya barmu a banzace kuɗi dinƙi dubu hamsin kawai ya bani fa. Ita kuwa ance sai ɓarnar kuɗinshi yake yi mata ta gama samun bakin zaren tun kafin ta shigo. Ke gashi kin ƙi ki bani haɗin kai mu haɗe mai kai mu buɗe mishi wuta.

Hmm wanzami akace bai son jarfa. Ita a nata auren wanne irin kuɗine ita da iyayenta basu tatsa ba? Amman yanzu bata son wata ta tatsa, harma kuɗin dinki dubu hamsin aka bata to ni nace me a matsayina na uwar gidan Babangida wacce sharar gidanta ta fita daraja?"

A zahiri sai nayi dariya nace.

Hamida kenan. Bazan hana ki yaƙin neman hakkinki ba, amman ni ta nawa ɓangaren ba zaki samu ko wacce iriyar gudunmawa ba. Ba yau na saba ganin zuwan kishiya ba. Wannan kishiyar ma ai taki ce ba tawa ni Sabuwa ba, kinga yaƙin naki ne ai"

Ta buɗe baki tace.

"Amman..."

Nayi saurin ɗaga mata hannu na miƙe tsaye.

Yanzu ne da Babangida zai ƙara aure kike tunanin ni dake mu haɗe kanmu mu ƙuntatama matar da zai auro ko? Ni dake muna rayuwa cikin gida ɗaya baki san ki mutuntani ba, burinki Babangida ya tozartani a gabanki, da kinga abu zaki kirashi ki gulmata mishi. Wai shin ma Hamida me kika ɗauke ni ne?

In kina tunanin bansan abinda nake yi ba kinyi kuskure. Daga yau kar ki sake shigo mun ɓarayina

Edit with WPS Office

na faɗa miki kenan ko wacce ta zauna a shashenta"

Ina gama faɗin haka na juya na shige kitchen ina tuno irin makirci da tuggu iri iri da Hamida ta ƙukkillamun a baya, har yanzu ma tana kan yi ai ita ta kira Babangida ta sanar mishi bana gidan na fita tun safe, shi kuma ɗan zargi ya kirani ya ƙaremun tanadi, shine zata biyo ni da wani bita da ƙullin alhalin da ita ake shirye_shiryen bikin ta fuskar gidansu Babangida.

Ni anan tazo tana gwadamun bariki dan iskanci. Har ni za'a nuna ma bariki ni Sabuwa tabb.

Haka dai cikin ɓacin rai na kammala dakan sakwarannan kaina kamar zai tarwatse. Ina zaune a falo ni da yara su suna cin abinci ni kuma ina zaune ne shiru ina ƙallonsu suna ta nishaɗinsu tare da yi mun santin sakwara.

Wayata ce tayi kara Babangida ke kirana

Ɗauka nayi na kara a kunnena.

"Ki saka kulolin sakwaran a basket kisa plate da cokali maza Mardiyya ta kawo mun ina mota a ƙofar gida. Ki tabbatar kulolin na fita kunya ne haka ma plate ɗin in da hali a ɓalle sababbi, in baki dashi ki karɓa a wajen Hamida"

To"

Shine iyakar abinda nace dashi. Ina daga zaune na ba mardiyya umarni ta haɗa komai ta fita da sauri ni jiri ke damuna sosai.

Hmmm sai biyun dare na jiyo shigowar motar Babangida yau bai kira yace a buɗe mishi get ba, kuma bai yi hon ba. Ɓarayinshi ya wuce tunda naji ya wuce minti ashirin bai buga ƙofar falonmu ba. Lumshe idanuna nayi inata kokawar in yi bacci amman wallahi idanuna sun soye, yadda naga rana bayin Allah haka fa naga dare. Sai sabon ciwon kai da ya dirarmun. A saddafe na sallami yara na ɗan gyara gidan sama_sama. Jiri na ƙoƙarin makantar mun da ganina

MRS BUKHARI

Yau dai Maigogul da Uzairu Zuchiyata suka ce ku huta🤣

Bincike ya nuna sama da mutune   miliyon goma sha biyar ke shan muyagun ƙwayoyi a najeriya.

Hakan kuma ya jawo asarar rayuka, taɓarɓarewar tarbiyya. Ya habɓaka fitinu da manyan lefuka a arewacin najeriya dama ƙasar baki ɗaya.

Tun kafin zama ya gagaremu mu koma bacci da ido ɗaya a buɗe. Lokaci yayi da zamu haɗa

Edit with WPS Office

ƙarfi da ƙarfe domin mu taimaka ma hukumar yaƙi da sha da fataucin miyagun ƙwayoyi.

Dan ganin mun kawar da wannan ta'asa dake shirin zame mana ruwan dare.

Shaye_shaye annobace ga al'umma.

Wannan saƙone daga hukumar yaki da sha da fataucin miyagun ƙwayoyi wato ( NDLIEA)

https://chat.whatsapp.com/IUKFTeuI76p2VaAvQ5nk0U

IDAN KAYA YA GAJI...

GAMMO MA YA GAJI

BADI'AT IBRAHIM MRS BUKHARI B4B GIDAN KAMSHI

LITTAFI NA FARKO

SHAGI NA GOMA SHA ƊAYA

Wajajen goman safe na kama hannun Malama ta rakani gidan maƙotanmu daura da gidanmu akwai wasu Amarya da kishiya masu dinki tun lokacin da suka shigo mana sannu da zuwa suka sanar mana suna dinki. Ita uwar gidan ta shisshigo wajena zaiyi sau biyar haka, nice dai ban taɓa shiga ba.

Da sallama na shiga gidan ina shiga naji saukar murfin tukunya a ƙirjina tab. Uwargidan gidance zata jefi amaryarta dashi ita kuma ta tsugunna ashe rabonane. Ga mijin yana gefe yana ƙoƙarin raba wannan faɗa sai zage_zage uwargidan take yi tana faɗin tura takaita bango da irin zaluncin satar kwananta da akeyi a kaima Amaryarta. Shigowata ce tai sanadiyyar rabon wannan faɗan kunji ƙudurar Allah.

Edit with WPS Office

Me gidan yana ganina ya shige ɗakin Amaryar tabi bayanshi tana harare_ harare. Uwargidan tace dani.

"Tunda aka auro wannan figaggiyar yarinyar ta hana mun kwanciyar hankali a gidannan. Hatta ɗinkin da take yi a hannuna ta koya bisa tursasawar mai gidan. Kullum bashi da aiki sai satar kwana yana kai mata. In  bai sata ya kai mata ba sai ta kirkiri ciwon dare duk randa miji ke ɗakina fa"

Tana yi tana kuka tana furzar da abinda ke damun zuchiyarta namiji namiji hmmm. Kuma a kyau da diri uwargidan ta kere Amaryar, macace kyakkyawar ƙin ƙarawa.

Kiyi haƙuri Maman Safara'u abinda haƙuri bai bayar ba ai rashin shi bazai bayar ba. Kinga dinki na kawo kuma ranar asabar zan yi amfani dashi da fatan zan samu dai?"

"Hmm muje daga ciki zaki samu"

Ta faɗa da sanyin murya, tayi gaba na bita a baya. Kekunan ɗinki huɗu ne da'ita a wani ɗaki dake cikin falonta, nan ɗakin ta shiga dani ga kayayyakin mutane nan da yawa, ga dinkuna wasu an ɗinka ba'azo an karɓa ba, wasu ana kan yi.

"Zauna kinji ga kujera, yarinya mai  ma sunan mancewa nake yi?"

Ta tambayi Malama. Uwar azagwaigwai tace.

"Sunana Malama ni"

Dariya mu ka yi dukkanmu. Bayan mun gaisa na zaro atampar na nuna mata.

"Okay wannan atampar muna tsakar gida Amaryarki Hamida ta kawowa Na'ila dinkin atampar wai ankon bikin mijinku ne zai ƙaro aure. A nanne ma take bata labarin irin kuɗin da mijinku ke kashema ita yarinyar daya aura ɗin tace har akwatin dannar ƙirji ita tayi muku"

Allah wadaran naka ya lalace. Hamida tayi asara da surutu. Murmusawa nayi kawai nace.

Hakane"

"To taso in gwadaki doguwa kike so ko mai siket?"

Ai mun mai siket ɗin ban fiye son doguwar rigar ba"

Nan ta shiga aunani anan ta sake ɓaro wata maganar tace.

"Ke guda ɗaya kawai zaki ɗinka? Kishiyarki kaya kala takwas ta kawo a ɗinka mata. Banda magungunan mata da naga Na'ila ta rakata gidan Maman Zarah ta jibgo. Kinsan gidan da daga namunnan sai nasu ƴar sokoto ce tana harkar magungunan mata sosai duk matan unguwarnan kya gansu a gidan. Shi yasa duk gulma take tasowa daga gidan."

Mamaki nayi wato har Hamida ta saba da maƙwabta tana shige_shigenta kenan. Harda su shan

Edit with WPS Office

magunguna su matan so kenan da miji ke kwanciyar aure dasu a ko da yaushe ni waya aikeni kashe kuɗina a banza wajen shan magungunan mata, ai wallahi ko zan sha maganin mata ba dai insha da Babangida ba. A zahiri nace mata.

Wannan ɗin kawai za'a dinka mun dake ina da sababbin kaya ɗinkakku shi yasa.

Wani style ta nuna mun mai ɗan karen kyau wuyan rigar anyi mushi kwalliyar fatan yayi kyau nace aimun irinshi, kunsan ƴan sinigal sun iya ɗinki mai wuya. Tun a wannan lokacin nera dubu shida dinkin tace dani gobe da daddare in zo in amsa ranar juma'a da daddare kenan. Kuɗin dinkin na bata duka har zan fita tace.

"Ina sai da ɗankunnaye fashion masu kyau na manyan mata bari kiga ko zaki ga wanda ya dace da kalan kayanki. Irin namu ne matan sinigal, ina saida sabulun gyaran jikima daga sinigal ake kawo mun.

Ta ɗakko mini dankunnaye da sarƙa masu kyau na ɗauki wata sarƙa da ɗankunne mai dutse ja. Sai kwalin sajen biyu ina da salateb nayi mana lalle, sabulun ma na ɗauki ƙaramar roba dubu da ɗari biyar.

A ƙofar gidan wannan mai maganin na hangi Hamida tayi wuf ta shige har tana waigen kar wani ya ganta. Ina tsakar gida saiga kiran Ƴar shuwa sai da naji kunya ni ban kirata ba amman ita ta dage sai kirana a waya take yi, dama dai ta fini wannan ƙoƙarin

Gaisawa mu ka yi ta tambayeni yadda duk zata yi da magungunan da Umar ya kawo mata nayi mata bayaninsu, mu ka ɗan tattauna matsalolin dake damuna da rashin lafiyar da take damuna dai daga bisani mu kai sallama da juna.

Ni dai haka na wuni a kwance babu lafiya dan yau ko girki na kasa sai tea muka sha da rana ni da Malama da yamma da su Mardiyya suka dawo makaranta suka taddani babu yadda nake ciwon kai da zazzabi ga jiri ya matsamin lamba. Makarantar islamiyyan da basu je ba kenan. Mardiyya yarinyar tana da ƙoƙari sosai ita tai ta aikace_aikace a gidan har girki ita tayi farar shinkafa ta tafasa dama bama rabo da miyar tumaturi kullum gaskiya. In ci abincin ma in ɗan haɗiyi fanado na kasa.

Mardiyya ki ɗan dafa mun indomi ruwa_ruwa ki haɗa mini shayi wannan shinkafar ba iya ci zanyi ba dama tuwone."

Mardiyya ta kalleni da tausayi tace.

"Akwai ragowar miyar kuka ummi bari in miki tuwon"

Idanuna na lumshe sai nake ji yarana sun ƙara ƙarfafani duk wuya zan zauna da su a gidannan. Amman ina tsoron mutuwar faraɗ ɗaya da ka iya samuna a ko da yaushe duba da zuchiyata tayi rauni da yawa cike take da baƙin ciki da dana sani marar iyaka. Ina mai nadamar haɗuwata ta farko da Babangida ba zan dena dana sani ba har izuwa ranar da nunfashina zai tsaya.

Edit with WPS Office

Haka Mardiyya ta tafi kitchen su Aɗɗa'u kuma suna tai mun sannu_ sannu har Mardiyya ta dawo da tuwo da miya a tire.

A hankali na tashi zaune na ko cinye tuwon tas na sha magani na tafi ɗaki na kwanta. Na umarcesu da su rufe ƙofa su je su kwanta in sun gama abinda suke yi.

Wajajen goman dare sai ga kiran Khalid ya shigo kamar bazan ɗaga ba sai na ɗaga domin inaso in mishi bayanin bani da lafiya.

"Sabuwa da fatan jikin malama da sauƙi dai ko?"

E da sauƙi nagode sosai "

Na bashi amsar a taƙaice.

"Muryarki tayi kama da ta marasa lafiya, yaya yanayin jikin naki?"

Kayya jikin ya matsanta mun sosai, kuma ban iya bacci ma sam"

Ina faɗar haka khalid duk yabi ya ruɗe.

"Shine baki kirani kin sanar dani ba Sabuwa. Na lura kina wasa da rayuwarki sabida baki san mahimmancin lafiya ba ko, to shi lurasarin mafaɗacin mijin naki baisan baki da lafiya bane?"

Ni dai bance komai ba sai nishi nake yi a hankali a hankali.

"Oh no bari inzo gidan naki in ɗaukeki in kai ki asibiti da kaina"

"A_a gobe zan zo asibitin ba sai ka zo ba."

A hankali yace.

"Shikenan gobe ƙarfe bakwai kiyi ƙoƙari tayi miki a asibiti ba'a wasa da lafiya"

Hon ɗin motar Babangida yasa na kashe wayar tawa da sauri. Agogo na kalla nayi murmushin takaici kurum. Ina jin sanda Mardiyya ta fita ta buɗe mishi get ɗin ya shigo ta dawo ciki.

Ni dai ina kwance bacci ya gagari idanuna sai jefin asuba bacci mai nauyi ya ɗebeni hayaniyar su Aɗɗa'u kuma ta tasheni, a zaune nayi Sallah sabida kaina kamar zai faɗo ƙasa haka nake ji.

Ina ban ɗaki ina ɗan watsa ruwan ɗumi khalid ya dinga kiran wayata. Ina ji wayar ta ƙaraci kiɗanta ta ƙare. Da bin bango na fito na zura doguwar riga ƴar kanti na yane mayafin rigar na suri jakata da wayata na fito.

Ina fitowa na samu Babangida a zaune a falo Mardiyya ta haɗa mishi kayan kari yana karyawa.

Ina kwana?

Na gaisheshi ciki_ciki yace.

Edit with WPS Office

"Lafiya. Yauwa Baba Malam yace yana nemanki kije ki sameshi. Sannan menene dalilin da yasa yara basu je islamiyya ba jiya sannan ina kikaje?"

Kujera na samu na zauna a hankali.

Bani da lafiya ne yanzu haka ma asibiti na fito zan koma. Shine dalilin daya hana yaran zuwa islamiyya. Kuma na sanar maka asibiti naje bayan asibiti banje ko'inaba .

"Dalla maƙaryaciyar banza da wofi kin dai tafi yawon iskancinki kawai"

Jin ya soma tijara Mardiyya ta tattare ƙannenta ta shige dasu ɗaki.

"In ba iskanci ba baki da aiki sai gantali ke kenan a yawo. To jiya kuma da safe ubanme ya fitar dake daga gidan kince baki da lafiya?"

Kallonshi nake yi sai zazzare idanu yake yi yana jaraba.

Ɗinki na kai maƙota ita munafukar data faɗa ma ai ya kamata ta sanar da kai me ya kaini. Mata bata da aiki sai haddasa husuma"

"Dallah ni rufa mun baki marar tarbiyya kawai. Maigogul yana can da ƴan iskan yayyenki suna ƙoƙarin watsar mana da darajar gidanmu, bashi da aiki sai yawo da mata, yayye daga ɗan shaye_shaye sai sara suka matan kuwa wannan azo a ajjiyeta a mota wannan azo a ɗauketa duk unguwa ta ɗauka har an soma kaima  Babavmalam ƙara. Shima bansan dalilinshi na wani basu gidaba ba yana da yara ba me yasa ba su kama mishi hayar ba, ko masu kuɗin da yake kaima mata ba sai su siya mishi gidan ba, naga kawalai ai suna da kuɗi shima kaya mai tsada yake sawa. Kasarma a hannun kawalai take, ni bamma taɓa ganin kawali mara kuɗi kamar Maigogul ba. Daya ma Malam zai wani basu waje a layinmu gashi ai suna son su tuntsurar mishi da mutuncin nashi"

Ya isa haka Babangida ya isa. Ni zanje asibiti bani da lafiya daga nan zanje makaranta in samu Baba Malam ɗin"

Kallona yayi da mamaki ya nuna kanshi yace.

"Ni Sabuwa kike dakatarwa dan dai Allahn da yayi ku bakwa son gaskiya? Karya nayi ba kawalin bane waye bai sani ba? Duk wani wajen banza da macen banza yana mu'amala dasu"

Kuma a haka ya haifa ma ƴa kake aure harda zuriya a tsakani ba. Dole in aka tsaga jikin Maigogul aka tsaga na yaranka za'aga jini gudane yake gudana a jikkunansu"

Ina gama faɗar haka na nufi hanyar ɗakin yara ina hawaye duk fa lalacewar iyayena ina son abina tunda Allah da ya haliccesu shi yaso mu fito ta tsatsonsu, ina musu adda'ar Allah ya shiryesu.

Jawoni Babangida yayi ta baya ya dawo dani gabanshi. Ganin hawaye na zuba a idanuna yasa yayi farin ciki babban burinshi shine ya ganni ina kuka.

Edit with WPS Office

"Saura ki wuce shagon samari ko in ji labarin an ganki a hotel mara nutsuwa".

Turani yayi gaba wallahi dake dama jiri nake yi yaran suna ciki suka ganni na faɗo kan gadonsu yif.

A guje suka yo kaina.

"Sannu ummi sannu"

Murmushi nayi nace.

Jirine ya ka dani. Babu komai ku shirya maza ku tafi makaranta, Malama taso muje in kai ki wajen Maman Usama ki zauna acan."

Tare da yaran yauma muka fito. Su suka yi gaba ni kuma na nufi ɓarayin Hamida.

Tana kitchen tana aiki, Babangida yana ciki dan ga muryarshi inaji.

Sallama nayi Hamida ta bani izinin shiga. Ni dai labulen na ɗaga ina doge a ƙofar ɗakin

Hmm Babangida yana zaune a kafet yana wasa da jaririya ya dage sai kisa kisai yake sakarma yarinyarnan. Ganina yasa ya sake ƙaimi har yana kiran yarinyar da ƴar albarka ƴar mai tarbiyya gata salaha uwarta hafiza.

Dama asibiti zani bana jin daɗi shine nace dan Allah Malama zata zauna a wajenki gama maganinta na rana ki bata in sha biyu tayi"

"Ayya gashi nima fita zanyi zan kai yaro asibiti jiya ba mui bacci ba. Sai dai ki tafi da'ita"

Ayya to Allah ya bata lafiya sai kun dawo."

Na sakar mata labulen na riƙo Malama muka fito, su Mardiyya suna gabanmu muna biye dasu a baya har zuwa titi. Abun hawa suka hau.

Mardiyya kai tsaye ku wuce can gidansu Malama Babba ba sai kun dawo gida ba nima daga asibitin zanje gidane"

Kafin ta amsa motar ta wuce fuu. Ina tsaye ina jiran mota, Babangida yazo ya wuce mu a mota Hamida da yaranta suna cikin motar. Har sun wuce sai naga motar na dawowa da baya da baya tazo har gabanmu Hamida ta zuge tangaran din tagar motar tace.

"Har yanzu baku samu abun hawan ba kenan hala wuya abun hawan yake yi"

Kallonta nayi ta nai mun murmushi, Babangida kuwa waya ma yake yi.

Bamu samu ba tukunna, amman ga wata motar ma".

Na kama hannun Malama muka shige bus suka ja motarsu fu har suka ƙule ina kallon kwanar

Edit with WPS Office

da suka yi, wani abune ya cure ya tokaremun makoshina da ƙyar nake iya haɗiyar yawu.

A bakin asibitin muka sauka na biya kwandasta kuɗinshi na lallaɓa na shiga asibitin. Sai da na samu benci na zauna kana na ciro katin Dr Binta da wayata. Na kwafe number na kirata ringing biyu ta ɗauka.

Dr ina kwana Sabuwa ce gani a asibiti bansan a wanne ɓarayin kike ba"

Kafin ta bani amsa sai naji an zare wayar daga kunnena juyowar da zanyi naga Khalid ne yana saye cikin wata dakakkiyar farar shadda sai haskawa yake yi da halama isowarshi kenan. Wayar ya saka a kunnenshi yace..

"Zan kawota Dr "

Kit ya kashe wayar maimakon ya bani sai yasa wayar a aljihunshi, ya riƙe hannun malama ina biye dasu a baya ina lallaɓawa har zuwa bakin ofishin Dr Binta.

Ga layin mata da yawa zasu kai goma duk wannan sammakon da nayi.

Mun shiga mun sameta tana duba wata mata. Wajen zama ta nuna mun na zauna. Khalid kuma ya fita da Malama a hannunshi, ga wayata a aljahunshi.

"Baiwar Allah ke kuwa me yasa kike ƙoƙarin hallaka kanki akan ɗa namijine? Jininki yaƙi sauka kullum sai hawa yake sake yi ina jiye miki tsoron kamuwa da ciwon zuchiya, ko cutar shanyewar ɓarin jiki ya kamata ki sassautama kan ki."

Wannan mata dake zaune tace.

"Dr ina iyakar bakin ƙoƙarina wajen yakice matsaltsalun dake addabar rayuwata amman ina. Kullum in gari ya waye sai ka gamu da sabon baƙin cikin da a cikinshi zaka wuni. Ga matsalolin kishiyoyi, ga matsalolin facala, uwa uba mijin kanshi shine babbar matsalar gani da yara. To yaya zanyi?"

Take tausayin kaina ya sake kamani tare da tausayin wannan matar. Dr Binta tayi rubutu ta miƙa mata takaddar"

"Waɗannan magungunan ki ne, ki yi ƙoƙari ki siya duka kinga wancan karon baki siyesu duka ba kinga matsalar da hakan ya haifar"

Hannu tasa ta amsa ta miƙe riƙe da kanta. Dr Binta hankalinta ya dawo gareni da murmushi tace.

"Sabuwa menene yake damunki yanzu haka"?

Dr rashin bacci dare biyu bana iya ko runtsawa idanuna sun soye sosai,ga ciwon kai ya tsananta mun, ga kirjina yana bugawa da auri, sai jiri da yafi komai damuna"

"To bari in dubaki mu gani".

Edit with WPS Office

Irin duk gwaje_gwajen da tayi mini shekaran jiya shi ta sake yi mini, ta jima sosai a kaina tana dubani. Ina daga zaune tace.

"Sabuwa menene matsalarki, kishiya, miji, dangin miji, ko menene?"

Dubanta nayi cike da rauni nace.

Babu abinda baya damuna cikin abinda kika lissafo. Ke dai meke damuna?"

Numfasawa tayi tace.

"Zan faɗa miki abinda yake damunki ne domin ni dake mu haɗu mu yaƙi ciwon. Bawai dan hankalinki ya tashi ba. Hawan jinine kika kamu dashi Sabuwa, kuma a halin yanzu jininki yana sama shi yasa kike jin zuchiyarki na aiki da sauri bisa rashin ka'ida. Sannan

Kina ɗauke da ciwon damuwa wanda a turance ake kira da deepretion, duk da wannan ban tabbatar ba zan haɗa ki da Dr Layla in na gama dake.

Dole zan ɗauraki akan magani so samu ne ma a baki gado dan kina da buƙatar hutu sosai"

Tunda ta soma magana nake fitar da hawaye. Hankalin Babangida ya kwanta ya ɗaura mun cutar da zata yi ajalina ya zauna a duniya shi ya dararraje. Yau ni Sabuwa nike ɗauke da cutar hawan jini harda ciwon damuwar da nake jin ana labarin yana damun mata da yawa, harda masu kashe mazajensu da yawa ance a cikin deepretion suke sanine ba'aiba.

"Sabuwa kina jina ko? Ba kuka zaki yi ba"

Ina ji Dr"

Na faɗa bakina na rawa"

"Akwai magungunan da zan rubuta miki sai dai suna da tsada sosai. Zaki je ki siyo ki dawo in nuna miki yadda zaki yi amfani da su. Bayan nan sai in kai ki wajen Dr Layla."

Rubutunta tayi ta bani takaddar.

"Ki fita in kika tambaya za'a nuna miki ɗakin magani sai ki siyo kizo. Ki fita a hankali banda garaje"

Da ƙyar jikina na rawa na fita sai jujjuya takaddar nake yi a hannuna ina hawaye.

"Ummi"

Na jiyo muryar Malama ta ruƙunƙunemun ƙafafuna. Idanu muka haɗa da Khalid. Ya girgiza mun kaina halamar in bar kukan. Tare da miƙo hannu ya zare takaddar maganin a hannuna.

"Zauna a nan bari inje in kawo maganin ki zauna ina zuwa. Kinma karya kuwa?"

Edit with WPS Office

Kai na girgiza mishi halamar a_a na zauna a kusa da matan da ke kan layi, kusa da wata fara lutiyar mata ( kamar Mrs Bash)tana waya kuma kamar da mijinta take magana.

"To Haladu yaya zanyi ciwo na damuna zan zauna in yima yarana asarar rayuwatane, tunda kai ka nuna sai da lafiya zaka iya zama da mace? Na koma gidanmu ne inna samu lafiyar kamar yadda ka ba kishiyoyina saƙon na dawo ko ka biyoni da takaddata"

Kit ta kashe wayarta tana haki, sai kuma ta haɗe kanta a tsakankanin ƙafafunta ta sau kuka. Wallahi ta daɗe sosai tana kuka kafin ta ɗago kai ta share hawayenta, daidai wata ma'aikaciyar jinya data fito ta kira suna.

"Hassana Haladu"

Matarnan ko da ta miƙe da sauri yib ta dawo ta zauna jiri ya kayar da'ita.

Wallahi in kuka ga layin mata ƴan hawan jini abun zai baku matuƙar mamaki.

Subhanallaah kiyi a hankali baiwar Allah"

Na faɗa a hankali dan jikina ni kaina rawa yake yi sosai.

"To nagode kinga jirine ya ɗebeni gani ba kaɗanba kamar Mrs Bash ban dai bigeki ba ko?

A_ahhh baki bigeni ba. Allah ya ƙara sauƙi"

Nan ta tafi ta barni a raina nace.

Oh mata na ganin bone, maza kenan da yawansu dai basu fiye imani ba.

Dawowar Khalid ne ya dawo dani daga dogon tunanin da ya daɗe da aurena.

"Taso mu shiga na karɓa miki maganin. Hawan jini ke damunki haka Sabuwa amman da a hakan kika ƙi a duba lafiyar taki? Taso muje, Malama zo in riƙeki.

Da sauri ta sauka a jikina tana murmushi taje ta riƙe hannun Khalid. Bayansu nabi muka koma ofishin Dr Binta anan muka tarar da wannan baiwar Allahn ana rubuta mata magani, Dr Binta nayi tana mata nasiha akan ta dinga ƙoƙarin rage ma zuchiyarta nauyin damuwoyi ko dan tseratar da rayuwarta.

"Ga magungunan ki je ki siyo ki dawo"

Ta miƙa mata takaddar ta fita.

"Dr tare da kai aka dawo? Gaskiya kana ji da Sabuwa sosai ina kishi fa"

Ta faɗa tana dariya, shima dariyar yayi ya zube mata magungunan a gabanta.

"Hawan jinine ashe yake damun nata? Yanzu kowa sai kiji hawan jini hawan jini  dai"

Edit with WPS Office

"Kai dai bari Dr nata yayi tsanani sosai so samu ma in bata gado ta huta ne fa ba wai in sallameta ba gaskiya "

A_a Dr Binta dan Allah ki sallameni nayi miki alƙawarin zan huta a gida sosai"

Dr Binta ta kalli Khalid ya gyaɗa mata kai halamar ta barni ɗin kamar yadda na faɗa.

Nuna mun yadda zan sha magungunan tayi, tare da rubuta yadda zan sha a ko wanne ledar magani kana tace.

"Nan da sati biyu sai ki dawo kuma. Ki tabbatar kin dawo ɗin. Sannan Dr Layla bata nan amman jibi tananan kizo jibi ofishinnan nawa sai in rakaki.

Da kinji halamar jikinki babu daɗi ki kirani ko Khalid. Kuma kar ki dinga kaɗaicewa"

To Dr nagode sosai. Amman hayaniyar ce ban fiye so ba, ba ko da yaushe ma nake son ganin mutum a kusa dani ba"

Kallona tayi tayi murmushi tace.

"Babu komai. Amman ki daure ki dinga shiga cikin mutane dai. Zaki iya tafiya Allah ya baki lafiya "

Miƙewa nayi muka fito, Khalid na riƙe da Malama har harabar asibitin.

Wata ƙatuwar mota ya nuna mun fara.

"Ga motata muje in kai ku gida"

Ban isa in yi musu ba jiri nake ji sosai ga yinwa da nake ji.

A bayan motar muka zauna ni da malama nayi lamo sanyin a.c da ƙamshi na dukan hancina

Wacce unguwar kike?"

Kargo zaka kaini gidanmu zanje"

Baice dani komai ba  ya ja motar muka fice a titi. Mun yi tafiya mai ɗan tsayi sai ya tsaya a wani wajen cin abinci.

"Bari in siyo miki abinci, Babyna kina son shawarma?"

Ya tambayi Malama ta ɗaga mishi kai halamar e zata ci.

Ya saka kai ya fita ya ɗan jima gaskiya sai gashi da ƙatuwar farar leda mai cike da kayan ciye_ciye ya miƙo mun na karba da godiya.

"Ki bata shawarmanta ta ci. Akwai goyot nasan kina mutuwar son yogot"

Edit with WPS Office

Ban ce mishi uffan ba na buɗe ledar na ciro shawarma da zafinta na miƙa ma Malama na zaro habeeb yogot na buɗe ina sha a hankali yana ta sharara gudu.

A guje muka wuce majalisar su Babangida babu kowa dake ranane sai zuwa yamma zata batse.

Ta wani lungu nace ya tsaya in sauka a nan.

Tsayawa yayi na ɓalle murfin motar na fito.

Wayata da kuɗi masu kauri ya haɗa ya miƙo mun.

"Sai mun yi waya ki kula da shan magungunan ki akan lokaci. Kuma zan yi ƙoƙarin kiranki in tunasar dake ko da kin mance.

Godiya nayi mishi Malama sai adabo take ta yi mishi. Muka shiga lungun da muna ɓullowa sai ga gidanmu.

Motar ƴan sanda na gani a ƙofar gidan ga jama'a sun taru na unguwa Baba Malam ma yana wajen. Maigogul yana riƙe da ƙugunshi yaci ado na kece raini.

To wani tashin hankalin ne kenan ya sake faruwa?

Ohh ni Sabuwa na dai shiga uku.

MRS BUKHARI

"

*Shin yar'uwa kina da labarin company na Oriflame?*

*Da k'arfin zuciya da guiwa na ke muku shunen inda zaku samu kayan da na zano a kasa cikin saukakkan farashi.*

Edit with WPS Office

🎈sinadarin tsarki me farin jini(Feminnille wash)🧴

🎈Mayuka masu inganci

🎈turare

🎈man goge Baki(toothpaste)

🎈Man gyaran gashi

Da sauransu......

*Idan kina bukatar Oriflame products ko wanne irin ne, ko Kuma kina sha'awar yin register da su*. *Ki tuntubi wnn number

08022059556

Akwai tsarin adashe na biya a hankali.me sha'awa ta shiga wnn link din👇🏽

https://chat.whatsapp.com/HLPG9S1Muh19s2RKVYf2Jp

IDAN KAYA YA GAJI....

GAMMO MA YA GAJI

BADI'AT IBRAHIM MRS BUKHARI B4B GIDAN KAMSHI

LITTAFI NA FARKO

SHAFI NA SHA BIYU

Edit with WPS Office

Gabana ya yanke ya faɗi da jan ƙafa na ƙaraso inda Malam yake tsaye da wani ɗan sanda.

Labbai ce ta iso ta karɓe ledar hannuna "

"Sabuwa ja hannun ƴarki ku shiga gida maza"

Cewar Baba Malam. Ina isa zaure sai ga Rakiya ƴan sanda biyu mata sun taso ƙeyarta, da Ma'aru Gaza suna biye dasu. Tare dani aka sake fitowa Hauwa tana daga bakin ƙofar zaure.

"Ku sata a gaban mota, ku ku shiga baya, Rita ki zauna da'ita a gaba."

Cewar ɗan sandan da suke tattaunawa da Baba Malam. Gaza yace

"Rakiya zamu je muma yanzu. Duk yacce za'ai zaki fito yau yau ki dena eh ta da hankalinki eh amfanin iskanci eh ai yawane dashi, kinsan Allah yau zaki fito. Ku kuma kutumar ubanme kuka taru kuna kallo eh wallahi in baku watse ba sai naci..... ku ubanku yaci....ehh"

Ya dinga ihu yana danno ashariya manya_manya harda wawurar sanda. Kafin kace me duk mata da yaran da suka taru suka watse da gudu.

Baƙin ciki kamar zai kasheni haka aka wuce da Rakiya a motar ƴan sanda. Nasan dai bazai wuce ace tasai kayan sata ba. Wannan sana'a tata ta kayi nayi ba dai haɗari ba"

"Malam kaga ni dai ko? Ana maganar neman gidan haya ga fitinar da mata suka kunno mana kuma. Waini da me zanji ne ma? Masifu goma da ashirin"

Cewar maigogul kenan. Ni dai naji ya ambaci gidan haya. Duk muna tsaye fa to me za'ayi da gidan haya kuma?

"Yanzu dai Maigogul kai da Labbai ko Adama ko Sabuwa ku bi bayansu, shi Gaza kar yaje gudun kada a samu matsala"

"Ah Dattijo bi a hankali ya uwata tana hannun kwalawa kace kar inje? Bar ganina ɗan iska eh nasan darajar uwata eh. Ka bini a hankali kar kayi zaton kona mance da ƙullin da aka ƙulle ne, inma kana tunanin ya kuntu, ehh naku ne ya kuntu mu namu yananan tamau. Labbai dallah ki tawo mu bi sawunta in dai dan wannan Dattijonne bai ƙi a kaita kurkuku ba ma" wannan kuma da Maigogul yake yi.

Gaza da Labbai suka gangara suna tafe Gaza na bubbuɗewa. Baba Malam ya girgiza kai yace.

"Allah ya shirya, Allah kuma ya kiyaye na gaba ya kamata ka bisu, duk yadda ake ciki sai ka sanar dani ko a waya ne"

"To to Malam in akwai ɗari biyar bani. Gidan ko abinci yau bamu ci ba sabida babu kuɗin, kuɗin motar da zan tafi ma ofishin ƴan sandan bani dashi"

Malam ya bashi dubu biyu ya karɓa yana washe baki ya gangara malamu_malum dinshi na cika

Edit with WPS Office

da iska.

"Lolo banga kular abinci a hannunki ba ko itace a ledar da Labbai ta karɓa?"

Maigogul ya juyo yana magana dani kai kawai na ɗaga mishi wallahi in buɗe baki inyi magana na kasa dan baƙin ciki.

Haka ya juya yaci gaba da tafiya.

"Zo tawo Sabuwa"

Cewar Baba Malam. Su Aisha da Qamariya sukai shigewarsu gida. Keɓewa mu ka yi da Baba Malam ina kuka.

"Kiyi haƙuri Sabuwa, na aika a kirawo ki kinzo kin tarar da wannan abu maras daɗi. Dama kiran akan na ba Maigogul nera dubu Shittin nace ya kama haya a wata unguwar su tashi. Sabida abubbuwane dai marasa daɗi ga maƙota na ƙorafin cewar su karnuka na damunsu da haushi, ga yawan rigima da faɗace_faɗacen su Rakiya, ga motoci dake zurubtu a layinnan za'a iya gurbata musu tarbiyar yara. Shine nace su tashi. Harma ya samu ɗaki yace a can unguwarku Zai. Tun jiya suna kan tattare kayansu ne fa kuma motar ƴan sanda tazo ta tafi da gyatumarku. Wannan shine dalilin kiran ki dena kuka ki shiga cikin gida ki zauna da ƴan uwanki"

Da kuka ƙaƙas na shiga gidanmu ina bin bango. Idanma Babangida bai kasheni ba baƙin cikin gidanmu kaɗai ya isheni.

Na shiga na samu Hauwa a tsakar gida duk ta fito da kayan ɗakinta ita dasu Sa'ada sunata haɗawa. Harara ta buga mun tace.

"Aikin banza aikin wofi dama uban mijinki ya bamu gidane dan a kwana biyu ya tozartamu. Danma ubanku ba mai xuchiya bane da me zai yi da dubu sittin ɗinshi"

Uzairu zuchiyata dake zaune a kujera yana goge kafarshi kwaskwarimar daya saba yace.

"A_a fa Hauwa kar ki zargi malam matsala daga gidannanne. Ko ni jiya ina taɗi Maigogul yaxo wucewa da waɗannan tsofaffin karuwan da suka kwana a gidannan. Ji nayi kamar ƙasa ta tsage in faɗa. Ai yama yi ƙoƙari duk cikinmu waye mai zuchiyar yi? Ni wallahi ko ina dashi bazan ba tunda hakkinmu a wuyan Maigogul yake, na gwammaci in sai wandon jeans da ƴar rigata ta shiga gari ko banza a yi mun kallon mutunci"

Ashe duk wannan rikicin da akeyi Uzairu zuchiyata yana cikin gidan shine ko leƙowa wajen baiyi ba? Duk ɗiban albarka irin na Gaza ya fito harma yabi sahun Rakiya. Ohh ni Sabuwa.

Aisha ta cabke da cewa.

"Wallahi nima ko ƙwandala bazan iya ba yarwa da sunan gyara gida ba su Rakiya da Hauwa da zaman gidan ya kama dole dai sai su san yadda zasui, in naga dama daga nan sai ɗakin saurayina wallahi in je in bararraje in miƙe ƙafa wannan masifa da me tayi kama ne"

Edit with WPS Office

Hmmm".

Kawai nace na yi shigewata cikin ɗakinmu magazin na kwance a katifa magashiyan ashe shima yananan yau, ga Salaha a zaune tana daddanna wayarta.

"Ah Lolo kece kika zo?

Nima fa ko awa banyi da shigowa garin ba nazo na tarar da wannan tashin hankali"

Zama nayi jagwab a katifar jirine ya karamun gudu.

Kinga miƙon ledar can in ci abinci in sha magani daga asibiti nake"

Ledar ta jawo mun na buɗe soyayyar shinkafa mai wadataccen hanta ce a cikin ci ka yar ( take away) sai kaza gashasshiya guda a wata leda mai ƙyalli, ragowar jus ne da tarkacen biskit.

Shinkafar na soma turawa da ƙyar ba dan daɗi ba sai dan inaso in sha magani in ɗan huta.

Salaha tayi maza ta matso ta tsoma hannu muka ci gaba da ci, loma uku ma nayi na bar mata ita da Aisha da ta shigo yanzu, kazar ko ko a bakina su na ba suka hau rabo.

"Magazin magazin ka tashi mu ƙarasa fita da katifa. Lolo an faɗa miki mun samu gida a unguwarmu ko?"

Cewar Aisha dake tsaye a kan magazin tana dukan ƙafarshi.

Sai da na watsa magungunana a bakina kana na kora da ragowar yogot ɗina na haɗiye sannan nace.

Wai me Rakiya tayi ne tukunna?"

"Ke dan uwarki ina kwance shine kike tashina danma nazo na kwanta a wannan ƙazamar katifar taku mai warin datti, wannan gidan muddin kana cikinshi babu kai babu kwanciyar hankali. Kinsan Allah Lolo nifa naji jin daɗin zaman gidan ɗan kande fiye da gidannan"

In ji mazagin daya taso kamar zai daki Aisha.

"Shegiya siririya kawai, ciki fal maganin tarin yara"

Idanu muka haɗa dashi yace.

" Alafiya Lolo. Wuya a  daji, wuya a hannun maza, wuya a hannunki Sabuwa mai sabon aiki. Sai kika zo kika samu gida a hautsine ko?

Salaha bani tawa kazar in lasa"

Miko mai tayi yayi wuf ya diro tare da hankaɗe Aisha ta faɗa ma Salaha jiki.

"Allah ya isa"

Edit with WPS Office

Ai kuwa kafin ta rufe bakin ya watsa mata mari nan kokawa ta kaure a tsakaninsu kasancewar magazin kamar a bige yake yayi dibge_dibge har ƙasa Aisha ta kaishi. Uzairu zuchiyata na kira ya shigo da gudu ya rufe Aisha da duka magazin ya samu ya tashi.

"Ke wai nike kika  doka dan kinga na taka rabarma na zame? Wallahi zaki gane kurenki yau sai na kasheki uban kowa ya huta"

Wuƙa ya zaro a ƙugunshi nayi sauri na shiga tsakaninsu Uzairu  zuchiyata ya fice a guje. Salaha kuwa sai yagar kazarta take yi hankali kwance.

Meye haka magazin ya da wuƙa haka tsirara ƴar uwar taka zaka kashe? Kema meye na dambe dashi kinsan kanwarku bata juƙuwa kofi ɗaya ai. Magazin ɗauki kazarnan ka fice muma yanzu zamu bar gidan"

Yana daga bayana yana zare ido yace.

"Wallahi taci darajarki. Ke amma in muka haɗu a lungu saina miki illah  ko insa yarana su keta mun ke"

Wuƙar ya mayar jikinshi ya ɗauki kasonshi ya fice yana daddanno ashariya ɗuma_ɗuma.

Zama nayi ina mayar da numfashi.

"Kema Aisha ki dinga kiyayar magazin sanin kanki ne ba mutunci bane dashi ni shi yasa bansa baki ba bazan manta yankan da ya taɓa yi mun ba kin ganshi shekara shida kenan."

Salaha ta nunq mata wajen yankan. Ni dai nace.

Ni me Rakiya tayi ne wai ku faɗa mun"

Aisha tace"

"Kayan sata fa ta siya Lolo bama yanzu bane tun muna can layinmu yanzu ne dai da aka kama ɓarauniyar da take saka yara sato mata kayayyakin da aka tambayeta a ina take siyarwa shine ta ce qajen Rakiya kayi nayi take kaiwa ta siyar shine akazo aka naɗe ta. Shi kuma sirikinki yace mu tashi mai a gida ya ba Maigogul nera dubu shittin ya kama ɗaki biyu mu koma yanzu fa Adama da Rahama sunje ɗakko motar kayane gidan su ummi baƙa anan aka samu ɗaki wai"

Idanuna na lumshe kafin in yi magana wayata tayi ruri Gaza ke kirana da sauri na ɗauka.

"Ke Lolo Rakiya fa ta wuce bayan kanta an garƙameta a sell ai kes ɗinta sai dai kuyi adda'a kar su ci yari. Dattijo zai dawo ya raka ku can gidan su ummi baƙa daya kama, ni kam na shiga gari dan babu beli a lamarin. Amman dai akwai wani babban Alhaji da muke yawan yima aiki wajenshi na nufa ko zai sa daga sama a saketa. Eh itama ai maganinta wallahi duk da wannan Dattijon mai matacciyar zuchiya shi ya ja mata, rayuwa ta baƙin talauci in bata nema ba mutuwa ake son tayi ne?"

Edit with WPS Office

Da bambami ya kashe wayar.

Innalillihi wa'inna ilayhil rajiun. Wannan masifar da me tayi kama. Wasu hawayen baƙin cikine suka zubo mini na kasa cewa komai har Hauwa dake tsakar gida taji abinda Gaza yace dan a firi na saka wayar.

Ni dai har su Adama suka shigo bana magana gefe na matsa inata sauke numfashi da ƙyar gashi ko sallah banyi ba. Haka dai aka gama kwashe komai muka fito Malama na riƙe a hannun Salaha duk muka fito, dasu Layuza da yanzu isowarta. Aika Aisha nayi ta je makaranta ta kaima Baba  Malam ɗan mabudin  gidan, daga nan muka yi titi dan tare abun hawa, a titin muka ga Labbai da Maigogul sun tare mai motar kayan maigogul na magana dashi, su Adama sune a gaban motar kayan. Bus muka shiga dukkanmu ta kaimu har Zai ni dai na zaro kuɗin na biya muka sakko.

"Ai da kin biya iya nasu Lolo Allah bai hana mu abinda zamu biya ma tamu uwar ba. Duk wannan tozarcin ai ke kika ja mana"

Cewar Layuza da take baƙin ciki dani tun muna ƴan mata kasancewar na taso da bala'in farin jinin samari masu hannu da shuni. Har gobe Layuza bata da maƙiyiya kamar ni a kab gidan.

"Ta baya ta rago kenan. Ni Layuza mamaki kike bani baga can ɗaki a gidan naki mijin ba ki ɗauki uwarki da ƙannenki su koma can da zama mana. Tunda ko wannan gidan surukin Lolo ne dai ya kama, ai kinsan uban naki bashi da ta gaban ƙirjin da zai iya kama musu mtsw aikin banza"

Cewar Labbai kenan. Layuza tace.

"Ni kike faɗama magana haka dan uwarki?"

"In na faɗa miki abinda yafi haka kina da abinda zaki yi ne?"

Labbai tayi kanta a zabure itama ta zaburo. Ni ɗince dai na shiga tsakaninsu buɗar bakin Hauwa tace.

"Layuza rabu da ita zawarci kinsan zafine dashi gashi jiya aka zo mana da labarin Badaru yayo aure gashi ta dawo layin zasu dinga haɗuwa da matar wannan kaɗai ya isheta, ga uwarsu a kulle a wajen ƴan sanda"

Jaye Layuza Qamriyya tayi suka wuce fu. Tsaki kawai nayi nace.

Gida kullum mu kenan a cikin raba hali abun kunya fal cikinmu tur wallahi."

Na sake jan tsaki na wuce a hankali, su Adama har sun gama fito da kayan Rakiya dama ba yawa garesu ba daga katifa sai jakunkunan kayansu da katon keji da karnukan Gaza a ciki.

Labbai ba kayanki bane a rumfar gidan Malam Habu ba?"

Na nuna ma labbai kayan da hannuna. Adama tayi saurin cewa.

Edit with WPS Office

"Nata ne muma haka muka ce da muka gani. Ba ance Badaru yayi aure ba"

Labbai ta lailayo ashariya ta danna tace.

"Shine dan yayo aure bazaii kirani in kwashe kayana ba ɗan ta abu ta kazan..."

Jirine yake neman dokeni in faɗi sai kawai na nemi dakali na zauna ina nishi.

Haka dai su Adama suka tarkato ma Labbai kayanta aka shiga dashi cikin gidansu Ummi ɓaka.

Ina jaye da ƙafafuwana da suke ɗaukar gangar jikina da ƙyar muka shiga gidan da sallama.

Duk matan gidan rabi da kwata suna tsakar gidan amman babu wacce ta amsa sallamarmu babu wacce ta kallemu.

Maigogul muka hango ya leƙo a cikin wani ɗaki dake lungu. Ganinshi yasa su Adama suka soma ɗibar kaya zuwa cikin lungun. Ko a lungun ɗakunane na mata yayi takwas.

Ina lekawa sai naga ai ciki da falo ne, su Adama da suka shigo da doguwar kujerar Labbai da ƙyar lungun suma sai suka dire mukai cirki_cirko haka suma su Layuza da Hauwa da suka ƙaraso da tarkacensu.

"Wai me kake nufi Maigogul ciki da falo ka kama mana ni da Rakiya mu zauna a ciki ko kana nufin nata ne wannan akwai nawa?"

Hauwa ta faɗa da jaraba har tana girgiza. Da lumana Maigogul yace.

"Uwarɗakin ta Rakiya ce falon kuma naki ayi haƙuri a zauna a haka a hakanma da ƙyar na samu hayar in aka samu masu can ɗakin suna tashi sai ke in kama miki. Inma basu tashi ba Hauwa haka zaku zauna iyakar abinda ya samu kenan. Amman dake jarabarku sai ku babu godiyar Allah dole ku magantu. Kinyi naki saura na Rakiya in ta dawo. To meye ma a ciki naga dai nine mijinku ko?

Hauwa tace.

"Bataliyar yarannan muyi yaya dasu duk tare zamu dinga gwamutsuwa kenan?"

Cikin masifa yace.

"Hauwa yaya kike son inyi ne wai? Yarannan duk randa nake uwar dakin Rakiya sai su dawo falo wajenki, duk ranar da a falo nake sai su shige wajen ita Rakiyan kafin dai in samu a gyara shi wancan gidan namu mu koma."

Yana faɗar haka yayi ficewarshi, binshi nayi da'idanu kawai har ya ɓace mun. To ya Hauwa ta'iya zage_zage da tur da Maigogul babu irin wanda bata yi ba. Mu muka soma shigewa da kayanmu tunda mune a uwar ɗaki. Aka kafa gadon Labbai na samu na kwanta zazzaɓi ne sosai a jikina, kujerar ma Allah yasa ta samu wajen zama, harda ƴar durowa ta zuba kaya, sai tarkace kayan

Edit with WPS Office

kitchen na Labbai dai su kam ƙarƙashin gado aka tutturasu, ɗan filin tsakar ɗakin baifi mutum biyu su kwanta ba ko yaya zasu yi wannan zama oho dai. A haka baccin wahala na magani ya kwasheni bani na farka ba sai bayan la'asar. Alwala na fita nayi a kofar ɗaki na koma ciki nayi azahar nayi la'asar. Nan aka shiga tattaunawa ya za'ayi batun Rakiya ya za'ayi dai. Mun baro gidan dab magriba akan su zawarawan zasu ma samarinsu magana ko akwai wata hanya, Maigogul ma fafutukar daya fita yi kenan. A haka dai muka rabu naba Aisha kuɗi tayi musu girki a kaima Rakiya zuwa gobe muka yi dasu zamu je can ofishin ƴan sandan.

Haka na koma gida, ina shiga na zube a kujera, sai da su Mardiyya suka dawo ta sama mana abinda muka saka a baki ni da malama, muka sha magungunanmu a daddafe nayi isha sabida maganin akwai na bacci ko wanka bam ba bacci ya ɗebeni nayi bacci har sai da Mardiyya ta zo ta tasheni.

Na tashi lokacin karfe bakwai saura na makara, a zaune nayi sallah sabida ciwon kai. Ina zaune akan sallaya nayi tagumi Mardiyya ta shigo da tire ɗauke da tea da buredi mai yanka da wainar ƙwai.."

"Ummi ya jikin naki?"

Da sauƙi Mardiyya, ya banga kun yi shirin nakaranta ba?"

A hankali nake magana dan kamar kaina zai ɓalle .

"Sabida baki da lafiya ne zamu zauna"

A_a ku shirya ku tafi zan kira Labbai tazo yanzu"

Jin nace hakane yasa har ta yadda taje ta shirya suka karya, sun tafi da mintuna bai fi goma ba Labbai da Uzairu Zuchiyata duka karaso a lokacin babu yadda nake ido ma da ƙyar nake buɗewa, haka na wuni bacci, sai dai in tashi in yi sallah in sha magani in ci abinci in koma bacci kawai.

Labbai ta kira Salaha tazo suka haɗu su uku su kai ta mun hidima, ganin jikin nawa har zuwa dare ya tsananta yaran ma duk hankalinsu ya tashi shine suka sanarma da Babangida ga halin da ake ciki.

Wajajen taran dare ne har kan ya ɗan sassauto mun na samu na zauna ina shan kunu.

"Lolo ɗazu an kawo miki ɗinkinki daga maƙota. Babangida mun kirashi mun sanar mishi babu yadda kike kinsan me yace mun kafin ya datse wayarshi?"

Kaina kawai na girgiza ma Labbai idanuna a lumshe.

"Cewa yayi ko yazo babu abinda zai miki shi ba likita bane, inda ya dace a baki maganin kinje. Yana faɗar haka ya kashe wayarshi. Kishiyarki ma tun magriba na aiki Mardiyya ta sanar mata mitsiyaciyar har yanzu bata leƙo ba"

Idanuna a lumshe murmushi kawai nayi ma Labbai nace ma Salaha.

Edit with WPS Office

Bani magungunan in sha Salaha"

Ɓaɓɓallowa tayi ta bani na watsa dukka a bakina na kora da ruwan tea da nake sha. Uzairu zuchiyata yace.

"Lolo wai sha'awar mutuwa kike yi ne niman? Baifa kamata ki dinga uzurama kanki akan tunanin tsohon maras mutuncin mijinnan ba. In nice a irin wannan gidan kinsan Allah babu abinda zai sha mun kai. Shi yasa kuka ganni wallahi bazan taɓa auren ƴar talakawa ba yadda nake da kyannan. Ni nama fi sha'awar manyan mata musamman macen da miji ya mutu ya barta da dukiya ta rasa yadda zata yi da dukiyar, sai in aureta mu taya ta muci. Zaku huta wato a lokacin gaskiya kambu wato zan shagwaɓaku ne da nera Allah"

Dariya muka yi dan dole Uzairu zuchiyata bashi da dama wajen shegen son kuɗi da kwaɗayin rayuwar hutu. Zuchiya fal buri babu aikin fari balle na baƙi.

Ya batun kuma Rakiya?"

Na tambaya ina mayar da numfashi"

"Uhm lamarin babbane, Maigogul yaje da manyan mutane sun kai uku, me gidan Gaza ma yaje amman wallahi anƙi sakinsu, belima a bayar abu yaci tura kotu ma za'a turasu yanzu haka dai a haka ake.

Idanu na kuma lumshewa ina jin yadda zuchiyata take aiki da sauri sauri

Babangida ne ya shigo daidai lokacin da Khalid yake kiran wayata.

Da fara'a su Salaha suka gaisheshi, shi ko ya haɗe girar sama data ƙasa. Uzairu zuchiyata yana gefe ya lalace a waya sai soyayya yake zubama. Wani mugun kallo Babangida ya watsa mishi kafin ya buɗe bakinshi yace.

"Lafiya"

Kaɗai ce ta fito a bakinshi hankalinshi na kan wayata da ake kira gabana sai faɗuwa yake yi dan ba ƙaramin aikin Babangida bane ya ɗauki wayar, ko ya haddace number ya kira a wayarshi ba shida da aiki sai bin diddigi.

Daga tsaye yace.

"Sabuwa ya jikin. Wai da kika je asibitin me ma akace yake damunki ne ma?"

Kaina na ɗaga sama hawayen baƙin cikine yake shirin zubo mun

Da sauƙi maleria ne yake damuna"

Ɗan taɓe baki yayi kawai. Yace

"Labbai sai yaushe zaku tafi dare nata yi. Sannan shi wannan ƙaton me yake yi a cikinku haka

Edit with WPS Office

goɗai_goɗai? Ya batun Rakiya an samu an ba da belinta kuwa?".

Idanu na buɗe na kalli Babangida, shima ni ɗin yake kallo fes.

"Ai dake bata da lafiya zamu ɗan kwana biyu anan kafin Allah ya bata lafiya. Rakiya kuma ba'a ba da belinta ba tukunna. Ita sawun ɓarawo ma ta taka"

Ai sai  ya sake yin kicin kicin yace.

"Gobe dai sai ku koma tunda yanzu dare yayi.

Shi kam Uzairu zuchiyata ya tafi gida wannan ba koyarwar islama bace. Duk da dai ku baku san wannan karatun ba.

Jibi akwai baƙi da yawa a gidan gaskiya"

Yana faɗan  haka ya fice ina jiyoshi yana kwaɗama Mardiyya kira.

Khalid ne ya kuma kirana.

"Yauwa Sabuwa tun safe mai number nan yake ta kira. Dana ɗauka sai naji namijine"

Idanu na ɗan zare nace.

Me yace miki?"

"A_a cewa yayi shi likita ne dama ya bugo yaji jikin naki ne. Sai na faɗa mushi yanayin jikin naki yace dai  hutu sosai kike buƙata ki zauna ki nutsu sosai ki huta"

Ɓoyayyar ajjiyar zuchiya na sauke na zame na kwanta.

Ku kwana anan kawai abinku Babangida ba dawowa zai yi ba. Mardiyya da Malama ma su shigo nan Uzairu zuchiyata ya tafi ɗakin su Adɗa'u ya kwana dasu. Uzairu zuchiyata ko zaka tafi gidane?"

"Wa in tafi ina?

Wallahi inanan mijinki bai isa ya hanani kwana ba a gidannan ba. Da dai aure bai haɗa bane amman tunda aure ya haɗa wallahi yau dai zan yi lafiyayyen bacci "

Mikewa yayi ya fice abunshi.

Kwanciya su Labbai suka yi basu daɗe ba su kayi baccinsu ga ac nata basu sassanyar iska. Nima har bacci ya soma dibana Khalid ya kuma kira, da sauri na ɗaga.

Ajjiyar zuchiya ya sauke baice komai ba.

Me yasa kake ta kirana?".

Edit with WPS Office

Na tambayeshi da muryar ciwo.

"Sabida sanin mahinmancinki, da damuwa da son jn lafiyarki. Baki san wunin yau yadda na kasance bane daga lokacin da ƴar uwarki tace jikinki ya tsananta. Amman yaya jikin?"

Idanuna na lumshe kawai, na tuno Babangida da ko a jikinshi ciwon da nake yi.

Da sauƙi, kar ka sake kirana a waya da daddare koma menene in mijina na kusa fa, ko so kake ka kashe mun aure ne?"

Shiru yayi kamar ruwa ya cinyeshi nayi zaton network ne ma sai caan ya sauke ajjiyar zuchiya yace

"Aimun afuwa bazan sake ba. Sai anjima"

Kit ya kashe wayarshi da idanu na bi wayar sai banji daɗin yadda ranshi ya ɓaci ba. Ajjiye wayar nayi baccin magani mai nauyi ya sureni bani na farka ba sai da Salaha ta tasheni.

Nayi Sallah na koma gado ina kwance ido biyu har su Mardiyya suka fito daga banɗakina Mardiyya tayi ma Malama wanka. Sabida gudun sanyi a banɗakin aka saka mata kaya ma, su Labbai kuma suna kitchen.

Malama ta hayo gadon, na jawota jikina ina tambayar nata jikin. Aɗɗa'u da Aminu suka gaisheni da jiki..

"Ummi ya jikin naki?" Cewar Mardiyya da take matsa mun yatsun ƙafata.

Da sauƙi har yanzu baku shirya zuwa makaranta ba? Yau ba islamiyya amman akwai taron bikin Babanku acan gidan Kawu in kuka dawo sai ku shirya kuje ni bana jin daɗi da tare zamu je"

Haɗe rai Mardiyya tayi tace.

"Ni babu inda zanje ummi, gara nayi baccina"

Aɗɗa'u da Aminu suma suka ce sufa ba zasu je ba. Na dubesu da mamaki wai suma uwarsu suke tayawa kishi.

To naji kuje maza ku shirya in Labbai sun gama abinci su baku kuci"

Fita suka yi suka bar Malama a kan gado tayi lamo.

Sun tafi ba'a daɗe ba sai ga Salaha da ɗanwake cikin tire yaji dafaffen ƙwai har da kabeji ga yaji da soyayyen kifi, sai suka dama kunun tsamiya.

"Sakko Lolo dake da autarki. Yakamata dai ki yima yarinyarnan ƙani".

Ɗan dariya nayi na sakko na zauna..

Edit with WPS Office

Ke dai kya yi mata amman ni da haihuwa ai nayi mata adabo, waɗannan ma Allah yayi musu albarka "

Labbai tace

"Wallahi ni fa ko yanzu nayi aure bazan wani haihu ba waɗanda na haifa a gidan Badaru ma sun isa. Family planning zanje inyi tun kan in shiga gidan miƙewa zanyi in ci amarci"

Sai da na hadiye ɗanwaken dana saka a bakina nace.

A gidan Malam Habun ne zaki ci amarcin shi da yake da zugar ƴaƴa ga kishiyoyi? Dan Allah Labbai ke sai ki auri wannan tsohon?"

Dariya muka saka har da ita Labbai ɗin har tana kwarewa sai da ta sha ruwa.

Babangida ne ya turo ƙofa ya shigo tinƙis tinƙis ya ci uwar kwalliya ya fito a ango sak sai ƙamshi yake busawa.

A haka kamar mutum mai nagarta, ammman nagarta a rigarshi kawai take. Uzairu zuchiyata dai yana falo nasan sun haɗu da Babangida.

"Ku bamu waje zanyi magana da Sabuwa"

Ya faɗa a gadarance, tashi suka yi suka fice, ya tako yazo ya zauna a bakin gado Malama ta tashi ta tafi wajennshi harda ɗan wakenta a hannu.

"Ah kar ki ɓata mun kwalliyata mai tsada jeki wajen uwarki"

Ya riƙe hannun da take riƙe da ɗanwaken ya turota.

"Am Sabuwa ya jikin? Ko da yake da sauƙi tunda har gashi ke da ƴan uwanki kuna cin abinci. Hmm an samu na gwamnati su Labbai harda ƙwarewa. Shi kuma wancan wan naki yana falo ya bararraje yana kallo ga tea da biredi ya tusa a gaba.

Wa billahillazi inna dawo na sameshi a gidannan yau kinsan Allah sai kin bishi kema. Nifa na gaji da abubuwan kunyarku.

Yanzu kamar fa ace nine sai in kwashi kafa in tafi gidan Alawaiyya in kwana hankali kwance.

Ai Sabuwa duk mai hankali bazai yi wannan aikin ba.

Ba wannan ba dama kwangilar dafa abinci zan baki gobe Amarya zata tare shine nake so ga kuɗi kiyi musu abinci mai kyau ga dubu ɗari in ma bai isa ba ki kirani"

Murmusawa nayi wani ƙwallon kishi yayi tsaye a ƙirjina. Kallonshi na dinga yi ina murmushi a zahiri a baɗini kuma wuta ce bal bal bal take ci a zuchiyata.

Amman kasan bani da lafiya ko? Kana ganin yanayin kondishon ɗina sai su Labbai ne suke mun

Edit with WPS Office

aikace_aikacen gida. Me zai hana ka ba Hamida tayi musu".

"A_a Malama ni banga wani kondishon ba wallahi  kada ki yi mun sharri gaki gadagau kina cin ɗanwake. Hamida ai kinsan jego take yi ko, ya zan haɗata da aiki. Ke ɗince zaki yi dole ko su Labbai sa taya ki sai su zauna dan dai a samu a fita kunya in yaso goben sa koma"

Magana yaga inaso in yi yayi saurin tashi.

"A_a Sabuwa kar ki tunzurani dan kinga ina lallaɓaki dole zaki yi wannan girki ga kuɗinnan kuma da kaji za'ayi ba da jan nama ba Amaryar bata cin jan nama"

Rafar kudin ya jefo kan cinyata daga tsaye ya fice.

"Aikin banza duk abinda zaka ma Sabuwa babu godiyar Allah ga ƴan uwanta duk an sako su sabida rashin tarbiyya. Yarinya sai mugun taurin kai. Baba Malam dinma dake daka ta rawarki ya soma gajiya da abun kunyarku"

Har ya fice yana bambamin masifa idanu na lumshe kawai na daure na ci gaba da cin abincinna har su Salaha suka shigo.

Mrs Bukhari

To wannan na gobe ne juma'a.

Asabar da Lahadi bazan samu fitowa ba sabida ina da aikin haɗama Amare show glass na turaren wuta aikin da yawa.

Sai zuwa monday in sha ALLAH zamu ci gaba.

A daure dai aimun uziri.

*Shin yar'uwa kina da labarin company na Oriflame?*

*Da k'arfin zuciya da guiwa na ke muku shunen inda zaku samu kayan da na zano a kasa cikin saukakkan farashi.*

🎈sinadarin tsarki me farin jini(Feminnille wash)🧴

🎈Mayuka masu inganci

🎈turare

Edit with WPS Office

🎈man goge Baki(toothpaste)

🎈Man gyaran gashi

Da sauransu......

*Idan kina bukatar Oriflame products ko wanne irin ne, ko Kuma kina sha'awar yin register da su*. *Ki tuntubi wnn number

08022059556

Akwai tsarin adashe na biya a hankali.me sha'awa ta shiga wnn link din👇🏽

https://chat.whatsapp.com/HLPG9S1Muh19s2RKVYf2Jp

IDAN KAYA YA GAJI...

GAMMO MA YA GAJI

BADI'AT IBRAHIM MRS BUKHARI B4B GIDAN KAMSHI

LITTAFI NA FARKO

SHAFI NA GOMA SHA UKU

*Shin yar'uwa kina da labarin company na Oriflame?*

*Da k'arfin zuciya da guiwa na ke muku shunen inda zaku samu kayan da na zano a kasa cikin saukakkan farashi.*

🎈sinadarin tsarki me farin jini(Feminnille wash)🧴

🎈Mayuka masu inganci

Edit with WPS Office

🎈turare

🎈man goge Baki(toothpaste)

🎈Man gyaran gashi

Da sauransu......

*Idan kina bukatar Oriflame products ko wanne irin ne, ko Kuma kina sha'awar yin register da su*. *Ki tuntubi wnn number

08022059556

Akwai tsarin adashe na biya a hankali.me sha'awa ta shiga wnn link din👇🏼

https://chat.whatsapp.com/HLPG9S1Muh19s2RKVYf2Jp

"Wannan kuɗin fa Lolo na gansu da kauri?"

Labbai ta tambaya tana jujjuya kuɗin.

Hmm kuɗin abincin dangin Amarya ne Babangida ya kawo mun wai inyi musu. Kunji wai Amarya bata cin nama ja dan haka da kaji za'ayi girkin hmm"

Na haɗiye wani ƙaton dutse mukut tare da ɗanwaken da nasa a bakina ko taunawa ban ba.

Salaha tace.

"Su dai maza babu sunnar da suka fi ɗabbakawa kamar ta ƙarin aure. Basu iya ɗabbaka kyautatama iyali, da taya su aikace_aikacen gida ba. Nima kishiyar za'aimun shine dalilin tahowata."

Idanu na zare na cire hannuna a abincin bakina ma ɗaci yake yi mini.

Yaji kika yi kome kike nufi?"

Labbai tace.

"Tabb wallahi gara ki koma ɗakinki bakinki alekum ai kinga ɗakin namu da muke turmusuwa mu kwana, ga bakin ciki, komai ke zaki ma kanki bafa ta sauya zane ba. Gara kiyi zamanki a gidanki ko babu komai kuma duk ƙanƙantarshi zaki ci"

Uzairu zuchiyata ne ya shigo da kofin tea haɗin murtuk yace.

Edit with WPS Office

"Ku rabu da'ita ai bari ba shegiya bace da ubanta "

"Kayya Labbai abar kaza cikin gashinta kawai. Amman dai zan koma sai nayi wata guda in suka gama amarci na koma" A cewar Salaha kenan.

Banɗaki na shiga na wanko hannuna nazo na sha magungunana na kwanta ina jinsu sunata tattauna matsaloli da haka nayi bacci sai zuwa azahar na tashi jikin babu laifi kanma ya sassauta sai jiri da rashin daɗin baki, jikin kuma babu ƙwari.

A falo na tadda su Labbai sun yi mun juyin ɗaki ai kuwa yayi kyau sosai. A kan kujera na zauna na soma kiran Maigogul"

"Lolo yanzu haka ina hanyar gidanki zan zo in duba ki bari inna ƙaraso sai muyi magana nasan akan Rakiya kayi nayi kike kirana to bari inzo kya ji kanun zancan."

To Maigogul sai ka ƙaraso"

Wayar na datse

Labbai Maigogul wai yana hanya zai zo."

Baki ta taɓe tace.

"Allah ya kawo shi lafiya. Ya maganar cefanen abincin goben ya kamata ki kawo mu je mu siyo duk abinda ya dace ba sai goben ba kar aikin yayi yawa. Kuma kinga dole mu ƙara kwana dan bai kamata kiyi aiki mai uban yawa haka ba ke ba lafiya ba. Amman tun wuri kiyi ma Babangida saƙon karta kwana ki sanar mishi kuɗin ba zasu isaba tunda da kaji za'ayi girkin ki samu ki fita da fitarki"

Numfashi na sauke a hankali nace

Hakane to me kuke ganin zamu yi musu ni da nace mu yi soyayyar shinkafa sai mu soya kaji mu sa a jajjage, sai a sai ruwan roba da jus na roba ko me kuke gani? Ku zaku yi aikin ni bazan iyaba da safe gobe sai su Aisha su zo su kama muku"

Haka dai muka tsayar. Muka rubuta kajin, kayan lambu, hanta, da kayan miya, sai kayan ƙamshi, ruwa, da abin sha kuɗi dai dubu saba'in  harda kuɗin mota muna da shinkafa, maggi, mai a kitchen dasu zanyi amfani. Saƙo na turama Babangida kan cewar kuɗin ba zasu isa ba. Sai ga dubu arba'in ta shigo account ɗina. Murmushi kawai nayi.

Sallamar maigogul muka jiyo daga can bakin ƙarayina.

Da kaina na yinƙura na leƙa.

Maigogul ka shigo daga ciki"

"To to Lolo" Ya faɗa yana wannan dariyar tashi.

Edit with WPS Office

Ya tako ya shigo. Gabaki ɗaya falon saida ya kaure da ƙamshin turarenshi ya ɗauki kwalliya ya ci malum_malum ga agogo ga gogul a manne a idanunshi yayi daram a kan hancinshi,  fararen haƙoran  makkanshi na yaudara sai ƙyalli suke yi, kusan kullum sai an wanke su da toka.

Gaisawa muka yi Labbai ta kawo mishi ruwa da abinci.

" Uhm Uzairu zuchiyata duk ashe kunanan ni aka barni inata watangaririya. To yanzu daga ofishin ƴan sanda nake ni da wani uban gidana da ƙyar yasa aka rufe kes ɗin Rakiya danma yana da ƙarfin faɗa ne. Amman ba'a sakota ba shi ɗan sandan yace da yamma muzo da dubu ashirin kuɗin beli kinji abinda ya kawo ni. Su Adama duk mun haɗu dasu acan na barosu suma sunce zasu zo su duba jikin naki ma.

In kina dashi ki bayar, in bai samu duka ba sai kuyi karo karo ke da ƴan uwan naki. Duk da nasan cewa zasu yi basu dashi. Yarane marasa albarka To ni dai na gama iyakar ƙoƙarina da ace Allah yasa an kai Rakiya kota to in sha Allahu da sai ta ci gidan ɗan kande babu makawa.

Salaha tace.

"Ni dai akwai dubu biyu a wajena"

Tashi tayi taje ta ɗakko Labbai ta ba da dubu uku dubu biyar ta tashi. Uzairu zuchiyata ya jefa ɗari biyar

Tashi nayi na shiga ɗaki a cikin kuɗin da Khalid ya bani na ƙirgi dubu ashirin cib, na jefa ragowar dubu talatin ɗin canjin abincin masu kawo amarya na fito.

Gashi dubu ashirin  ɗin Maigogul in yaso nasu Labbai ko cefane ayi dashi"

Baki ya washe yasa hannu ya karɓa dai_dai buɗe labulen Hamida.

Da sallamarta da buɗe labulen duk lokaci guda tayi. In taso munafurci haka take yi musamman in taga ina da baƙi.

"Umman Aminu ashe baƙi kikayi, dama leƙowa nayi in miki yaya jiki, in miki sallama zani gidansu Baban Aminu akwai biki da akeyi wannan ne ma ankon"

Ta karashe tana dariyar munafurci a tunaninta ai bansan komai ba.

Ayya jiki da sauƙi"

"Ina wuni Baba?"

Ta gaishe da Maigogul. Shiko da fara'a ya amsa mata sai kallon kuɗin hannunshi take yi tana girgiza kanta. A haka tayi mun sallama ta wuce.

"Lolo samo leda ko kwano ki juye mun wannan abincin in naje gida naci ba zama ya kawo ni ba. Allah yayi miki albarka dan Allah ki kiyaye abinda zai ɓata ran Babangida mu dai ko babu komai

Edit with WPS Office

yayi mana sutura kin fita zakka a cikin yarana. Yan baya da suka firfito a gidan miji muna musu fatan samun rabo irin naki"

Ɗan murmushin dole nayi kawai.

Salaha samu kula ƙarama ki zuba ma Maigogul abincin ki haɗa mishi da lemun roba da ruwa, Labbai miƙo mun wannan ɗin inci lokacin shan maganina yayi.

Salaha taje ta zubo mishi ta kawo mishi, Labbai ta miƙo mun nashin. Tare suka fita dukka shi ya nufi gida shi da Uzairu Zuchiyata su kuma suka tafi cefane.

Abincin na tusa a gaba inata kallo a zahiri a badini kuma tunanine fal cikin raina da wannan na jiyo dariyar su Adama suna shigowa.

Abincin na soma ci ina musu sannu da zuwa. Adama ta bararraje a ƙasa.

"Lolo ƙara mana Ac mu sha raɓa mun shawo rana. Rahama ke kuma nemo mana lemo ɗaɗɗara a firji mu sha"

Acn na ƙara musu nima na sakko ƙasa Adama ta ɗauki cinyar kazar dake cikin plate ɗina ta kai mai wawan gatsa.

"Yaya ƙarfin jikin Lolo? Wallahi har kin ƙara ramewa, ke kam duk ni'imar nan da kike ciki kin ƙi kiba zuchiyarki haƙuri ki rungumi ƙaddara ba'afa ɓari a kwashe duka Lolo. Mu kaɗai mun isheki abin misali ki zauna ki rungumi yaranki ki watsar da fitintunun maza. In dai damuwar namiji zaki dauka ki saka a ranki ya dinga baki assignment kenan, daga karshe ki faɗi jarabawarshi. Ki duba su Rakiya duk irin halin Maigogul gashi suna zaune har matakin girma baƙin ciki da takaici wannene basa gani har gobe?

Dallah Rahama bani jus in kora kinji. Daɗine yayi ma Lolo yawa fa"

Ta warce kwalin 5alive da Rahama ta kawo yanzu. Ta ɓalle ta ɗaga kai ta dinga kwankwaɗa. Rahama ta saka hannu ta soma cin abinci.

"Mun shawo rana da yinwa, dukkanmu babu wacce ta karya daga ofishin ƴan sanda muke an dai gama komai Alhajin da Maigogul ya tawo dashi shi ya tsaya akan komai har kuɗin beli dubu ashirin ya ba Maigogul dan sunce sai dare za'a je a biya beli a tafi da Rakiya"

Kallonta nayi nace.

Yanzu fa Maigogul yazo na bashi dubu ashirin Salaha dubu biyu Labbai dubu uku, Uzairu zuchiyata ɗari biyar yace za'ayi belin Rakiya ashe salon aiki ne kawai?"

Dariya suka tuntsure dashi harda tafawa, Adama ta miƙe da plate a hannunta zata ƙaro abinci tace.

"Yaci biredi ya yaga leda wallahi an bashi kuɗin beli har da na shan ruwa ma. Su Labbai ban

Edit with WPS Office

gansu ba ko ta ja Salaha yawon nata na tsiya ne ace yarinya da iddarki a ka sai yawo?"

A_a cefane suka je yi na abincin dangin Amarya gobe zata tare, yau ana can gidan ƙanin Baba Malam anata biki nima ciwo ne ya hanani zuwa"

Su Labbai sai la'asar suka shigo niƙi_niƙi da kayan cefane nan mu kai Sallah aka buɗe shafin hira har magriba  su Mardiyya suna can ana shagalin biki tare dasu. Da ƙyar na lallaɓasu suka samu suka je. Tuwon shinkafa miyar lalo Labbai tayi mana da kifi sukumbiya sai da su Adama suka ci suka ƙoshi sannan suka tafi mun rabu dasu akan washegari da wuri zasu zo ayi komai dasu.

Suna fita Baba Malam ya kira wayata yake sanar dani su Mardiyya a can gida zasu kwana sai gobe sa biyo ayarin dangi su tawo.

Nace dashi babu komai nima banji daɗi bane shi yasa ban samu zuwa wajen bikin ba.

Haka dai mu kaita hirar gida ni dasu Salaha muna dariya, dukkanmu sai muka samu sauƙin zafin zuchiya tunda dukkanmu a cikin matsala muke ko wacce dai da irin tata.

A gidan mu kaɗai muka kwana babu Babangida, babu Hamida gidanma a buɗe ya kwana sabida bansan basu kwana a gidan ba sai da garin Allah ya waye tukunna.

Sassafe na soma share ɓarayina su Labbai kuma suka shiga aikin hura gawayi da gyaran kayan lambu. Wajajen taran safe sai ga Adama da Rahama sun iso su kuma suka soma gyaran kayan miya. Farar shinkafa na jiƙa mudu biyu inaso in yi masa ko ba yawa a aika ma da maƙota kar suga ana sha'ani ba'a kai abinci ba.

Adama na shan tea da biredi tace.

"Lolo ki zauna ki huta naga kina haki kinsan ba daɗi kike ji ba, bari dai cikina ya ɗauka kiga in soma aiki ka'in da na'in."

Zama nayi a dokin ƙofa ina maida numfashi, Salaha ta karashe wanke shinkafar aka saka yis da surfaffen wake kaɗan amman, Salaha ta leƙa ta kira almajirai suka tafi niƙan masa da kayan miya.

Labbai kuma ta shiga zuba ma kajin data ɗaura a wuta ɗanɗano da kayan ƙamshi.

Ana cikin haka muka soma jiyo muryoyi a tsakar gida da tsayuwar mota a waje. Su Sa'a ne da dangin Malama Babba da dai danginsu na wajen Baba Malam ƴan Ringim suka zo kusan su rai ashirin harda tukwanensu na girki da kayan cefane. Su Mardiyya kuma suka yo ciki ita ta kama aikin yankan alayyawo da nake yi, su Aɗɗa'u kuma suka sake komawa tsakar gidan dan ina jiyo muryoyin yaran su Sa'a suna guje_guje a tsakar gidan.

Uwar gulma ce ta shigo ɓarayin nawa da fara'arta. Taci uwar kwalliya wallahi kwa yi tunanin itace Amarya, har kitso aka yarfa mata da lalle, harda ashole a kanta. Ganin an soma suyan kaji,

Edit with WPS Office

ga tafasassun kaji cikin bawo ga kabeji Rahama nata yankawa taga mun kacame sai aiki muke yi sai jikinta yayi mugun sanyi, ranta yayi matuƙar ɓaci.

"Umman Aminu girkin bikinne kike yi? Ai ga cefane can a tsakar gida Baban su Aminu ya ba yar mun yi yace ayi abincin bikin. Naga kina yin naki daban"

Ta kasa haƙurin danne gulmarta yau dai. Sai kallon kajin take yi sunata soyuwa a ƙatuwar bojuwa cike da mai.

Wallahi kuwa ango ne ya bani girkin tarbar Amarya da danginta, kinsan wannan girkin na musamman ake yi, shi yasa yace ni inyi ku kuma kuyi wanda ya baku na gama garin jama'ar biki"

Na karashe maganar tare da ɗaukar kabewa na soma yankawa."

Dariyar dole tayi nan ta shiga gaishe da su Adama da suka gwafe suke ta aiki.

"Dama baho nazo ara zamu zuba naman rago da aka yanka ashe kema kina aiki dasu"

Nace da'ita.

Wallahi kuwa duk gasu muna aiki dasu sai dai ki je maƙota"

Barin wajen ma nayi na koma ɗaki na zauna a kujera na rufe idanuna ji nayi ƙirjina na tsananta bugawa,ga  yanayin jikina da babu daɗi. Bansan sanda Hamida ta tafi ba, ban kuma san adadin lokacin dana diba a zaune idanuna a rufe ba, ni ba mai bacci ba, ba kuma idona biyu ba.

A hankali na sauke ajjiyar zuchiya na buɗe idanuna a hankali na fice a falon.

Masha Allah ƴan uwa abun wuya. Su Adama kusan sun gama duk aikin abinci wanke kayayyakin da aka ɓata suke yi, komai sun zuba a kula banda masa da yanzu Mardiyya take juyewa a kula.

Sannunku da aiki Adama ashe har kun kammala?"

"Ai kuwa ke dai kije ki yi wanka ki shirya gidan cike yake da jama'a naga bikin na gaske ne a wannan karon. Kinga rumfuna fa aka kakkafa a tsakar gidan naku"

Yawu na hadiye ban iya cewa uffan ba na wuce.

Ina wanka ina tunanin ko wacece wannan Babangida zai kawo mana oho, koma wacece tana da matsayi mai girma a zuchiyarshi duk aure aurenshi bai taɓa zagewa yayi hidima irin ta wannan karon ba.

Har na fito, na shafa mai, na saka wani jan lace nawa mai tsada ɗinkinshi mai kyau sosai. Ban yi kwalliya ba ɗan kunne kawai na ciro na saka sai turare dana feffesa sosai.

Gabana fa sai faɗuwa yake yi wallahi bansan dalili ba. Bazan ce muku bana kishin auren da Babangida yayi ba kwata_kwata ba. Amman kuma bansan dalilin da yasa wannan auren yafi tsayamun a zuchiya fiye da ragowar matan da mu kai zaman kishi a baya dasu ba. Wata ƙila

Edit with WPS Office

hakan na da nasaba da irin yadda take da matsayi a rayuwar Babangida dama mahaifiyar Babangidan.

Ina fita falo naga mata a zazzaune har an zubo musu masa da miya wasu sun  soma ci wasu basu kai ga cin ba.

"Ga uwargidan gidan nan ta fito"

Inji wata mata da za tai sa'ar Maman Safwan a ido dai.

Sannunku bayin Allah ina wuninmu?"

Na faɗa tare da aro juriya na yafa.

Nan muka shiga musayar gaisuwa a tsakankaninmu.

"Dama daga maƙotanku ne. Munji ana biki duk da dai baku kawo goron gayyata ba muka ce dai bari mu shigo sabida hakkin maƙwabtaka, tare da baku uziri ƙila hidimace tasa kuka sha'afa."

Ɗan murmushi nayi musu nace.

Gaskiya mun gode sosai hidimace tasa muka mance gaskiya. Amman munji daɗi da wannan uzirin. Bari a kawo muku abun sha."

Mardiyya na kira nasa ta kawo musu lemun koka kola ta ajjiyema kowa a gabanta ta fita.

Adama ce ta leƙo ta kirani, nan na tsallake matannan na fita.

"Lolo kinga irin dukan da Sa'a take ma Aɗɗa'u kuwa. Bakya jiyo kukanshi? Kije ki karɓoshi karta yi mishi illah. Mu kuma kar muje mu yi lefi kinsan akuyarmu ta daɗe da yin kuka. Kuma wallahi in dai ni naje saina rama mishi dukan kema sarai kin sanni"

Murmusawa kawai nayi. Ina jiyo sautin duka da kukan Aɗɗa'u raɗau a kunnena da irin yadda take aibantani tana kunce mun zani.

Barta ta kasheshi amman ni bazan je ba wallahi kema na roƙeƙi kada kije. Nema na suke da jafa'i a kansu zai ƙare. Kunga kuzo mu shiga kuyi wanka ku yi Sallah la'ar fa tayi ma"

"Tabb ni kam zanje in fincikoshi in tayi mun kuma in mayar mata me tsoron a mutu shi yake soma mutuwa. Baki seta musu zama bane shi yasa suke miki haka. Sai kace ba Lolon da in aka nuna ma yatsa take ɓallawa ba"

Fuu Labbai tayi hanyar waje. Ajjiyar zuchiya na sauke

Labbai kura ce tayi lafiya. Ita kanta Sa'ar ta san ƙyalesu kawai nake yi"

Ni dai ciki na koma wajen wannan mata, suma suna shirin fitowa.

Edit with WPS Office

A har kun fito? To mun gode Allah ya saka da Alkhairi"

Wata daga ciki tace.

"Wallahi mun fito. Allah ya sanya alkhairi ya haɗe kawunanku. Zamu leka wajen mejego itama"

Sallama su kai mun suka tafi, nima na shige uwarɗakina na tarar da su Adama, Salaha dai na wanka, Rahama na Sallah.

Labbai ce ta shigo tana zage_zage da Aɗɗa'u a hannunta an haɗa mishi jini da majina.

Raina ba ƙaramin ɓaci yayi ba ganin yadda tayi ma yaro dukan sa'a.

Me kayi mata ta dokeka?"

Cikin shesshekar kuka yace.

"Wai dan Musa ya dake ni na rama shine take ta dukana wai ba'a koya mana tarbiyya ba"

Yawu na haɗiye na dubi Mardiyya nace.

Ku je ɗakin ku yayi wanka sai ya kwanta. Har su Aminu duk ku shigo ciki ku je ɗakinku kunji?"

Mardiyya ta ja shi suka fita tausayin yaran ya doki murfin zuchiyata.

Haka dai su Labbai sukai wanka suka saka kayana.

Abinci muka ci muka ƙoshi muna ji an soma kaɗe_kaɗe a tsakar gida da ihun mata mu dai muna daga ciki.

Abincin su Rakiya na cire a gefe, su Adama ma na cire musu nasu.

Dab magriba sai muka ji guɗar mata daga nesa halamar Amarya ta iso. Gabana sai ya sake tsananta duka, duk yadda kike a wajen mijinki dole in zai ƙaro aurennan sai kinji sai dai ki basar kawai.

Bayan minti talatin su Adama suka je har ɗakin Amarya suka kai musu abinci da abun sha. Suka dawo sunata santin kyau da tsarin ɗakin Amarya, amma ita dai basu samu ganinta ba.

"To bari mu jira muga ko zasu kawo amarya ɗakinki sai mu tattara mu tafi haka kuma"

Cewar Labbai kenan.

An daɗe ana kiɗa da rawa da ihu a tsakar gidan, Adama ce ta leƙo mana tsakar gidan ta dawo.

"Duk yadda akayi Amarya ta haɗa iri da Kanuri ko shuwa ku kunji ƙamshin turaren wuta duk an cika gidan dashi, ga amarya da danginta kab ɗinsu lafaya suka saka. Hmm Babangida da kab abokanshi ashe suna tsakar gidan. Kunga fa kuzo mu tafi zai yi wuya amaryarnan a kawo ma Lolo ita yau."

Edit with WPS Office

Haka suka tarkata suka barni da damuwa da faɗuwar gaba. Yara suna ɗakinsu ma har sun yi bacci ni kuma ina kwance zuchiyata na suya. Sai wajajen ɗayan dare aka tashi daga wannan shagalin biki.

Ajjiyar zuchiya na sauke na lumshe idanuna. A wannan dare dai sai jefin assalatu bacci yayi gaba dani baifi na minti talatin nayi ba aka kira sallah na tashi. Ciwon kai yace salamu alaikum ai sai a zaune na yi Sallah ko falo bana jin zan iya fita yaranma a kwance suka shigo suka sameni muka gaisa.

Mardiyya akwai ragowar masa ku turara sai ki dafa tea."

Kafin ta miƙe sai ga Babangida ya shigo kamar zararre ko sallama babu. Idanu na ƙura mishi fuskarshi sai ƙyallin angwanci take yi.

Da sauri yaran suka gaisheshi suka yi maza suka fice.

"Sabuwa ki haɗa ma Amarya kayan kari wallahi ta gaji ba zata iya aikin komai ba."

Zama nayi zaune nace.

Naga bazawarace itama sai an mata girkin safe? Ga Hamida ai sai tayi ko? Ni ba ishasshiyar lafiya bace dani."

"Ohhhhh Sabuwa kekam halinki sai ke babu tarbiyya ba'a koya miki yadda zaki yi magana da miji Bil hikmatu wal mau'izatil hasana ba. In kinga dama kar kiyi wallahi akan wannan yarinyar zaki iya komawa gidanku ki je ki haɗu da zawarawan gidanku aci gaba da ɓel_ ɓel"

Hmmm Babangida kenan wallahi kana bani mamaki. Amman babu komai wata rana sai labari. Kaci gaba da yin duk yadda kake so duniya zata koya maka hankali. Da kake cewa zan koma gidanmu to sai me in koma mana, ka ganni bana tsoron komawa gida"

A cikin ɗakin na fito na barshi. Yana kiran sunana banza nayi mishi.

Masa ce nasa aka turara dasu, Mardiyya ce tayi komai nace ta kai musu maza ta dawo.

Ni kuma na zuba ma yaran nasu ni zallan tean kawai ma zan sha shima sabida zan sha maganine.

Da sauri naga Mardiyya ta shigo sai zazzare idanu take yi.

Ke lafiya kika shigo a firgice?"

Na tambayeta tare da kafe ta da idanu.

"Babu komai ummi. Wai tace in gaisheki"

Hmmm

Edit with WPS Office

Kawai nace na dinga shan shayinnan da zafi ina jin da ina da dama da na fita a rayuwar Babangida kwata_kwata. Gidanmu da irin rayuwar da inna fita zan koma ne, da kuma goben yarana shi yake zaune dani a cikin gidannan.

Ina gama shan tean naje nayi wanka na sha magungunana. Ina shafa mai Babangida ya leƙo a lokacin goma na safiyane.

"Ki same ni a turakata yanzu inason zan haɗaku"

To zanzo"

Ya saki ƙofar yayi gaba. Kofar nabi da kallo nayi shiru kamar ruwa ya cinyeni.

Jikina na rawa na zari mayafi na ɗan fesa turare na fito.

Aminu yana sharar falo, Mardiyya kuma ina jiyo ɓuruntunta a kitchen. Malama da Aɗɗa'u suna kan kujera suna wasa kasancewar yau babu makaranta suna hutu.

Sannunku ko, ina zuwa zanje wajen Babanku yanzu zan dawo"

"Sai kin dawo ummi"

Suka haɗa baki dukkansu harda Mardiyya dake kitchen.

A tsakar gida na hangi Hamida itama fitowarta kenan ta ci sabuwar atampa ta dau kwalliya harda takalmi me tsini.

Tana shiga zama kawai tayi nima na shigo da sallama.

Na samu waje na zauna a ɗayar kujerar dake kusa da ta Hamida, su kuma Babangida suna fuskantarmu.

Amarya ce ta ɗago kanta tace.

"Yaya da Yaya ina kwananku"

Cike da faɗuwar gaba na ɗago. Ko cikin mafarki naji muryarnan nasan mamallakiyarta, muryar da mai shi take da daraja, muryar da na ɗauki mai ita tamkar jinina.

Ina ɗagowa muka yi ido huɗu da Yar shuwa Aminiyar da duk duniya bani da tamkarta, aminiyar da duk sirrina nata ne, sirrinta nawa ne.

Cikin ɗimuwa da fargaba na nuna ta da da yatsana, amman in buɗe baki in yi magana wallahi na kasa ko ina a jikina ɓari yake yi harda harshena.

"E itace nasan tambayar da zaki yi mata kenan.Itance  dai ƴar shuwa aminiyarki itace matar dana aura, a daren jiya ta zama ni na zama ita. Hamida ga Amarya ke kam kun haɗu tun jiya kuma dama kinsan da zuwan nata"

Edit with WPS Office

Duk wannan maganganun da Babangida yake yi yinsu yake cikin salon tura haushi da baƙin ciki. Ni kuma fa yatsana yana nan ina nuna Yar shuwa dashi na kasa saukewa. Sai murmushin tsantsar mugunta take yi mun, haka ma Babangida.

Da ƙyar na samu mallakar kaina na sauke hannuna a hankali.

Yar shuwa dama kece Amaryar da Babangida ya auro?"

Na tambayeta hawaye ya gama wanke fuskata fes.

"Kwarai nice Sabuwa. Matar mutum kabarinshi Allah ya ƙaddara mana auren miji ɗaya. Tunda ba haramci a ciki kuma, nice dai Amaryarku da fatan bazai taɓa amincinmu ba?"

 Idanuna na lumshe wasu hawaye masu mugun yawa suka sake sakkomun Miƙewa nayi tsaye da sauri duk da jirin da ke ɗibata, ga zuchiyata sai dokawa take yi da ƙarfin gaske.

A zuchiyata nace

Lallai akwai matsala gagaruma hakiƙa alƙiyamata ta tsaya.

TO FA KUNJI WATA SABUWA.

Wa.me/2348179523215

Ina manyan mata masu capacityn  suke?  ku fito lambarku ce ta fito.

Yar uwa turaren wuta kike nema nau'ika daban_daban masu musulmin ƙamshi da kama muhallu? Ba itacen banza masu sanya gida ƙauri da hayaki kamar an kunna taohuwar bespa ba.

Matso gasu MRS  BUKHARI B4B GIDAN KAMSHI nazo miki da duk abinda kike buƙata na ƙamshi. Kama daga turarukan wuta irin na gidan alfarma. Zuwa humrori iri daban daban masu musulmin ƙamshi da riƙe jiki.

Bugu da ƙari muna da turarukan kaya, na fesawa dana turara kaya.

Muna da kulaccam nau'i daban daban masu gyara jiki da lausasa  fata mata, ga kuma ƙamshi mai inganci.

Muna da turarukan tsugunno na musamman masu sirri Hajiyata

Edit with WPS Office

Muna da room freshener iri_iri

Muna da mopping mix masu kama waje.

Akwai turarukan kafet dana kujeru.

Sannan akwai box _ box  setika na Hajiyoyi masu ƙyallin goshi.

Muna da Amarya package.

Muna da uwargida package

Muna da maijego package

Muna bayar da sari ko a ƙasar waje kike, muna tura kaya

Saudiyya

Nijar

Ghana

Camaron

A duk ƙasar da kike kayanmu zai iso miki cikin aminci da yardar Allah.

Hajiya akwai Humrar matan aure wannan ta musamman ce.

Duk wani abu da kika sani na ƙamshi babu irin wanda bamu dashi a kamfaninmu.

Muna da turaruka designer na maza da mata wanda kamfaninmu ke bugawa Hajiya babu inda zaki je ki ci karo da mai irin ƙamshinki.

MRS BUKHARI B4B GIDAN KAMSHI TAZO MUKU DA DUK ABINDA KUKE SO NA KAMSHI HAJIYA.

KUNSAN KANURI MUNE KAMSHI DAMU AKE KOYI

SIYAN NAGARI MAIDA KUDI

MUNA MARABA DA MASU SIYAN ƊAYA KO SARI.

LAMBAR DA ZA'A SAMENI KAI TSAYE ITACE.

Wa.me/2348179523215

SAI NA JIKU

Edit with WPS Office

IDAN KAYA YA GAJI...

GAMMO MA YA GAJI

BADIAT IBRAHIM MRS BUKHARI B4B GIDAN KAMSHI

LITTAFI NA FARKO

SHAFI NA GOMA SHA HUƊU

Ina manyan mata masu capacityn  suke?  ku fito lambarku ce ta fito.

Yar uwa turaren wuta kike nema nau'ika daban_daban masu musulmin ƙamshi da kama muhallu? Ba itacen banza masu sanya gida ƙauri da hayaki kamar an kunna taohuwar bespa ba.

Matso gasu MRS  BUKHARI B4B GIDAN KAMSHI nazo miki da duk abinda kike buƙata na ƙamshi. Kama daga turarukan wuta irin na gidan alfarma. Zuwa humrori iri daban daban masu musulmin ƙamshi da riƙe jiki.

Bugu da ƙari muna da turarukan kaya, na fesawa dana turara kaya.

Muna da kulaccam nau'i daban daban masu gyara jiki da lausasa  fata mata, ga kuma ƙamshi mai inganci.

Muna da turarukan tsugunno na musamman masu sirri Hajiyata

Muna da room freshener iri_iri

Muna da mopping mix masu kama waje.

Akwai turarukan kafet dana kujeru.

Sannan akwai box _ box  setika na Hajiyoyi masu ƙyallin goshi.

Muna da Amarya package.

Edit with WPS Office

Muna da uwargida package

Muna da maijego package

Muna bayar da sari ko a ƙasar waje kike, muna tura kaya

Saudiyya

Nijar

Ghana

Camaron

A duk ƙasar da kike kayanmu zai iso miki cikin aminci da yardar Allah.

Hajiya akwai Humrar matan aure wannan ta musamman ce.

Duk wani abu da kika sani na ƙamshi babu irin wanda bamu dashi a kamfaninmu.

Muna da turaruka designer na maza da mata wanda kamfaninmu ke bugawa Hajiya babu inda zaki je ki ci karo da mai irin ƙamshinki.

MRS BUKHARI B4B GIDAN KAMSHI TAZO MUKU DA DUK ABINDA KUKE SO NA KAMSHI HAJIYA.

KUNSAN KANURI MUNE KAMSHI DAMU AKE KOYI

SIYAN NAGARI MAIDA KUDI

MUNA MARABA DA MASU SIYAN ƊAYA KO SARI.

LAMBAR DA ZA'A SAMENI KAI TSAYE ITACE.

Wa.me/2348179523215

SAI NA JIKU

"Meye haka Sabuwa dallah nemi waje ki zauna, ke da ba'a abun arziki dake kwata_kwata"

Edit with WPS Office

Cewar Babangida dake magana dani da tsawa. Cike da kirsa da makirci Yar shuwa tace.

"Bita a hankali dan Allah Jannati, kasan abinne yazo mata bagatatan dake ta kwana biyu bata leƙawa cikin group ɗinmu da har hotunan bikin zata gaggani na tura a can group ɗin. Ka huce kayi mata uziri zamu sasanta kanmu"

Jirine ya zaunar dani daɓas kaina yana jujjuyawa yayinda zuchiyata take dokawa, kaina ya kulle dunɗum. Wallahi kuimun uziri ko kece akaima wannan cin amanar dole kanki ya buga. Shin kunsan a daidai lokacin abunda nake ji kuwa?.

"To ga Habibaty Allah ya ƙaddara ta shigo cikin rayuwarmu. Abubbuwa da dama zasu sauya a cikin gidannan da tsarin komai da komai.

Ke Sabuwa bari in soma dake tunda ke kece babbar dolen . Habibaty gata ta shigo ke nasan baki da matsala da'ita duk wani halinta kin sani ƙarewa tare kuka taso baki da aminiyar data wuce ta. Bazan lamunci rashin zaman lafiya ko fitina ba dan ku mata haukacewa kuke yi idan aka auri macen da kuka sani.

Kar inji kar in ga ranar da zaki takali Habibaty da wata fitinar, ko baƙar magana kar ki bari ya haɗaku kiyi mata magana da usulubi hasana inta kama dole sai kunyi maganar kenan.

Sannan daga yau ni Babangida na dawo kacokam turakata da zama duk macen dake da girki ita zata biyoni turaka ba zaku kuma ganina a ɓarayinku ba."

Ta inda ya shiga ba tanan yake shiga ba ya dinga rakarkato sokiburutsun zance maras kan gado.

Yar shuwa ta wani riƙe ma Babangida hannu tace.

"Ai babu matsala ka bar mun komai a hannuna zan ji dashi, tunda dai na shigo gidan abubbuwa da yawa zasu sauya Jannati"

Murmushi yayi yana wani kallonta. Hamida ce tayi gyaran murya halamar zata yi magana. Ni ko ina zaune ina ganin almara. Ganinsu nake yi kamar sinima.

"To Amarya duk da dai ba baƙuwa bace a gidan gidan kin saba dashi, Uwargidan sha ƙundum aminiyarki ce komai zai zo da sauki ina miki maraba da zuwa. Kuma ni jego dama nake yi na bar miki kwanakin jegon nawa wata guda cib inna gama jego sai mu ci gaba da rabon kwana. Kinsan a waya ma na faɗa miki hakan za'ayi tun kina Maiduguri"

Ran Hamida fes take wannan maganar a tunaninta ai ƙunci nawa ne ni kaɗai. Amman da ta san wacece ƴar shuwa dariya ba zata yi ba ko da kuwa an bata damar yi.

"To godiya nake yi umman Usama. Jannati ya kamata kai mata tukuici gwaggwaɓa ko?"

Ji nayi kamar in dira a wuyan mitsiyaciya in mata kafirin duka.

Kunji bariki. Shi ko Babangida yana washe baki yace.

Edit with WPS Office

"Kinci kyautar nera dubu ɗari Hamida zan tura miki in muka gama. Sai mu dawo batun girki dama dai kowa girkinta take yi. Habibaty kema kince wannan tsarin yayi miki inaga iyakar abinda zance muku kenan. Ke Sabuwa kinji ƴar uwarki ta bamu wata ɗaya ke kwana nawa zaki bamu?"

Murmushi nayi ina karkaɗa kai. Da ƙyar na iya mallakar kaina. Zuchiyata sai tunzurani take yi. Wallahi Allah a lokacin da zan biye ta zuchiyata ko da ba wannan labarin akeyi ba wani akeyi daban. Da labarin a jarida da kafafen sadarwa zaku tsinceshi cewar wata uwargida ta kashe Mijinta da Amaryar da yayi a washegarin tarewa. Cike da dauriya da dakiya, cikin mallakar kai nace.

Ina taya ki murnar shigowa wannan gida Ƴar shuwa. Ina fatan ki rayu da Babangida har tsufa da izinin Allah. Kaima ina taya ka murnar samun macen aure. Batun kwana kuma na bar miki Babangida har izuwa lokacin da zaki gaji dashi, ko shi ya gaji dake. Ina fatan har gaba da abada kada Allah ya nuna mishi ranar da zai gaji dake. Kai da kake batun rabon kwana ko ƙarin kwana ai tunda ka auri wannan ƙazamar ragowar ƴan iska ire_irenka ni da sake wata mu'amular Aure har abada. Bama baya kaina ita mitsiyaciyar daka auro ai tasan waye Sabuwa"

Ina gama fadar haka na sake murmusawa na miƙe da dabara na yi hanyar waje.

Ina ji Babangida yana wani mun kiran ƴan tasha, banza nayi dashi. Da taimakon Allah na isa ɓarayina babu ko sallama sai ganina suka yi a tsaye na jingina da bango idanuna a lumshe hawayene kawai yake kwarara a idanuna, na kasa mallakar kaina a gaban ƴaƴana. Duk sai suka zo suka taru suna tambayata ko lafiya. Mardiyya dake ita babbace sai cewa tayi.

"Ummi kiyi haƙuri nima da naje kai musu abinci ne na ganta. Dan Allah ki dena kuka"

Da ƙyar wallahi na ɗaga musu kai halamar to, na bi bango na shige ɗakina na kulle na faɗa gado nayi kuka mai yawan gaske. Ko ba'a cemun ba nasan in aka aunani jinina tuni ya hau fiye da kima.

Tuno lokacin yarintarmu ni da ƴar shuwa na shiga yi da makarantarmu Day Gadadin, bencinmu ɗaya tare muke cin kuɗin break ɗin juna.

Gidan aurenta na tuno da irin baƙar azabar da kishiyarta Kanuri ta gana mata ta mayar da'ita bora a cikin gidan, rama da kuka babu irin wanda ƴar shuwa batai ba. Da ƙyar kishiyar ma ta yarda aka saketa bazan mance ba sai da na rakata wajen Maigogul a lokacin yana ganiyar aikin tsubbu shi yayi yadda zai yi ya raba auren shine ta samu salama.

Bayan ta dawo gida ta shiga zawarci mai lasisi yau tana Abuja, gobe tana Lagos, jibi tana wannan hotel, gata tana wannan ges house ɗin. Mu'amala take da manyan hamshaƙan maza ni ai tama faɗo data auri Babangida a nawa ganin.

Surrukana dake hannunta sune suke damuna sosai, duk da nasan bata da ƙarfin zuchiyar fallasa sirrina ni nasan sirrinta fiye da yadda tasan nawa.

Edit with WPS Office

Ajjiyar zuchiya na sauke a hankali take naji nutsuwa na saukarmun. Wayata na laluba na shiga group dinmu na matan Oga na soma bin chart ɗaya da ɗaya har zuwa kan hotunan Babangida da ƴar shuwa na Aure.

Jikina na rawa na soma buɗewa ina kallo kusan kala biyar ko wanne suna cikin soyayya sannan sunyi kyau.

Murmushi nayi kawai da naji Amina ta ɗuma wani ashariya da ganin hoton. Ni ashe yaƙi akayi a gidan banma sani ba dake rabi da kwatan group ɗin ƙawayene, sai kwata da suke bare a cikinmu.

Take naga Labiba ta cire ƴar shuwa a group ɗin.

Inata gangarawa da masu ganin ba'aimun adalciba da masu ganin abinda ƴar shuwa tayi daidaine ko su suka samu dama zasu iya yin wuf da Babangida.

Dariya nayi sosai kamar mahaukaciya. Wallahi dariyar baƙin ciki ne da takaici kawai da suka ce suma in suka samu dama zasu yi wuff da Babangida.

Ficewa nayi a group ɗin da duk group na ƙaruwa da nasan muna ciki tare da Yar shuwa.

Saƙonnin Khalid na gani fin ashirin har zan shiga wayar Labiba ta shigo.

Hello Labiba ya gida?"

Na faɗa kamar babu damuwa a tattare dani.

"Hmm Sabuwa me yasa kika fita a group ai da kin zauna abinki kefa kika kawo Yar shuwa ba ita ta kawo ki ba. Sannan kiyi haƙuri ni dai wallahi bazan taɓa iya kiranki in sanar miki abinda yake faruwa a group bane tun daga ranar da Yar shuwa ta turo hotunan bikinta na buɗe naga mijinki ne. Ai na kirata mu kai uwar watsi ta dinga zagina har tana cewa data sani da mijina ai ta aura. Kiyi haƙuri wannan kar yasa ki yi wani abu da zai salwantar miki da aurenki. Naji a wajen Amina tace mata wallahi sai ta fitar dake a gidan, bake kaɗai ba ma harda sauran kishiyoyin naku wai ashe tun kafin ya aureki take son shi ma."

Murmushi nayi nasan zata aika. Amman wallahi ko ta fitar dani a wannan gidan ƙaddarar bazai dameni ba. Yaƴanane damuwar dan nasan saita ɗaiɗaita mun su ta tagaiyara mun rayuwarsu shine kaɗai tashin hankalina wallahi Allah.

Take jikina ya shiga rawa ina hawaye, gashi da hannuna na bata asiri danta mallake mijin, dangin mijin, dama mu kishiyoyinta. Nasan Babangida ko a buzu take kwana asiri ba zai kamashi ba. Nasan dai duk iskancinshi baya wasa da ibadarshi kuma baya kwanciya da kazanta a jikinshi. Dangin mijin kaɗai zata iya mallaka sai Hamida, ni wallahi nafi ƙarfinta.

Bazan karya asirin bane sabida nasan ni bazai taɓa cina ba. Dangin Babangida kuma taje ta taita mallakarsu. Hamida kuwa kashinta ya bushe jar munafuka. Ajjiyar zuchiya na sauke nace.

Edit with WPS Office

Ba komai Labiba nagode"

Wayar na kashe duka na kwanta dafe da kaina dake barazanar tarwatsewa. Bana son jin wata Maganar suma ganinsu nake yi a matsayin munafukai ai.

Kwana nawa data turo hotunan amman a rasa wacce zata tako tazo har gida ta sanar mun. Abubbuwa sukaita jujjuyawa a zuchiyata.

Ina cikin wannan yanayin har ɗayan rana anata kiraye kirayen Sallah amman na kasa sakkowa, daga kwance ma jiri nake ji hawaye yaƙi tsaiwa a idanuna wallahi. Sai nayi kamar na dangana, inna tuno da wasu abubbuwa manya sai in sake fashewa da kuka.

Nayi imani da Allah da Yar shuwa da Babangida sun haɗe kaine domun su rabani da numfashina"

Baki isaba wallahi. Ba zaku kasheni ba ba zan mutu dan baƙin cikin ku ba"

Da mugun ƙarfi nake maganar kamar zautacciya. A zabure na miƙe wata zuchiyar tana aiyanamun inje in kashe Yar shuwa ko in kashe Babangida.

Hannuna bibibyu nasa na dinga dukan katifata ina watso fululluka.

Ina jiyo su Mardiyya sunata buga ƙofar suna kuka ita da ƙannenta.

Banɗaki na shiga na saki ruwan sanyi a jikina ya dinga zubowa, kuma sanyi akeyi. Wallahi in ruwan sanyin ya sauka a jikina kafin ya sauka kafafuna yayi ɗumi sabida irin zafin da jikina yayi na zazzaɓi.

Na daɗe sosai a haka nayi kuka na share hawayena saina ɗauro alwala na fito.

Ina Sallah ina kuka harna idar, wallahi Allah bansan me na karanta a sallar ba ni dai nayi. Na ɗaga hannu ina son in roƙi Allah shima na kasa sai kuka.

Allah kana gani Allahna"

Na sauke hannuna ina sauke numfashi da ƙyar. Wani abune ya faɗo mun sai nayi murmushi kawai na miƙe tsaye a hankali na buɗe ƙofar ɗakina na bi bango na fito.

Da sauri yaran suka juyo jin motsin fitowata.

Murmushin dole nayi musu, na samu waje na zauna a tsakiyarsu duk sun yi wani iri kamar wasu marasa lafiya. Bana fatan abinda zai rabani da yarana ko kaɗan.

Mardiyya ce ta kawo mun abinci, Aminu ya ajjiye mun ruwa, sai nan nan suke yi dani.

Me yasa baku kunna tv kunsa kallo ba?"

Na tambayesu murya a dashe.

Edit with WPS Office

"Babu komai Aminu kunna mana"

Murmushin dole nayi dan naga sun damu da yawa. Abincin na dinga turawa dan dole sai da na cinye tas na sha ruwa.

Mardiyya kije ɗakina gefen gado zaki ga ledar magungunana maza ɗauko mun. Malama ta sha nata maganin?"

Dariya suka saka duka, nima ina dariyar na tambayesu.

Menene bata sha bane ƴar baɗo

"Tasha ummi Aminu ne ya zuba mata maganin a kofi cikin ruwa ta zaci jus ne tana sha taji ɗaci. Ai ta dinga kuka harda birgima.

Dariya muka kwashe dashi dukkanmu daidai shigowar Babangida.

Wani ƙududun baƙin cikine ya tokareni. Ban nuna na ma san Allah yayi ruwan tsaronshi ba. Naci gaba da dariyata harda ta ƙeta.

"Ina abincin Habibaty Sabuwa. Ya zaki bar ƴar mutane da yinwa tana Amarya? Kawar taki ma sai kin nuna mata baƙin halinki ne?"

Banko kalleshi ba balle in San Allah yayi ruwan tsaronshi ma.

Mardiyya kuje ɗaki zan kiraku"

"Babu inda zasu je. Ku zauna ko in tattakaku dan uwarku"

Babu shiri suka zazzauna suna zare idanu.

Miƙewa nayi nazo wuya iya wuya. Har gabanshi nazo nace.

Bazan girka ba wallahi. In duk duniyarnan gatanta ne bazan mata girki ba kaji na rantse. Wallahi duk abinda ka taka nice maganinka. Dan kaga nayi sanyi? "

Da mamaki yake kallona yana nuna kanshi ya nuna ni a lokaci ɗaya.

"Sabuwa kin dawo da shaye_shayene amman? "

Mardiyya da taji abinda yace da gudu ta zura ta shige ɗakinsu, su Aminu suka bita da gudu suna kuka.

Hawayene suka zubo mun. Kallona ya kuma yi yace.

"Shaye shaye kika dawo dayi kenan a gidana?".

Dama nace maka na dena ne? Ai akai ka ganni kuma a haka ka aureni. Girkine bazanyi ba"

Edit with WPS Office

"Wallahi ba'ayi ƴar iskar macen da zata kawo mun wannan irin iskancin in ƙyaleta ba. Ko kiyi girkin ko ki tattare ki koma gaban iyayenki wallahi, kuma karki kuskura ki tafi mun da yaro ko ɗaya. In yinwa ta isheki da kanki zaki dawo kuma kiyi duk abinda na saki. Kinsan ni ruwan randa zan sha in fiki tumɓele da iskanci. Na gaji da aurenki wallahi na gaji.

Murmusawa nayi cikin tsiwa nace dashi.

Idan kaya ya gaji gammo ma ya gaji Babangida kacigari. Kai a tunaninka mutuwa zanyi ne in na bar gidanka ko me? Kayi kuskure wallahi zan tafi ga gidanka nan ga kuma yaranka nan suma. Ga kuma ƴar Shuwa itama da sannu zaka san kai da kanka ka daɓa ma kan ka wuƙa. Sai dai bari in tunasar dakai sakina tamkar ka karɓi tikitin tainuwarka a hannunka ne"

Fuuuu na wuce ɗaki na soma firfito da kayayyakina ina sakawa a  akwati duk wata atampa mai tsada saida na naɗe abina. Inayi ina kuka, ga fargabar tafiya da zanyi in bar yarana, to wa zai kula mun dasu kenan inna tafi na barsu? In kuma ban tafin ba bansan abinda zai biyo baya ba.

Jingina nayi a jikin  sib ɗin ina tunanin yaya zanyi.

Zuchiya ta debe ni na zari hijabina na fito jaye da akwatina. Da gudu yaran suka iso suka rungumeni suna kuka, Mardiyya tayi sauri ta karɓe akwatin dana ƙanƙame ta shigar dashi ciki ta dawo ta tsugunna a gabana.

"Ummi kar ki je ko ina dan Allah. Ke kaɗai muke gani muji daɗi a cikin gidannan kiyi haƙuri ki zauna zanyi girkin kinji wallahi zanyi musu duk abinda suke so Ummi kada kije ko ina"

Allahu Akbar yarana dukkansu harda Malama suka ja hannuna suka mayar dani ɗaki suka zaunar dani a bakin gado.

Aminu da Adɗa'u suka shiga mayar mun da kayayyakin dana zubar a ƙasa da wanda na zuba a akwati. Malama ta ɗafeni ɗab

Nima bana fatan in tafi in barku yarana kune sanyin idaniyata kune farin cikina. Nayi imani inna tafi na barku lalacewa rayuwarku zata yi nama ya dahu romo danye kenan.

Duk wannan maganganun a zuchiyata nake yinshi ina ta kallon su Adɗa'u da suketa jera kayayyaki. Nayi shiru ina sauke ajjiyar zuchiya.

Wayata dake jakata ce naji halamar shigowar saƙo na ciro a jakar hannuna.

Khalid ne ya mun saƙo yana tunatar dani ya kamata yau monday na dawo asibiti ne. Sannan yana son ganina a keɓe.

Rubutu na soma yi mishi na amsa.

Mu haɗu a wani waje na shakatawa inda kasan ba za'a iya ganinmu ba. Ka shirya haɗuwar taran dare, kar ka kirani inna fito ni zan kiraka"

Edit with WPS Office

Na tura mishi na mayar da wayar jakata.

Mardiyya ce ta shigo da sauri.

"Ummi na kai musu abincin dana dafa mana, na ɗaura mana taliya mu"

Agogo na kalla nace.

Me kuke yi baku ci abincin ba dama?"

"Ummi ke muke jira ki fito in kika ci sai muma muci"

Murmushi kawai nayi. Iya wannan kalamin sai ya ragema zuchiyata turirin da take yi.

Allah yayi muku albarka in sha Allah bazan tafi ko ina in barku ba yarana. Mardiyya kullum ina miki nasihar ki rike mutuncinki kar ki bari samarin wannan duniyar su rudeki, duk wanda yace yana sonki ki tabbatar kin zo kin sanar mun, kar ku kula samari a titi.

Aminu kaima ka haɗe kanka da Aɗɗa'u, Malama itace karama ko bayan raina kar kuyi wasarere da zumuncinku.

Su kai shiru na jima ina musu nasiha masu ratsa jiki.

Yarannan suka gyare mun ɗaki tsab muka fita falo tare dasu sai ga wasu mata sun shigo har su biyar. Yaran suka bamu waje nan muka gaggaisa ko wacce ta soma jero mun damuwarta.

A_a ya'isa haka dan Allah na dena wannan harkar na ajjiyeta ku yi haƙuri ku nemi wasu"

Ai wacce ta fisu zakewa tunda suka zo jin na faɗi haka ai saita zube a ƙasa harda kuka.

"Sabuwa kiyi mun rai. Wallahi babu kalar malaman da ban bi ba babu biyan buƙata ance mun wajenku ne kat. Ko nawa kike so zan baki"

Hmm wallahi na dena ne baiwar Allah. Kema ina mai baki shawarar ki dena kashe kuɗinki a kan ɗa namiji in rijalu ne kina rufe wannan ƙofar zai ɓallo miki wata ƙofar. Keke nan a cikin seseta al'amura. Ni kaina bokancina bai tsinanamun komai ba tunda ƙasa bata nuna mun mijina zai auro mun aminiyata ba, kasa taci amanata waye ku da ƙasa ba zata ci amanarku ba?"

Naja bakina na tsuke sukai mun magiyar duniya, nima na ƙeƙashe ƙasa nace nadena.

Suna fita na dakko tiren da ƙasar duban take ciki, da carbi, da turarukan aikin da magungunan duk naje ta kofar bayan kitchen ɗina na cinna musu wuta. Ina tsaye ina kallon wutar dake ci bal_bal wallahi zafin da nake ji a zuchiyata yafi na wutarnan. Idanu na lumshe na koma ciki.

Haka wunin ranar ya kasance da daddare nayi sakwara da miyar ɗanyen kifi harda Yar shuwa nasa a kula Mardiyya ta kai musu ta dawo da kulolin na rana da ta kai abincinma ko ci ba'aiba dan wulaƙanci. Kwafa kawai nayi.

Edit with WPS Office

Tunda nayi sallar isha na soma shirin fita dan Khalid yayi mun text din inda zamu haɗu dashi. Duk da inajin tsoron fitar ita kanta, amman zuchiyata nutsuwa take buƙata ina bukatar wanda zai rarrasheni a wannan yanayin da nake ciki in samu kafaɗar da zan kwanta in yi kukana.

Karfe tara daidai na fito. Saye nake da doguwar riga abaya mai ruwan toka, na yane kaina da mayafinta, sai baƙin takalmi da baƙar jalata ƴar karama. Ko mai ban shafa a fusksta ba balle azo batun kwalliya, fuskar da idanun a kumbure suke sossi ma.

ɗakin yaran na leƙa na tarar duk suna baccinsu.

Sabuwa anya kinyi ma kanki adalci kuwa, dama su kansu yaranki?"

Zuchiyata ce ta gargadeni girgiza kai kawai nayi na fice a hankali, tare da toshe bakina da hancina da abinda ma'aikatan jinya ke amfani dashi yayin tiyata ( face mask).Harna fice a gidan banyi tunanin akwai wanda ya ganni ba. Babangida ma baya gidan dan banga motarshi ba.

A tsorace na samu abun hawa.

Malam Dutse Royal hotel zaka kaini. Nawa zan biyaka ni kaɗai zaka ɗauka?"

Mai mota yace.

"Ki bayar da dubu da ɗari biyar ki shigo muje"

Gabana na faɗuwa na buɗe gidan baya na zauna. Na yima khalid text cewar ina hanya ya fito ya tarbeni daga get.

Jingina bayana nayi da kujerar motar. Wasu zafafan hawaye sukaita zubowa daga guraben idanuna.

Ina tuno abubbuwa da yawa game da dutse Royal hotel ciki harda daren ƙaddarar daya zarge rayuwata muka zama abu ɗaya dani da Babangida.

Idanuna la buɗe a hankali ƙwaƙwalwata ta shiga tariyomun abubbuwa masu nauyi, iskar waje sai kaɗani take yi zazzaɓin dake jikina ina ƙara jinshi kau.

"Malama mun iso fa harna tsaya naga baki sauka ba."

Kafin ma in Kai ga bashi amsa, ko in kai ga bashi kuɗinshi sai ganin Khalid nayi a tsaye ta gefen direba.

"Malam nawa ne kuɗinka?"

Cewar shi Khalid dake magana da Direba amma idanunshi na kaina.

"Dubu da ɗari biyar mukai da'ita. Amman Alhaji in ka ƙara mun ma bazan ƙi karɓa ba"

Dariya Khalid yayi, ya zaro dubu biyu ya bashi. Ya dago da kallonshi gareni.

Edit with WPS Office

"Sakko muje, ko saina taimaka miji naga jikinki babu ƙwari?"

Ɓalle murfin motar nayi na fito. Jakata ya karɓa ya riƙe mun na dinga binshi muna tafiya har zuwa cikin wani waje, wajene inda mazan banza da matan banza ke haɗuwa a sheƙe aya, wasu shaye_shaye da kallon raye_rayen mata ke kawosu, yayinda wasu ya zame musu jiki babu ranar da basa ziyartar irin wajajennan.

Khalid bana son hayaniya sam, ko zamu canja waje?"

Nayi mishi raɗa. Sannan ga mata da mazan cikin wajen da yawansu na sansu suma fa sun sanni.

Hannuna ya jawo na zame da sauri. Haɗe hannayenshi biyu yayi irin na indiyawa ma'ana yana neman afuwata.

Ni dai bance ƙala ba har muka fice a wajen  muka nufi cikin restaurant ɗin wajen. Inda a ciki manyan masu kuɗinmu suke zuwa cin abinci, wasu tare da iyalansu, yayinda wasu suke kawo zawarawansu, ko ƴan matansu.

Muna shiga na hango Maigogul yaci uwar kwalliyar tamkar wani hamshaki tare da wani babban mutum mai faɗa aji sai wata mace ɗaya dake gefen Maigogul a zaune.

Da dukkan halama sana'ar kawalcinshi ce ta kawo shi wannan waje.

Ga farfesun kaji a gaban Maigogul yana ci suna hirarsu hankali kwance.

Duka duka anan na kawo ƙarshen free page.

Ki biya 700 ayi wannan tafiyar tare dake. In kuma a group ɗina kike 500 zaki biya kacal.

Duk wacce ta biya kuɗin littafinnan tamkar anyi haɗin guiwa da'itane wajen taimakawa marayu

Na rantse da Allah ko nera biyar bana ci a kuɗin duk dana samu daga littattafaina saima ƙarawa da nake yi daga aljihuna dan taimakama bayin Allah marayu

700 ne kuɗin karatu

Amman duk wacce take cikin wannan gida mai albarka zata biya 500 ban cire kowa ba ko ba zaki yi karatu ba ki saka 500 a taimaki marayu dashi

Lambar asusun bankin saka kuɗin gashi a ƙasa.

Edit with WPS Office

0044442984

Buhari Ibrahim Ladan Gt bank.

Ku biyo ni dan ji yadda zata kasance taku har kullum....

MRS BUKHARI

https://chat.whatsapp.com/IUKFTeuI76p2VaAvQ5nk0U

Ina manyan mata masu capacityn  suke?  ku fito lambarku ce ta fito.

Yar uwa turaren wuta kike nema nau'ika daban_daban masu musulmin ƙamshi da kama muhallu? Ba itacen banza masu sanya gida ƙauri da hayaki kamar an kunna taohuwar bespa ba.

Matso gasu MRS  BUKHARI B4B GIDAN KAMSHI nazo miki da duk abinda kike buƙata na ƙamshi. Kama daga turarukan wuta irin na gidan alfarma. Zuwa humrori iri daban daban masu musulmin ƙamshi da riƙe jiki.

Bugu da ƙari muna da turarukan kaya, na fesawa dana turara kaya.

Muna da kulaccam nau'i daban daban masu gyara jiki da lausasa  fata mata, ga kuma ƙamshi mai inganci.

Muna da turarukan tsugunno na musamman masu sirri Hajiyata

Muna da room freshener iri_iri

Muna da mopping mix masu kama waje.

Akwai turarukan kafet dana kujeru.

Sannan akwai box _ box  setika na Hajiyoyi masu ƙyallin goshi.

Muna da Amarya package.

Edit with WPS Office

Muna da uwargida package

Muna da maijego package

Muna bayar da sari ko a ƙasar waje kike, muna tura kaya

Saudiyya

Nijar

Ghana

Camaron

A duk ƙasar da kike kayanmu zai iso miki cikin aminci da yardar Allah.

Hajiya akwai Humrar matan aure wannan ta musamman ce.

Duk wani abu da kika sani na ƙamshi babu irin wanda bamu dashi a kamfaninmu.

Muna da turaruka designer na maza da mata wanda kamfaninmu ke bugawa Hajiya babu inda zaki je ki ci karo da mai irin ƙamshinki.

MRS BUKHARI B4B GIDAN KAMSHI TAZO MUKU DA DUK ABINDA KUKE SO NA KAMSHI HAJIYA.

KUNSAN KANURI MUNE KAMSHI DAMU AKE KOYI

SIYAN NAGARI MAIDA KUDI

MUNA MARABA DA MASU SIYAN ƊAYA KO SARI.

LAMBAR DA ZA'A SAMENI KAI TSAYE ITACE.

Wa.me/2348179523215

SAI NA JIKU

Bincike ya nuna sama da mutune miliyon goma sha biyar ke shan muyagun ƙwayoyi a najeriya.

Hakan kuma ya jawo asarar rayuka, taɓarɓarewar tarbiyya. Ya haɓɓaka fitinu da manyan lefuka a arewacin najeriya dama ƙasar baki ɗaya.

Tun kafin zama ya gagaremu mu koma bacci da ido ɗaya a buɗe. Lokaci yayi da zamu haɗa

Edit with WPS Office

ƙarfi da ƙarfe domin mu taimaka ma hukumar yaƙi da sha da fataucin miyagun ƙwayoyi.

Dan ganin mun kawar da wannan ta'asa dake shirin zame mana ruwan dare.

Shaye_shaye annobace ga al'umma.

Wannan saƙone daga hukumar yaƙi da sha da fataucin miyagun ƙwayoyi wato ( NDLEA)

A bayan kujerar da suke muka zauna. Ina girgiza kaina. Maigogul sai dariya yake yi yana shan farfesu.

"Me kike bukatar ci ko sha in sa a kawo miki?"

Hmmm Khalid kenan ruwa kaɗai ya isheni, dama zan samu sigari ne da sai in ɗan busa kirjina yayi nauyi da yawa gaskiya"

Kallona yayi ido cikin ido ya girgiza kai irinna cikakkun ƴan bariki.

"Har yanzu baki dena shan taba ba? Ai na ɗauka tunda kinyi aure harda haihuwa kin watsar da maganar shaye_shayennan. Kuma kinsan yanzu baki da ishasshiyar lafiya, ciwon hawan jini baya shiri da irin waɗannan abubuwan asalima yana iya jawosu."

Dariya nayi nace.

Khalid kenan mai bunu a ƙugu ke kai gudunmawar gobara. In zaka bani sigari ka bani kawai"

Dariya yayi mun ya wuce inda ake saka odar abinci.

Ina zaune kaina da zuchiyata suna buga wani tambura, a gaban idanuna wannan Alhajin dake teburin su Maigogul ya dunƙulo kuɗi ya bashi, da sauri ya saka kuɗin a aljihu yasa kai ya fice sai ƙamshi yake yake zubawa, yayi kyau ina faɗa muku fiye da shi Alhajin ma.

Kaina na girgiza wasu hawaye suka zubo mun, zuchiyata tamkar zata fashe dan zafi. Shikenan shi Maigogul haka rayuwarshi kenan zata ƙare?

Dawowar Khalid ne ya seseta mun nutsuwata. Gashasshen kifi lafiyayye ya dure a gabana da soyayyen dankalin turawa, sai ruwa da kwalin sigari harma da ashana.

Edit with WPS Office

Ɗaukar kwalin sigarin nayi na zaro ɗaya na kunna, ba shiri na buɗe fuskata na soma zuƙar sigarinnan idanuna a lumshe dan tsabaragen daɗin da nake ji.

Shi kuwa yana cin nashi kifin hankalinshi na kaina baice mun ba, bance mishi ba. Har saida na shanye kara biyu ina shirin ɗaukar ta ukune yayi saurin ɗauke kwalin. Idandunana jawur dasu na kalleshi.

Da kasan irin sauƙin da ruhina ya samu da ba zaka ɗauke ba. Khalid damuwar dake damuna da yawa"

Kur yayi mun da idanunshi .

"Sabuwa ba sigari bace kaɗai maganin matsalarki ba. Yau na sake tabbbarwa lallai kina cikin deepretion mai tsanani. Amman in kika nutsu zan zame miki maganin damuwarki. Bani labarin bayan rabuwa"

Murmusawa nayi nace.

Ina ka shiga bayan rabuwa? Ni kasan gidan aure na shiga ina da yara huɗu biyu maza biyu mata. Ga tarin tulin takaicin ɗa namiji da yai mun katutu, ga matsaltsalun rayuwa da suka addabeni. Wannan dalilinne yasa na zaɓi fitowa in shaƙi iskar duniya mai sanyi, gidan da rayuwar sun mun duhu"

Dariya na yi kamar wata zautacciya. Shima dariyar yayi yace.

"Bayan rabuwarmu ingila na koma, kasancewar mahaifina yana da burin son ganin nayi karatu mai zurfi. To nayi karatu mai zurfi har Allah yasa na soma aiki acan daga baya na yanke shawarar in dawo ƙasata kawai. Kinsan masu iya magana na cewa kowa ya bar gida gida ya barshi"

Murmushi nayi nace.

Hakane. Aure fa ba ka yi Aure bane har yanzu Khalid?"

Sai da yayi dariya mai isarshi kafin yace.

"Meye yazo zuchiyarki da kika gammu a nan a zaune muna hira? Na ɗauka wannan zai farune kaɗai a cikin duniyar mafarki. Ban taɓa tunanin zan sake tozali dake ba a rayuwata ba. Banyi yinƙurin zuwa gidanku ba domin Sagi tun ina ingila ya sanar dani kinyi Aure. Rayuwar da muka gudanar a baya a tsaye take ƙyam a zuchiyata. Sabuwa aurenki da ƴaƴanki ya kasa ture sonki da matsayinki a zuchiyata wallahi"

Kallon kallone ya shiga gudana a tsakankaninmu zuchiya ita kuma da bata da ƙashi tuni ta shiga zigani gami da yi mun ingiza mai kantu ruwa a game da Khalid. Abubbuwan da suka faffaru a shekarun baya na dinga ganinsu muraratan a idan zuchiyata.

Ajjiyar zuchiya na sauke.

Edit with WPS Office

To yanzu me kake so dani Khalid. Kasan ina da Aure fa?"

"Aurenki banyi tunanin zai zama shamaki ba a tunanina. Ni dai ki bani wata ƴar dama kawai Sabuwa. Zan baki kulawar da duk duniya babu wanda zai iya baki. Ke kin sanni ko a baya ai, nayi imani bayan mun rabu baki ƙara samun kulawa daga wajen ko wanne namiji makamanciyar ta Khalid ba. Khalid da banne ke kin sani"

Kana da Aure, ko dai tambayar nauyi take ma harshenka ne?"

Kafin ya bani amsar da nake son ji. Wayarshi ta bani amsa Matarshi ke kiran wayar ga sunan ɓaro_ɓaro Matas. Kallona yayi ya yimun dariya tare da nuna mun kwalbar wayar tashi.

Murmushi kawai nayi na soma cin kifina tare da kallon agogon dake tsintsiyar hannuna daya nuna sha biyu saura kwata.

"Dear yaya akayi, har yanzu baki yi bacci ba?"

Cewar Khalid. Ta cikin wayar bani da kunnen sauraron me tace dashi na dai ji ya mayar mata da martani da cewar.

"No aikine ya riƙe ni kin ganni a asibity inata fama da marasa lafiya. Ban san ko zan samu dawowa gidan ba ƙila kuma sai zuwa safiya"

Duk wannan Maganar da yake yi idanunshi ƙyam a kaina yana ta cike ni da kallonshi mai rikitarwa.

Murmushi nayi a raina nace.

Oh wato da aiki maza ke ninke matan gida baibai, su fita sharholiya da ƴan matansu. Matan cikin gidan basu da darajar matan wajen, sannan sunfi samun lokacin maza fiye da matan gidan.

Duk da dai wannan karatune daɗaɗɗe a ƙwaƙwalwata . Baga mahaifina shi kanshi bai jima da ficewa a nan wajen ba. Shekara nawa kenan a haka nasan Maigogul yau ya kwana a gida, gobe a hotel, jibi yaje kai mata Abuja da makamantan haka dai.

Ohh mu matan gida maza na gara ƙwaƙwalenmu, duk da bana nufin duk maza haka suke da yaudara da ƙarya, akwai maza bayin Allah masu halin dattako."

"Amma me A'isha kiyi haƙuri in ɗaya tayi ki cire rai da dawowata kiyi kwanciyarki, kinsan aikinmu na ceton raine ko?"

Da haka ya yaudare matarshi tas sukai sallama hankalinshi ya dawo gareni kuma, muka shagala da ciye_ciye gami da tattauna hirarrakin yaushe gamo. Zuchiyata kar kuyi tunanin a nutse take sam. Amman inna tuno da manufata, da ƙudirin dake zuchiyata sai in sake inci gaba da dariya a ƙasan raina ina kukan baƙin ciki zubar da mutuncin ƴaƴana da nayi. Bana ta kaina ko Babangida sai iyaka yaran kawai.

Edit with WPS Office

A wannan daren na rage damuwa da dama, na kuma ɗaurama kaina sabuwar damuwa tare da dashen sabon tunani kuma.

Hmmm wajajen ƙarfe uku na dare Khalid ya ajjiyeni a ƙofar gidana. Ya kalleni murya a karye idanunshi cike da so.

"Sai yaushe zan sake samun wannan damar kuma Sabuwata?"

Saida na ja fasali kana nace.

Mu ƙarashe komai a waya. Yau daren naka ne in ka bani shi kyauta saimu ƙarashe kwanan muna chart, ni zan shiga gida sabida gudun ƴan tsurku"

Murmushi yayi idanunshi a kaina.

"To Shikenan. Dani da lokacina ai duk naki ne, ki dinga shan magani a kan lokaci sannan ki daure kiga Dr Layla Dan...."

A_a Khalid"

Na dakatar dashi ina lumshe idanuna mugun bacci nake ji.

Bana buƙatar Dr Layla dan Allah. Babu ciwon damuwar da zai samu nasara a kaina, fatana dai kawai ka tsaya a bayana kawai in zan faɗi ka tallafoni"

Da haka mu kai sallama na sakko da kayan siyayyata. Unguwar babu motsin kowa sai kuka gyare da kwaɗi kawai. Saida khalid ya tabbatar na sa key na buɗe ƙaramar ƙofa na shiga kana naji tashin motarshi.

Tsakar gidan tsit babu motsin komai, a hankali na suɗaɗa na shige ɓarayina. Key nasa na buɗe ƙofar falona a hankali na shiga gabana na dokawa.

Tsaye nayi a ƙofar ɗakin su Mardiyya duk suna bacci hankalinsu a kwance. Kai na girgiza tausayinsu na ratsa duk ƙofofin jikina. To ya zanyi ne? Nayi alƙawarin sai na koyar da Babangida darasi babba a rayuwarshi wanda har gaba da abada bazai mance da Sabuwa ba ko bayan mun rabu.

Kofarsu na ja musu na shige nawa ɗakin, madadin fa in samu sauƙi sai aka samu akasin hakan.

Ina dai kwance na harɗe hannayena a ƙirjina ina kallon sama, tunaninaka masu yawa nayi a wannan daren. Kwaƙwalwata ta tariyo mun rayuwata tun daga farko har izuwa wannan bigiren da nake kai a yanzu.

Wayar Khalid ce ta katse mun hanzarina, ɗagawa nayi na saka a kunnena.

Yaya akayi Khalid nafa ce ka dena kirana a waya ko?"

"Cikin ƙasa_ƙasa da murya yace.

Edit with WPS Office

"Kince zamu ƙarashe komai a waya fa, amman baki online ɗin ma sam"

Idanu na lumshe a hankali tare da cewa.

Ka bari zan kiraka gobe da safe, a halin yanzu bacci nake ji, na kwana biyu ma banji bacci irin na yau ba"

A haka mukai sallama, ina ajjiye wayar bacci mai nauyi ya kwasheni. A wannan daren nayi bacci irin wanda na mance yaushe rabon da in samu nutsttsen bacci mara algus irinshi, ko da na tashi da asuba, sai naji jikina yayi sauƙi sosai, kuma kaina ya rage ciwo da kusan kaso mafi rinjaye.

Da walwala na gama haɗa mana kayan kari ni da kaina yau. Funkason alkama nayi mana dana ga akwai ragowar miyar masarnan har yanzu a firji. Ina kan rabawa Babangida ya shigo kitchen ɗin ina tsaye da Mardiyya.

"Baba ina kwana?"

Ya zare idanu a lokaci guda ya ƙanƙance idanunshi.

"Ubanme kuke yi baku tafi makaranta ba nace?"

Jikinta na rawa dan da tsawa yake magana.

"Dama_dama an yi hutun meet time break ne Baba shi yasa" ( a gafarceni in turancin baiyi daidai ba)

"Okay dan anyi hutun makarantar boko islamiyya ma sai aka ce kar kuje ko Yaya, ita Sabuwan ce tace ku zauna a gida?"

Bata ce komai ba.

Tsawa ya daka mata tare da kawo mata duka, bai sameta ba ya sameni a kafaɗata fab, dukan ya ratsa ƙashin kafaɗata ya dinga gangarawa a hankali. Sama da ƙasa Allah baisa ko kallonshi nayi ba. Dan a wannan lokacin ji nake yi tamkar in shaƙeshi inta gwara kanshi da bango.

"Kayi haƙuri dan Allah. Saboda bata da lafiya ne shi yasa, ni nake yin girki"

Baki ya riƙe ya kalleta, ya kalleni niko wallahi kamar ma bansan yana kitchen ɗin ba haka na nuna.

"Oh jiya ma ke kika yi masar da aka kaima Habibaty kenan?"

Da ɓarin murya tace"

"A_a ragowar ta biki ce muka dumama"

"Kuka ɗumama, abinci rana kuma fa shima ke aka bari kikayi ko?"

Edit with WPS Office

Kai ta ɗaga mishi halamar  E ita tayi shima.

Cike da hargagi da zagi ya koreta a kitchen ɗin da zata fita yasa ƙafa ya tokareta.

Nifa nazo wuya a mugun hasale nake, ji nake kamar in yi kukan kura in rukunkune wuyanshi duk wacce za'ayi ayi.

"Ke Sabuwa dan iskanci nace kiyi girki ma matata shine zaki sa yarinya tayi. Dan bura'ubanci kuma har da wani dumamen masa?. Nace ki tafi gidanku, ki tafi gidanku kwaɗayi da son abun duniya ya hanaki tafiya. Gaki ga gidan ai"

Sama da ƙasa Allah bai bani ikon tanka mishi ba ya fita fuu.

Wawuyar ajjiyar zuchiya na ja na baƙin ciki, naci gaba da rabon funkasonnan ina jujjuya maganganun Babangida. Ina zuba miya sai na jiyo karan takalmi kwas_ƙwas ta bayana da wani ƙamshin humra. Irin ta matan aure sak ta MRS BUKHARI B4B GIDAN KAMSHI.

Ina waigowa muka haɗa idanu da yar shuwa ta caɓa ado, ta ɗauko jar lafaya ta naɗe jikinta dashi, gashin data ziro ta gaba iyakar tsawon wuyanta.

Ina kan ƙare mata kallo Babangida ya tsaya a bayanta.

"Ya baki shiga ba Habibaty na ganki a tsaye. Ko ina fa gidanki ne, ki shiga kiyi abinda ya kawoki mana?"

A mugun shagwaɓe ta juya suka fuskanci juna, tana magana tana gyara mishi tsayuwar boturin rigarshi.

Murmushin baƙin ciki da takaicine ya subuce mun. Na girgiza kai ina ta zuba murmushi in da ranka ka sha kallo.

"Naga uwargidanka tana ciki, ga abinci ta baza, ya kamata ta gama kafin in shiga ai Jannaty".

Kamar tayi mishi allura ya wuce ta ya shigo ya soma tattare abincin yara dana zuba yana fita dashi.

"Sabuwa ki koma ɗakin ki Habibaty zata yi amfani da kitchen ɗin ɓarayinnan kafin a kawo mata gas ɗinta"

Cewar Babangida fa, yana jan tukunyar miya nima ina ja.

Abincin ba gashi na gama ba, harda ita Habibatin nayi ai"

Na faɗa a hasake dan ji nake kamar in watsa musu miyarnan.

"Ai ke baki da kunya duk abinda nace sai kinyi musu. Nan gidanane kuma tana da damar da zata shiga duk inda take so a cikin gidan. Wallahi in cewa tayi wannan ɓarayin da Baba Malam ya zaɓa miki take so, dole ki fita ki bata. Ke akan Habibaty babu abinda bazan iya ba fa"

Edit with WPS Office

Yana riƙe fa da tukunyar miyarnan yana ja ina ja. Tsabar haushi na sakar mishi tukunyar, to dake ya riƙe ya ja da ƙarfi ina sakewa miyarnan tai musu wanka daga shi har Amaryar tashi, ga miyar da zafi.

Naga makirci ido da ido ranar, ba sai Yar shuwa ta faɗi ta daka wani irin ihu ta sume ba.

A zabure Babangida yayi kanta idanunshi a rufe idonshi cike da miya ga yaji.

Rigar jikinshi ya tuɓe ya goge fuskarshi da'ita ya shiga jijjiga Yar shuwa. A guje Hamida ta shigo har inda muke, ganin halin da ake ciki saita sake zuzuta lamarin harda kukanta.

Ranar ni naga makirci, lamarin da ya sake jagula lissafin komai da komai na rayuwata kenan

Funkason da banci ba kenan dan saida Babangida ya kwakkwaɗamun maruka har saida ya fashe mun baki, ya shaƙeni a jikin bango na dinga kakari, da ƙyar na harhaɗo ƙarfina na tureshi yaje ya daki gas. Sai da yaga na zaro wuƙa ya shiga taitayinshi dani.

Ita kuma mitsiyaciyar tana kwance ta farfaɗo Hamida ta yayyafa mata ruwa.

"Bana gani Jannati matarka ta kashe mun idanuna"

Ranga_ranga Babangida da Hamida suka kinkimeta.

"Kafin in dawo ki tattare inaki inaki ki bar gidannan mara zuchiya wacce bata san mutunci ba. In ko kika bari na dawo na sameki wallahi saina kasheki, kuma na kashe banza dan ba gata bane dake"

A gaban kishiyoyina fa akemun irin wannan cin kashin.

Idanuna na lumshe ina murmushi kawai.

Ina fita a kitchen ɗin dokin zuchiya, da baƙin ciki yasa na shige ciki na zari hijabi da jakata sai wayata, ga bakina a fashe, ga wuyana inda ya shakeni duk ya fashe.

Dakin su Mardiyya na leƙa ƙananun sunata kuka ita da Aminu kuma sun yi tagumi.

Ga abincinku ku fito kuci, ni zan je kemis ɗin bakin titi. Kar ku je ko inafa"

Ina gama faɗin haka nayi sauri na fice dan bana so suga hawayen daya tawo a guje.

Ina fita na hau abin hawa zuwa gida.

Ina zaune a abun hawan ina share hawayena a raina ina aiyana na bar Babangida har abada ko da kuwa shine autan maza.

Khalid ne ya kirani a wannan lokacin, ina ɗagawa na rushe mishi da kuka duk na bi na tashi hankalinshi, sama da ƙasa in yi magana na kasa wayar kawai na zare na danna a jakata.

Edit with WPS Office

Dana sauka a bakin layinmu sai na cusa rabin fuskata a hijabi gudun kar magulmata suga halin da nake ciki.

Da sallama na shiga gidan

A cike tsakar gidan yake anata rikici da Rakiya dai akan waɗannan karnuka na Gaza. Gida ya cika maƙil harda maƙota.

Ina shiga Gaza ya tawo daga lungun ɗakinmu a guje da adda.

Dukka taron matannan aka shiga tururuwar gudu, duk ɗakin dake kusa da kai nan zaka faɗa.

A guje nabi tawagar matan muka faɗa wani ɗaki mune har kan gadon matar.

Sa kuɗin karatunki a cikin wannan asusun domin taimakon marayu.

Yar uwa daure ki shiga jerin masu ganin marayu sun samu rayuwa mai kyau

0044442984

Buhari Ibrahim Ladan Gt bank

MRS BUKHARI

IDAN KAYA YA GAJI...

GAMMO MA YA GAJI

BADIAT IBRAHIM MRS BUKHARI B4B GIDAN KAMSHI

LITTAFI NA FARKO

SHAFI NA GOMA SHA SHIDA

Edit with WPS Office

Ina manyan mata masu capacityn  suke?  ku fito lambarku ce ta fito.

Yar uwa turaren wuta kike nema nau'ika daban_daban masu musulmin ƙamshi da kama muhallu? Ba itacen banza masu sanya gida ƙauri da hayaki kamar an kunna taohuwar bespa ba.

Matso gasu MRS  BUKHARI B4B GIDAN KAMSHI nazo miki da duk abinda kike buƙata na ƙamshi. Kama daga turarukan wuta irin na gidan alfarma. Zuwa humrori iri daban daban masu musulmin ƙamshi da riƙe jiki.

Bugu da ƙari muna da turarukan kaya, na fesawa dana turara kaya.

Muna da kulaccam nau'i daban daban masu gyara jiki da lausasa  fata mata, ga kuma ƙamshi mai inganci.

Muna da turarukan tsugunno na musamman masu sirri Hajiyata

Muna da room freshener iri_iri

Muna da mopping mix masu kama waje.

Akwai turarukan kafet dana kujeru.

Sannan akwai box _ box  setika na Hajiyoyi masu ƙyallin goshi.

Muna da Amarya package.

Muna da uwargida package

Muna da maijego package

Muna bayar da sari ko a ƙasar waje kike, muna tura kaya

Saudiyya

Nijar

Ghana

Camaron

A duk ƙasar da kike kayanmu zai iso miki cikin aminci da yardar Allah.

Hajiya akwai Humrar matan aure wannan ta musamman ce.

Duk wani abu da kika sani na ƙamshi babu irin wanda bamu dashi a kamfaninmu.

Muna da turaruka designer na maza da mata wanda kamfaninmu ke bugawa Hajiya babu inda

Edit with WPS Office

zaki je ki ci karo da mai irin ƙamshinki.

MRS BUKHARI B4B GIDAN KAMSHI TAZO MUKU DA DUK ABINDA KUKE SO NA KAMSHI HAJIYA.

KUNSAN KANURI MUNE KAMSHI DAMU AKE KOYI

SIYAN NAGARI MAIDA KUDI

MUNA MARABA DA MASU SIYAN ƊAYA KO SARI.

LAMBAR DA ZA'A SAMENI KAI TSAYE ITACE.

Wa.me/2348179523215

SAI NA JIKU

Asusun da zaki saka kuɗin karatunki

0044442984

Buhari Ibrahim Ladan Gt bank

BABANGIDA:.

Bayan sun fito daga asibity shi da su Hamida da ƴar shuwa da take ta faman raki, idanun nata sun ƙanƙance sun kuma yi ja dake miyar da yaji. Amman duk ragowar abubbuwan da suka faru makircine kawai burinta ta fitar da Sabuwa a gidanta shine kawai.

Babangida yana tuƙi yana tsaki lokaci zuwa lokaci. Yar shuwa kuma sai tunanin hukunci mafi ɗaci da zata yanke a kan Sabuwa dan gane da wannan wulaƙancin da tayi mata akan kitchen take ta yi.

Ta lashi takobin sai Sabuwa ta wulaƙanta sai ta fasa ƙwan da aka ɗauki shekara da shekaru ana ririrashi dan gudun faɗuwarshi da warinshi.

Murmusawa tayi da ta tuno da irin samfurin irin ramakon da zata yi ma Sabuwa akan miyar data

Edit with WPS Office

watsa mata kafin tsarin abubbuwan data tsara su biyo baya. Duk da dai ko  babu komai Sabuwa zata je ta zauna a gida cikin turmutsutsun yayye da ƙanne, ga ba abinci, ba wajen kwanciya, ga tunanin ƴaƴanta data baro. A duniya ta kwana da sanin babu abinda Sabuwa ta tsana kamar barin yaranta da barin gidan Babangidan kanshi.

"Wallahi ni na gaji da halayyar Sabuwa, na gaji kwata_kwata da'ita. Ace mace bata da aiki sai taurin kai da kangaremun a matsayina na mijinta? Allah ya bata sa'a inje gidan in samu tana ciki zata ga ɗanyen hukuncin da zan yanke a kanta mai tsaurin da sai ya girgiza zuriyarsu. Yanzu da shikenan ba dan Allah ya taƙaitaba sai dai a buga mu a jarida da babbakakkiyar fuska kenan. Zafin kishi yasa ki kwatsa ma miji miya da kishiya dan baƙin hali"

Hargowar Babangida ce ta katse mata hanzarin tunaninta ya katse ba tare data gama ayyana muguntocin da take son shiryama Sabuwa ba.

Hamida dake  bayan motar tare da jinjirarta a goye tace.

"Ai bata kyauta ba wannan irinsu ne masu kashe miji, ko su tafasa ruwa su watsa ma mutum ya mutu a banza."

Murmusawa Yar shuwa tayi da taji aidiya tazo mata a cikin maganganun Hamida. Ai kuwa sai ta ce.

"Jannati dama ni maganarce ban yi ba. Daga nan kai tsaye ofishin ƴan sanda ya kamata mu wuce mu kai rahoto ayi a rubuce duk abinda ya same ni Lolo ce, kuma duk abinda ya samu lafiyar idanuna sai mun yi Shari'a. Dan Lolo zata iya kasheni ma yadda take jin haushin na aureka, kuma kaga yanayin rashin tarbiyyar gidansu ai"

Kai ya gyaɗa halamar gamsuwa da abinda tace. Hamida ta daura da cewa.

"Tun wuri kafin matsalar ta girma gara aima tubkar hanci gaskiya watsa miya mai zafi a fuska babban laifine ba dan ALLAH ya taƙaita ba da yanzu wats Maganar akeyi. Ni kuma ina ganin sabida kin fita kyaune tasa taso ta nakasa miki fuskar"

Da wannan ziga ta su Hamida Babangida ya wuce chaji ofis, a zuchiyarshi yana jin daɗin Sabuwa zata shiga sabon ruɗu duk da a gefe kuma yana shakkar kada Baba Malam yaji ya kai Sabuwa chaji ofis yasan abun bazai yi mishi kyau ba, bashi kaɗai ba har Malama Babba. Amman sai da suka je suka shigar da ƙara tare da ba da kwatancen gidan su Sabuwa ma ƴan sanda.

"Zamu je mu tawo da'ita Alhaji, kaje in nasa yara suka kawota zan kiraku ayi a rubuce ai musu tsakani"

Cewar D.O.P kenan.

"To Shikenan D.P.O sai na jika zamu zauna a cikin shiri."

Edit with WPS Office

"Ok ai danma Hajiya tana da kyan zuchiya tace dai tsakani kaɗai take so ayi musu, da ba dan haka ba kes ɗin ai babbane. Yanzu haka muna da kes a ƙasa makamancin wannan uwargida ce ta ɓara ma mijinsu kai da taɓarya a daren da yayo aure. Shi mijin yana asibiti, ita matar muna tare da'ita anan kotu zamu turasu."

Nan dai su kai sallama da D.P.O

suka dawo gida.

Suna shiga ɗaki Yar shuwa tace.

"Jannati nace ba, tunda naga akwai ɗaki dake gefen turakarka me zai hana a mayar dashi store ɗin gidan ka dinga jibge abincin a can, in yaso duk wacce zata yi girki sai taje ta ɗiba. Naga ɓarnar da Sabuwa take yi da abinci yayi yawa hakanne yasa ƴan uwanta suke yawan zuwa, aita ɗaura tukunya ana saukewa, banda wanda take dafawa in zata gida. Ni na taɓa ganin an dafa abinci an tafi dashi gida ba Sallah ba ba komai ba in ba a wajen Sabuwa ba."

Nan Yar shuwa ta dinga yi ma Babangida Famfo, tare da haɗawa da ƙaryarta, dama kuma me neman hanyar takurawane aka nuna mishi hanya.

Yana shafa fuskarta yace.

"Hakane kam, ina takaicin wanda take dafawannan ta kai gidansu wallahi. Duk ƴan kajin nawa tai musu miya"

Murmushi Yar shuwa tayi da ta fahimci zugarta na samun shiga.

"Ah ko ni sau nawa ta sha auna abinci ɗanye, dasu Maggi tana bani ina miƙawa gidansu? Ai ko su Labbai da su Adama duk sanda suka zo sai ta auna musu abinci sun tafi dashi gidajen nasu"

Kai ya shiga girgizawa cikin ɓacin rai tare da jin zafin barnatar mishi da dukiya da akeyi yace.

"Zan kwashe komai kuwa na kayan abincin ɓarayin sabuwa, ita Hamida ki bar mata nata tunda ita bata ma da dangi a gari balle su zo tai ta mun ɓarna"

Ai take Yar shuwa ta haɗe rai. Me ta tuna_me ta tuna kuma sai ta yi maza ta saki ranta tace.

"Ai gara ayi dukka. Kar ka mance tun kafin in shigo nayi ma alƙawarin sauya tsarin gidannan ya dawo kan seti ko Jannati?"

Murmushi yayi ya kamo ƙugunta yana shaƙar ƙamshin humrori irinna matan Shuwa masu tasiri da sirrin rikita miji da sanya mishi nutsuwa ta musamman. ( Duk wacce take so akwai a wajena ta biyo ni pc)

Nan suka dulmiya cikin faranta ran juna. Bayan komai ya lafa ne ya shiga barayin Hamida ya ɗakko musu abinci jallof ce ta shinkafa da wake ta mangyaɗa harda alayyawo wadatacce, ga naman saniya anyi musu ƙananun yanka.

Edit with WPS Office

Suna ci suna farin ciki, anata darzar Amarci, Amarya sai shigewa jikin ango take tana rikirkitashi.

"Ni bansan ma in Hamida ta yi arba'in yaya zanyi in bana jinki a kusa dani ba. Ai Habibati a kwana biyu tak wallahi kin sauya mun tunanina, kin daukeni kin daurani a kan wani tsanin da banma san akwaishi ba."

Dariyar hilata tayi tace.

"Duk matan daka aura kana nufin na fisu kenan ko me?"

Ya ɗan zare idanu tare da ƙanƙancesu duk lokaci guda, irinna cikakkun mazan bariki yace.

"Sosai ma kuwa. Ai duk matan dana aura babu Shuwa, gaskiya matan Maiduguri kuna da wata iriyar baiwa ta musamman da Allah subuhanahu wata ala yayi muku, gashi kun iya saisaita murya tare da watso kalmomi masu daɗin saurare"

Dariya tayi taji wani irin daɗi da nutsuwa ta saukar mata. Lallai ta samu Babangida a hannunta, tana mutuwar sonshi har mamakin yadda take jinshi a ranta take. Aikinta ɗayane kawai ya sallami Hamida dan itace kishiyarta. Ita Sabuwa a tafin hannunta take ita da ita kar ce ta san. Tafi son ta zauna ta shanye bakin ciki kafin a sallameta tayi alƙawarin ita zata miƙa mata takaddar sakinta da hannunta.

Wayarshi ce tayi ruri, da yaga mai kiran, sai ya wayance da tari kamar irin ƙwarewa yayi.

Ta tafi da sauri zata ɗakko ruwa, shi kuma ya ɗauki wayar.

"Sumy bani minti goma yanzu zan zo"

Iyakar abinda ya faɗi kenan ya datse wayar dan Ƴar shuwa ta dawo har ta zauna a cinyarshi.

A baki ta bashi ruwan ya sha.

"Nagode sosai. In ina tare dake kamar kan in fita. Ga yara sun dameni da kira akwai wasu tirela biyu da zasu wuce ikko shine suke buƙatar sanya hannuna. Inaso zanje. Amman ina sa musu hannun zan dawo, in kuma zaki je to muje. Duk da wajene na taron maza bazan so a irin kyau da zati da Allah yayi miki ace kina fita ba"

Wasu kalamai masu narkar da duk wanda akaima tare da sashi yaji babu yashi, su ya raɗa mata tare da sumbatarta. Ta rakashi har gaban mota sai da ya fice tukunna ta wuce, tana doka ma Mardiyya harara wacce ta dawo daga get ta buɗe ma Babangida har yarinyar ta shiga ɓarayinsu ta kwaɗo mata kira.

"Ke Mardiyya zo nan"

Rai a ɓace ta iso tare da tsayawa nesa da Ƴar shuwa.

"Uwarki tana cikin gidanne ko ta fita"

Edit with WPS Office

"Ta fita"

Murmushi tayi zuchiyarta tayi sanyi kamar ƙanƙara ta sallami yarinyar ta koma cikin gida. Tana shiga ta tarar da mahaifiyarta na kiran wayarta.

"Mama barka da safiya"

Daga cikin wayar tace.

"Yauwa ya sabon gida, ina fatan Lolo bata baki matsala ba dai ko? Duk da kince a dofane take a gidan, kuma dama mun san da yadda akayi aurenma tun farko?"

Dariya tayi ta nemi waje ta zauna.

"Ke dai bari ai yanzu haka ma tana gidansu nasa ya korota ya horata dan na fi son ta zauna ta ƙunshi baƙin ciki kafin in sa ya sallameta. Mama su Jamila su zo su karɓa muku kayan abinci da kuɗi. Dan ranar da aka kawo ni washe gari yayi mun kyauta ta alfarma. Yabona da ɗayar matar kawai tayi saida ya bata dubu ɗari"

Nan ta shiga ba Mamansu labari har dalilin zuwan Lolo gidansu.

To dama Mama itace jagora kan gaba a gidanta ta tsare gaba ta tsare baya, ta hana mahaifinsu Ya Shuwa ƙarin aure, tun yana nema tana wargaza lamarin, harma ya haƙura ya ɗauko ido ita da yaran ya saka musu.

Da wannan dalilin suma suka lalace, tun kafin su tafasa suke ƙonewa. Babancin Yar shuwa da gidansu Lolo a kan yayyensu maza ne, su a nitse suke kuma suna bin mahaifinsu kasuwa a inda yake siyar da kayayyakin haɗa turarukan wuta, danginsu lubban, Hawee, misik, garin sandal, farce da dai sauransu.

Kuma basa shaye_shaye. Amman matan gidan su uku Yar shuwa itace babba a mata dukkansu a tambaɗe suke yawo kwararo_kwararo kamar dai yadda su Qamriyya suke, shi yasa ma ƙawance ya haɗe wannan ƙawaye waje guda hausawa na cewa sai hali yazo ɗaya ake abota. ( A gaba zamu ji cikakken tarihin zai fito a cikin labarin Sabuwa).

SABUWA:.

Haki na dinga saukewa baƙin ciki yasa na miƙe na fito tsakar gidan. Babu kowa a tsakar gidan sai Gaza yana karta takobi a ƙasa. Takobin na wuta

"Kece maras kunya dan uwarki shine kika fito. Yau saina yanka kowa a gidannan akan waɗannan karnukan nawa"

Edit with WPS Office

Haba Gaza wai meye haka daga dawowarmu gidannan mu kenan baza'a zauna damu lafiya ba kowa sai ya raba hali?"

"Dallah rufa mun baki. Wai ke kin zama ustaziya irin abinda kika diga ai babu shegiyar data diga a cikin ɗakinmu, har ɗakin Hauwan ma.

Kinga su Rahine ne aka saka musu idanu wai saina fitar dasu a gidannan. Ni kuma da a taɓasu gara uban kowa ya mutu Rahine fa da yaranta. ( Sunar karyar Gaza kenan Rahine)"

Ya jima yana zabga tijara shigowar Maigogul da wasu ƴan mata su biyu ne yasa ya harareshi tare da jan tsaki ya wuce su ."

"Ace anyi mutum bashi da aiki sai yawo da mata Hotel_Hotel wannan rayuwar gara na mutu ma in huta." Maigogul yace

"Aikin banza da wofi ƴaƴa du babu na arziki tur da wannan haihuwa dai. Salima ku tawo muje"

"Wai tur da wannan haihuwar Dattijo ai sai dai muce tur da wannan uban wallahi ehh ku kuma wallahi kuci gaba da biyoshi Allah wata rana sai kun rasa kafafun guduwa ma."

Yana gama faɗin haka ya fice a guje tamkar mahaukaci.

Jin muryar Maigogul yasa duk matan gidan suka firfiti, ganin babu Gaza a tsakar gidan suka shiga yin Allah ya isa gami da tofin Allah ya tsine. Ni dai a tsakar gidan na baro su Rakiya suna faɗa da matan gidan. Faɗan rashin gaskiya dan matan gidan sun fisu gaskiya.

Da sallama na shiga lungun, matan lungun suna zazzaune a tabarma ko wacce a dokin ƙofarta. Labbai tana daga wajen kejin karnukan Gaza tana zuba musu abinci da ruwa.

Gaishe da matan lungun nayi, suka amsa a ciki_ciki.

"Lolo kece da safe haka, naga kamar bakin ki a fashe?

Bance mata uffan ba na shige ciki.

Hauwa na takiyar gadonta tana shan shayi da bidedi. Matan da maigogul ya kawo ya ajjiyesu a tabarma a ɗakin Hauwa, shi kuma yana cikin ƙurya ɗakin Rakiya kenan.

Hauwa ina kwana?"

"Lafiya Lolo ya yaran?"

Lafiyansu ƙalau"

Iyakar abinda nace kenan na shige cikin uwar ɗakin, a ciki na tarar da su Aisha suna baccin asara. Uzairu zuchiyata kuwa yana gaban madubin dake manne a bangon ɗakin da farar hoda a hannunshi yana zazzagawa a tsumma yana shafawa kamar wata tsohuwar karuwa. Maigogul yana daga can lungun katifa yana laluben suturunshi.

Edit with WPS Office

"Labbai wai bata  kai mun ruwan wankan bane Uzairu zuchiyata tana ganin baƙi nayi zamu fita?"

Uzairu zuchiyata dake dangwalar yawu yana goge hodar kan gashin girarshi dan ya kwanta yace.

"Ta dai fita ƙila ruwan Takai. Lolo ki zauna kinga ɗakin a hargitse babu masaka tsinke ko? Hmm ni kayana ma zan tattare a ɗakinnan in nemi ɗakin abokai in koma rayuwar ta isheni wlh"

Ni jikinane ya mace mus ganin tsukukun ɗakin ga jama'ar ɗakin sun yi ma ɗakin yawa, ga tarin jakunkunan kayan sawa jibge a hakanma an saka sib ɗin Labbai fa. Komai a matse yake babu masaka tsinke. Akan kujera na zauna, maigogul ya fito daga lungun da wata farar dakakkiyar shadda ɗinkin Sake babban ɗinkin da ko sarakai dashi suke ji, ga hularshi yayi dai-dai da surfanin gaban rigar.

"Lolo ya shi Babangida da yaran?"

Lafiya ƙalau Maigogul. Amman shi Babangida ne ya sallameni"

Kafin in idasa maganata ya yar da rigar hannunshi, Sadiya ta miƙe zaune hannu a ƙirji, Uzairu zuchiyata yayi turus.

"Sakin ki yayi Babangida Ina Malam to?"

Cewar Maigogul da bakinshi har rawa yake yi.

"Wa kuma aka saka ni Rakiya bala'i goma da ashirin?"

Ta shigo tare da neman waje ta zauna.

Ba sakina yayi ba. Cewa yayi in dawo gida. Rakiya Yar Shuwa fa Babangida ya auro dan tsantsar cin amana irin nata. Ko maza sun ƙare ta auri Babangida? Wallahi na gaji da zaman gidan kuma ni bazan taɓa yin kishi da'itaba"

Miƙewa tsaye Rakiya tayi.

"Kika ce Yar shuwa ya auro? Biri yayi kama da mutum. Jiya mun haɗu da uwarta naga an mayar musu da kwanonsu daya fita, muka gaisa ba yadda muka sababa ashe ita ta san me suka shuka. Sabida Allah ya baki gidan rufin asiri shine itama ta tura ƴarta. Wallahi sunci amanar Aminta. Kab layinnan waye baisanki da Yar shuwa ba mitsiyaciya yanzu tana can? "

Labbai ce ta shigo a ruɗe.

"Wacce Yar shuwan naji kuna cewa Babangida ya aura wai? Lolo dama ita aka kawo miki a matsayin kishiya. Lallai Yar shuwa ta cika matsiyaciya. Kuma fa wallahi idona idanta zata ga yadda zamu yi da'ita tab."

Hauwa kanta saida ta shigo kuma ta jinjina lamarin sosai, duba da sun san halin uwar Yar shuwa ciki da bai. Duk su Aisha saida suka tashi barci ya ƙare. Uzairu zuchiyata yace.

Edit with WPS Office

"Kawai tunda bai sake ki ba, kiyi komawarki gidanki ko banza kya ci kaza ki kora da jus, ki kwanta Ac na dukanki. Kuma in tace zata kawo miki wargi ki zage kuci uban juna ko ba haka ba Rakiya? Ai ni nama raina wayonki a wannan gaɓar ko nayi niyyar tafiya wallahi bazanje ko inaba, ki nuna mata iyakarta. Saifa kin fito musu a Yar iskarki ta da za'a samu salama"

"Sosai kuwa. Ai kice zaki bar mata gidan ma kinci baya kuma ita ai hakan take so ace ta koreki ta mallake gidan da aka gina domin ƴaƴanki. Yaranki ki barsu a hannun wa?"

Uzairu zuchiyata yace

"Ku faɗa mata ni kam na fita ina da Appointment"

Ya saka kai ya fita yana kwambo. Maigogul ya zauna a bakin gado a sanyaye.

"Lolo da kika ce kin gaji ba zaki iya zaman gidan Babangida ba. Sai zaman gidannan ne zaki iya sabida baki da tunani? Dubi ɗakin da uwarki take zaman aure Lolo ki dubi naki gidan ko dakin yaranki yafi nan sau dubun dubata. Hatsaniya kuka samu sabida auren Yar shuwa ko? Sai kace bani ne ubanki ba. Ni kinga wani na ɓata mun rai har in kwana cikin damuwa ne?"

Ina kuka na basu labarin abinda yake faruwa.

"Tashi maza. Rakiya ɗau mayafi mu mayar da,ita ɗakinta tun wuri kafin Yar Shuwa ta game binne_binnenta"

Rakiya tace.

"Bari in sa wani abun a cikina. Sadiya ba da hamsin ko waina ce a siyo mun"

Maigogul cikin zaƙuwa yace.

"Wohoho Rakiya. Tashi muje kya karya acan ga abinci lafiyayye acan. Ke Salaha tawo muje ke da Labbai wallahi zaman aure yanzu aka soma, saina shiga na fita na kashe wannan auren cin amanar. Tsubbu zai dawo kenan akan Sabuwa zan iya yin komai"

Mikewa mu ka yi dukka. Sai ga Uzairu zuchiyata ya shiga yana kwaɗa kiran sunana. Saina tsinci gabana da faɗuwa.

"Lolo ƴan sanda na waje suna nemanki. Kuma Babangida ne yasa a kamaki, sai dai basu faɗi dalili ba."

Wasu hawayene suka gangaro mun da gudu, wani kullutun baƙin ciki da nadamar sanin Babangida ya tokare mun maƙoshi.

Maigogul ya fiji hannuna muka fice kab ɗakinmu zuwa waje.

"Me Lolo tayi muku ofisa da kuka zo kamata?"

Cewar Maigogul kenan. Ofiisa yace.

Edit with WPS Office

"In muka je can zata yi bayani Dattijo kuma zata ji abinda tayi. Ke Rose ku kamata"

Wata ƴar doka mace ta tasa ƙeyata zuwa mota, Maigogul da Rakiya suka shiga suma. Akayi _akayi su sauka Maigogul ya tusa tijara dole aka ja motar tare dasu. Salaha da Labbai suka biyo bayanmu.

A kanta aka ajjiyeni ana mun bayanin dalilin zuwana wajen. Kafin ma su gama yi mun bayanin sai ga Babangida tare da Yar shuwa. Sun shigo

Murmusawa nayi kawai ina mata kallo tsana.

D.P.O ne ya umarci mu shiga daga ofis ɗinshi ayi abun a sirrance.

"Ke Sabuwa zaki saka hannu a wannan takaddar ki sani duk abinda ya samu abokiyar zamanki kece sila kuma zamu kamaki. Kinci sa'a sune basu nemi mu turaku kotu ba da kotun zamu turaku. Kes dinki babbane yanzu da kika watsa musu miya da kin babbaka su sai ki fito kafar sadarwa kina cewa ƙaddarace ke baki san kin aikata ba. Dan Allah ki saka hannu anan kafin raina ya ɓaci"

Takaddar ya miƙo mun, na dubi Yar shuwa data ɗaure fuska tamkar ma bata taɓa ganina a rayuwa ba. Na dawo da kallona kan Babangida wanda shima ni ya zuba ma idanu. Na juyo na dubi iyayena gami da ƴan uwana babu wanda yace uffan. Idanuna na lumshe inajin azaba daga ƙasan zuchiyata. Hannu nasa a takaddar hawaye yaso zubo mun na daure na mayar dashi dan dole. Wallahi murmushi ne kawai a kan fuskata tamkar babu, harna kammala na ajjiye biron akan takaddar.

"Shikenan Yar Shuwa Babangida, yana rubuce duk wani abu da zai taso gaba zai mana amfani wannan yarjejeniyar.

"Yaro babu abinda zai faru ma. Wannan daya faru ma tsautsayina. Babangida ina baka haƙuri"

Buɗar bakin Babangida yace.

"Me yasa zaka goyi bayanta alhalin baka wajen abun ya faru? Ko da yake dama kai ka lalata in ba haka ba ai ba zata yi ba.."

Ya ishake wallahi Babangida kacigari. Ya isheka nace, kul ahir ɗinka da cin zarafin iyayena a gaban idanuna"

Na faɗa a tsawace harda miƙewa.

D.O.P ne ya daki bencinshi yace.

"Ya isa haka kisan a inda kike wannan waje ba wajen wasa bane."

", Lolo tawo mu tafi, ai babu komai. Fitsararrene daman can shi yasa. Amman ai ko a gidan giya aka ɗaura aurenku baya mun haka ba"

Edit with WPS Office

Maigogul ya faɗa yana dariya kamar yadda ya saba"

Baƙin ciki kamar ya kasheni haka nake ji.

Haka muka fita Maigogul yaci gaba da bama Babangida haƙuri, shi kuma sai jefo maganganu yake yi. Wallahi Allah nafi ƙaunar mutuwata fiye da auren Babangida kune kuke ganin kamar sanshi nake yi.

Matarshi ya saka a mota ya ja ya barmu a titi muna neman abun hawa, su Labbai kuwa sai kallon ƴar Shuwa suke yi cike da mamakin yadda ta rufe idanunta kamar ma bata sansu ba. Da ƙyar muka samu abun hawa  muka shiga ya kaimu har ƙofar gida, kuɗinshi na zaro na bashi muka shige ciki. Bamu ci karo da kowa ba har muka shige ciki.

Su Mardiyya suna jiyo muryoyinmu suka fito daga ɗaki suna murna. Nima dana ga yadda suke farin cikin ganina sai na ɗanji dama_dama dai.

"Kafin komai Mardiyya bamu abinci muci"

Cewar Rakiya ta cire mayafinta. Labbai kuwa tv ta kunna tana ta canja tashoshi.

"Lolo wato na lura yar shuwa da shirinta ta shigo cikin gidannan. Da zaki daure sai ki jingine babinta kinga waɗannan yaran ki ɗauka zamansu kawai kike yi. Duk tsiya gidannan fa yafi gidan ubanki, ƴan uwanki burinsu su samu miji kamar Babangida, ko ma wanda ya fishi. Ki yi haquri ki kuɓuta daga duk sharrin da zata miki. Babangida dama ba ɗan arziki bane jibi yadda yake yaɓamun magana duk surukaina basu ɗaukeni a bakin komai ba."

Maigogul ne yake magana. Ni wallahi hankalina ma baya tare dasu sam, na lula duniyar nema ma kaina hanya mai bullewa.

Miƙewa nayi na shige ɗakina, jakata na buɗe na ciro karan sigari ɗaya, da ashanata nayi banɗaki. Ina zaune zaman dirshan a cikin banɗakin ina shan sigarinnan hawaye na zubo mun a kumatuna. Ga room freshener a hannuna sai fesawa nake yi gudun kada warin taban ya fita yarana suji warinta, saida na shanye sigarina tas, sai nayi wanka na fito.

Wayata a cikin jaka sai ringing take yi. Ina cirowa naga Khalid ne, ɗagawa nayi.

"Sabuwa kin ɗaga mun hankalina sosai. Na kirani kina kuka,  amman daga baya  na kuma  kiraki kinƙi ɗagawa, wallahi dama na yanke hukuncin in na kuma kira baki ɗaga ba zan tawo gidan naki inji meke damunki Babyna"

Murmushi nayi gami da ajjiyar zuchiya.

Khalid kenan. Kai dai ka nema mana inda zamu haɗu yau, ƙila ma tare zamu kwana"

Sassanyar ajjiyar zuchiya ya sauke, nayi saurin rintse idanuna ina tausayin ƴaƴana, amman yaya zanyi dole in nema ma kaina inda zan samu salama in ba haka ba mutuwa zanyi a banzan banza.

Edit with WPS Office

"To Shikenan ni kuma zan shirya miki tarba mai kyau gimbiyar mata. Nayi kewarki sosai Sabuwa".

Kai da kake da mata wane kewata ni Sabuwa zaka yi?"

Nan ya shiga zubo mun kalaman ƙauna, tare da kurantani. Har saida yasa nayi murmushi har ƙasan raina. Mun ɗan jima muna hirarmu kafin mu kai sallama.

Kaya na sake na koma falo na samu su Maigogul sai dannan funkaso suke yi ga tea mai shegen kauri sunata kurɓa.

Mardiyya zubo mun guda biyu da tea, kar ki saka mun miyar amman. Malama tawo inji yaya jikin naki"

Na miƙo ma Malama hannu halamar tazo, ita kuma Mardiyya ta tafi da sauri ta kawo mun. Magungunana dana umarceta data kwaso mun in watsa su ko na ɗan samu sauƙin daya kamata.

Sai wajajen sha biyu su Rakiya suka miƙe da zummar tafiya. Shinkafa mudu biyu, da taliya leda biyu, sai dubu biyar na ba Rakiya, nai musu rakiya har bakin titi. Da dai zamu fita naga Yar shuwa tayi sauri ta fito daga ɓarayinta. Cikinmu babu wanda ya nuna ma ya ganta kuma duk mun ganta.

Ina tafe kamar zautacciya sai tunani nake faman yi. Wallahi ban sani ba ashe mota ce a gabana take ta matsa hon matar dake cikin motar. Tsananin damuwa da neman mafita yasa ban ko ji ba saida naji na daki wani gabu gab. Ina dawowa hayyacina naga ashe mota naje na buga, a tsakiyar titi ma nake tafiyar. Namiji ƙanin ajali kenan.

Haƙuri na ba baiwar Allahn nan na kauce a hanya, naci gaba da tafiya har na dawo.

A falo na tarar da yaran sunata musu, daga kitchen kuma na jiyo ƙamshin abinci.

Mardiyya yar shuwa ce a kitchen ɗina wai?"

Na tambaya ina ƙare musu kallo amsa kawai nake son ji daga garesu.

Kafin ma su bani amsar ta fito.

"Ke Mardiyya zo ki yi mun fira"

Ba zata yi ba. Wallahi kinci ƙarya kin kwana da yinwa. Duk abinda kike gadara dashi kin tara kin samu. Ku kuje kuyi kwanciyarku ku huta."

Yaran suka wuce. Ita kuma tana dariyar cusa haushi tace.

"Kawata kar ki yi sake kishi ya rufe miki idanu kizo kina dana sani. Kinga ai ko iyayenki naga neman kai suke da ke. Shima mijin baki da wata daraja karfa ki manta a tafin hannuna kike. Ai Ni da na ɗauka a matsayinki ta bokanya zaki iya dukan ƙasa ta baki labarin komai. Ashe bata iya

Edit with WPS Office

baki kabarin abinda zai faru dake ba?

Kin ganni da kike ganina nan? Wallahi nafi ƙarfinki duk abinda kike tunanin zaki mun ki huce takaici, ko ya zame miki ramuwa akaina. Wallahi _wallahi Sabuwa nafi ƙarfinki. Kinga wannan gidan? Sai dai ki tafi ki barni a cikinshi dan duk maitar Maigogul da son daya ɗaurama zamanki a gidannan yana gida watarana zaki je mishi da takaddarki a hannunki ta sakin da babu kome a cikinshi"

MRS BUKHARI

Tabb me kuke ganin zai faru?

IDAN KAYA YA GAJI..

GAMMO MA YA GAJI

BADIAT IBRAHIM MRS BUKHARI B4B GIDAN KAMSHI

LITTAFI NA FARKO

SHAFI NA GOMA SHA BAKWAI

SABUWA:.

Sama da ƙasa Allah bai bani ikon tanka mata ba. Har ta karaci iskancinta dai.

"Kice yarinyarnan ta fito ta mun aikinnan Sabuwa wallahi ko in baki mamaki. Ki bini a hankali kar

Edit with WPS Office

ki tunzurani ki kaini bangon da zan fasa ƙwan da warinshi zai gumameki ya sake jefa rayuwarki cikin wani ukun"

Mikewa nayi na shige ɗakin yara nayi kwanciyata a gadon su Aminu amman fa zuchiyata tafasa kawai take yi a wannan lokacin. Dan bana son wata hayaniya shi yasa na ƙyaleta yau da saina zaneta wallahi. Kwan dan ubanshi ya daɗe bai fashe ba.

Ban jima da kwanciyar ba na jiyo hargagin kiran Mardiyya da Babangida yake yi.

A zabure yarinyar ta miƙe ta fita har tana tuntuɓe.

Bayanta na bi, a falona na samu Ƴar shuwa tana zaune ta harɗe a kujera tana karkaɗa ƙafa kamar gidan ubanta. Babangida kuma ya dage yana dukan Mardiyya kamar Allah ne ya aiko shi.

"Kara mata Jannaty"

Da sauri naje na ƙwaceta na fisgeta a hannun Babangida. Ya ɗaga bulalar zai zuga mun nayi saurin riƙewa. Na girgiza sosai.

Kayi kaɗan ka dakeni. Ka sani zan iya kwaɓewa mu daku dan bana tsoronka maras mutunci wanda baisan abinda yake yi ba. In ka cika ɗan halak ka sakeni ba wai ka korani gidanmu ba. In ka sakeni bazan zauna maka a gidaba. Kuma inna tafi gidanmu Babba ma dole ta tafi nasu gidan ka san da sanin wannan."

Da maɗaukakin mamaki ya kalleni ya nunani da bulalar hannunshi.

"Ni kike furzarma da magana masu ɗaci sabuwa? Ai kema kinsan ƙaddarar da tasa muke zaune a ƙarƙashin inuwa ɗaya. Wallahi Allah ba dan inason in gama da Baba Malam lafiya ba da yau kwananki ya ƙare a cikin gidannan, ƴar iska maras mutunci"

Ga ƴar iska maras mutunci kana aure. Da sannu zaka san ka ɗauko kara da kiyashi. Da ace ɗan iskan gaske ne kai da tuni yanzu ka yago takaddata ka bani. IDAN KAYA YA GAJI GAMMO MA YA GAJI"

Ina gama faɗar haka na ja hannun ƴata muka wuce.

Babangida ya jima yana tijarshi a falo, ya shiga store ya tattare duk wani hatsi dake ciki ya fita dashi.

Ya gama hargitsa mun kitchen da ma falon dukka.

A zafafe yazo bakin ƙofar ɗakin yara yace.

"Na gaji da halinki na almubazzaranci, da kwashe abinci da kike yi ki kai gidsnku. Daga yanzu keyn store yana hannun Habibaty in kina so sai kije wajenta zata auna miki abincin da zai isheku."

Edit with WPS Office

Ai baka burge ba tunda baka bata mu kyauta mun zame mata bayi ba Babangida kacigari. Sannan in dai wajen Yar shuwa zanje ta auna mun abinci sai dai mu mutu da yinwa wallahi. Ka rubuta ka ajjiye na haƙura da duk abinda zai fito ta hannunka ɗan abu ta....😆

Ina gama faɗar haka na fita a ɗakin na bangajeshi yayi taga_taga na koma nawa ɗakin na bar yara a nasu ɗakin.

Yan kuɗaɗen dake hannununa su na ƙundume na siyo kayan abinci na jibge mana a kitchen.

Gaga_gaga dare na yi misalin tara na fice a gidan, a wani babban hotel muka haɗu da Khalid.

Mu ka ɗanyi ciye_ciyenmu

Ina zaune a bakin gado ina shan sigari Khalid ya fito daga banɗaki ɗaure da tawul a ƙugunshi, kallonshi nake yi idona a lumshe. A gefen gadon ya zauna jikinshi na gugan nawa jikin. Hannunshi yasa ya zare sigarin dake bakina ya mayar nashi bakin.

"Ya kamata ki watsa ruwa mu kwanta ko? Kinga ƙarfe sha ɗayan dare ya kamata ace kina baccine yanzu. Sigarinnan ki rage shanta sabida lafiyarki uhm. Nayi nayi ku haɗu da Dr Layla kinƙi yarda. Sabida lafiyarki nake son kije ki ganta ki duba wannan lamarin"

Mikewa nayi ina kashe mishi ido naje na yi wanka da zazzafan ruwa na fito ɗaure da tawul, sunkutata Khalid yayi cancakat zuwa lallausan gadon yayi mun rumfa, hancinshi na gugan nawa, numfashinmu a sarƙe.

"Na yi tunanin wannan yanayin ya wuce har abada sai dai a duniyar mafarki, ashe zamu sake jin ɗumin juna Sabuwa? Na rantse miki da Allah ina miki son da babu wanda zai iya miki shi a duniya"

Ban samu zarafin bashi amsaba ya dannemun bakina da nashi. Nan al'amura suka shiga wakana a tsakaninmu. Idanuna a lumshe ina zubar da hawaye har komai ya lafa Khalid ya matseni ƙam a ƙirjinshi ya dinga shafa mun kaina, yana raɗamun kalamai masu daɗin saurare a kunnena har dai bansan sanda bacci yayi awon gaba dani ba.

Gaga_gaga haka na faɗa cikin wannan rayuwar, kullum muna maƙale da Khalid a waya, ko muna charting, muna aikema da juna saƙwannin da basu dace ba. haɗuwarmu kuma gudun matsala sai muka tsara yawanci da yamma, ko kuma da daddaren amman duk rintsi zan dawo in kwana a ɗakina gudun kar yara su fahimci halin da nake ciki.

Kuɗin da nake samu a hannun Khalid sai nasa aka saka harsashen ginin gidanmu, ɗaki biyu sai banɗaki, wannan karon ginin bulo akeyi.

Baƙin cikin da Babangida yake cusa mun kullum dai ƙaruwa yake yi, duk da kayan abinci daya kwashe hakan bai isheshi ba ni kuma na tattara al'amuranshi da matanshi na zuba a bola. kullum yarannan jira yake su yi abu kaɗan ya hau dukansu. Hamida da Yar shuwa kuwa sun ɗinke sun haɗe kansu, kullum suna manne da juna, in Hamida bata ɗakinta to tana ɗakin Yar

Edit with WPS Office

shuwa, itama haka in bata ɗakinta tana ɗakin Hamida. Amman ita Hamida bata fahimci juyata Yar Shuwa take yi ba, ta shige mata jiki ta mugun takurata sosai bata bata wata dama da zata yi wani abu na sirri ba. Ni ko ina gefe na ɗauki ido na zuba musu. Na fita cikin harkar kowa. Kawayenmu ma ashe duk munafukaine cikinsu ƙalilanne basu kawo ma Yar shuwa ziyara ba, ƙannenta kullum a tafe suke in zasu tafi a cika musu ƙaramin buhu da kayan masarufi. Ba tai wata guda ba cib Babangida ya ci gaba da kwanan waje, yau ya kwana a gida, gobe yace musu zai yi tafiya ta kwana ɗaya. Da cefanen abincina ya ƙare na kwashi jiki har gidan su Babangida nayi ma Baba Malam bayanin halin da nake ciki. Kai ya jinjina yace.

"Kar ki je wajen matarshi karɓo abinci gudun fitina. Ni kuma na riga na ɗauki ido na saka ma Babangida duk wani abinda ya shafi ragowar matanshi ke kinsan bana ciki. Hatta mahaifiyarshi ta dalilin aurenku ke da Babangida na gane asalin wacece ita. Zan dinga turo miki kuɗi duk wata ki dinga siyan kayan abincin kuna ci ke da yaranki, ko kuma in saka Ramadan ya dinga kawo muku. In ya tambayeki kice mishi nine nake ciyar daku tunda dama zamana kuke yi duka. Duk abinda kike so Sabuwa ɗaga wayarki ki kirani zan miki. Ni dai inata ƙara baki haƙuri Sabuwa a daure dai ko dan saboda yara."

Haka rayuwar taci gaba da garawa.

Yau na wayi gari da son zuwa gida jiya aka kirani ake sanar mun Maigogul bashi da lafiya yana kwance.

Duku_duku na kammala duk aiyukana, na soya doya da ƙwai cikin kula harda tea mai kauri a flaks na zuba.

A gurguje na fito sanye da riga da zani na lace, na yafa mayafi da gyalena, da jakata daidai da lace ɗin. Babu komai a fuskata sai man baki dana murza.

Babangida ne ya ɗaga labule babu ko sallama.

Kuɗi ya miƙo ma Aminu, kuɗin mota dana break ɗinsu, bai ko kalleni ba.

Inaso zanje gida Babangida Maigogul bashi da lafiya"

"Ina ruwana da rashin lafiyarshi. Allah ya raka taki gona. Inma Hotel zaki je sai kin dawo. Duk ranar dana kamaki da wani wallahi saina kasheku."

Kai kawai na girgiza.

Maza ku yi ku gama cin abincin mu fita maza"

Nace da yaran, suna gamawa muka fito a tare, kulle ɗakina nayi na miƙa ma Mardiyya keyn ta saka a jakarta.

Muna fitowa tsakar gidan muka tarar da Babangida da Yar shuwa a gaban wata mota mai ruwan toka sai tsallen murna take yi. Tana ganinmu ta rungume Babangida harda sunbatarshi, ga yara

Edit with WPS Office

suna kallonsu.

"Ohhh nagode sosai Jannaty yanzu wannan motar ni Yar Shuwa tawa ce? Lallai yau kana da babban tukuici a turaka"

Shi kuwa yana maƙale da kugunta sai kallona yake yi, har mun gibtasu yace.

"Ke Cus"

Yaran nasa su yi gaba ni kuma na iso inda yake.

"Habibaty ta faɗa mun baki taɓa zuwa ta baki abinci ba. Kuma kina girki, tunda ga abincinma da kika dafa zaki kai gidanku, a ina kike samun kuɗin, ko yawon banza kike fita da aurenki?"

Baba Malam ne yake ciyar damu, tunda kai ka gaza, kuma kaga ai zamanshi nake yi ko? Yawon banzan ma in nayi ai ba aibu bane tunda a yawon banzan muka haɗu da kai ko?

Na ƙarashe maganar ina dariya.

Ina gama faɗar haka na juya zan yi wucewata, jikinshi duk ya mutu.

"Haba Lolo me yasa baki da burin daya wuce ki sake farraƙa Jannaty da mahaifinshi. Abincin ba gashi a store ba amman girman kai ya hanaki kizo ki tambaya in auna in baki"

Murmushi nayi mata kawai nayi tafiyata na barsu nan.

A bakin titi muka rabu da yaran, ni dai harna isa gida ina juya maganganun Babangida da Yar shuwa.

Da sallama na shiga gidan. Su matan gidan basu cika amsa sallama ba, ƴan lungunmu dai su kan amsa harma a gaisa. Ina shiga na tarar da Maigogul a kwance daga shi sai gajeren wando a gadon Hauwa.

"Lolo ashe gyatumar taki ta faɗa miki banji daɗi ba?"

E Maigogul yaya jikin naka?"

Hauwa tace.

"Hmmm ga jikinnan dai da sauƙi za'ace"

Naga ciwuka a jikinshi hatsari suka yi ne Hauwa?"

Ai kafin Hauwa ta tanka Rakiya ta leƙo daga ƙuryarta tace.

"Matasane suka kai ziyara wajen da suke sheƙe ayarsu shine suka farsu da sara kan me uwa da wabi. Ai Maigogul matsawar baka nutsu ka kama girmanka ba ka dinga haɗuwa da abubuwa kala daban_daban ina amfanin wajajen da kake zuwa, ina kuma amfanin sana'ar daka riƙe? Ka

Edit with WPS Office

duba fa sanadiyyar halayyarka ji yanda yaranmu suka dawo. Wallahi kaji tsoron Allah tun kafin lokaci ya ƙure maka. Ace tun kana saurayi kake abu ɗaya har zuwa girmanka"

Shiru nayi ina tunanin a yadda muka taso muka tarar da Maigogul a yanzu haka ma ai yayi sanyi za'ace.

Sai nake jin maganganun Rakiya kamar hannunka mai sanda.

Anya nayi ma kaina da ƴaƴana adalci kuwa dana jefa kaina a mummunar rayuwa. Shin in Babangida ya kasance mane min mata ni sai in sallamar da darajar ƴaƴana. Shin in ɗiyata ta girma ta gajeni ko mahaifinta shin zanji daɗi?"

Take zufa ta soma yanko mun tako ta ina,  nadama da dana sani ya aureni.

Miƙewa zaune Maigogul yayi zai soma zazzago ma Rakiya raddi nayi sauri nace.

Kayi haƙuri Maigogul ka koma ka kwanta kaga jikinka duk rauni. Rabu da Rakiya tafi son kullum kayi ta fusata"

Da Allah ya taimakeni sai ya koma ya kwanta kuma bai ce komai ba, sai huci da ƙwafa da yake yi.

Hauwa ta taɓe bakinta tare da kawar da kai.

Maigogul amman kaje asibiti an duba ka?"

Sai da ya sauke ajjiyar zuchiya kana yace.

"Naje Lolo sun gyara mun wajen ciwukan su suka sa mun filastannan, an mun allura, ga ƙwaya duk sun bani. Gaza da Magazin ina jin muryarsu a waje ɗazunnan. Gaza na yi ma karnukanshi wanka, shi kuma Magazin yana ta bushe bushen wiwinshi. Wallahi Lolo babu wanda ya shigo ya duba ni. Gaza fa har ciki ya shiga ina jinshi da Rakiya yana mata maganar zasu gina ɗaki ɗaya a gidana su dinga kwana, shi ya gaji da rayuwar kango da surutai na marasa hankali dai.

Ita Layuza da tazo ta jiya wallahi haka tazo hannunta na dukan cinyarta fa, Rahama ma haka. Amman ke na ganki da leda niƙi_niƙi nasan wani abun daɗin kika kawo mun ko?"

E doya ce da ƙwai na soyo maka sai  tea mai madara"

Nan ya washe bakinshi, ya daddage ya zauna.

"Hauwa ɗakko kula da kofin silba ta zuba mun nawa kason.

Tana surutai ta ɗakko kwanon ta dangwarar mun da kofin dukka.

Zai yi magana. Na ɗaga mishi hannu. Ya sake yin shiru dai.

Ni dai zuba mishi nayi jingim ragowar nayi shigewata ciki dashi. Kwaya uku Rakiya ta watsa a roba, da tea kwatan kofi ta miƙa ma A'isha dake zaune tana raba musu kaza gashasshiya.

Edit with WPS Office

"Jefa mata ko fika_fikine in ba Labbai tunda tafi kusa ta miƙa mata"

Sai da ta gama ƙunƙunninta ta jefa mata wuya. Labbai ta leƙa ta bata har zata karɓa Qamriyya tace.

"Allah ya sitiri buƙui me zata yi da wannan kayan naku. Ai bata haifi mai mutuwar zuchiya ba. Hauwa akwai gashasshen kifi da jus a ledar da na shigo dashi harda ragowar kek ki karya dasu, ni inna tashi zan dafo indommi"

Labbai ta ja dogon tsaki ta juyo ta bar Hauwa na bambamin masifa.

A haka dai na wuni a gidan bana wani jin daɗi sai kasala, sai jin bacci, haka naita bacci har azahar na tashi naga Rakiya na rabon taliyar hauwa ta manja harda kifi.

A faranti ta zubo mana namu duka, ana ci anata labari ana dariya harda Rakiya. Daga falo muna jiyo muryoyin su Layuza suma suna cin nasu abincin suna shewarsu, hira harda Maigogul.

Ina yin sallar la'asar sai na soma shirin komawa gida. Ina gidan ban tafi ba aka bugo Rahama ta haihu. Mu wallahi babu wanda yasan ma ciki ne da'ita.

Dama ita ciki a jikinta baya nunawa.

Tare da su Labbai muka fito, su suka wuce gidan Rahama. Ni kuma na wuce gida, ina shiga Khalid ya kira wayata, kamar dai bazan ɗauka ba sai na ɗauka, amman na kasa magana.

"Yau laifin mai nayi my love kika barni da kewarki haka, baki a online ɗin ma. Yau ba zamu haɗu bane my love ɗuminki kawai nake da buƙata. Madam ma bata gari gidana nake son kizo amman yau kwana zamu yi ki rufamun asiri bakya isata, wannan ƴan awannin ni a wajena ɗanɗani haukaci ne kawai."

Idanuna na lumshe zuchiyata cike da dana sanin dawo da Khalid cikin rayuwata da nayi, gashi yayi mun tasiri sosai kamar da.

Khalid kayi haƙuri ba zamu sake haɗuwa ba. Kuma ba zamu sake haɗa jikiba. Dan Allah inaso ka manta da Sabuwa har abada...."

"No Sabuwa bazan iyaba. Kar ki azabtar damu duka mana. Nasan kina samun nutsuwa tare dani. Ina baki kulawa da duk lokacina. Kar ki manta mijinki ba sonki yake yi ba. Da yana ƙaunarki bazai ƙaurace miki a shimfiɗa ba kuma bazai auri aminiyarki ba. Come on Sabuwa kar ki ruguza mun zuchiyata na roƙeki da Allah. In kuma laifi nayi ki faɗa mun?"

Idanuna na lumshe muryar khalid na ratsa duk rassan jikina. Haƙiƙa na jarabtu ainun da son kasancewa da Khalid. A wajenshi kaɗai nake jin sanyi. Ina tsoron kamun Allah, ina tsoron ni da kaina in jawo ma ƴaƴana abinda zai zame musu masifa da abun kwatance.

Bai barni nayi magana ba ya dinga roƙona, yana faɗamun irin sona da yake yi. Wallahi kuka wiwi Khalid ya fashe mun dashi sosai.

Edit with WPS Office

Shikenan zan fito. Ka bani adireshin gidan naka zan zo da kaina. Kasan dole sai muna yin taka tsantsan gudun matsala gani da budurwar ƴa."

"Wai Allah my love. Wallahi har jinina ya haura. Rabuwa dake ai kasada ce mai girma.

Zan tura miki adireshin gidan nawa, kuma zan zauna in jiraki. Yau zan shagwaɓaki sosai"

Murmusawa nayi na ajjiye wayar tawa, na nufi kitchen. Ina kan girki sai ga ƴan makaranta sun dawo, tun daga falo ake faɗa a tsakanin Aɗɗa'u da Aminu harda dambe dama sako da sako ba dama ne.

Lafiya ya daga dawowarku zaku soma kokawa? Maza kuyi Babanku in yana nan ya jiyo ku, ai kunsan sauran"

Mardiyya tace

"Ai Ummi sunga babu motarshi ne a gidan shi yasa."

Na shiga yin aikin sulhu dai.

Kafin magriba su kai wanka, bayan mazan sun dawo sallar magriba Mardiyya ta zubo mana shinkafa da miya da latas da nayi a ƙaton tire. Na shiga tsakiyar yarana muna ci zuchiyoyinsu a cike da farin ciki, nima sai naji farin ciki ya baibayeni sosai.

Bayan an yi isha, suka yiyyi assignment ɗinsu sai kuma aka tafi kwanciya, ni dai ina falon ina kallo a zahiri a baɗini lissafine da tubkewa da warwarewa ya addabi ƙwaƙwalwata. Inata jiran shigowar Babangida ni kuma in kama gabana bai shigo ba har goman dare.

Dama ni a shirye nake, kawai sai na fice ta ƙaramar ƙofar baya da take ɓellewa da kai zuwa layin baya.

Adireshin gidan Khalid na bi sai gani a ƙofar gidanshi"

BABANGIDA:.

MAJALISA:.

Isowarshi kenan ya samu ana cabta.

Edit with WPS Office

Zama yayi aka tattafa.

"Wai hayaniyar me nake ji tana faman tashi ne yau a majalisar tamu?"

Yusuf yace.

"Ai yau tunda muka zauna muke tattauna waɗannan lamura.

Ashiru ne ya saki Maryam kuma har saki uku, shine iyayenta suka ce sai sun kaishi kotu"

Baki ya taɓe tare da ƙanƙance idanu yace.

"Saboda an saki yar tasu shine zasu sashi a kotu dan rashin mutunci? Kut ai wallahi ba'ayi macen data isa tozarta ni ba bare har ta kaini kotu ba. Ita Maryam ɗin dan ubanta bata ga suna da yara bane?"

Ashiru ya saka dariyar mugunta yace.

"Da na saketa fa almura sai ta hau iskokan da ni bansan ma tana dasu ba. Wallahi ta dinga ɓarnatar da kwalaben turaren wutarta. Ni tana wannan birgimar iskancin ma na yi fitowata. Ni damuwata shine suna shirin kaini kotu ni da zan angwance nan da mako guda"

Dariya aka saka a majalisar harda masu hawaye dan mugunta

"Haha wallahi ka ban dariya. Su je su kai duk inda zasu kai ba dai saki uku bane? Ai dole su barka.

Nima fa ina zaman zamana a office sai ga kiran uban Farida wai Farida ba lafiya za'a kaita asibiti waya mutu wa zai dawo.

Ai tunda nace zan neme shi ina aiki ban sake bi ta kanshi ba. In zai nema ma ƴarshi lafiya ya nema mata in zai barta ya barta mana."

Nan kowa ya tofa albarkacin bakinshi. Can Babangida ya hango Uzaifa a gefe sai huci yake yi. Ya ɗan daki Ashiru yace.

"Wai Uzaifa Sauma'iya ta sake kai sunanshi wajen malaman zaure ne? Ni naga duk hirarnan yaƙi cewa uffan fa?"

Mustapha yace.

"Kama matarshi ta tsakiyan yayi fa tana charting da wani ƙaton gardi soyayya ma suke yi, duk da bai gama karanta saƙonnin da suke ta aike ma juna ba ta fisge wayar ta doka ta da ƙasa muguwar.

To wallahi tunda yazo ya zauna bayan ya labarta mana matsalarshi shine yayi gurum. Tabb da nine wallahi da tuni jinina ya haura."

Edit with WPS Office

Ai sai Babangida ya miƙe tsaye yana nuna Uzaifa da hannu yana huci

"Kuma dan iskanci wanne hukuncin ka ɗauka a kanta. Ina dai fatan kayi mata dukan da sai iyayenta sun kashe kuɗi a kan jinyarta? Bura uba da aurena akan mace ta dinga neman wasu mazan in kamata ban kusan kasheta ba ai ba dai Babangida kacigari ba wallahi. Ina da kishi na tashin hankali ku kun sani. Zan iya mutuwa inna kama matata da wani fa.

Ai da nine da tuni zuchiyata ta buga ta yi daga_daga. Gonar tawa in yi shuka wani gardi yayi girba. Amman dai kai Uzaifa lusarine dai wallahi. Ai rungumarta ya kamata kayi kuyi mutuwar kasko uban kowa ya huta"

Da faɗa yake maganar yanata huci.

Mustapha ne ya miƙe ya riƙe kafaɗarshi suka dawo suka xauka.

Uzaifa yace.

"Wallahi Babangida kacigari kaina ɗaurewa yayi. Kai kaji zuchiyata yadda take mun wani irin daka kuwa? Kasan wanzami baya son jarfa. Na rasa wanne mataki zan ɗauka a kanta ne wallahi"

Babangida ya daki kafaɗarshi da ƙarfi yace.

"Tabbb. To wai in tambayeka bayan ta fasa wayar kai yaya kayi mata? Nifa zuchiyata tafasa take yi"

Wayarshi ce ta shiga ruri, yana ɗagawa yaga Sumy ke kiranshi. Da murmushi ya ɗauki wayar, yana ɗagama majalisar hannu akan su sasauta sautin muryoyinsu.

"Yaya akayi rayuwata. Abincin ya kammala ne, ko kina son in tawo miki da wani abunne?"

A shagwaɓe irin na gogaggun matan da in suka kama mijin wata sai tayi da gasken gaske kafin ta iya gane kanshi tace.

"Da abincin da wacce tayi abincin duk kai suke jira B House ( Babangida)

Amman dai kana tashi a makaranta kai tsaye zaka tawo ba sai ka koma gidanka ba ko?"

Take tsigar jikin Babangida ya soma tashi. Idanunshi ya lumshe tare da lasar leɓenshi na ƙasa. Murya a kasalance irin na mai ɗauke da ƙishin ruwan sanyi yace.

"Bazan je makarantar ba yau. Sai dai ɗalibai su yi haƙuri. Sahun giwa ya take na raƙumi. Suma matan gidan zan sanar musu bazan kwana a gidanba. Rayuwata kici gaba da shiryawa kafin in zo ki sake gashinshi nafi son inga gashin mace a kunce a sake duk rashin yawan gashin. ( Jan hankali gareku mata. Mata mu kasance cikakkun mata ba raka_raka ba. A wannan zamanin mace ta gyara ya take cikawa a wajen namiji balle batai gyara ba?. Kuma dama shaiɗan yafi ƙawatama mazajenmu matan waje. Yanzu dai ku duba Babangida Allah ya bashi mata

Edit with WPS Office

tsula_tsula har uku ko wacce tasan ita kyakkyawace. Kuma ta ɓangaren Yar shuwa da Hamida yana samun duk abinda yake so, ruwan idanu da son zuchiya, da kuma zina ta da shiga jikin Babangida ya rufe mishi idanu. A matsayinki ta mace ki kasance kin iya duk abinda ya dace. Mata muna bari kunya tana kashemu da yawa a gidan aure. Bama ba mazajenmu irin abinda matan wajen suke basu. Ki zauna ki nutsu kisan duk abinda mijinki yake so, na kwalliya ko ado. Misali shin doguwar riga yafi so, wacce iri ta kanti ko ta atampa? Sannan mai matsewa ko me buɗewa. Shin riga da zani yake so, atampa, leshi, shadda, yadi, ko me da makamantansu da dama. Kitso yafi so, ko yafi son ki gyara kan kawai, shin kitson ƙanana ko manya, shiku, shade, na gaba, ko dukka baya? Yana fa da kyau mu sani. Kar kice can ta matse mishi, ko ki dinga jin ke kinfi ƙarfin kiyi abu dominshi, ko kice ai baya siya miki kaza, baya yabawa da dai sauran ƙorafe ƙorafen dake mayar damu baya. Mu farka mata wallahi mu farka)

Yana sauke wayar suka soma zolayarshi, shi kuma jinshi yake kamar me.

"Dan Malam kaƙi halin Malam. Yanzu yau ɗinma ba a gida zaka kwana ba kaida kake da sabuwar Amarya?"

Dariya yayi harda tuntsurawa kana yace.

"Kai rabu da sabuwar Amarya kaji? Kai kasan tuwon kwaɗayi yafi daɗi. Duk da dai wallahi nake faɗa muku Auren Shuwa duniya ne, kai ina kwasan ƙamshi da laushin fata ga gashi ma malam har baya. Kasan Allah in ina shafa gashinta ina wannan film ɗin indiyan na self Ali khan da preety zenta ɗinnan daya fito shi baya son haihuwa?"

Yusuf yace.

"Salam namaste wai?"

"Kaji ɗan gari to gashinta fa kamar na Preety zenta sai in jini kamar a Aljanna. Amman hakan bazai hana a taɓa na kwaɗayi ba, Sumy ai aljannar duniyace ta musamman ce tunda har kuka ga har izuwa yanzu bamu rabuba. Sai na ci na suɗe mannan tas wallahi kafin in cillata kwandon shara. Kai mu dawo batun matar Uzaifa fa. Wallahi kar ka kuskura a mayar da kai ɗan iska wallahi. Kayi mata kafirin dukan kawo wuƙa kafin ka saketa. Kuma wallahi duk abinda kasan kai ka se mata kar ka bar mata dan ubanta"

Nan kowa ya shiga tofa albarkacin bakinshi har zuwa sallah.

Bayan sunje sun dawo nan suka shiga cin abinci, anayi ana korawa da gahawa da magungunansu na maza duk a majalisa ake kawo musu suke siye. Da ƙyar Babangida ya yakice ya bar majalisar a hakanma yana gudun Malam ya aiko ai kiranshi ne in anga bai zo makaranta ba.

Sai da yayi burki a wajen suya ya sai kaza da fura da nono, banda sauran ciye_ciye kafin ya kama hanyar gidan Sumy.

Edit with WPS Office

A hanya ya tsara matanshi tare da ce musu kayane za'a kwana ana lodawa za'a wuce dasu lagos. Da wannan ƙaryar ya rarrashesu baya ta Sabuwa dan ya ƙudure a ranshi ya dena kwanciya da Sabuwa taje ta riƙe daɗinta har izuwa lokacin da zata neme shi. Shi dai yayi alƙawarin bazai sake nemanta ba har mahadi ya bayyana.

A falo ya samu Sumy tana kallon wani American series mai ɗan karen kyau irin wanda ya dace da irin rayuwarta da Babangida.

Mrs Bukhari

Sai Allah ya kaimu ranar Monday kuma zamu ɗora daga inda muka tsaya.

Sanya kuɗin karatun a cikin wannan lambar asusun

0044442984

Buhari Ibrahim Ladan Gt bank

Lambar da zaku turo shaidar biya gasu kamar haka

08022059556

Ko kuma

08105932041

Masu son magana da marubuciyar kai tsaye kuma ga lambata

Wa.me/2348179523215

Ina manyan mata masu capacityn suke? ku fito lambarku ce ta fito.

Yar uwa turaren wuta kike nema nau'ika daban_daban masu musulmin ƙamshi da kama muhallu? Ba itacen banza masu sanya gida ƙauri da hayaki kamar an kunna taohuwar bespa ba.

Matso gasu MRS BUKHARI B4B GIDAN KAMSHI nazo miki da duk abinda kike buƙata na ƙamshi. Kama daga turarukan wuta irin na gidan alfarma. Zuwa humrori iri daban daban masu

Edit with WPS Office

musulmin ƙamshi da riƙe jiki.

Bugu da ƙari muna da turarukan kaya, na fesawa dana turara kaya.

Muna da kulaccam nau'i daban daban masu gyara jiki da lausasa  fata mata, ga kuma ƙamshi mai inganci.

Muna da turarukan tsugunno na musamman masu sirri Hajiyata

Muna da room freshener iri_iri

Muna da mopping mix masu kama waje.

Akwai turarukan kafet dana kujeru.

Sannan akwai box _ box  setika na Hajiyoyi masu ƙyallin goshi.

Muna da Amarya package.

Muna da uwargida package

Muna da maijego package

Muna bayar da sari ko a ƙasar waje kike, muna tura kaya

Saudiyya

Nijar

Ghana

Camaron

A duk ƙasar da kike kayanmu zai iso miki cikin aminci da yardar Allah.

Hajiya akwai Humrar matan aure wannan ta musamman ce.

Duk wani abu da kika sani na ƙamshi babu irin wanda bamu dashi a kamfaninmu.

Muna da turaruka designer na maza da mata wanda kamfaninmu ke bugawa Hajiya babu inda zaki je ki ci karo da mai irin ƙamshinki.

MRS BUKHARI B4B GIDAN KAMSHI TAZO MUKU DA DUK ABINDA KUKE SO NA KAMSHI HAJIYA.

KUNSAN KANURI MUNE KAMSHI DAMU AKE KOYI

SIYAN NAGARI MAIDA KUDI

MUNA MARABA DA MASU SIYAN ƊAYA KO SARI.

Edit with WPS Office

LAMBAR DA ZA'A SAMENI KAI TSAYE ITACE.

Wa.me/2348179523215

SAI NA JIKU

IDAN KAYA YA GAJI...

GAMMO MA YA GAJI

BADIAT IBRAHIM MRS BUKHARI B4B GIDAN KAMSHI

SHAFI NA SHA TAKWAS

Follow this link to join my WhatsApp group: https://chat.whatsapp.com/Hnb3Ee00TCQKqHgDwWfyx0 maman Muhammad kitchen Etims kayan mu available munasaida atanfa lace shadda mayafai takalmi da jaka akwai jewelrys

Munayin adashin gata nakayankici munaturakayanmu ko inakake cikin yardar Allah Ina wayanda basu da jari tum gada matasamu saki iyatallata kayanmu kema kisamunaki

Location dinmu Kano tudin Yola get 5 rukar Fulani gidan su baba sadiq 07044545303

Sanya kuɗin karatun a cikin wannan lambar asusun

0044442984

Buhari Ibrahim Ladan Gt bank

Lambar da zaku turo shaidar biya gasu kamar haka

Edit with WPS Office

08022059556

Ko kuma

08105932041

Masu son magana da marubuciyar kai tsaye kuma ga lambata

Wa.me/2348179523215

SABUWA:.

Ina tsaye a bakin get ɗin gidan Khalid. Sai gashi ya fito saye da baƙar jallabiyar data sake bayyana hasken fatarshi.

"Shigo madam ai gidan yau naki ne, me gidan dama dai shi mallakinkine, yadda kike moreshi ko matarshi bata moreshi haka"

Yana maganarne yana jifana da wani irin kallo mai sauke kasala.

Khalid kenan yanzu zamu shigane, ko sai maƙotanku duk sun ganmu tukunna sun kira Madam ɗinka a waya sun sanar mata?"

Baice komai ba ya shige gaba na bi bayanshi tiryan_tiryan har zuwa babban falon gidan.

Amman bamu zauna a falon ba kai tsaye ɗakinshi ya wuce dani.

"Ki shiga ki watsa ruwa, ni kuma bari in kawo miki abu mai ɗan ruwa_ruwa da zaki saka a cikinki. Kinsan irin wannan yanayin sai da farfesu mai ɗan yaji_yaji, ki cika cikinki da romo'

Dariya ya sakani sosai. Ni ina dariya shi kuma ya shagala sosai da kallona. Mikewa nayi na cire kab kayan jikina, na wuce banɗakinshi mai kyau da tsabta sai ƙamshi yake zabgawa. Da sabulunshi na nibiya nayi wankana tsab na jima a tsaye ruwan shawa na zuba a jikina zafin ruwan na ratsani.

Edit with WPS Office

A wannan daren dai ni da Khalid mun murge junanmu sosai gaskiya. Bani na baro gidan ba sai dab asuba ɗinnan yazo ya saukeni a ƙofar gidan na shige wuf. A hakanma ji nake yi kamar kada mu rabu, wani irin tarairaya da tattalina Khalid yake yi tamkar zai mayar dani cikinshi. Ajjiyar zuchiya na sauke da naga na shigo cikin gidan ta ƙaramar ƙofa. Wuce ɗakina nayi na lallaɓa na leƙo tsakar gidan. Ajjiyar zuchiya na sauke da naga Babangida shima ba a gidan ya kwana ba.

Babangida:.

Tana juyowa idanunsu ya sarƙe ana juna.

Da gudu tazo ta faɗa kirjinshi, shi kuwa yayi mata riƙon alawar yara, babu shiri ya watsar da ledojin hannunshi izuwa ƙasa.

Da baya da baya ya dinga tafiya da'ita zuwa cikin uwarɗakin dashi da'ita suƙa faɗa gado yif.

Nan suka shiga yamutsa junansu. Babangida gwanine gangaran a wannan fagen, haka Sumy itace tafi yi mishi daidai da yanayinshi, amman duk da hakan a bayan yadda yake ji game da Sabuwa take. Shi yasa suke samun nutsuwa da gamsuwa mai kyau tare da junansu.

Tare sukai wanka suna cuɗa juna suna watsama juna ruwa da kumfa.

Daga nan kuma suka baje a falo, Sumy na ba Babangida farfesun kayan ciki a baki, shi kuma Yana charting ɗin banza da Zeee, tsaraicinta ta turo mishi yana buɗewa ya shaƙi ruwan farfesunnan ta hanci yawunshi ya sarƙe ya shiga tari gami da kakarin amai. Da ƙyar ya dawo hayyacinshi da Sumy ta bashi ruwa ya ɗan kurba sau uku. Zee sabuwar budurwarshi ce da suka haɗu shekaran jiya.

Wayar ya kuma ɗauka yana ƙarema halittarta ta mace kallo yawunshi na tsinkewa, Sumy ta ajjiye cokalin ta yi ƙoƙarin fisge wayar ya zabura ya yi carab da wayarshi.

"Ayi haƙuri Rayuwata afuwan. Wasu ƙarafaine aka turo mun to shine nake dubawa"

"Ko kuma kana charting ɗin banza da ƴan matanka ba, ko matanka. Ni ina zaune ina zamanka amman kaƙi aurena matan gidannan sufa duk a tunaninsu aure muke yi. Ni fa Babangida na gaji tura kuma ta kusan kaini bango. Kasan Allah da girma yake daga lokacin da zaga cike gurbina. Ma'ana kayi mata huɗu ni ina matsayin dadiro. Wallahi daga lokacin in duk duniyarnan gatanka ne saina tuni asirinka. Har gidanku wallahi zanje.

Narantse da Allah buwayi gagara misali sai mun yi aure da figi da yagi. Baki isa kaci biredi ka

Edit with WPS Office

yaga ledar ba."

Fuu ta miƙe ta yi shigewarta ciki.

Ai babu shiri Babangida ya tafi rarrashi.

Kirjinshi ya jawota yana shafa bayanta da sumar kanta dake ta faman ƙyalli.

"Sumy kina da fitina. Hauka nake yi ne da zan rabu dake, ko in ƙi aurenki alhalin nasan zamana kike yi na katangeki da maza.

Sannan ai ke fishi da ɗaukar zafi ba ma naki bane kwata_kwata  sabida kin fiye mun kab matana sau dubun dubata. Ke bari fa kiji a wajenki kaɗai nake samun nutsuwa. Gobe zanje in kwaso kayana su waɗancan shashashun zan sanar musu zanyi tafiyane. Kwana biyar zamu yi tare amman Abuja  zamu tafi gobe akwai wata semina ta ƴan kasuwa da zamu halarta da walimar cin abinci da aka haɗa mana kowanne zai tafi da matarshi.

To naso in ɗauki Amarya muje tare nayi mata alƙawarin hakan dai. Amman zan san yadda zan lallaɓata in ɗan bata wasu kuɗaɗe nasan tafi buƙatarsu akaina sai in zo mu wuce"

Da wannan daɗin bakin Babangida ya shawo kan Sumy.

Komawa suka yi suka ƙarashe cin abincin kafin suka buɗe sabon shafin masha'a. Da komai ya lafa kuma suka ƙanƙame juna basu suka motsa ba sai asuba.

A gurguje yayi alwala dan shi baya kwana da rashin tsarki, jallabiya ya zura ya fice masallaci tare da mazajen gidan.

Bayan an idarne suka ɗan gaggaisa da mazan gidansu.

Baban Zainab yace.

"Ai Alhaji gaskiya aikinku baya baku damar zama waje ɗaya sam, watarana kwana ɗaya kake samun zuwa kayi mana a gidan ma"

Babangida yayi murmushi yace.

"Dake kasan matana huɗu duk da ita Sumayyan hutun nawa kuma bashi da yawa, in an rarraba baya wuce kana ɗaɗɗaya suke samu ma. Yau ma Abuja zan wuce amman da ita Sumayyan zan tafi"

Suna tafe dai sunata hirarsu har suka shigo gidan kowa ya nufi ɗakin matarshi.

Jijjiga ya samu Sumy na yi a falo. Kallonta yayi ta harareshi, shima ya rama dan tasan ba tayar baya bane shi.

"Ke lafiya kike hararata? Kwana biyu ban shiga jikinki da duka ba ko?"

Edit with WPS Office

Murmusawa tayi sai ga hawaye ya gangaro a kumatunta.

"Lallai Babangida ka gama rainani. Ashe amaryarka har mota ka sai mata, ni kullum sai dai in fita in hau abun hawa ya kaini office."

Kallonta yayi. Yayi dariya ya nunata da yatsa.

"Amman kinsan ba aure muke yi ba dake ko? Dadurone fa. Kuma ke a daduron ma ai ke me sa'ace tunda babu abinda bana yi miki"

"Au haka ma zaka ce Babangida haka zaka ce mun dan iskanci ni ina zaune babu mota. Wallahi bazan yarda ba"

Dariya yayi yace.

"To yaya kike so ayi kenan Sumy?"

"Motarka zaka barmun, ko kuma ka karɓo mun ta wajen amaryar take"

Kur yayi mata da idanunshi yace.

"In duk ba'a yi hakan ba kuma sai me zai faru yarinya?"

Ya tambaya tare da karantarta.

"Sai ayi uwar watsin da za'ayi dan wallahi Allah bazan yadda ba"

Tsaki yayi ya nufi hanyar shiga ciki dan mugun bacci yake ji. Amman ko da ya kwanta Sumy ta zo ta tsaya a kanshi ta dinga zazzago ruwan masifa ta dinga zaginshi. Daya tunzura ya zabura ta fita falo a guje, har ta sa ƙafarta ɗaya a waje a ƙofarta ta falo da zai sadata da tsakar gidan. Babangida yayi carab ya riƙota ya jawota kiiii.... ta shigo ciki.

Nan dambe ya kaure a tsakankaninsu, ta yar dashi ya yar da'ita dai sukaita turka_turka. To ƙarfin namiji ba ɗaya bane Babangida yayi mata ligi_ligi har saida mazan gidan suka shigo suka kwaceta. Dama in dai tashancine sun riga da sun saba maƙota ma sun san halinsu.

Wanka yayi ya fice a gidan fuu. Ya barta da fashasshen baki, duk da shima ta fasa mishi leɓenshi na ƙasa ta ciki.

SABUWA:.

Ina sa key na buɗe barayina na tarar da Mardiyya a ƙasa tana murƙususun ciwon ciki, Aminu yanata mata sannu, ragowar yaran suna cikin ɗakinsu.

"Yauwa ga ummi ta dawo. Ummi ina kika je?"

Edit with WPS Office

Gabana na faɗuwa na ƙarasa kusa da Mardiyya na dafa kanta.

Meke damunki naga kinata juyi, ko cikinki ne ke ciwo?"

Cikin muryar damuwa tace.

"Tun ɗayan dare  cikina yake ta mun ciwo. Munje ɗakinki ƙofarki a kulle"

Cikin ya kuma murɗa mata dole tayi shiru.

"Eh Ummi. Da cikin ya matsa mata har wajen Umma muka je muka kirawota. Amman bata zo ba har yanzu"

Babu shiri nayi zaman daɓaro a kujerar da Mardiyya take kwance tana riƙe da cikinta.

Hmm akwai abinda kika ci ne Mardiyya?"

Kallon Aminu naga tayi tuni ma na fahimci abinda ke damunta. Korashi ciki nayi na dubeta da kyau na yi mata tambayoyi dangane da abubuwan data sani game da jinin haila. Alhamdulillah amfanin ilimi Mardiyya tasan komai sai ɗaura mata nayi da cewa.

To sai ki sake kulawa da kanki sosai Mardiyya girma ya kamaki, nasan a islamiyyarku an faɗa muku komai.

Sannan duk abinda zai faru kar kuje cikin gida da maganar ba saurarenku zasu yi ba.

Ni ɗinma naje gidan Rahama ne cikin dare aka kirawoni jikinta ya tsananta. Lokacin kuma dana fito kun daɗe da yin bacci. Tsumma kika saka a jikin naki?"

Ta ɗaga mun kai.

To muje in baki audiga, duk wata in hakan ya riskeki ki dinga zuwa ina baki audigar mata.

Mun shiga ɗakina anata kiraye_kirayen Sallah. Na ɗauki audiga da magani na bata nace ta haɗiya.

Tana fita na zauna jigum ina tunanin ya zamemun dole in dena fitar darennan in kula da yarana sosai, duk abinda za'ayi duk bala'i ayishi da rana gaskiya.

To da Yar shuwa ta shigo da Shikenan asirina ya gama tonuwa.

Ni dai har yara na sallamesu suka fita inata tunanin rayuwa da yadda lamura suke tafiya.

Misalin takwas na safe na jiyo hon ɗin motar Babangida, har naje zan buɗe tunda Mardiyya bata nan sai naga kamar mai gadi ya ɗauka ya fito daga ɗakin masu gadi da sauri ya wangale mishi get.

Juyawa nayi zan yi komawata ciki a zuchiyata ina barka da daukar me gadi da akayi.

Edit with WPS Office

Da Yar shuwa muka haɗa ido ta tawo tarbar me gida takobin yaƙi, sai wani rausaya take yi, ta ci kwalliya mai ƙayatarwa harda tabarau a idanunta.

Banza nayi kamar ma ban ganta ba, sai ji nayi ta ambaci sunana harda dariyarta.

"A_a Sabuwa barka da safiya, ya yaran nawa?"

Da mamaki na dubeta, na juya baya sai naga ashe Babangida ta gani shi yasa tayi wannan barikin.

Tsaki naja nayi shigewata cikin ɓarayina.

Me akayi, ya akayi wajajen taran safe na gama aikace_aikacen gidana tsab, na ɗanyi ma Rahama farfesun bushasshen kifi karfasa. Sai na soma jiyo kamar ana rikici a tsakar gidan. Baki na taɓe na zari jakata dama mayafina yana jikina, na ɗauki ƴar ledar dana saka kular farfesun na kulle gidana.

Ashe rikici aketa tabkawa, me ya faru oho.

Na dai ji Hamida tana faɗin babu adalci ai kwananta ne taya za'ace za'a tafi da yar shuwa Abuja a cikin kwananta.

Bakina na taɓe na ƙarasa kusa da motar.

Dan Allah inason magana da kai ne"

Na faɗa muryata a sake. Yar shuwa tana tsaye a gefen wajen mai zaman banza sai murmushi take yi ma Hamida, ita kuma Hamida ta rufe idanunta fur ita bata yarda da wannan tafiyar ba.

Babangida shi kuma sai wani huci yake yi.

Tinƙis_tinkis ya ƙaraso inda nake.

"Ke kenan zuwa gida, ko wacce tsiyarce a gidanku oho. Kullum bakya gajiya da kai musu abinci, amman baki taɓa tunanin girka abinci ki kaima Malama ba. Shi kanshi Malam ɗin da kike yin zamanshi baki iya yin girki kin kai mishi ba sai dai Maigogul.

Dakata dan ALLAH zani gidan Rahama ne ta haihu jiya"

Ya ƙanƙance idanunshi yace.

"In na hana kuma fa?"

Sai in zauna"

Na bashi amsar a taƙaice.

Kuramun idanunshi yayi kawai, yanata wani ƙarema fuskata kallo. Ita ko yar shuwa hankalinta

Edit with WPS Office

na kanmu da taga kallon yayi yawa sai ta ambaci sunanshi.

"Jannaty lafiya dai ko? Lokaci nata ƙurewa, tafiya ba'a jirgi ba. Ka barta  taje inda zata je karta ɓata mana lokaci a banza"

Murmushi yayi, nima murmushi nayi inajin tsanarsu dukkansu tana ninka kanta da kanta.

"To kije kinci albarkacin mai daraja. Kya gaishe da Maigogul ɗin naji labarin an sassaresu a club. Sai ɓoyewa kike yi baki san duk sirrin gidanku a tafin hannuna yake ba"

Yana kaiwa haka ya koma wajen motarshi.

Ni dai har na fita Hamida tana tsaye tace sai dai kuwa a tafi tare dasu dukkansu. Sai kuka take shiryawa. Ai bata soma ganin komai ba in dai Yar Shuwa ce.

Ya suka ƙare wannan kuma matsalarsu ce.

A ƙofar kwaraɓaɓɓen gidansu Rahama da babu ƙofa babu labule ko na buhu ne na hangi shigan Labbai ni kuma ina kan tawowa.

Bayanta na bi na shiga da sallama.

Gidan ƙazanta kenan, gidannan kaca_kaca, ga kayan wanke_wanke da wanki duk a jibge a tsakar gida, ga shanyar kayan fitsari a igiya, ga girki duk a tsakar gidan.

"Fatima ina kwana, ya kwanan masu jego kuma?"

Kishiyar Rahama ta tsakiyan kenan. Mai yara bakwai haihuwar konika, yarinyar mace amman ƙazanta duk ta cinye mata yarintar tata, tana zaune tana tsifa kura na tashi a kanta.

"Lafiya masu jego suna ciki"

Labbai ta juyo tace.

"Kamar tare muke, kinga fa shigowata kenan"

Dariya nayi mata na yaƙe nace da'ita.

Ai ina ganin sanda kika shigo."

Nan dai muka faɗa ɗakin maijegon tana gado ita da jaririyarta, Adama tana zaune a ƙasa tana rabama yara dumamen tuwo wanda aka dumama cikin miya. Wallahi miyar sabida tsabar rashin kaurinta ko kama tuwon bata yi.

"Kaga manya. Kune a tafe, haka gida kika soma zuwa dubo jikin Maigogul kuka tawo tare da Labbai?"

Saida na ture tulin kayan wanki na zauna a kujera nace.

Edit with WPS Office

Tafiyarmu daban_ daban a tsakar gidannan muka haɗu. Ina kwananku?"

Nan muka shiga gaggaisawa, yaran Rahama ƴan matan duk suka gsishemu, aka zuba musu tuwon da ruwan kokko suka fice tare da ƙannensu ƙanana.

Ga ɗan farfesu Rahama na kifi nayo miki. Ga ɗan kayan tea ma na ƙullo miki a leda"

Na zuge jakata na ciro madara zata yi gongoni biyu, sigarma haka, harda furanto.

Tana washe baki ta karɓa.

"Kai amman naji daɗi sosai. Allah ya bar zumunci nagode Lolo. Ga yarinyar Labbai ɗauketa ku ganta"

Labbai ta miƙo mun yarinyar muka ganta tubarkalla masha Allah.

"Lolo Labbai ku sakko mu karya"

Murmushi nayi nace.

A_a ai saida na karya na fito. Sai dai Labbai"

Nan  Labbai ta zauna suka soma karyawa, Rahama kuma tana ta cin farfesunta.

Nan na shiga fitar da duk kayan wankin ɗakin tare da gyare_gyare ɗaki kamar na mahaukata.

"Lolo anfa kawo sadakin ɗiyarmu ƴar wajen Rahama Rakiya, bikin kuma wai wata biyu fa aka saka"

Cewar Adama da takai lomar tuwo.

Wata biyu. Tabb ai wata biyu yayi kaɗan ina laifin rabin shekara, bayan ƙaramar Sallah da wata ɗaya kenan fa"

Labbai tace.

"Koma shekarar ba. Karfa ki mance Laraba da suka aurar me shi Tanimun ya tsinana? Gado da katifa kawai ya siya, kiga irin kunyar dai da akasha a bikin yarinyarnan, har gobe babu kujera a ɗakinta, dangin miji sai goranta mata suke yi. Duk da ita Rakiya idanta a buɗe yake tana ɗan tarin kayan kitchen a maƙota tace. Rahama fa me ta tara a matsayinta na uwa? Mu dai bamu dashi abinci ma saika fita ka nema, ko abinci akayi in babu kuɗinka a ciki ya zama haramiyarka. Wannan rayuwa da ciwo. Ke dai Lolo kakarki ta yanke saƙa, kece kaɗai kikai dacen auren tajiri"

Dena ninke kayan nayi na zauna, dan kwana biyu kasala na ɗan damuna, harda tashin zuciya haka dai.

Tabbb ke yanzu Rahama me yasa baki yi ma Tanimu ƙorafi akan a ƙara watannin ba? Kinga kowa bashi dashi, ni ginin su Rakiya na saka a gaba duk da an riga an gama naso ayi katanga, to

Edit with WPS Office

amman inaga gara su koma ko da kwano a katange"

"Hakane. Yanzu ma dana baro na barone anata buga rabta za'a mayar da tsofaffin kwanukan dake kai.

To dama kece ma gudunmawarki zata ɗanyi kwaɓi, mu da muke fama da zawarci ɗan abinda zamu samo baya wuce na tanadin wani auren tunda bakasan ina zaka shiga ba."

Ina manyan mata masu capacityn  suke?  ku fito lambarku ce ta fito.

Yar uwa turaren wuta kike nema nau'ika daban_daban masu musulmin ƙamshi da kama muhallu? Ba itacen banza masu sanya gida ƙauri da hayaki kamar an kunna taohuwar bespa ba.

Matso gasu MRS  BUKHARI B4B GIDAN KAMSHI nazo miki da duk abinda kike buƙata na ƙamshi. Kama daga turarukan wuta irin na gidan alfarma. Zuwa humrori iri daban daban masu musulmin ƙamshi da riƙe jiki.

Bugu da ƙari muna da turarukan kaya, na fesawa dana turara kaya.

Muna da kulaccam nau'i daban daban masu gyara jiki da lausasa  fata mata, ga kuma ƙamshi mai inganci.

Muna da turarukan tsugunno na musamman masu sirri Hajiyata

Muna da room freshener iri_iri

Muna da mopping mix masu kama waje.

Akwai turarukan kafet dana kujeru.

Sannan akwai box _ box  setika na Hajiyoyi masu ƙyallin goshi.

Muna da Amarya package.

Muna da uwargida package

Muna da maijego package

Muna bayar da sari ko a ƙasar waje kike, muna tura kaya

Saudiyya

Nijar

Ghana

Edit with WPS Office

Camaron

A duk ƙasar da kike kayanmu zai iso miki cikin aminci da yardar Allah.

Hajiya akwai Humrar matan aure wannan ta musamman ce.

Duk wani abu da kika sani na ƙamshi babu irin wanda bamu dashi a kamfaninmu.

Muna da turaruka designer na maza da mata wanda kamfaninmu ke bugawa Hajiya babu inda zaki je ki ci karo da mai irin ƙamshinki.

MRS BUKHARI B4B GIDAN KAMSHI TAZO MUKU DA DUK ABINDA KUKE SO NA KAMSHI HAJIYA.

KUNSAN KANURI MUNE KAMSHI DAMU AKE KOYI

SIYAN NAGARI MAIDA KUDI

MUNA MARABA DA MASU SIYAN ƊAYA KO SARI.

LAMBAR DA ZA'A SAMENI KAI TSAYE ITACE.

Wa.me/2348179523215

SAI NA JIKU

MRS BUKHARI

IDAN KAYA YA GAJI...

GAMMO MA YA GAJI

BADIAT IBRAHIM MRS BUKHARI B4B GIDAN KAMSHI

SHAFI NA SHA TARA

Sanya kuɗin karatun a cikin wannan lambar asusun

Edit with WPS Office

0044442984

Buhari Ibrahim Ladan Gt bank

Lambar da zaku turo shaidar biya gasu kamar haka

08022059556

Ko kuma

08105932041

Masu son magana da marubuciyar kai tsaye kuma ga lambata

Wa.me/2348179523215

Follow this link to join my WhatsApp group: https://chat.whatsapp.com/Hnb3Ee00TCQKqHgDwWfyx0 maman Muhammad kitchen Etims kayan mu available munasaida atanfa lace shadda mayafai takalmi da jaka akwai jewelrys

Munayin adashin gata nakayankici munaturakayanmu ko inakake cikin yardar Allah Ina wayanda basu da jari tum gada matasamu saki iyatallata kayanmu kema kisamunaki

Location dinmu Kano tudin Yola get 5 rukar Fulani gidan su baba sadiq 07044545303

Edit with WPS Office

Kai kawai na iya jinjinawa nama rasa me kuma zance. Adama tace.

"To ke me kika tara? Ni kaina ƴan mata ukune a gabana, damma samarin nasu babu laifi suna ɗan musu ihsani, mun ɗan sai kayan robobi, da ɗan fulasai, sai cokula. Suna ƙarƙasshin gado. To naji suna cewa za sui labule irinna na yayi.

Ubansu shima gadone da katifa sai kujeru  wan_wan yake yi, iyakacinsu kenan ga yayyensu da ƙannensu na ɗakin  Kande du hakan dai yake yi."

Shine ai gara muji me ta tanada sabida musan yaya za'ayi ko da karo_karone a soma tun wuri"

Na faɗa amai na yinƙuromun.

Babu shiri na fice a guje na ƙarasa magudanar gidan na dinga sharara amai kamar zan amayar da ƴan hanjina.

Cikine dani ya tabbata kuwa, to amman cikin waye Khalid ko Babangida?"

Na tambayi kaina, yayinda Labbai take ta yi mun sannu. Ruwa ta soma ziraromun ina wanke bakina da fuskata.

Kila cikin na Babangida ne, amman dole sai naje asibiti an tabbatarmun da cikin na wata  nawa ne da wannan ne zan iya gane na waye. Duk da zubarwa zanyi koma dai na waye in huta gaskiya irin wahalar da renon ciki yake bani wahalace ta gaske, yau asibiti gobe gida, jibi lafiya,gata ciwo ƙaƙas.

Tunowa da abinda ya faru a rayuwata da sharaɗin likita a kaina yasa jikina ya mutu murus

"Sannu Lolo ah Allah ya raba lafiya ai Malama ta girma babu ƙani. Nifa wallahi nayi ma tunanin allurar tsare iyali kike yi ma"

Ni dai na miƙe da ƙyar muka koma ciki. Kirjina na bugawa

"Ahh abun fa yazo ciki na tonon silili kenan. Ke dai ciki baya ɓuya a jikinki. Wai ni Lolo ya labarin ƴar shuwa mitsiyaciyar gaske. Ina dai fatan bakya shiga harkarta kuma baki bari tana miki shisshigi ba? Naji labarin ai duk abinda ya faru a tsakaninku abu har da danganawa da ofishin ƴan doka. Ni dai Lolo shawarata ɗaya ce. Wallahi kar ki kuskura ki biye mata ta turguɗa miki aurenki, tunda dai da mugun nufi ta Aure mijinki. Ku taso tare, ƙawancenku a unguwa waye bai sani ba, amman ta rasa wanda zata aura sai Babangida abun da mamaki. Maza ƙannen ajali, wani sa'inma su suke zama ajalin naka" Labbai tace.

"Ai wallahi sai Babangida yayi mata korar kare. Jiya Maigogul akan buzu ya kwana sai kiran aljanu yake yi iri_iri duk akan Yar Shuwan ne zai zata gane kurenta ƙila turen aljanu zaiyi mata ne oho."

Hmm kawai nace dasu abinda yake gabana shine a gabana. Ni da Labbai muka shiga kintsa ɗakin tsab. Kayan wankin dana fitar dashi na kira yara akan su kai wankau suke sanar mun ai

Edit with WPS Office

kishiyar uwarsu ce mai wankau ɗin.

Karasowa tayi ta ƙirga kayan Rahama tas.

"Ɗari uku, sai sabulu nera ɗari omon hamsin"

Ɗari biyar na bata. Ƴan matan Rahama kuma na aikesu su yo cefanen abincin rana har da na daren ma.

Anata hira ana shewa, maƙota sai barka suketa shigowa sunaita ma Rahama tsiyar basu san tana da ciki ba.

Amman Rahama ai gara ki tsayar da haihuwarnan haka. Rayuwarma ba daɗi akeji ba amman sai kwatso ƴaƴa kuke yi. Ji kishiyoyinki duk ciki garesu"

Adama tace.

"Wallahi kuwa waɗanda ka tara ma baka iya musu ba.

Abinci saika nema ka ciyar da yaran. In sallah tazo duk mu firgice wajen fito da yara kunya. Rahama gaskiya kiyi ma kanki faɗa gaskiya."

Ana cikin wannan hira sai ga ƴan gida su Sa'ada da su Amina dukkansu sun shigo. Nan ɗakin yafi ƙarfin zamanmu, dole muka ragu zuwa tsakar gida, ni duk wannan abun da akeyi ina kwance ina juwa dama ni cikina akwai wuya.

Da rana shinkafa da wake jallof muka dafa. Da daddare sai da Adama tayi ma Rahama tuwon dare harda ɗumame miya harda kifi yara sun shigo suna tallan ɗanyen kifi ɗari ɗari shida ɗari biyar na siya musu, rabi Rahama tace a soya mata gobe ayi girki dashi, rabin kuma aka yi miyar karkashi dashi.

Dab magriba dukkanmu ko wacce ta kama gabanta.

Bani na shiga gida ba sai bayan isha, yara suna falo suna kallo, Mardiyya kuma littafin Hadith ne a hannunta.

Dukkansu a guje suka yo kaina ana mun oyoyo.

Har wani ajjiyar zuchiya suke saukewa. Unguwa kawai naje ina ga na bar gidan, ko na bar gidan duniyar baki ɗaya shin yaya zasu kasance? Lallai shi yasa da yawan iyaye suke dagewa duk wuya duk daɗi su zauna kan ƴaƴansu. Shi yasa akace in kuka haihu da namiji ya gama cutarki sai dai haƙuri.

Cikin ƴaƴana na shiga, sukaita hidima dani, me kawo mun ruwa daban me kawo mun abinci daban. Macroni da miya suka dafa, ni kuma bana cinta dama, balle yanzu da bani kaɗai bace take ma naji amai ya zo mun.

Edit with WPS Office

Ai kuwa a guje na shiga banɗaki na dinga kwarara amai ƴar shinkafar da naci da rana duk na fitar da'ita.

Yaran sai sannu suke yi mun a mugun galabaice na kallesu.

Kuje ku jirani a falo, Mardiyya dafa mun indomi tayi ruwa tayi yaji sosai zanyi wanka in yi Sallah.

Malama tace.

"Ummi nima zanci dan Allah"

Murmushi nayi nace.

To kuje, in kuma zaku ci ki haɗa ki dafa mana"

Ina jinsu kowa na zaici zaici har suka fice

Wanka nayo na yi sallar magriba da isha.

Ina kan sallaya ina tunanin in zubar da cikin duk abinda zai faru dani ya faru? ko in bar abina ɗa dai na Babangida ne kawai a barshi a hakan.

Ina tsoron inje in zubar da cikin gargaɗin da likita yayi mun a baya yazo ya tabbata a kaina in mutu yarana su tagayyara, sannan bazan so in mutu ta wannan hanyar ba domin bansan makomata ba. kuma a cikin ƴaƴanka baka san wanda zai taimaka maka a rayuwa ba kuma baka san waye mai arzikin a ciki ba.

Da wannan tunanin na daure dai na fito falo, sai ƙiriniya yara suke yi musamman Malama fitinanniya duk ta addabi Aɗɗa'u da surutu.

Mardiyya kawo mun indomin inci, kuma kuci naku kuje ku kwanta dare yayi kuna da makaranta"

Miƙo mun nawa tayi, sauran wanda ya rage kuma suka zauna suna ci suna jan hanci.

"Ummi an kawo sadakin Yaya Kaula wai bayan Sallah da sati biyu bikin"

Kaula ɗiyar Sa'a ce. Baki na taɓe nace.

Ayya. Kinga ma Rakiya ma an kawo sadakin nata bayan Sallah ne itama bikin nata. Bayan sallah akwai biki"

Nan Mardiyya ta tsiri murna har ta soma tambayata zan tambayar mata Babansu yayi mata anko?"

Tashi kuje ku kwanta Allah ya kaimu lokacin muna cikin rayayyu tukunna koni ai sai in miki Mardiyya.

A zaune a wajen suka barni ina mai da numfashina sai ga kiran Khalid ya shigo.

Edit with WPS Office

Idanu na lumshe na ɗauki wayar.

"Yau Madam ko nema na baki yi ba, ni kuma aikine yayi mun yawa a asibiti. To kin wuni lafiya ƴan mata na?"

Lafiya lau. Nima dake yau na fita ban zauna ba shi yasa ka jini shiru"

Sassauta murya yayi yace.

"Ina kika je da ya hana ki nemana?"

Yaya Rahama ce ta haihu shi yasa, gobe ma ba zama zan yi ba. Amman nayi niyyar kiranka dan inada magana da kai. Amman nasan ba lallai mu wanye lafiya ba ma"

Ina faɗan haka na miƙe na koma ɗakina na baje a gado ina lumshe idanu na gajiya da bacci.

"Ina saurarenki, Allah yasa ba abinda zai jagula mun wannan daren nawa zaki faɗa mun ba."

To kusan haka, so nake mu dakatar da haɗuwarmu zuwa nan da shekara guda kafinnan na haihu lafiya, dan ɗana na sunnah ne bazan so in shafa mishi ƙazanta yana ciki ba."

A mamakince yace.

"Cikinne zai hana mu haɗuwa Sabuwa, kika sani ma ko ɗan nawa ne kike ƙoƙarin farraƙashi da ubanshi tun yana ciki? Wallahi cikinane ma"

Idanuna na runtse maganar tai mun wani irin harbi a zuchiyata. Ni nasan ɗa nashi ne. Amman inaso in ture mishi wannan tunaninne sabida gaba. Akwai sharaɗin likita mai zafi a kaina dangane da lafiyata. In nayi yinƙurin zubar da cikinnan mutuwa zanyi da bakina shiru ma zan zubar ba tare da kowa ya sani ba. To amman babu dama dole in haife cikin.

Khalid kar ka sheganta mun ciki. Cikina na sunnah ne, ka dai yi haƙuri zuwa in haihu, sannan ina buƙatar kuɗi masu ɗan yawa.

Ajjiyar zuchiya ya sauke, munfi minti talatin muna tababa akan ko a wata sau ɗaya ne in bashi damar ganina ni kuma naƙi fur. Da ƙyar ya amince mun da hakan, mu kai sallama na ajjiye wayar a daren ya turamun kuɗin, da saƙonnin soyayya masu daɗin gaske.

A haka bacci ya ɗebeni.

Zuchiyata cike da fargaba haifo ɗan da bana Babangida ba kuma a gidanshi.

Shin zai ma yarda cewar wannan cikin nashine kuwa? Duk abinda ya tafasa ya daɗe bai ƙone ba. Ko ya yarda ko kada ma yarda mitsiyacin ai abinda yake yi da ƴaƴan wasu ne ake yima matarshi shima.

Nasan adadin matan da yayi ma cikine shi ɗin?

Edit with WPS Office

BABANGIDA:.

Suna kan titin Abuja suna tafe anata hira a tsakanin Amarya da ango.

"Jannaty ashe Hamida itama ba kunya bace da'ita ba? Yau nayi mamakin abinda tayi. Ya ina Amarya take tunanin zaka ajjiyeni ka tafi da'ita da ɗanyen goyo ai wannan rashin adalcine. Ni da naso in ci amarcina a Dubai, dan dai ƙarfin sonka ya rabani da Alhaji da nake tare dashi kafin zuwanka dashi na aura da yanzu muna wata ƙasar"

Rai ya haɗe dan Babangida gwanine wajen zafafa kishi. Itama da biyu ta faɗa domin ta cimma manufarta.

"Ya zaki dinga ambaton wani namijin bani ba a gabana, kuma kina son nuna kamar yama fini arziki ne? To nima ƴar umararnan zamu je tunda kinga azumin ma saura kwanaki . To ki shirya a makka zamu yi karamar Sallah"

Wani irin ihu ta saka tana girgiza ƙirjinta data fahimci anan maitar Babangida take. Ai kuwa ƙur ya zuba ma ƙirjin kallo har yana haɗiye yawunshi ( gareki shin ke kinsan menene a jikinki yafi komai ɗauke hankalin mijinki, ko kema har yanzu baki sani ba?)

Waje ya samu a gefen titi ya faka ya jawota jikinshi.

Ai kuwa nan ta shiga tura mishi saƙo mai kyau ta gama gigitashi da ƙyar yake iya buɗe idanunshi.

"Anya zan iya tuƙinnan kuwa Habibaty ai kin gama sukurkutani sosai.

Yana maganar yana shafan wuyanta...

"Ka daure, ai tanadin da nayi ma in mun isa tanadi ne babba, na tabbatar zaka ji daɗi sosai "

Da kalaman soyayya masu zafi ta ribaceshi yaci gaba da tuƙin awa shida suka shiga garin Abuja. Babangida ya kama musu hotel me kyau da nutsuwa sosai. Babban ɗaki ya kama musu, bai ko zauna ba yace mata.

"Kinga na mance da wayoyin nawa a mota, ki shiga ki watsa ruwa ina zuwa, daga nan sai in musu magana su kawo mana abinci. Me zamu ci? Ni dai inason inci sakwara ne"

Murmushi tayi tace.

Edit with WPS Office

"A haɗo da farfesu, ni ban fiye cin sakwara ba lalatamun cikina take yi."

"To Shikenan"

Ya saka kai ya fice. A zabure ta miƙe ta buɗe jakarta ta ciro wayarta ta danna number Mamanta cikin sa'a ringing biyu ta ɗauka.

"Yaya akayi ya gidan? Yanzu su kattime suna shirin tawowa gidanki"

"Ai muna Abuja yanzu muka iso. Inaso in yi amfani da wannan damar in tatsi kuɗi masu kauri a hannunshi"

Mamanta tace.

"Ai gara dai. Mai kujeru ma jiya saida ya turo yara, cikon kuɗinshi da yawa sosai ga mai gold itama wallahi ɗazunnan da safe ta kirani bamma ɗauka ba dai amman zuwa ƙarshen sati zaki ganta. Ki samu ki tatso da yawa sabida in aka ɗan babbasu an rage kuma zasu ɗan ƙara ɗaga ƙafa"

Ƴar shuwa ta yi dariya tace.

"Ki kwantar da hankalinki ni da a hanya ma yake sanar mun zamu wuce Umara da azuminnan. Ga mota ya sai mun, kuma wannan tafiyar zan tatseshi sosai kafin mu dawo"

Kabbara mahaifiyarta ta shiga yi tana murna. Itama ƴar shuwan dariya take yi.

"Zan kiraki yanzu bari in yi wanka kafin ya shigo"

Datse wayar tayi ta faɗa banɗaki.

Shi kuwa Babangida daya gangaro ya shiga mota, maimakon ya ɗauko wayoyin ya fito sai yayi zaman dirshen yana kiran Sumy a waya dan suna hanya ta kirashi yafi sau goma wayar ya sakata a inda ba zata yi kiɗa bane sai dai tayi wuta, Hamida ma yana gani tana kira banda saƙonni da sukaita shigowa.

"Sumy yaya akayi kin kirani ina hanya ne?"

Da mamaki tace.

"Hanyar ina kuma bayan na gama shiryawa kai nake jira. Ashe da gaske kake yi ka fasa zuwa dani bayan dukan da kayi mun ka kyauta mun kenan?"

Sai kawai ta sakar mishi kuka tana faɗin abinda yafi ƙi.

"Shikenan ni dai dama bani da wani amfani a wajenka. Garinmu zan koma in je in yi aurena kamar kowa "

Nan ya shiga faɗa yana bambamin mita. Daga baya ya sassauto ya shiga rarrashinta tare da

Edit with WPS Office

faɗa mata ta ƙara haƙuri lokacine zasu yi aure bata da wani miji sai shi. Da haka ya rarrasheta dan ita Sumy ta riga ta jarabtu ainun da Babangida. Shi kuma a ranshi yana ganin ko mata sun ƙare baiji zai iya auren Sumy ba.

Hamida ya kira itama basu ƙare lafiya ba, tana faɗa yana faɗa sukai uwar watsi ya kashe wayarshi yana huci.

Fitowa yayi yana tafe yana mita.

"Yarinyarnan gani take kamar bazan iya rabuwa da'ita bane shi yasa ta samu waje take farfaɗamun maganganu. Bata san dan jaririyarta bane kaɗai na ɗaga mata ƙafa ba. Yanzu ina sallamarta ta tafi da yarinya sun samu saniyar tatsa kenan. Ba ga Farida a hakan sai tatsa suke yi ba. Yau ta kwanta a asibiti, gobe za'aje awo."

Abinci yayi musu oda ya wuce sama akan za'a kawo musu in an kammala.

Cikin shigar matsattsun ƙananan kaya na tarbar miji ya shiga ya tadda Yar shuwa sallah ma ta idar tana ninke hijabinta ƙamshinta ya cika ɗakin.

Banɗaki shima ya wuce ya ɗauro alwala ya gabatar da sallar la'asar da ake binshi. Agogon hannunshi ya duba yace.

"Habibaty bari inje Sallah akwai masallaci a jikin hotel ɗinnan nafi son sallah a jam'i. Gashi yinwa nake ji sosai"

Murmusawa tayi tace.

"Ai nima cikina fal yinwar abinci da yinwarka Jannaty"

Idanunshi ya lumshe mata cikin salon kashe jiki yace.

"Ai ni in dan wannan yinwarce yau zan ƙoshi sosai da sosai Habibaty. Masu abinci zasu ƙwanƙwasa sai ki buɗe musu su ajjiye."

Yana gama faɗin haka ya fice yana mata murmushi.

Magungunananta na mata ta ɗakko wata ƙaramar jaka shaƙe da kayayyakin mata, wasu da yawa a cikinsu ƙwayoyin baturene. Ta sha zallan na baturen tare da ruwa ta mayar da jakar cikin akwatinta tana dariya

"Yau akwai kukan jarirai kenan jannaty. Wato ashe haka auren wanda ya iya soyayya yake ni Ƴar Shuwa ban sani ba. Ai ni da Babangida sai dai mutuwa ta rabamu yau zan tatsi kuɗi masu tsoka Allah dai ya taimakeni .

Masu kawo abinci ne suka kwankwasa ƙofar taje ta buɗe masu wani namiji ya shigo da abincin a ƙaton tiren silba.

Edit with WPS Office

Saida ya fita ta ta da kabbarar Sallah tana jiyo ana sallah ma a masallacin da Babangida yace zaije Sallah.

Ana idarwa ya dawo, yana cin sakwararshi ita tana shan farfesunta ta wani yi gurum ta dawo kalar tausayi.

Ɗagowa Babangida yayi ya dubeta duk ta damu. Riƙo hannunta yayi yana murzawa.

"Menene yake damunki naga lokaci ƙanƙani kin canja yau ai ranarki ce, kuma nayi tanadi mai yawa a cikinta."

Murmusawa tayi ta lumshe idanunta tace.

"Mamaki nake yi wai yau nice da auren mijin aminiyata wacce bani da madadinta. Jannaty naso ace Sabuwa ta rungumeni mun samama lafiya da nutsuwa mu haɗe kan yaranmu muyi zama mai kyau. Amman kash sai bin zugar ƙawayenmu take ji, da dama ba dan Allah tun can suke tare da'ita ba ma"

Sakwararshi ya yanko ya ɗebo miyar egusinnan da taji naman rago da kifi, ya saka a bakinshi ya tauna ya haɗiye kafin yace.

"Kinsan menene? Ki dena tunanin sabida Sabuwa zaki takura kanki. Ke kinsan ƙaddarar data haɗamu tun farko, kinsan komai. Zaman Baba Malam Sabuwa take yi ba zamana ba, ai kinga hatta ciyarwa shi yake basu. Kab zuriyata basa ƙaunarta ƴaƴanma baƙin jininta dana ahalinta ya shafesu. Ai kece ƴar gaban goshin dangina dani kaina haka Allah ya tsara"

Ai kuwa Ƴar shuwa ta miƙe kafarta ta ƙara suncema Sabuwa zane a gaban Babangida, ta sanar dashi abubbuwa da dama a game da Sabuwa. Sai dai manyan surrukan Sabuwa bata sakesu ba, bata da niyyar sakinsu yanzu akwai lokacin data ɗibarma kanta da zata fasa ƙwai. Amman sai ta tabbatar ta kafu a gidan ta inda ba'a isa an tugeta ba.

Babangida ya sake jin tsanar Sabuwa da danginta ya kuma tsananta mishi, dan a wannan daren ba dan ƴar shuwa ta gigitashi a shinfiɗa ba ba lallai ya runtsa ba tsabar dana sani da takaicin haɗa jini da Maigogul.

A wannan daren Babangida yasha daɗin da bai taɓa jin irinshi ba, sai yake ji kamar ranar ma ya soma kwanciya da mace.

Bayan ya tafi sallar isha ƴar shuwa tayi cushe_cushe a ƙasanta magunguna fin huɗu, harda kasko da gawayin kanti ta tawo dashi tafi da gidanta ta tsugunna a wani turaren ƙara saukar da ni'ima.

Daman kafin ya dawo tayi lumtsum shi kawai take jira. Shi kuwa dama mai nema ne ya samu ba shiri ya shiga aiki. Ta cire kunya ta bashi hakkinshi sosai, a duk abinda zai mata ta dinga taimakonshi har damo ya isa ga harawa.

Edit with WPS Office

Washegari da safe suna karyawa ta jefo mishi da buƙatar dubu ɗari zata biya bashin kayan fitar biki data ci bashi.

"No nawane duka kuɗin da ake binki ai gara a biya zaifi ko yaya kikace Sarauniyata?"

Tun jiya da daddare ya dinga raɗa mata wannan sunan a kunnenta dama.

"Da yawa gaskiya kar daga zuwana in ɗaura maka ɗawainiya Jannaty"

"Kar ki damu girmankine ki ɗaura mun dukkan nauyiinki ni kuma zan biya miki buƙatarki dan ke aka yini"

Murmushi tayi a zuchiyarta tace.

"Lallai gayennan ya shigo hannu. In asari baya kamaka kirsa tafi magani.

"Dubu ɗari biyu da hamsinne kaga ai da yawa"

Wayarshi ya ɗakko yace.

"Karanto mun lambar asusun yanzu in saka musu kuɗinsu Habibaty."

Ai kuwa nan da nan ta karanto mishi account number Umar ƙaninta ya saka kuɗin.

Rungumarshi  tayi ta shiga aika mishi saƙon godiyar da ya kaisu ga shiga waccar duniyar.

A gurguje su kai wanka suka kwanta basu suka farka ba sai azahar.

Jallabiyya Babangida ya saka ya fice masallaci ai kuwa ya tafi ya mance wayarshi sai da Yar shuwa ta idar da Sallah bayan sun gama waya da mahaifiyarta kana taga wayar Hamida nata aikin kiran wayar babu aji. Saƙon Sumy ne ya shigo sai hankalin Yar shuwa ya koma kan saƙon.

Jan tangaran ɗin wayar tayi izuwa ƙasa saƙon ya bayyana gabaki ɗaya.

Da sauri Babangida ya shigo har yana tuntuɓe.

Taso ta karanta saƙon amman tana ji tana gani ya zare wayar a hannunta sai ga kiran Hamida.

"Ni Babangida Hamida ta dameni sosai ko yaya take son in yi oho"

Ɗaga wayar yayi ya kara a kunnenshi. Sai yaji tana kuka kamar ranta zai fita.

"Ke menene kike kuka gobara gidan yayi, ko mutuwa akayi muku ne?"

"A_a wallahi mufida ce take ta suma tun asussuba. Nama kawota babban asibiti an bamu gado. To babu ishasshen kuɗi a hannuna kuma Usama yana gida na barshi a kwance. Ka kira Sabuwa ka sanar mata ta ɗauko shi zuwa ɓarayinta."

"Ya zaki tafi ki bar yaro a ɗaki shi kaɗai dan iskanci? Ke me yasa baki faɗa ma Sabuwan kafin ki

Edit with WPS Office

fito ba. To wallahi ki tabbatar kin  kirata taje ta ɗakko yaronnan ni dai na faɗa miki. Mufida kuma meke damunta likita yace miki?"

Jikinta a mace tace.

"Basu sanar dani ba tukunna. Amman dai ko nono tun jiya taƙi kamawa kota kama sai tayi amanshi."

"To Allah ya sauwaƙe zan tura miki dubu hamsin ki riƙe a hannunki, ki kira kuma Malama ki sanar mata, Sabuwa kuma kice nace ta dinga yo girki tana kai muku har a sallamoku. Zan shirya in tafi semina yanzu sai mun yi waya"

Da sauri Hamida tace.

"Amm ai daka tura dubu ɗari sabida kar in zo in kira wayarka kaƙi ɗagawa kana tare da ƴar gol"

Kit ya datse wayarshi yana sauke ajjiyar zuchiya. Shiryawa suka yi suka tafi Semina

da aka haɗa tare da liyafar cin abinci.

Ko wanne ɗan kasuwa tare da iyalinshi sai ɗaiɗaikune suka tafi su kaɗai.

An yi taro tare da yin bayanin daya jiɓanci kasuwanci. Daga bisani aka shiga gaishe_gaishe. Nan Babangida ya haɗa Yar shuwa da manyan matan ƴan kasuwa, waɗanda suma ba'a barsu a baya ba.

"Ai Alhaji Babangida sai ka haɗani da Amarya mu wuce Dubai saro dogayen riguna kawai ko?"

Cewar Hajiya  Turai matar hamshaƙin ɗan kasuwa kuma abokin Babangida suna yawan haɗuwa a  makamantan tarukan semina haka. Sannan sun taɓa haɗuwa a china kowanne tashi ta kaishi.

Murmusawa Babangida yayi yace.

"To Shikenan ai Hajiya tunda zaki zame mata idanu ai babu damuwa sai a samar mata jari"

"Abinda za'ayi da daddare gobe muna gayyatarku dina a gidanmu dake wuse zone 2. Daga nan sai in nunnina mata dogayen rigunan shekaran jiya_jiyannan na dawo Dubai "

Babangida yace mata zasu je, haka ya kutsa da Yar shuwa cikin manyan mata ƴan kasuwa ya dinga nunata. Dake itama ba damane akaita musayar numbobin waya. A take ma wata matar Abokin kasuwancin Babangida ta sakata cikin wani group na manyan mata na kasuwanci da tattauna matsaloli.

Itama a Jigawa suke, a jirgi ma suka tawo wannan taron ita da mijinta, kuma a yau ɗin zasu yi komawarsu.

Ciye_ciye da lashe_lashe shi yazo a ƙarshe kafin magriba kowa ya watse.

Edit with WPS Office

MRS BUKHARI.

Ina manyan mata masu capacityn  suke?  ku fito lambarku ce ta fito.

Yar uwa turaren wuta kike nema nau'ika daban_daban masu musulmin ƙamshi da kama muhallu? Ba itacen banza masu sanya gida ƙauri da hayaki kamar an kunna taohuwar bespa ba.

Matso gasu MRS  BUKHARI B4B GIDAN KAMSHI nazo miki da duk abinda kike buƙata na ƙamshi. Kama daga turarukan wuta irin na gidan alfarma. Zuwa humrori iri daban daban masu musulmin ƙamshi da riƙe jiki.

Bugu da ƙari muna da turarukan kaya, na fesawa dana turara kaya.

Muna da kulaccam nau'i daban daban masu gyara jiki da lausasa  fata mata, ga kuma ƙamshi mai inganci.

Muna da turarukan tsugunno na musamman masu sirri Hajiyata

Muna da room freshener iri_iri

Muna da mopping mix masu kama waje.

Akwai turarukan kafet dana kujeru.

Sannan akwai box _ box  setika na Hajiyoyi masu ƙyallin goshi.

Muna da Amarya package.

Muna da uwargida package

Muna da maijego package

Muna bayar da sari ko a ƙasar waje kike, muna tura kaya

Saudiyya

Nijar

Ghana

Edit with WPS Office

Camaron

A duk ƙasar da kike kayanmu zai iso miki cikin aminci da yardar Allah.

Hajiya akwai Humrar matan aure wannan ta musamman ce.

Duk wani abu da kika sani na ƙamshi babu irin wanda bamu dashi a kamfaninmu.

Muna da turaruka designer na maza da mata wanda kamfaninmu ke bugawa Hajiya babu inda zaki je ki ci karo da mai irin ƙamshinki.

MRS BUKHARI B4B GIDAN KAMSHI TAZO MUKU DA DUK ABINDA KUKE SO NA KAMSHI HAJIYA.

KUNSAN KANURI MUNE KAMSHI DAMU AKE KOYI

SIYAN NAGARI MAIDA KUDI

MUNA MARABA DA MASU SIYAN ƊAYA KO SARI.

LAMBAR DA ZA'A SAMENI KAI TSAYE ITACE.

Wa.me/2348179523215

SAI NA JIKU

IDAN KAYA YA GAJI...

GAMMO MA YA GAJI

BADIAT IBRAHIM MRS BUKHARI B4B GIDAN KAMSHI

SHAFI NA ASHIRIN

Follow this link to join my WhatsApp group: https://chat.whatsapp.com/Hnb3Ee00TCQKqHgDwWfyx0 maman Muhammad kitchen Etims kayan mu available munasaida atanfa lace shadda mayafai takalmi da jaka akwai jewelrys

Edit with WPS Office

Munayin adashin gata nakayankici munaturakayanmu ko inakake cikin yardar Allah Ina wayanda basu da jari tum gada matasamu saki iyatallata kayanmu kema kisamunaki

Location dinmu Kano tudin Yola get 5 rukar Fulani gidan su baba sadiq 07044545303

SABUWA:.

Da safe bayan na sallami yara na gama duk kaye_kayen daya zamema duk wata mace jiki.

Wajajen takwas da rabi sai na jiyo sallama a bakin ƙofa. Kafin ma in bada dama sai ga Naja ta shigo afujajan

Tana zama a kujera ta saki kuka.

"Sabuwa ki mun rai. Asirin da kika bani ya karye mijina ya sakeni ma yanzu haka. Na bi duk bokayen garinnan amman sun kasa dawo mun da hankalin mijina."

Dariya nayi na ajjiye kaskon turaren wutan dake hannuna na zauna.

Dama an baki labarin ni ina rabon rai ne Naja? To wallahi bari in baki shawara ki saki bokaye da ƴan tsubbu ki rabu da rijalu shine kaɗai  mafita. Ni na dena harkar bokanci har abadan abidina. Kuma bazan je gaban wani boka da zummar ya bani magani ba dan in mallaki miji ba wallahi.

Naja tashi ki fice mun a gida. Maganar gaskiya kar in kuma ganinki a gidana"

Naja ta tsugunna zata roƙeni na kuma dakatar da'ita.

Haka ta fice a sanyaye. Nima ajjiyar zuchiya na sauke kawai na koma kitchen dan ganin ko abincina ya tsotse, ai kuwa ya tsotse harma ya soma kamawa.

Kula na ciro a sama na juye tare da zura kular a cikin leda na fito falo.

Wayata ce ta shiga ruri, maigogul ne yake kirana. Ban ɗaga ba har saida na ɗakko mayafina da jakata, na kulle barayina, ina tafe na kirashi.

Edit with WPS Office

"Lolo kin fito ne dan Allah?"

E yanzunnan fitowata kenan ina hanya.

"To to ai harma mun tattare mun koma gidanmu. Dama batun abinci zanyi miki duk gamu nan duru_duru babu wanda yaci abinci tsakanin ni da iyayen naki. Har gara su ƴaƴansu sun san musu sun lasa, ni kam babu wanda yake ta ni, ga ciwo"

Kai na girgiza kana nace.

Gani nan ƙarasowa na riga dana dafa abincin. Ammam mai ya faru har kuka koma haka da sassafe?"

Na'ila ƙawar Hamida na gani ta fito daga ɓarayin Hamida jaye da Usama a hannunta.

"Umman Aminu barka da safiya fita zaki yi ne da safe haka?"

Wayar na datse nace.

Wallahi kuwa haihuwa akayi mana shine naketa suntirin zuwa"

Daga haka ban sake cewa da'ita komai ba, ina gaba tana biye dani a baya har muka fice a gidan, tayi nasu gidan nibkuma na wuce titi na hau abin hawa zuwa gida.

A ƙofar gidanmu naga Maigogul tsaye da Abokinshi babban Amininshiwanda ya kasance ɗan Daudu kuma sana'arsu ta kawalci ɗaya shine ma ya riƙe hannun maigogul izuwa kawalci.

"Ahhh Sabuwa Lolo kece a tafe? Kaga ƴar albarka wacce aka haifa tsiya na baccinta magashiyan"

Bani da zaɓi haka dole na gaisheshi, ya amsa yana ɗaɗɗaga hannu gami da keɓe bakinshi irin na cikakkun ƴan Daudu.

"Ubanki ya faɗamun ke kikai mishi wannan ginin. Kai Sabuwa Lolo abun yayi kyau. Allah ya saka ma da wannan yaro Babangida Albarka. A haka kamar bazai arziki ba duba da irin badaƙalar data shiga tsakaninmu"

Maigogul yace.

"Ai  kai akwaika da tone_tone. In ana cin ɓaure kai dai ba'a tona cikinshi.

Ke Lolo abincinnan kar a sake a buɗeshi sai na shigo.

Ni inaga Chicib ni kam zan ma shiga gida"

Yace da abokin nashi.

"Ahh ni Chicib to ai Shikenan nima dama can ges house din Alhaji Wada zani su Sauma'iyya

Edit with WPS Office

acan suka kwana zanje karɓar balans"

Nan na yi shigewata ciki zuchiyata na tuƙuƙi ina mai takaici da baƙin cikin abokar maigogul da Chicib Allah ya sani. Shi kuma Maigogul Chicib bashi da tamka a wajenshi.

Ina shiga na tarar da gidan a hargitse anata aiki.

Gaza yana zaune a turmi yana bama karnukanshi hanta sunata kokawar ci.

Rakiya kuma fitowarta daga ɗaki kenan.

Hauwa na dokin ƙofarta tana yayyanka tuwo ga murhu a gefe da tukunya akai.

Uzairu  zuchiyata kuma wanki yake ta faman yi, kowa dai da abinda ya dameshi.

Rakiya na ganina ta yashe bakinta.

"Yauwa Lolo ai in muka ganki ƙoshi yazo. Maza tawo daga ciki dama yinwa duk ta addabeni"

Jin abinda Rakiya tace ne ya dawo da hankalin ƴan gidan zuwa kaina.

"Yauwa Lolo wallahi daman nima yinwa nake ji. Yan kuɗin nawa kenan na cire na siyama su Rahine hanta.

Rakiya a raba dani eh."

Yana magana yana ciccije bakinshi irinna ƴan daba.

Harara Rakiya ta sakar mishi harda tsaki.

Hauwa kuma tace.

"Hmmm nayi nadamar watsi da tarbiyyar da iyayena suka ɗaurani a kai da nayi. Da yanzu mutum na wani gida na karamci yana aurenshi ba irin wannan ƙaddararren gidan ba"

Shewa Rakiya ta saka harda buga cinya.

"Ta baya ta rago. Kwaɗayin abun duniyane ya kawo ki gidan. A tunaninki kuɗi gareshi shi yasa. Kinga wankan galila da tentalin

To ai ga gidannan dani dake muna kwasar gashi kuma wannan gashin har abada. Ni dake baƙin cikin Maigogul ne zaiyi ajalinmu muna nan tare Hauwa"

Hauwa bata tanka ba, tana bakin murhu tana saka tuwon data yayyanka a cikin miya zata ɗuma shi.

Nasan ganin idanun Gaza ne yasa ta kasa magana dan baya raga mata kona misƙala zarratin.

Ɗaki na shige abina, Rakiya ta biyo bayana.

Edit with WPS Office

Su Labbai sai ninke suturu suke yi ko wacce na jejjera nata a jakar bako. Da sib ɗin ba zata ishesu ba

Labbai kuma tana riƙe da wani koɗaɗɗen zanin les duk ƙuraje jikinshi ta gasa tagumi. Su kuwa su Aisha waƙa ma suka sake a rediyo.

Labbai lafiya wannan tagumi haka?"

Na tambayeta tare da neman gefen katifa na zauna a kusa da magazin dake zaune yana shan koko da ƙosai.

Ajjiyar zuchiya ta sauke naga tana ƙare mun kallo, sai da tayi ma'ishinta kafin tace.

"Lolo jibeki fes dake haskenki sai sake fitowa yake yi. Ni kuwa jibeni yadda duk na lalace ga ba suturar aziki ma da mutum zai sa yayi zawarci ko Allah zai sa a dace. Ni ina ganin wajen bokaye zanje su bani maganin farin jinin maza masu kuɗi. Tunda daga ke har Maigogul kun dena tsubbu.

Dariya dukkanmu muka tuntsure dashi harda magazin shi dan mugunta ma harda ƙwarewa.

"Ke kiji wannan shashashar wai maganin farin jini take nema. Mazan ma masu kuɗi. Wallahi ki ma kan ki Alam nashara ki aure Malam Habu ya fiye miki. Babu wani me kuɗi da zai shigo lungunnan ya wani aureki a irin wannan gidan. Ke yarinya bar ganin ke fara ce, ba zaki shiga ba. A gidanne matsalar kar ki zargi maza."

Sadiya  tace.

"Hmmm muma da kike ganin masu motar suna sauke mu. Harkace ta duniyanci da zaki ce ma wani ya fito kun rabu har abada. Mu ma mun gaji da wannan gantalin fatana in tsugunna a ɗakin miji in ci karena babu babbaka"

Hmm kuruci dangin hauka, kunji wai taci karenta babu babbaka.

A ina zata ga karen ma balle har taci babu babbakar?  Ina cikin wannan zancen zuchin na ji Labbai na cewa.

"Hmm yarinya mazan bariki kika sani ba mazan gida ba. Ina zaki ga karen ma balle kici babu babbaka?. Sanin kanki ne iskancin da muka yi, da kwanan club har ku mutu ba ku isa kunyi ba. Ruwane ya daki babban zakara kawai Sadiya. Ita dai A'isha na taya ta murna zuwa bayan Sallah za'a sha biki a karo na biyu. Abun daɗin ma ba garin bane dan da garinnanne da tuni ƴan hana ruwa gudu sun kai musu gulma. Batun zama da kishiyane kuma fa nan fa wani aikin ya ƙaru.  A wannan auren zaki ɗanɗana abinda masu kishiya suke ɗanɗanawa. Zaki bambance zare da abawa"

Da mamaki nace.

Sadakinta aka kawo ne babu labari?

Edit with WPS Office

Magazin yace.

"Jiya da daddare aka kawo. Shegiyar babu wanda ta faɗama  zuwan baƙin haka baƙinnan kawai ni ina tsakar gida ina Dan shan sigari sai sallama muka jiyo. Wallahi sai Labbai aka tura ta siyo musu shinkafa da miya a maƙota da soɓo"

Maigogul ne muka ji yayi magana a kanmu

Sabida hira ma bamu san ya shigo ba.

"Toh wato kun samu zuba sai yi kuke yi ko? Ke Labbai ɗebo kwanuka maza ga abinci ya samu a rarraba.

Kai kuma ka tashi ka fice"

"Ya ya ya  fice kuma haka akeyi ne suna hirarsu ta zumunci?"

Cewar Gaza da ya shigo yanzu ya nemi waje ya zauna daga dokin ƙofa.

Maigogul da kanshi ya rarraba abincin yace kowa ya ɗauka.

Ɗan kaɗan kaɗan ya zuzzuba ma kowa.

"Wannan ɗan abincin zaka zuba mun?"

Cewar Rakiya kenan da tayi tsaye a kanshi.

Robar ya warce ya ƙara mata ludayi ɗaya yau na lura baya jin faɗanne ma dai.

Muna cin abincinne Maigogul yake sanar dani batun sadakin Aisha da kuma lokacin da iyayen angon suke son ayi bikin. A aljihunshi ya saka hannu ya ciro mun wata kwalba da jan ruwa a ciki ya bani.

"Kinga wannan? Ki yaiyafa a ƙofar ɗakin Yar Shuwa in dai ta taka tabar gidan Babangida har abada. Ke aurenma ba lallai ta sake yinshi ba. Hannu na saka na karɓi kwalbar ina jujjuyawa na dai saka a jaka nayi mishi godiya.

"To sai kusan yadda zaku gagganɗa a soma karo _karo tun wuri harfa daku Garzali. Sabida sunce aurene kusan bakwai za'a haɗe ayisu a lokaci guda. Ni dai kunsan ban aje ba ban kuma ba kowa ajiya ba. Balle ma irin wannan abu na bagatatan fisabilillahi ina zan sa kaina. Ga raunuka linkib a jikina sana'ar tawa dole in tsayar zuwa in samu lafiya tukunna.

"Kadai faɗi wani abun ba wannan ba. Ko lafiyarka ƙalau me kake yi mana a gidan? Tsakanin ni da Hauwa sai dai fa ƴaƴanmu su harhaɗa mana kuɗi ko wacce tayi girki. Ko kuma ni in na siyar da kaya in ɗan cefano mana abinda zamu ci. Duk yaran dana aurar ko allura me ka taɓa sai musu?"

Maigogul yayi shiru tare da yin kasaƙe yana kallon Rakiya har ta gama maganarta.

Edit with WPS Office

"To hakane kuma. To sai kusan yadda zaku yi tunda ke ba daraja bane dake"

Tashi yayi ya fice da robar abincinshi a hannu.

Gaza yace.

"In dai wannan mutumin biye mishi za'ayi da tuni zuchiya ta ɗebi mutum ya shaƙeshi ya mutu uban kowa ya huta Allah nake faɗa muku.

Mu dai ɗan abinda muka samu zamu kawo a haɗu a rufa ma kai asiri"

Yana gama faɗin haka ya ajjiye robar abincin daya gama ci ya bar gidan

Magazin ma yana gama ci ya fice, Uzairu zuchiyata kuwa yana can gefe yana waya sai sassauke murya yake yi.

"Kunga kuwa da ace akwai kuɗi a ƙasa ma akwai kayan gado na wata Amarya haihuwa ɗaya auren ya mutu jiya jiyannan aka kirani naje naima kayan kuɗi ɗari biyu da hamsin harda labuleye da kafet da akwai kuɗin ai sai a siya a adana dan sunyi kyau. Dake yarinyar mai tattakice ba kwa ce kujerun ma sun shekara ba"

Aisha tayi carab tace.

"Dama zaki ɗan jinkirta zuwa yamma ai sai in fita ko bashi ne in ciyo in ɗan harhaɗa da kuɗaɗen hannuna mu biya ko a gidan Lolo ne a ajjiye mun"

Labbai tayi carab tace.

"Kuɗinnan kina dasu fa. Inaji jiya kina cewa dubu ɗarin ta shigo fa. Kema kinsan a gidannan kai kake ma kan ka komai kar kiji su Gaza sunce zasu kawo wani abun. Allah yasa ma in lokacin bikin yayi ki gansu "

Aisha tace.

"Hmmm ai na sani. Dubu ɗarinma a daren na turama Mabaruka na sai wasu kuloli da tukwane. Allah ya soni a hankali a hankali na gama siyan kayan kitchen ɗina tsab. In na sai kayan gadon shikenan sai jiran lokaci"

Nan akaita tattaunawa har Adama ta shigo.

Ni dai ana magana ina jujjuya kalmomin

Ace ɗiya mace bazawara bata aikin siɗi bare saɗa amman itace zatai ma kanta komai na aure hatta gara da abincin da za'aci a bikin. Wannan tarbiyya da mi tayi kama, kuna mamaki ko? Wallahi babu mamaki akwai ire_iren gidajenmu da yawa a faɗin Arewa dake iriyar wannan rayuwa har sama da hakan. Cikin layinmu ma bamu kaɗai bane akwaisu ratata.

"Nima Rakiya in an samu masu dama_dama ai mana magana. Jiya Amaryar ta dungule dubu

Edit with WPS Office

tamanin ta bani akan batun kayan katakon. Akwai dashi da jibi zan kwasa dubu talatince babu yawa sai a cika ya zama ɗari da goma. So samu mu samu gado da katifa, kujerar ko doguwa ɗayace, sai labule da ledar tsakar ɗaki. Kinga in aka samu haka shikenan asiri zai rufu ƴan ragowar kunji_kunji kuma Allah zai kawo mafita"

Rakiya tace.

"Babu damuwa ki kawo kuɗi sabida wani sa'in kayan a hannu a hannu ake samunsu. Duk abinda aka samu sai a siya a jefar.

Yanzu dai ku kama musu su ƙarashe gyaran wajen ni zan fita ganin wasu kujeru da aka tallata mun su."

Miƙewa tayi ta zari mayafinta ta fice a gidan.

Ni dai na kasa aikin komai sai aikin amai kawai da tashin zuchiya.

Su Adama ne sukai komai aka gyara ko'ina.

Hauwa itama sunata aikinsu da bataliyarta.

Duk futa amai ina ganin layuza a bakin murhu tana girkin abinci.

Da ɗaya da ɗaya zawarawan gidan ko wacce tayi kwalliya ta fice.

Wayata ce tayi ruri ina zaune muna tattauna batun biki da Adama.

Malama Babba ce ke kirana. Ko lafiya yaushe rabon da ta kira wayata. Duk sanda wayarta ta shigo wayata ma ba alkhairi zata faɗa ba.

Jikina a mace na ɗauka a mugun galabaice nake.

"Baki da labarin Hamida na kwance a asibity da yarinyarta ne? Azahar har ta wuce muna jiran abinci har yanzu ba'a kawo ba balle kuma ke kizo ki duba jikin yarinya. Akwai abinda yake damunki ne, ko kuwa shi Babangidan bai isa yasa ki dafo abinci ki kawo bane?"

Ni kasa magana ma nayi.

To me ma zance ni Sabuwa. Zancen ta baibai ma ni yazo mun.

A tsanake nace da'ita.

Ai bansan tana asibity ba. Kuma ni babu wanda ya kirani yace inyi girki, bani da Allahn musuru."

Ai ina wuta Malama ta saka ni a ciki.

"Au ni kike faɗama magana cewar baki da Allahn musuru? Lallai Sabuwa wuyanki ya isa yanka, amman zan maganinki. Yanzu zaki kawo mana abincinne ko kuma ba zaki kawo ba in tabbatar

Edit with WPS Office

da ƙwanƙwarewarki ɗiyar marasa tarbiyya masu yawon barbaɗa kwararo_kwararo"

Wasu siraran hawayene suka surnano a kumatuna. Wani ɗaci na turniƙeni. Wallahi ji nake yi kamar ince bazan girka abincin ba. Sai dai na tuno ko banza taci albarkacin Baba Malam dama jikokinta.

Zan dafo, amman bananan inna koma zan girko, wanne asibiti ne?"

Tsaki tayi tace.

"Muna babban asibiti. Ke kenan baki da aiki sai gantali"

Ina jiyo muryar Hamida tana cewa.

"Ai kusan kullum saifa ta fita. Gashi in zata je gida sai ta girka abinci him"

A hankali na zare wayar a kunnena na lumshe idanuna sababbin hawaye suka ci gaba da zubowa.

Dafani Adama tayi tace.

"Tashi maza ki tafi kije ki musu girkin ki kai. Da sharri suke nemanki a kansu zai ƙare. An riga an haɗu ko Malama taso ko bata so ba ƴar abu ta kazan..

Jeki in Rakiya ta dawo zan sanar mata kin tafi gida"

Jakata na zuge na bata kuɗin abincin dare nace tayi musu, na saka mayafina na tafi gida. A hanya na zuge jakata na ciro maganin da Maigogul ya bani a kwalba na cillar dashi.

Bana fatan Yar Shuwa ta bar gidan Babangida, na fi son ta zauna su rayu ta ƙunshi baƙin cikin da yafi wanda na ƙunsa.

Dana shiga gida ko zama ban ba. Ina girkinnan ina kwarara amai ƙamshin naman sai hautsinamun cikina yake. A haka yara suka shigo suka tadda ni, wanka suka yi suka ci abincin ranansu, kana suka wuce islamiyya basu dai da hutu. Bani na kammala girkin ba sai wajajen bayan la'asar. Tuwon shinkafa miyar Egusi nayi musu lafiyayye. A basket na jera komai na kulle ɗakina na fice.

Ban shiga asibitin ba sai ana kiran Sallar magriba.

Da tambaya na shiga ward ɗin yara. Ina shiga na hango Malama Babba, da Sa'a, sai Hamida, ga Baba Malam a tsaye shi da Ramadan ƙanin Babangida.

Assalamu alaikum. Sannunku"

Na faɗa a sanyaye.  Baba Malam da Ramadan ne kaɗai suka amsani. Ɗan risinawa nayi na gaishe da Baba Malam, ya ko amsa mun fuskarshi yalwace da fara'a.

Edit with WPS Office

Malama na gaisar ganin kaifin idon Baba Malam ne yasa ta amsa ni a dakile. Su Sa'a nima ganin idon Baba malam yasa nayi musu jam'in gaisuwa. Hamida ce ta amsa tana daga bakin gado. Mai jikin na tambaya.

"Jiki da sauƙi"

Hamida ta faɗa a taɓe.

"Sai yanzu kika ga damar kawo abincin dan tsabaragen mugunta. Abincin da ya kamata a kawo safe, rana, dare. Kin bar ƴar mutane da yinwa ko dan  bata da kowa a garin?"

Kur Baba Malam yabi Malama Babba da idanu baice komai ba, itama taƙi kallonshi fur.

Kai kawai ya girgiza ya dubi agogon hannunshi.

"Ramadan wuce muje mu yi Sallah daga nan mu wuce gida. Ke Sabuwa ki bar kawo abincin, zan sa ƙannenku su dinga kawo abincin daga gida. Ko Ramadan zai kawo tunda yana da lifan."

To Shikenan  Baba Malam nagode"

"Amman Malam..."

Cewar Malama Babba.

Hannu ya ɗaga mata halamar tayi mai shiru baya son jin maganarta. Dole ta tsuke bakinta tayi shiru.

Baba Malam na ficewa a ɗakin nace.

Allah ya ƙara sauƙi ni zan wuce yara yanzu nasan sun dawo gida babu kowa"

Wucewata nayi, ina jiyo Malama tana faɗan magangu marasa daɗi akan iyayena.

Ni dai ko oho haka na fice ina jin daɗin sauwaƙe mun da  Baba Malam yayi.

Sai bayan isha na shiga gidan na tad da yara a falo suna Sallah. Malama kuma tana zaune tana cin tuwo.

Wash Allah na. Malama ke kinyi Sallah ne kike cin tuwo?"

Na tambayeta. Kafin ta bani amsa amai ya tunkudo mun sakamakon nama da take taunawa. A mugun guje na yi ɗakina, na dinga sharara amai, sai da na gama na ɗauro alwala nayi magriba nayi isha.

Ina zaune yaran suka shigo dukkansu.

"Ummi baki da lafiya ne?"

Mardiyya ta tambaya tana taɓa wuyana da yayi kau.

Edit with WPS Office

Bani da lafiya Mardiyya."

Nan suka shiga yi mun sannu dai. Tea na umarci Mardiyya ta dafo mun.

Kai kuma Aminu ɗakko mun ledar magungunana maza"

Da sauri shi da Aɗɗa'u suka tashi, sai kuma suka shiga riƙe juna wannan yana cewa shi zai ɗauko, wannan yana cewa ya riga ɗan uwan nashi.

Sai nake tuno sanda muke yara kamarsu bamu da aiki sai dambacewa.

Da gudu Malama ta kawo mun ledar maganin ta raba gardama.

Dariya muka saka dukanmu har dasu masu faɗan.

Kun dai ji kunya. Malama gashi to ta raba gardama ai sai ku zauna a bani labarin me ya faru a makaranta."

Mardiyya ta shigo da ƙaton kofi shaƙe da tea ta ajjiye mun. Ina sha sunata bani labarai ina saurarensu, sai nake jin zuchiyata tana yi mun wasai duk wannan hirar da suke yi mun Mardiyya da malama suna kan gadona, su kuma su Aminu suna ƙasan kafet.

Mun ɗau lokaci mai tsayi muna hira kafin nace su je su kwanta su huta gobe asabar babu makaranta wanki zamu yi kafin su tafi Islamiyya.

BABANGIDA:.

A gajiye suka ƙarasa hotel ɗinsu Yar Shuwa sai hira take janshi dashi tana shan cikinshi. Shi kuma namiji sai ɓarin zance yake ta yi mata.

A wannan daren ma Yar Shuwa ta faranta ran Babangida sosai a shinfiɗa.

Washegari kuma bayan sun karya ya ɗan fita da'ita yawo da shopping.

Tana zaune tana dudduba wasu manyan lace da wata Hajiya ta turo a group ɗin kasuwanci da aka sakata.

Ta lalace tana ta bin chart ɗin group ɗin dake ba iyakar kasuwanci ake yi a group ɗin ba. Asalima tallah ne asabar da lahadi sauran ranakun na hira ne kawai.

Babangida shi kuma yana waya da Hamida yana tambayar yadda suka kwana.

"Kasan sai bayan isha Sabuwa ta kawo mana abinci? Hmmm"

Edit with WPS Office

Idanu ya firfito waje.

"Mene sai bayan isha fa kika ce. To me take yi haka da yaushe to ta kawo na safe da rana kuma?"

Hamida cikin dariyar mugunta tace.

"Ai sau ɗaya jal ta kawo abincin shine na bayan isha. Shima sai da malama ta kirata a waya kafin ta kawo. Ta nemi ma ta faɗa ma Malama magana maras daɗi ma"

"Zata aikata in dai Sabuwa ce. A gidansu ai babu babba babu yaro kowa ɗan iskan kanshi ne. Amman zan yi maganinta dan zan kirata yanzu"

Jin an ambaci Sabuwa ne yasa Yar Shuwa ta ɗago da sauri ta zuba ma Babangida idanu, ta baza kunnuwanta kuma"

Sanya kuɗin karatun a cikin wannan lambar asusun

0044442984

Buhari Ibrahim Ladan Gt bank

Lambar da zaku turo shaidar biya gasu kamar haka

08022059556

Ko kuma

08105932041

Masu son magana da marubuciyar kai tsaye kuma ga lambata

Wa.me/2348179523215

MRS BUKHARI

Edit with WPS Office

IDAN KAYA YA GAJI

GAMMO MA YA GAJI

BADIAT IBRAHIM MRS BUKHARI B4B GIDAN KAMSHI

SHAFI NA ASHIRIN DA ƊAYA

Follow this link to join my WhatsApp group: https://chat.whatsapp.com/Hnb3Ee00TCQKqHgDwWfyx0 maman Muhammad kitchen Etims kayan mu available munasaida atanfa lace shadda mayafai takalmi da jaka akwai jewelrys

Munayin adashin gata nakayankici munaturakayanmu ko inakake cikin yardar Allah Ina wayanda basu da jari tum gada matasamu saki iyatallata kayanmu kema kisamunaki

Location dinmu Kano tudin Yola get 5 rukar Fulani gidan su baba sadiq 07044545303

BABANGIDA

"To ai baka ma sani ba sanda ta kawo abincin tazo ta samu Baba Malam da Ramadan. Baba Malam yace ba sai ta ƙara kawo abinci ba zai sa a dinga kawo mana. Ba tai mana ko ya jikin yarinya ba tayi ficewarta bako sallama da taga wanda take ganin girman nashi ya fita"

Hamida tana faɗar maganar cike da zuzutawa.

"Tabb wallahi bata isaba sai ta kawo Allah. Ubanta naga da yaje club akai musu duka saida tayi girki ta kai. Haka siddan ma in zata gida sai tayi girki take tafiya, ace ɗiyata babu lafiya Sabuwa ta kasa kai abinci?

Gobe jirgin safe ma zamu biyo mu dawo. Shi Usama dai yana wajenta ko"?

Hamida fa an samu nayi, nanma wata sabuwar ƙaryar ta kuma zuƙalowa.

"Ina fa ta ɗaukeshi. Sai Na'ila ƙawata daga maƙota da dai taji kukan yayi yawa shine ta shiga gidan namu. Yaronnan a wannan sanyin yana tsakar gida yanata kuka babu ko wando Sabuwa tayi mishi kunnen uwar shegu. Tuni na daɗe da sanin bata ƙaunata ai. Lokacin da zaka auro

Edit with WPS Office

amaryarka wanne irin ziganine batai ba akan sai dai mu yi maka bore ni kuma naƙi"

Hamida dai saida ta kunna Babangida ya hau yai suntum ya saki layi ya dinga zage_zage. Wayar ya kashe a zafafe ya lalubo wayar sabuwa amman ya jita a kashe.

"Jannaty kar damuwar Sabuwa ta dameka kaga tuƙi kake yi. In ita bata buƙatarka a raye mu muna buƙatarka. Ashe dama haka itama take baka ciwon kai kamar yadda sauran yayyenta suke ba mazajensu ciwon kai?"

Idanu ya lumshe yana kallon titi rai a jagule yace.

"Ai zata gane ta taɓo gidan rina bari mu koma gobe sai mun kwashi ƴan kallo ni da'ita.

Murmushi Yar Shuwa tayi tace.

"Wai me yasa ba zaka sauwaƙe mata ka huta ba? Duk da ko kun rabu Sabuwa ta gama cutarka tunda ta gurɓata muku zuriya"

"Ke dai ki bari. Wannan dalilin yasa kowa ya tsani Sabuwa a haularmu fa. Dalilin da yasa ban saketa ba inaga ke kinfi kowa sanin dalilin Habibaty, kinsan ma ƙaddarar data haɗemu muka zama ma'aurata ai"

Numfashi taja tana jin tsanar Sabuwa sabo a zuchiyarta.

"Amman bayan an yi auren da duk irin yadda kake ƙinta bai hanaku haifar ƴaƴa ba har huɗu. Yanzu haka ma zan iya ganinta da wani cikin ma. Halinku dai na daɗin bakin rijalu babu irin wanda ban sani ba"

Murmusawa yayi kawai.

A wani ƙaton kanti suka tsaya yai mata shopping har tsaraba tayi ma mahaifiyarta dama Malama Babba da ƙaramar duka, Malam ma ta sai mai turare.

Zuwa bayan isha suka kammala shirinsu tsab kai tsaye Babangida yabi adireshin Alhaji Mujahid tiryan_tiryan sai gasu a katafaren gidansu mai gadi ya wangale ƙofar gidan.

A hankali motarsu ta kutsa zuwa cikin gidan, lallai gaba da gabanta duk yadda Babangida yake jin ya ƙera gida sai daya shigo wannan gidan ya raina nashin. Harma a ranshi yake jin kamar ya ɗan sake canjama nashi gidan fasali, koma yayi ƙoƙarin ɗaura saman kawai tunda dakin ne a saman in yaso sai yayi tsari me kyau.

"Alhaji  Babangida bismillah mu ƙarasa daga ciki"

Cewar Alhaji Mujahid daya fito tarbarsu har zuwa wajen ajjiye motoci.

Fitowa sukayi aka ɗunguma zuwa ciki.

Lallai dukiya akwai daɗi masu kuɗi sun iya ƙawata gidajensu ainun. Wani sanyin ac da ƙamshin

Edit with WPS Office

turaren wutan Mrs Bukhari ne ya doke musu hancinsu.

Hajiya Tana daga zaune a hakimce ta cika 1 sitter dake akwaita da ƙiba. Kamar ( Mrs Bash. Mazaunanta kuma kamar na Khadija maidoki)

"A_a Hajiya Shuwa kun ƙaraso maraba lale. Bismillah ga waje"

Ta nuna musu manyan kujerun suka zazzauna, nan aka kwashe mintuna biyu ana gaggaisawa.

"Kaga mata dai sun fimu zumunci jibi muna yawan haɗuwa dakai a duk samina ammman bamu taɓa tunanin ziyartar junanmu ba sai da mata suka yi wannan tunanin"

Babangida yayi dariya tare da cewa.

"Wallahi kuwa. Mu dake kai ya cika da lissafe_lissafen kasuwanci da abokan cinikaiya yaushe mutum ma zaiyi tunanin daya dace"

Hajiya tace.

"Kun dai ji kunya. Nima fa ba mazauniya bace kawai dai zumuncin muka fiku. Alhaji Babangida kamfanin me kake dashine?"

Ta tambayi Babangida sai wani sauke kai yake yi kamar wani kamilin gaske.

"Kamfanin Baban bola nake dashi, ina siyan robibi in niƙesu, sannan ina siyan ƙarafai. Ina harka da ƴan China kasuwar tamu kenan"

Kai ta girgiza tace.

"Ayya Alhaji kuma kamfanin yadi gareshi na maza, sai kuma kamfanin shinkafa. Ni kuma ina harkar kasuwanci daga najeriya zuwa Dubai. Sannan ina kawo motoci daga kwatano, ko legas."

Nan dai aka tattaɓa hira daga bisani aka buɗe liyafar cin abinci. Alkubus da miyar kabewa da nama haka_haka aka tarbesu, sai lafiyayyen kunun aya da yaji madara. Sai kuma soyayyun talo_talo da aka tsomasu cikin jajjagen attaruhu da akbasa.

Sun ci sun sha anata hira. Hajiya ce ta gayyaci Yar Shuwa zuwa ɗakin baccinta.

Ajjiyar zuchiya kawai Yar Shuwa ta sauke da suka shiga ɗakinnan ba'a magana.

Wata durowar bango mai bango guda Hajiya ta buɗe ta dinga ɗebo kaya tana jibgewa a gaban Yar Shuwa.

Sai da ta ɗebo ma'ishinta sannan ta soma warewa harda takalma da jakunkuna na manyan matan Abuja, da sarƙoƙi da ɗankunnaye.

"Kinga dai kaya gasunan. Kuma Allah ya dafa mini a gida nake duk wannan kasuwancin Alhaji yaki yarda da shago. Sai dai duk abinda na kasa saina siyar dan ba ƙaramin kuɗi nake ba

Edit with WPS Office

malamai suna jawo mun ciniki ba. In kina sha'awar kiyi kuɗin kan ki ki taimaki rayuwarki data ƴan uwanki, kiyi ma kishiyoyi zarra dama danginku baki ɗaya zan taimakeki"

Ajjiyar zuchiya Yar Shuwa ta sauke. Yanzu ne take ganin tabbatuwar mafarkinta dama cikar burinta na san auren mashahuri, koma ace itace mashahuriyar. Ashe Babangida shine tsanin da zata taka tayi arziki shine ta zuba ido take kallonshi tsawon shekaru.

"Hajiya inaso. Nima ina da nawa Malaman ni shuwa ce daga Maiduguri nake kinsan muma ba'a barmu a baya ba. Sai dai ban wani jima da yin auren ba shi yasa ban shiga malamai ka'in da na'in ba ina son in kafu tukunna."

Dariya Hajiya tayi ta zauna tana ɗaga mata wata riga.

"Ai daidai kenan Amarya mai maganar siga. Yanzu ne zaki fito da salo_salo na maɗe ki haɗa da asirin ki yagi abinda zaki yaga kizo a nuna miki duniya. Bari ina zuwa naga kina da sanya"

Miƙewa tayi ta shige wani ɗaki dake cikin ɗakin baccin. Sai gata da wata kwalba, wani ɗan leda baƙi."

"Wai kinga wannan kwalbar? Maganin mata ne a ciki. In kika shanyeta kamar bayan magriba. Kika zizara wannan kwallin, ku kai mu'amular aure. A wannan daren ko nawa kike buƙata mijinki sai ya baki ko a buzu yake kwana wallahi "

Ƴar Shuwa tace.

"Asiri bai fiye tasiri tattare dashi ba. Akwai mugun tsari a jikinshi. Kafin in aureshi babu irin abinda ba'a birne ba wallahi kinga a banza. Kishiyata wacce take uwargida a gidan bokace fa, mahaifinta ma bokanne wallahi haka suka buga suka barshi"

Dariya tayi sosai tace.

"Ke Hajiya Shuwa wannan daga wata uwa duniya aka kawoshi fa. Ba irin naku bane Shuwa da kuke haɗawa da ayoyin Allah ba. Wannan tsubbu ne ba bokanci, ko malinta ba.

Zan goga miki kwallin a jikin abun sakace, duk ranar da kika shirya sai ki zizara. Maganin kuma zan raba biyu in baki rabi. Wallahi ko kuɗinshi na lukudi ne sai ya ciro ya baki iya adadin da kika tambayeshi. Sai ki dage ki yanka da kauri, domin wannan maganin ba zaki taɓa iya cire kuɗi nan kusa ki siya ba. Miliyoyin kuɗi na cire na siya  Kuma shi baya daɗewa a jiki rana ɗaya ne. Taimakon da zan miki kenan, ina ganinki naga hankalina ya kwanta dake ki dai yaga da yawa damarki ce wannan. Ke kuwa yaya kike wanyewa da kishiya bokanya ni ƴasu?"

Dariya suka saka dukkansu.

"Ada na tsorata ainun. Amman da naje wajen malamin Babarmu ya tabbatarmun akwai haske a Auren, akwai abubbuwa masu kyau, duk da yace akwai wata guguwar daka iya tashi. To ita Sabuwa na riga na gama da'ita surrukanta a tafin hannuna yake. Wannan guguwarce nake

Edit with WPS Office

neman yadda za'ayi kada ta taso."

Sun daɗe suna tattauna al'amura da hirarraki ko wacce ta saki jikinta sukaita fallasa asirin cikinsu.

Daga bisani Alhaji Mujahid ya leƙo yayi kiran Hajiya akan Babangida yace iyalinshi ta fito zasu wuce.

Hajiya ta ba Yar Shuwa wannan magani da kwallin a jikin abun sakace, ta haɗa mata da doguwar riga mai tsada sosai. Sannan ta nuna mata wani jaka da takalminshi mai tsada sosai, da mayafi sabon fitowa na matan Abuja.

"Wannan muje sai ya siya miki ko akan buzu yake.ki ƙara doguwar rigar ke bafa a sanya tunda har ya zaɓe kuka tawo semina Muje kiga yadda akeyi"

Ai kuwa Hajiya Turai da kanta taima Babangida bayanin ya kamata a siyama amarya wannan kaya sabida cancanta. Babu musu gudun zubewar mutunci haka ya cire dubu ɗari da hamsin a wannan lokacin ya tura ta lambar asusun bankin Hajiya, take gumi ya shiga tsattsafo mishi.

Har sai da motarsu ta fice a gidan kafin suka koma gida.

Yar Shuwa dai tunda suka shiga motarnan sai jikinta yayi sanyi tayi shiru tanata lissafe_lissafen yaushe ya dace ta zirara wannan kwallin?

Ajjiyar zuchiya ta sauke data tuno kamata yayi ta bari suje Umara su dawo, gudun kar azo a fasa zuwa umarar baki ɗaya. Ita burinta shine tai ta cusama Sabuwa baƙin ciki da takaici na har abada.

"Yaya akayi ne Habibaty. Har muka iso hotel baki ce komai ba sai ajjiyar zuchiya dai kike saukewa. Bani labarin me kuka tattauna to"

Dariya tayi kawai tace.

"Hirar kasuwanci ne dai mu kai tayi. Sai naji na kwaɗaitu sosai da in soma kasuwancin. Dan da turaren wuta naso in soma yi, tunda a gidanmu ma shi ake saidawa. Amman yanzu ko da zanyi sai dai ya biyo kasuwancin dogayen rigunannan. Ai zaka bani jarin ko?"

Dariya yayi mata yana kallon tsakiyar idanunta.

"In aka nitsa zuwa shekara biyu sai a baki ai Habibaty.  Kinsan kasuwanci irin na fita wata ƙasar kasuwancine da so samu mutum ya zuba kuɗi masu yawa ya siyo kaya shine ribarshi.

Amman ni ina ganin ki bari zuwa shekara ɗaya gaba in kuɗaɗen suka samu ko a hannunta ne sai ki soma sara kafin ki soma binta kinsan komai a hankali ne ake somawa'

Kai ta kaɗa a ranta tace.

Edit with WPS Office

"Zaka gane kurenka zanyi maganinka sosai, ai wallahi ko da in ka ban kuɗinnan zaka zama talaka saina tambaya kuma sai ka bani.

A zahiri kuma tace.

"Ai hakanma zaifi ina ni ina fita wata ƙasar ma in tafi in barka wai da wa Jannaty. Bayan nasan a wajena kake samun farin ciki"

Murmusawa kawai yayi baice uffan ba.

Fitowa sukai daga cikin motar zuwa ɗakinsu na hotel.

A wannan daren Babangida zagewa yayi sosai ya faranta ma kanshi, itama ƴar shuwan ta bashi haɗin kai sosai da sosai dalilin daya saka lamarin yayi armashi kenan.

Washegari sassafe suka hau hanyar komawa Dutse kuma"

BABA MALAM:.

Bayan dawowarshi daga asibity, kai tsaye cikin gidan ya shige Ramadan kuma ya wuce makaranta wajen ɗalibai

A tsakar gida ya tarar da Malama ƙarama a zaune a tabarma cikin barandar ƙofar ɗakinta, tana cin tubani ita da Mashi

"Sannu da dawowa Malam "

Cewar Mashi daya ɗago ya ƙurama mahaifin nasu idanu dan ya fahimci ranshi a ɓace yake sosai.

"Yauwa Mashi Me kake yi anan, ga ɗalibai can suna jiranka a makaranta, sannan ina matarka da zaka zo kana ci mun abincin gida?"

Karasowa yayi ya zauna a gefe.

"Sannu Malam yaya mai jikin ka samesu?"

Kai ya ɗaga sama halamar tunani da tsantsar damuwa. Daman tasan za'ayi haka tunda dai lamarin daya shafi iyalin Babangida yaje. Amman ta lura damuwar a wannan karon tayi yawa, to ko Babangidan ya kuma yin wani abunne"

Da sauri Mashi  ya wanke hannunshi ya fice da ɗan gudu.

Edit with WPS Office

Malama ƙarama kuma ta dure ma malam gidauniyar abincinshi, ta zuba mishi.

"Malam kayi haƙuri ka cire wannan damuwar a ranka. Na roƙeka ka samama kanka lafiya. Haba Malam sai kace ba kaine kake jaddada mana yadda da ƙaddara ba komai muninta ba? Babangidan ya sake yin wani abunne, inace inaji su Sa'a suna faɗin bayanan yayi tafiya?"

Kanshi ya sauke idanunshi sun yi jawur hawaye tab.

"Karama kenan. Ke dai ayi sha'ani kurum. Ai wannan lamarin abadan bazai gogu a zuchiyata ba. Kar kiyi mamaki ma ya zama ajalina, dan cin rayuwata yake yi babu dare babu rana"

Shiru tayi tana jujjuya maganganun Malam. Tabbas wani sa'in ko taga laifin Malam. In ta tuno da faruwar komai da yadda abin ya faru ya wanzu, sai taga yayi namijin ƙoƙari a hakanma.

Amman ba zata gaji da bashi kalma ba.

"Ayi haƙuri dai Malam  ka sake akan wanda kake yi. Haƙiƙa Babangida yayi ma haular gidannan baƙin fentin da jikoki da rattaba kunne ma sai labarin ya iskesu. Ace yana ɗan malamai ciki da waje a sameshi da irin waɗannan dabi'un"

"Ai ƙarama kab haulata babu irin Babangida ni na ɗaukeshi a matsayin jarabawa daga Allah. Silar mutuwata da baƙin ciki. Mahaifiyarshi wannan bana son gani. Sabida ta haɗe kanta da yaronta suna cusgunama baiwar Allah. Alhalin a cikin wannan lamari ni banga ta ina Sabuwa take da laifi ba. Ko dan shi lefe tudune hawa naka kakeyi ka dinga hangen na wasu ko? Hmmmm Allah ya bamu lafiya akwai ranar kuka, ranar kasa runtsawa, ranar dana sani marar amfani, ranar da ɗan Adam zaiji dama duniyar zata iya dawowa baya da bazai kwata abinda ya aikata a baya ba ko kusa."

Malama ƙarama dai taita tausar Malam. Malam na cikin cin abinci suna taɓa hirarsu a nutse Malama Babba ta shigo. Ganin Malam na hira harda murmushi yasa tayi turus.

A lissafinta Malam yafi shekara goma sha wani abu bai taɓa buɗe haƙoranshi da sunan yi mata dariya ba, ko ya zaunar da'ita yana cin abinci tana yi mishi hira ba. "Yanzu shikenan Karama taci nasarar kwace mun Malam kenan, ina da rai na zama marar amfani a rayuwar Malam? Malam ɗin da shine ya ɓareni a kwali mu ka gudanar da rayuwar soyayyar da danginshi haɗe da nawa dangin suke alfahari da irin bayyananniyar soyayya da kulawar da Malam ke nuna mun har a gaban mahaifana."

Duk wannan maganganun a zuchiya Malama take fesar dasu. Tuno ranar data haifo Babangida take yi a asibity dan haihuwarshi ba ƙaramin zuwa da tangarɗa tayi ba dan harma an cire rai da Malama.

Ta tuno lokacin da Babangida yake rungume a jikin Malam yana mishi huɗuba.

"Rayuwata wai kinsan menene?"

Edit with WPS Office

Cewar Malam dake shafa kyakkyawar fuskar jaririn dake hannunshi.

"Sai ka faɗa. Naga tunda ka ɗauki yaronnan kake farin ciki gashi ba ɗanka na fari ba,kuma ba shi ne ɗanka namiji na farko ba. Amman a haihuwata ta fari ma banga annuri irin haka a fuskarka ba"

Murmusawa yayi tare da ƙarema Malama kallo"

"Wato rayuwata abinda kika faɗa hakanne. Wannan yaron ya kasance na daban a zuchiyata gaskiya ya kasance na musamman. Da dukkan halama shine zai gaji sunan Baba, kinga ya zama mahaifinki mahaifina kuma sai mu rinƙa kiranshi Babangida ko me kika ce?" Ya tambayeta yana sake mata lallausan murmushi.

"Kin dawo Babba ya mai jikin?"

Malama ƙarama ta katse mata tunaninta.

"Nadawo ƙarama. Jikin kuma da sauƙi"

Tana faɗin haka ta sa kai ta wuce ɗakinta ko gani sosai bata yi.

Akan doguwar kujera ta tarar da Autanta yana waya da wacce zai aura.

"Kinga ga Malaman ma yanzu shigowarta zan kiraki zuwa anjima in sha Allah"

Ya faɗa tare da kashe wayar. Sai kuma yabi Malama Babba da kallo wacce ta zauna jiɓur a kujera tana mayar da nunfashinta.

"Malama jikin jinjirarne yayi tsanani ne?"

Ya tambaya murya a raunane.

Malama dake ta taɗin zuchi, da zafin zuchiya tace.

"Jikinta da sauƙi Umar. Me kake yi baka shiga makarantа ba? Malam fa yana cikin gidannan kasan zai iya ɓatarma"

A gurguje Umar ya fice. Malama kuma ta shiga aikin tunano rayuwarta da mijinta a shekarun baya da suka wuce.

A wannan daren da Malama da Baba Malam da ƙyar suka runtsa ko wanne cikinsu aikin tunano baya yake yi sai dai tunanikansu sun sha bam_bam dana juna

Da wannan garinsu ya waye aka ci gaba da harkokin yau da kullum.

MRS BUKHARI

Edit with WPS Office

Sanya kuɗin karatun a cikin wannan lambar asusun

0044442984

Buhari Ibrahim Ladan Gt bank

Lambar da zaku turo shaidar biya gasu kamar haka

08022059556

Ko kuma

08105932041

Masu son magana da marubuciyar kai tsaye kuma ga lambata

Wa.me/2348179523215

Ina manyan mata masu capacityn  suke?  ku fito lambarku ce ta fito.

Yar uwa turaren wuta kike nema nau'ika daban_daban masu musulmin ƙamshi da kama muhallu? Ba itacen banza masu sanya gida ƙauri da hayaki kamar an kunna taohuwar bespa ba.

Matso gasu MRS  BUKHARI B4B GIDAN KAMSHI nazo miki da duk abinda kike buƙata na ƙamshi. Kama daga turarukan wuta irin na gidan alfarma. Zuwa humrori iri daban daban masu musulmin ƙamshi da riƙe jiki.

Bugu da ƙari muna da turarukan kaya, na fesawa dana turara kaya.

Muna da kulaccam nau'i daban daban masu gyara jiki da lausasa  fata mata, ga kuma ƙamshi mai inganci.

Muna da turarukan tsugunno na musamman masu sirri Hajiyata

Muna da room freshener iri_iri

Muna da mopping mix masu kama waje.

Edit with WPS Office

Akwai turarukan kafet dana kujeru.

Sannan akwai box _ box  setika na Hajiyoyi masu ƙyallin goshi.

Muna da Amarya package.

Muna da uwargida package

Muna da maijego package

Muna bayar da sari ko a ƙasar waje kike, muna tura kaya

Saudiyya

Nijar

Ghana

Camaron

A duk ƙasar da kike kayanmu zai iso miki cikin aminci da yardar Allah.

Hajiya akwai Humrar matan aure wannan ta musamman ce.

Duk wani abu da kika sani na ƙamshi babu irin wanda bamu dashi a kamfaninmu.

Muna da turaruka designer na maza da mata wanda kamfaninmu ke bugawa Hajiya babu inda zaki je ki ci karo da mai irin ƙamshinki.

MRS BUKHARI B4B GIDAN KAMSHI TAZO MUKU DA DUK ABINDA KUKE SO NA KAMSHI HAJIYA.

KUNSAN KANURI MUNE KAMSHI DAMU AKE KOYI

SIYAN NAGARI MAIDA KUDI

MUNA MARABA DA MASU SIYAN ƊAYA KO SARI.

LAMBAR DA ZA'A SAMENI KAI TSAYE ITACE.

Wa.me/2348179523215

SAI NA JIKU

IDAN KAYA YA GAJI...

Edit with WPS Office

GAMMO MA YA GAJI

BADIAT IBRAHIM MRS BUKHARI B4B GIDAN KAMSHI

SHAFI NA ASHIRIN DA BIYU

Sanya kuɗin karatun a cikin wannan lambar asusun

0044442984

Buhari Ibrahim Ladan Gt bank

Lambar da zaku turo shaidar biya gasu kamar haka

08022059556

Ko kuma

08105932041

Masu son magana da marubuciyar kai tsaye kuma ga lambata

Wa.me/2348179523215

Bincike ya nuna sama da mutune miliyon goma sha biyar ke shan muyagun ƙwayoyi a najeriya.

Hakan kuma ya jawo asarar rayuka, taɓarɓarewar tarbiyya. Ya habbaka fitinu da manyan lefuka a arewacin najeriya dama ƙasar baki ɗaya.

Tun kafin zama ya gagaremu mu koma bacci da ido ɗaya a buɗe. Lokaci yayi da zamu haɗa ƙarfi da ƙarfe domin mu taimaka ma hukumar yaki da sha da fataucin miyagun ƙwayoyi.

Dan ganin mun kawar da wannan ta'asa dake shirin zame mana ruwan dare.

Shaye_shaye annobace ga al'umma.

Edit with WPS Office

Wannan saƙone daga hukumar yaki da sha da fataucin miyagun ƙwayoyi wato ( NDLIA)

SABUWA:.

Washegari kamar Yadda nace da wanki muka tashi, muna kammala karyawa muka firfito da wanki tsakar gida kusa da famfom tsakar gida da rijiya.

Ni ina saɓi na farko Mardiyya na yin saɓi na biyu, Aminu na yin ɗauraya yana tarawa a bawo babba. Aɗɗa'u da Malama kuma sai wasan guje_gujensu suke yi a tsakar gidan.

Sallamar maƙociyarmu mai ɗinki muka jiyo da fara'a na tarbeta ta nemi waje ta zauna akan tabarma.

"Yau kuma maman Mardiyya da wanki kuka tashi ne?"

Da dariya nace.

Ai kuwa wankinne ya taru sosai yau dai muka dirar mishi. Kinsan kuwa kamar kinsan inason in zo in kawo miki ɗinkinmu na sallah ni da yara yau ɗinnan?"

Dariya tayi tace.

"Wato dai ƙawance dani dai ba'aso sai dai a kawo mun ɗinki kawai."

Hannuna na ɗauraye a famfo ina dariya nace tazo mu shiga daga ciki.

Falo na kaita na kawo mata tea da biredi da wainar ƙwai. Tana ci muna ɗan hira.

"Nifa wata muhimmiyar magana ce ta kawo ni wajenki. Da fatan ba zaki mun wata fassara mummuna ba. Na kawo miki maganar ne domin kisan matakin da zaki ɗauka ko kuma kisan irin takunki"

Gabanane ya yanke ya faɗi, da sauri na kalleta nace.

Kar ki damu ina saurarenki"

Edit with WPS Office

Muskutawa tayi, tare da shanye ragowar shayinta sai da ta ajjiye kofin shayin kafin tace.

"Me yasa kika ƙi karbar Usama Maman Mardiyya, naga Usama yarone kuma yaron mijinki ne, ko da akwai rashin jituwa a tsakanin ki da uwarshi ai da kin daure kin riƙeshi. Baki ji yadda ake gulma a maƙota ba kinsan Na'ila da shegen bin maƙota sai barbaɗa zancan take yi. Sannan ance ki dinga girki kina kaiwa asibity kin ƙi kaiwa. Sannan tace duk sanda zaki je gidanku sai kin yi girki. Wallahi wasu maganganun ma ba zasu faɗu ba irin aibantaki ke da danginki da take yi bana wasa bane. Bama wannan ba wajen bokaye ma suke zuwa akan a fidda ki daga gidanki. Sannan tana shirin ƙulla miki sharri a wajen mijinku akan ƙin karɓar Usama da kika yi. Maman Mardiyya dan Allah ki kiyaye ko da wani abun ci ko sha Hamida zata kawo miki kar ki sha."

Maman  Safara'u ta dinga bani labaran da na gamsu na tabbatar daga bakin Hamida suka fito. Hatta auren Yar Shuwa na cin Amanata da tayi sai da Hamida ta kai labarin.

Ajjiyar zuchiya na sauke tare da lumshe idanuna.

Shikenan Hamida ta gama watsar mun da mutunci a unguwa. Matan layi zasu dinga kallona a matsayin mutuniyar banza ni da iyayena.

A zahiri nace.

Kinsan Allah Hamida bata kirani tace ga yaro ba, bansan an kwantar da yarinya a asibity ba. Haɗuwa nayi da Na'ila jaye da hannun yaro fa kawai. Ina gidanmu surukarmu ta kirani take sanarmun ance in kawo abinci ban kuma kawo ba. Babu wanda ya faɗa mun. Haka na dawo na girka na kai. Uban mijinmu yace basai na sake kawo abinci ba daga can Family house zai sa a dinga kaiwa.

Menene laifina a ciki? Hatta wanda nake zamanshi bai sanar dani komai ba, sabida dai na zama bolar da kowa zai zuba shararshi akwai.

Batun wanu asiri da bin bokaye. Wallahi maman Safara'u batta taje bata isa ta yi mun abinda Allah bai ƙaddara a cikin ƙaddarorin rayuwata ba naci dubu sai dai ceto. Su wannan gidan ya dama wallahi Ni ta kaina nake yi, in suka sa aka sakeni ma ni sun taimaka mun ne."

Rai a mugun ɓace nake maganar. Maman Safara'u tace.

"Hakiƙa na fahimceki Maman Mardiyya. Muita adda'a Allah ya nesanta mu da sharrin abokan zamanmu kawai. Amman in sha Allah wata rana zan baki labarina nasan dake da masu karatu zaku tsinci  abubbuwan ɗauka.

Da yawa yawan tashin hankulan dake wanzuwa a zamantakewar gidan da ba macce ɗaya bace a ciki ba mazan sune munafukai a tsakankanin matan.  Su suke zama munafukai masu yaɗa zantukan ɗakunan.

Nifa da kika ganni bani da kowa a Najeriya ni ƴar Senegal ce dangina sau biyu kacal suka taɓa zuwa inda nake a sakamakon talaucin da suke fama dashi.

Edit with WPS Office

Ƴayƴana sune komai na rayuwata. Miji kuwa tuni ya mance duk wani halaccina dana dangina yasa ƙafa ya shure duk soyayyar da na nuna mishi.

Amman lefina shine zaɓarshi da nayi'

Hawaye ta share haƙiƙa mu mata muna ganin bone. Amman duk wanda yayi haƙuri zai ci ribar haƙurin ko a duniya ko a lahira.  Zan so jin tarihin Maman Safara'u kamar yadda nasan su Anty Zee Musa suma zasu so jin wannan labarin da Maman Inteesar uwar wutar ciki kenan. Dasu Amina madaki

A da hankalina bai kwanta da maman Safara'u ba, amman ɗan tsokacin da tayi sai yasa naji zan iya amsarta a matsayin ƙawa baya_baya amman dan naga sharrin ƙawaye da butulcin Aminiya.

Hmmm sai hakuri amman ai Allah ya fisu. Kana zaune watarana za'a gane amfaninka. Kuma ko da mutuwa kayi duk daren daɗewa sai an yabeka sakamakon tuno da wani abu naka. Bari in kwaso ɗinkunan ki gani, bukukuwa muke dashi zuwa bayan Sallah har biyu. Yar yata da ƴar yar mijinmu"

Murmusawa Maman Safara'u tayi tace.

"Allah sarki nima zuwa bayan Sallah zan je Senegal akwai bikin ƙanwata da muke uba ɗaya zanje, shekara biyar banga iyaye da dangi ba"

Idanu na zaro waje nace.

Wai lalle kin jima baki je gida ba kam"

Wucewa nayi ciki na ciro akwatin da Ƴar Shuwa tayi mana na ɗebo kaya kala huɗu atampa biyu leshi biyu, sai na zaro shadda itama. Yara fa zanma dan wallahi nafi ƙarfin in saka wannan kayan.

Ina da atampopi manyan holan guda biyu na haɗa dashi na fito.

Kinga gasu. Waɗannan atampa ɗaya leshi ɗaya Mardiyya da malama za'a ɗinka ma. Wannan atampopin kuma nawa ne, sai waɗannan biyun amaren nake so ayi ma kayan fitar biki zan turosu suzo a gwada su. In aka fitar da anko sai in haɗo da ragowar nawa kayan in kawo.

Su kuma mazan zan kai musu ɗinkin wannan shaddar ne"

Kayan take ɗaɗɗagawa tace.

"Gaskiya kaya sun yi kyau sosai. Nakinnan har naga ɗinkunan da zanyi miki kinsan fa mu matan Senegal akwai ɗinki da kwalliya ma. Atampa da lace ɗinnan zan haɗama amaren ayi musu Senegal combination na atampa da lace sai dai ɗinkin yana cin kuɗi gaskiya. Kema da so samu ne da wannan holan ɗin ai sai ayi miki ki siyo lace ko shadda yadi biyu sai in miki mai zani. Zaki yi kyau"

Edit with WPS Office

Dariya nayi nace.

To Shikenan zan siyo lace ɗin sai in saka ranar idi ma ni nawan tunda amare da biki zasu saka nasu"

Bata jima ba tace zata tafi, a leda na saka mata kayan na ɗakko dubu goma sha biyu na bata ta soma riƙewa. Har bakin get na rakata ta fita akan in turo su Malama da yamma a gwadasu.

Dawowa nayi muka ci gaba da wankinmu ina jujjuya lamarin zaman gidannan da irin sharri da makircin Hamida. Duk da ita ba komai bace in akace da Yar Shuwa za'a haɗata. Sai dai ina ganin wautar Yar Shuwa data zaɓi cin Amanata ta rasa wanda zata aura sai Babangida ni da nake mata adda'ar samun nagartaccen miji sai ta ɓige da auren Babangida ragowar ƴan bariki. Nasan duk yadda dai Babangida yake ganin saki da mace ba abakin komai ba. A wannan karon ya ɗakko ƙarfen ƙafa ko a buzu yake kwana bazai iya sakin Yar Shuwa ba. Ni kaina tunda ta shigo bazan so ya saketa ba zanfi so ta zauna taci uwar da akeci a gidan.

Wani tukuƙin turirin kishi ke turniƙeni. Kar kuga laifina dan nasan wasu zasu iya jin haushina. Akwai ciwone ace mijinka ya auri Aminiyarka Aminiyar da duk duniya babu wanda yasan sirrinka kamar yadda ta sani.

Tsorona Allah akwai wani ƙwai mai wari dake hannun yar shuwa fashewarshi nake tsoro duk da in ta fasa wannan ƙwan tamkar ta saki igiyoyin aurenta ne na rantse da Allah. Ina tsoron wata rana da Yar Shuwa zata ji bari ta fasa wannan bara gurbin.

Kirjinane ya doka da ƙarfi take idanuna suka tara kwalla mai ƙuna na tunanin baya. Duk yadda zaku fassara bazai fassaruba har sai kunji asalin gundarin labarin.  Marubuciyar tayi amfani da hikima ne wajen mayar da tsakiyar labarin ya dawo shine farko. Ni kaina na jinjinama baiwar fikra da hikima da Allah ya bata.

Haka dai naita lissafe_lissafe muna aikinnan har muka gama. Na taya yara sukai kwalimar ɗakinsu shima muka gama. Taliya fara na sulala musu nayi miyar ƙwai suka ci dashi, suna gama ci sukai Sallah na basu kuɗin mota suka wuce makaranta.

Ni sai ruwan bunu na ɗan sha na kasa kai komai bakina. Kirjina sai bugawa yake yi da ƙarfi sakamakon  tunani da yaima kaina yawa. Sai da na watsa magani  kafin na ji dama_dama.

Wajajen ƙarfe uku na rana ina kwance ina bin sanyin tayil sai ga kiran waya Babangida ne yake kirana kiranda nayi imanin ba alkhairi a cikinshi.

Ɗaga wayar nayi bance komai ba. Shima bai damu ba ya soma jero mun dalilin kiransa.

"Muna hanya nan da awa ɗaya da rabi zamu iya shigowa. Ki yi mana abinci, sannan ki yi mun farfesun kayan ciki. Nasa yara zasu kawo miki cefane suna hanya ma."

Kit ya kashe wayarshi ba tare da ya tabbatar naji ko banji ba.

Edit with WPS Office

Ina mai cike da mamaki na jiyo sallamar Labbai da Adama niƙi_niƙi da kayayyaki a leda.

"Lolo tare muke da motar kayan Aisha tana waje."

Miƙewa nayi da ƙyar nace.

To akwai me gadi ya buɗe get su shigo, bari in ɗakko mukullin gareji."

Tashi nayi na ɗakko mukullin gareji a ɗaki naje na buɗe musu. Masu mota na kan loda kayayyakin yaron da Babangida ya aiko ya kawo saƙon niƙi_niƙi harda kayan marmari ƙwallo_ƙwallo.

Binshi nayi ya ajjiye mun a falo. Hannu yasa a ajjihu ya ciro dubu biyar.

"Yace in baki kuɗin gas wai"

Gas na maimaita a raina, dana fahimci  me yake nufi Sai nayi dariya kawai nasa hannu na karɓa.

Adama ce ta soma shigowa tana haki sannan Labbai ta shigo.

"Gidan babu kowa Yar Shuwa ni ko nake son in gani so nake inga ko zata iya kallona, dukka nasan a ƙwanƙware take maci amana ƴar iska maras mutunci.

Ai dama ni tun farkon ƙawancenku Allah bai yi jinina ya haɗu da mitsiyaciya ba kina gani da yaya ma na soma sake mata ko gidana tazo?"

Wani ƙududune ya tokareni a wuyana. Dana tuno irin son da na nuna ma Yar Shuwa. Ni da ita kayanmu a haɗe suke ko bata nan zan shiga ɗakinsu inyi duk abinda nake so, in ɗauki komai a kayanta. Haka itama  take yi mun, duk inda na taka saita taka amman wai yau muke auren miji ɗaya. Narantse da Allah ko ban rabu da Babangida ba mu'amular Aure dani dashi har gaba da abada"

"Wai basu dawo daga asibitin ba ita waccan gulmammiyar?"

Furucin Labbai ne ya dawo dani cikin hayyacina wanda hakan yayi daidai da kwaɗa kiran sallar la'asar da akayi a masallacin unguwarmu.

Ba'a sallamesu ba suna can. Ni kaɗaice a gidan Babangida da Amaryarshi sun yi tafiya"

"Kinsan Allah Lolo Maigogul yana gida yana ta zage_zagen ya kwana a buzu ya miki aiki aljanu sun faɗa mishi wai kin yar da maganin to yana can yace ke da shine sai ya miki kafurin duka."

Labbai ni ba wannan ba dan Allah ki taimaka ki girka mun wannan abincin jallof ɗin shinkafa ce sai soyayyen kaza, kayan marmarin ina daga zaune sai in yanka kayan cikin kuma farfesu za'ayi. Akwai wani kayan cikin a gidan ƙanƙara ki ƙara akai."

Ai kuwa labbai dake yaro ba ƙyuya ce nan da nan ta shiga aiki. Abun mamaki Babangida yasa an siyo harda kayan miya, maggi, mangyaɗa da hatsi.

Edit with WPS Office

Ina yanka kayan marmari Adama ta ciro anko guda uku ta ce.

"Kinga wannan atampar itace ankon bikin nasu dukka. Wannan lace ɗin da nace mu ƴan ɗakinmu sai muyi ankonshi ko? Wannan atampar kuma ta ƙawayen Amarya ce. Ya kike ganin yayi miki?"

Yayi sosai atampopin sun yi kyau. Kuma nawa atampar da lace ɗin?"

Miƙo mun tayi na karɓa.

"Kin gansu atampar dubu shida, shi kuma leshin dubu sha biyu na dai yi karambani nace mu ma ɗinka yan ɗakinmu kinga ƴan ɗakinsu Hauwa lokacin bikin Zara'unta suma kinsan haka suka yi suka ware kansu suka ɗinka shadda galila."

Na tuna. To ai Shikenan hakanma yayi Adama.

Mu dai atampa da lace zamu siya. To yaushe ya kamata mu siya sabida ɗinkin?"

Ajjiyar zuchiya ta sauke tayi laƙwas.

"Hmm Allah dai ya hore ni kam sai zuwa bayan Sallan zan siya sabida babu kuɗin Lolo. Kinsan Allah haka na fito gidannan ba'a ɗaura ko tukunyar ruwan zafi ba balle a saka ran abinci. Yaran duk basa gidan suna yawon ta zubas. Lolo in nace na hanasu yaya zanyi dasu, ubansu dai bai damu dasu ba, ni ba shine dani ba. Yarannan su suke taimakawa ɗan abinda suka fita suka roro dashi muka dogara. Ga Usaini Lolo yaronnan ya dena kwana a gida, lamarin Usaini yafi ƙarfina na ɗauki ido na zuba mishi kawai"

A kullum ire_iren irin labarannan da nake jinsu daga bakunan ƴan uwana shi ke sa inji in yankan namana akeyi gara in doge in zauna in kula da tarbiyyar ƴaƴana ko zasu zama na daban a dangi, ko zasu zama abin kwatance a dangi. Allah na gode maka daka bani nutsattsun ƴaƴa. Aɗɗa'u da yake rashin jin Allah ka shiryashi shima.

Mufa kullum muka haɗu tauna matsaloline aikinmu. Labbai ta gama girkin ba da jimawa ba suna zaune suna ci motar Babangida ta shigo cikin gidan. Take ɗan farin ciki da dariyar da nake yi da ƴan uwana ya ɗauke.

Shigowarsu baifi da minti talatin ba na jiyo takun Babangida ya shigo ɓarayina. Babu ko sallama ya buɗe labulen ɗakina daidai Adama tana gutsurar cinyar kaza. Kur yayi mata da idanu cikin murtukewar fuska.

"Ina Wuni Babangida kun dawo ashe?"

Adama ta faɗa tana sake cusa shinkafa a bakinta.

Kai kawai ya girgiza harda guntun tsaki.

"Ke ina abincin da nasa ki girka. Kaddai shine kika kwashe kika ba ƴan uwanki jibi kaji a

Edit with WPS Office

kwanukansu an samu na banza ko?"

Ya faɗa cike da faɗa da hargagin da bai taɓa yin irinshi ba. Kafin inyi Magana sai ganin Yar Shuwa nayi ta faɗo cikin ɗakina tana kare ma anbincin da su Adama suke ci da kallo.  Da Adama da Labbai kuwa ko a jikinsu bil haƙƙi suke cin abincinsu kamar basu san Allah yayi ruwan tsaron Babangida da Yar shuwa ba.

"Jannaty ai ta kwashe musu kajin kasan fa inaso mu ci har dare ne"

A kwakkwaɓe irinnan sangartattun ƴan iskan mata tayi maganar.

"Iko sai Allah Butulci bai yi ba. Na shiga uku na ni Adama wai yau a gabanmu kike kiran Babangida kacigari da janbaty ƴar abu ta kazan... Kin yi asara wallahi kuma zaki tarar da wulaƙanci a gaba mafiyin na wacce kika ci ma amanar."

Adama ta faɗa tana kama baki.

Abincinsu suka kwashe suka wuce ɗakin yara sai da Adama ta bangaje Yar shuwa kafin ta wuce.

"Kiyi magana in dakaki kema kinsan bana wasa dake"

 Ita kuma makirar da murmushin cusa haushi ta bita.

"Ke Sabuwa dake nake yi. Me yasa zaki kwashe kaji ki ba danginki? Ji yadda suke mata cin yinwa, cin wulaƙanci. Kuma a gabanki Adama ke zagin Habibaty har tana datsa sunana tsirara ko Bismillah babu baki iya tsawatar mata ba ko?"

Ina daga zaune ina kallon ikon Allah. Yar shuwa tayi tsaye a kaina turarenta har kaina nake jinshi amai nake ji sosai muddin nace zanyi magana to tabbas amai zanyi.

Tsam na tashi na nufi ɗakina, ina shiga na saka sakata na nufi banɗaki da gudu na dinga sheƙa amai.

Babangida kuwa tamkar zai ɓalle ƙofar dan jar masifa ƙafa yasa ya dinga dukan ƙofar.

Ranar Babangida babu irin zagin da bai mun ba. Haka yake kiran sunaye yana ɗuro ashariya yana ɗumawa Ina durƙushe ina sheƙa Amai ina kuka mai gunji. ( Masu ganin kamar na ɗaurama kaina damuwar tayi yawa. Allah baku saka ƙafa a takalmina bane shi yasa. Duk girman matsala in kallonta kake yi kafi tunanin mafita. Wanda yake cikinta kuma rashin kwanciyar hankali kaɗai ka iya toshe mishi ƙwaƙwalwar tashi ma)

Ina jiyo su Adama na bashi haƙuri.

"Jannaty tunda sun baka haƙuri muje kawai taci albarkacinsu."

Adama ta ɗumo ashariya da ɗumama Yar Shuwa.

Kamar tayi mai allurar bin umarni ya bita suka fice ina bakin gado na yi zurfi cikin damuwa da

Edit with WPS Office

tunanin ni shikenan a haka zan ƙare ne na jiyo Adama na kirana.

Buɗe musu ƙofar nayi suka shigo, ashe yaranma sun dawo suna tsaye a bakin ƙofar.

Mardiyya dake itace babba sai naga fuskarta a murtuke sosai.

Kun dawo Adda? To sannunku"

"Sannu da gida ummi"

Yaran suka bini suna tai mun sannu.

Kyallen atampa da shadda ta miƙo mun

"Malama ƙarama ce tace in kawo miki ankon biki. Atampar tamu ce yaran gidan. Shaddar kuma taku ce.

Labbai ce ta karɓa tana kallon zanen atampar tayi kyau iya kyau.

To Shikenan kuje ku yi wanka abincinku na kitchen kuci zan sallami su Adama in fito"

Sai da suka fita Adama tace.

"Ni yaran sha'awarsu nake yi Lolo. Jibesu a nutse sosai ga karatu kullum. Ni ina ganin wannan kaɗai ribace ta auren Babangida. Dan da ace samarinki na baya kika aura ba lallai ki samu yara nagartattu haka ba. Lolo ki dena damuwa da masifar Babangida ki dena shiga shirginshi dashi da Yar Shuwa sharrine ya shigo da'ita gidan. Sharrinta a iyaka kanta zai tsaya.

Nama dai mun ci, kuma da basu kwashe abincin ba wallahi da ƙarawa ma ni zanyi. Ni na zaci ba zasu ɗauki abincin ba sai naga shaƙundum ɗin da kanshi ya ɗauki kulolin"

Ni dai bana iya cewa uffan.

Saida sukai magriba suka kama hanya, Abinci na zuba ma labbai a kwano nace ta tafi dashi sa ɗumama ko da safe ne. Dama lokacin da zata yi girkin na riga na ƙara abincin da kazar sabida ai Labbai ba zata yi mun girki in hanasu ba. Ko ba ita tayi ba ya zama dole suci tunda dai wajena suke zuwa.

Ina zaune a falo ina kallo bayan mun yi sallar magriba. Sai banga Aɗɗa'u ba ga ƴan uwan suna zaune sunata hirarsu da manyance.

Wai Aminu ina yaronnanne ko banɗaki ya shiga?"

Sai da na tambayesu suma hankalinsu ya kai baya nan.

"Ummi bamu san inda yake ba. Ni yanzu na fito daga banɗaki baya ciki, kuma baya ɗaki"

Cewar Mardiyya.

Edit with WPS Office

A kiɗime ni da ita muka fice nemanshi gida_gida. Abu tun fa muna yi muna ganin wasa ne wallahi sai ƙaramar magana ta zama babba. Babu Aɗɗa'u babu labarinshi. Tuni jinina ya yayi sama

MRS BUKHARI

Ina manyan mata masu capacityn  suke?  ku fito lambarku ce ta fito.

Yar uwa turaren wuta kike nema nau'ika daban_daban masu musulmin ƙamshi da kama muhallu? Ba itacen banza masu sanya gida ƙauri da hayaki kamar an kunna taohuwar bespa ba.

Matso gasu MRS  BUKHARI B4B GIDAN KAMSHI nazo miki da duk abinda kike buƙata na ƙamshi. Kama daga turarukan wuta irin na gidan alfarma. Zuwa humrori iri daban daban masu musulmin ƙamshi da riƙe jiki.

Bugu da ƙari muna da turarukan kaya, na fesawa dana turara kaya.

Muna da kulaccam nau'i daban daban masu gyara jiki da lausasa  fata mata, ga kuma ƙamshi mai inganci.

Muna da turarukan tsugunno na musamman masu sirri Hajiyata

Muna da room freshener iri_iri

Muna da mopping mix masu kama waje.

Akwai turarukan kafet dana kujeru.

Sannan akwai box _ box  setika na Hajiyoyi masu ƙyallin goshi.

Muna da Amarya package.

Muna da uwargida package

Muna da maijego package

Muna bayar da sari ko a ƙasar waje kike, muna tura kaya

Saudiyya

Nijar

Ghana

Camaron

Edit with WPS Office

A duk ƙasar da kike kayanmu zai iso miki cikin aminci da yardar Allah.

Hajiya akwai Humrar matan aure wannan ta musamman ce.

Duk wani abu da kika sani na ƙamshi babu irin wanda bamu dashi a kamfaninmu.

Muna da turaruka designer na maza da mata wanda kamfaninmu ke bugawa Hajiya babu inda zaki je ki ci karo da mai irin ƙamshinki.

MRS BUKHARI B4B GIDAN KAMSHI TAZO MUKU DA DUK ABINDA KUKE SO NA KAMSHI HAJIYA.

KUNSAN KANURI MUNE KAMSHI DAMU AKE KOYI

SIYAN NAGARI MAIDA KUDI

MUNA MARABA DA MASU SIYAN ƊAYA KO SARI.

LAMBAR DA ZA'A SAMENI KAI TSAYE ITACE.

Wa.me/2348179523215

SAI NA JIKU

IDAN KAYA YA GAJI...

GAMMO MA YA GAJI

BADIAT IBRAHIM MRS BUKHARI B4B GIDAN KAMSHI

SHAFI NA ASHIRIN DA UKU

Sanya kuɗin karatun a cikin wannan lambar asusun

0044442984

Buhari Ibrahim Ladan Gt bank

Lambar da zaku turo shaidar biya gasu kamar haka

Edit with WPS Office

08022059556

Ko kuma

08105932041

Masu son magana da marubuciyar kai tsaye kuma ga lambata

Wa.me/2348179523215

Babangida:.

Fuuu ya fice a ɗakin Sabuwa tare da yi mata boll da bokatai duk suka fashe, wasu suka tsattsage.

Zuchiyar ƴar Shuwa cike da murna t gashi Babangida yakwashe kulolin abincin da akasa Sabuwa ta girka.  Tabi mijinta zuwa turakarshi.

Yana tsaye ya goya hannayenshi a baya yanata kai komo a tsakar ɗakin ranshi a mugun jagule yake sosai.

Ƴar Shuwa ta shigo da tiren plate data ɗauko a ɗakinta dasu jus bakinta da sallama cikin kyawun lafazi.

Sai da ta ajjiye tiren ta matsa inda yake ta dafa kafaɗarshi kana tace.

"Jannaty sai haƙuri. Bazan ɓoye maka ba tunda nake ban taɓa ganin gidan mutanen banza irin gidansu Sabuwa ba. Kuma wannan yuyar ta gidansu in ba hanasu zuwa kayi ba wallahi baka ga komai ba.

Duk da ko basu zo ba Sabuwa har gidajensu take binsu da hatsi. Kai kana zaune kasan Sabuwa ita ke ciyar da gidansu kuwa? To ita ke ciyar da gidansu ta siyar maka da hatsi tayi abinda take so da kuɗin."

A fusace ya juyo ya cafe kafaɗunta du biyun yana magana yana jijjigata.

"Yanzu ke duk kinsan da wannan kika kasa sanarmun Habibaty? Ina zaune ana ciyar da rida riɗan banza da dukiyata yanzu ta dawo ciyar dasu da dukiyar ubana. Allah ya tsine ma Mustapha da ya zama silar haɗuwata da Sabuwa"

Edit with WPS Office

Kafaɗun nata ya sake ya zauna jiɓir. Sai lokacin ta sauke ajjiyar zuchiya dan ba ƙaramin riƙo yaima kafaɗunta ba duk yabi ya jijjige mata.

Zama tayi a gefenshi ta dingi yi mishi famfo akan Sabuwa da danginta. Babangida ya sake hawa dokin tsanar Sabuwa yayi ɗare_ɗae.

Cikin rarrashi tare da ciyar dashi da shayar dashi a baki ƴar shuwa ta shawo kan Babangida.

Zuwa bayan magriba kuma suka ɗau wanka suka nufi asibity dubo Hamida da ɗiyarta.

A asibityn suka samu Goggon Hamida ita ke jinyar yarinyar ita kuma Hamida tana zaune akan dadduma  tana aikin charting da karance_karance littattafan Hausa. Ganin Babangida ya tawo da matarshi ba ƙaramin baƙanta mata rai yayi ba. Da ace bata shakkar Yar Shuwa da jin shayinta yau da sunga shegiya a asibitynnan. Har mamakin yadda in taga Yar Shuwa take faɗuwar gaba take yi. Wata zuchiyar tace.

"Anya ba asirinsu na Shuwa tayi miki ba kuwa?"

Hmmm biri fa yayi kama da mutum.

Muryar Yar Shuwa dake gaishe da Goggo ne ya dawo da Hamida daga tunanin data faɗa.

"Hamida ya dai tunanin me kike yi haka kuma?"

Cewar Babangida daya nemi kujera fara ya zauna yana fuskantar ta. Yar Shuwa kuma tana bakin gado tare da Goggo.

"Hamida ya mai jikin? Duk da naga jikin da sauki"

Ta dubi Yar Shuwa a tsorace tace.

"Jiki kam da sauƙi yaya hanya?"

Sai da ta saki wani hajiyan murmushi kana tace.

"Alhamdulillah hanya anje an dawo"

Goggo ce tace.

"Ni Babangida uwargidanka basa zaman lafiya ne da Hamida? "

Babangida dake ta kallon ƙirjin Hamida ƙur, Yar Shuwa kuma na kallon yadda yake haɗiye miyau yace.

"Me kika gani Goggo?"

Goggo ta gyaɗa kai tace.

"A_a naga tunda nazo asibitinnan banga tazo ba. Ban kuma ga wani nata ba, sannan bata kawo

Edit with WPS Office

abinci ba. Usama ma ance yana maƙota. Wannan wanne irin zamane akeyi a gidanka Babangida? Ina tsoron kada yaranka kansu ya rabe abun bazai yi muku kyau da daɗi ba. Kaji tsoron Allah ka yi ƙoƙarin kulawa da ratayayyen nauyin dake bisanka"

"Wallahi Goggo ina iyakacin bakin ƙoƙarina dan ganin matana sun zauna lafiya, yarana sun yi zumunci.

To ita Sabuwa ce ke da babbar matsala.

Yaron nace akai mata bata karɓa ba. Abinci nace ta kawo taki.

Ayi haƙuri zan ɗauki mummunan mataki akan hakan daman ban ma nutsu ba tunda na dawo, ban yi maganar da'ita ba zan yima tubkar hanci."

A haka rai a ɓace Babangida yaje yaga likita ya dawo, Hamida ya ba kuɗi suka kama hanya zuwa can gidansu Babangida.

Malama Babba dan murna da jin daɗi rasa inda zata tsoma Ƴar Shuwa tayi ta dinga nan nan da'ita.

Itama ta saki jikinta sosai a kwano ɗaya malama ta zubo musu dambun dawa yaji gyada da zogale jin ƙamshin man shanu yasa Babangida ya sakko yasa hannunshi, suna cikin ci Baba Malam ya buɗe labule da sallama zai shiga, ganin Babangida da iyalinshi yasa yayi turus. Kur ya ƙura ma kwanon abincin idanunshi yana kuma ƙarema Yar shuwa kallo duk a lokaci guda.

"Baba Malam barka da dare, mun same ku lafiya?"

Cewar Babangida daya ƙarasa inda yake ya durƙusa har ƙasa kanshi a ƙasa kamar na Allah.

Baice uffan ba har Yar shuwa itama ta ƙaraso ta tsugunna kamar yadda mijinta yayi.

"Baba Malam ina wuni mun same ku lafiya?"

"Lafiya ƴarnan. Babba kizo ina da magana"

Ya faɗi rai a murtuke ya saki labulen.

Jikin Babangida a sanyaye ya dawo ciki ya zauna a kujera. Ƴar Shuwa ta cicciro tsarabar da taima kab ƴan ɗakinsu Babangida na Malama Babba na musamman ne.

"An gode sosai Shuwa. Ni kam zanje ɓarayin malam Babana mu kwana lafiya"

Ta saka kai ta fice tana jin wani irin ciwo da yaji a kirjinta.

Shi kanshi gogan tuƙi yake yi amman hankali da nutsuwarshi basa tare dashi sam tunani da damuwa su suka dami zuchiyarshi. Ƴar Shuwa ganin halin damuwar da yake ciki saita tsuke bakinta tayi shiru ta shiga lissafin yadda zata tatsi kuɗi a hannun Babangida in suka dawo daga Umara.

Edit with WPS Office

Suna shan kwanar layinsu suka hango Sabuwa da Mardiyya zasu shiga wani gida, wani irin wawan burki Babangida yaja wanda sai da Ƴar Shuwa da kanta ta tsorata.

SABUWA:.

Tun daga nesa na hango motar Babangida, har zuwa burkin da ya ja.

"Ke Sabuwa me kike yi a waje da daddare haka ke da yarinya. Da izinin wa kika fito?"

Aɗɗa'u ne ya sulale ya fice tun ɗaxu muke nemanshi gida_gida bamu ganshi ba"

"Mene gida_gida yaron nawa a irin wannan lokacin yaro ƙarami? Shikenan zaki gurɓata mun tarbiyyar yaro. Dalla ki wuce gida nace miki zanje da kaina in dubo shi. Jibi kayan da yake jikinki yadda ya bayyana surarki."

Fuuu ya ja mota ya barni a tsaye sororo.

Mardiyya ce ta ja hannuna muna takawa a hankali kafin mu ƙarasa kofar gidan har Babangida ya fito ya shiga neman Aɗɗa'u. Mu kuma muka shige ciki inata tsaye a falo ina duba agogo sai wajen sha biyun dare sai ga Babangida riƙe da Aɗɗa'u yana jibgarshi yayimishi mugun dukan mutuwa yaronnan saida ya bani tausayi . Bayan ya gama ya dira a kaina akan rashin riƙe Usama da ƙin kai abinci asibity. Wai ai da danginane da kullum saina dafa nakai jikina na rawa. Yayi mun cin kashi ainun.

Ajjiyar zuchiya na sauke nabi bayan Babangida daya fice fu da kallo. Na karkato da kaina kan Aɗɗa'u

Ina kaje da daddarennan Aɗɗa'u bana hanaka yawo ba,so kake yi ka lalace ko me?"

Ganin ya kasa magana yasa nace

Tashi kaje ka kwanta da safe mayi magana.

Gaga_gaga_gaga_gaga

Haka lamura suka ci gaba da tafiya ranaku suka ci gaba da shuɗewa a kwana a tashi har gashi yau mun ɗauki azumin watan Ramadan.

Baba Malam da kanshi yazo ya kawo mun cefanen azumi komai da komai harda su dankalin turawa da kayan sallan yara har da nawa ma.

A cikin kayan na ɗebi dankalin turawa'doya na haɗa musu mu Rakiya da taliya guda shida sai kayan tea, siga, madara, milo, biredi na haɗa musu kaya cikin leda biyu ana gobe za'a ɗauki azumi acan na wuni na tadda Layuza ma ta kaima Hauwa siga da makaroni

Wuni muka yi anata tauna yadda biki zai kasance Aisha dai ta gama komai lokaci kawai ake jira

Edit with WPS Office

iyakar abincin da za'aci da bikinne ba'a siya ba. Mu kuma yaran gidan aka ɗaura mana nauyin.

Gaga_gaga azumi nata tafiya, ni sabida tsabar laulayi da ciwon damuwa da a cikin azuminnan ya far mun na zama kamar marar hankali sai ni kaɗai inta muzurai ko kuma ɗan motsin abu kaɗan yasa in firgita.

Nayi amfani da wannan damar na durfafi yin adda'a babu dare babu rana saina samu sassauci alhamdulillah inata lallaɓawa dai

Tunda aka soma azumi ban saka Babangida ko matanshi a cikin idanuna ba tamkar ba gida ɗaya muke rayuwa ba kullum ina ɗaki a gaban tv ina sauraren tafsiri azumi daga bakunan malamanmu masu albarka. Ba wani ganewa nake yi ba ina dai saurarene kawai. Ko da Hamida aka sallamosu asibity banje na ga mai jikin ba, nima lokacin da muka kwanta da Malama haka taimun.

Wasa_wasa azumi yau in mun kai mun kai na goma sha tara kenan. Yau dai na daure na ɗauka nace bari in jarraba.

Da yamma ina zaune ina fere dankalin turawa na jiyo sallamar Yar Shuwa ta shigo falo na. Jin ɓuruntuna yasa ta nufo kitchen kai tsaye.

Kallon _kallo mu kai ma juna tayi wani kyau ta sake ƙiba.

"Hmmm kina kallona kina saka mugunta a ranki ko? Hahahh Sabuwa kenan. Ba faɗa bane ya kawo ni ba nazo ne in miki sallama zamu tafi umara ni da Jannaty"

Miƙewa nayi da dankalina a na nufi wajen wanke_wanke na sakar mishi ruwa, ban sake juyowa ba ina ji taja dogon tsaki ta fice.

"Aikin banza nasan dama sai kinji dan baƙin ciki kamar ki mutu nima hakan dama naso kiji"

Ta fita tana faɗe. Murmushin baƙin ciki kawai nayi na tsane dankalina a kwando ina tsaye ina ɗan ɗauraye kayan dana ɓata na jiyo muryar su Mardiyya.

Duu suka shigo kitchen ɗin har da su Aɗɗa'u yau yana azumi in ya kai yayi uku kenan, Aminu kuma goma yayi, Mardiyya bata sha ko ɗaya ba sai yau data tashi da jinin al'ada shekarar data wuce ma dukka tayi.

Nan suka cikani da surutu sai haki nake yi ina jin zuchiyata na mun zafi.

A wahale na kai azumin muka gama shan ruwa yau dai da na ji dama_dama nace mu je su rakani mu amso ɗinkin su Mardiyya, nasu Aminu dai har an ɗinka lokaci kawai ake jira.

A tsakar gida na tadda Maman safara'u tana cin kosai da ruwan tea ita da yaranta.

"Ahh maraba da zuwa yau kune a tafe Umman Mardiyya?"

Edit with WPS Office

Na'ila na jin haka wallahi sai gata tsulum ta fito, ganin mun zuba mata idanu kuma saita kiɗime ta shiga dube_dube daga ƙarshe dai kitchen ɗin tsakar gidan ta faɗa ta ɗibi kunu ta koma.

"Hmmm Na'ila kenan. Kinga ƙawata zauna ki dena mamakinta. Ko da yake shige daga ciki ku kuma Mardiyya ku zauna bara a ɗebo muku ƙosai kuci. Safara'u kawo musu ƙosai.

A zaune a kujera ta shigo ta same ni ta debo mun dinkunanmu gaskiya sun zabga kyau sosai kamar ba hannune ya ɗinka ba harda na su Aisha ta gama. Wanda Baba Malam ya kawo mun ma duk ta ɗinka mun.

Cikon kuɗinta na ƙirga na bata tasa hannu ta amshi kuɗin

"Bari kiga wata sarƙa da nasa aka sai mana a Senegal da za'a siyo mun ɗankunnaye"

Allah ya soni ina gama mayar da kayayyakinmu leda sai ga Na'ila ta buɗe labule tana tambayarta yaji in tana dashi"

"Yajin kinsan yana kitchen a farar roba fa"

Sai tayi dariya ta sosa kanta.

"Ai ashe yana kitchen na duba ne ban gani ba"

Ta saki labule Maman Safara'u tayi dariya tace.

"So take taga wanne irin kaya na dinka miki ƙyes ta faɗa ma kishiyarki dan bata da aiki sai zuwa gulma duk sirrin gidanku yana tsakar gidanmu. Ɗaxunnan fa ta leko take faɗama Na'ila wai Amayarkar ku an tafi da'ita Umara ku baku taɓa zuwa ba. Ammam mijinku yayi mata alwarin shekara me kamawa da'ita zashi in dai ba goyo take yi ba."

Ni dai dariya kawai nayi nace.

Allah ya kyauta"

Sarƙar ta nuna mun tayi ɗan karen kyau ɗaya nata ɗaya nawa. Amsa nayi nace mata Mardiyya zata kawo mata kuɗin

Tattare kayan nayi nai mata sallama muka koma gida.

Nan muka baje a falo muka shiga aikin gwargwada kayan. Washegari da zamu gida ni da yaran na tafi ma da su Aisha nasu. Ganin ɗinkin yadda yayi kyau yasa Adama dasu Rahama suka bata dinkin ankon biki suma.

Duk fa wannan gwagwarmayar Babangida tunda suka tafi bai kira waya ba, nima ban kirashi ba.

Alhamdulillah ana gobe Sallah Baba Malam ya aiko mana da cefanen Sallah harda kaji huɗu da naman saniya mai yawan gaske.

Edit with WPS Office

Wuni mukai muna aiki da yaran da daddare nayi mana lalle nida mata_matan

Washegari Sallah tun asussubar fari na ɗaura tandar masana na hau suya dama nayi miyata tun dare miyar gyaɗa taji naman saniya ga man shanuna a soye.

Zuwa ƙarfe bakwai na kammala suyar masata kwano biyu na cika babbar kula.

A gurguje na shiga wanka yaran dai na barsu a falo suna shan tea   da masa amman basu saka miya ba ko wanne yasa kayan sallanshi sun yi kyau.

Atampa na saka mai ja da fari a jiki, takalmina da ƴar jakata duk jajayene haka ma mayafina, sarƙar wuyana kuwa irin mai cika wuyannanne ta matan Senegal.

Karfe takwas muka fito ni da yara gari ya ɗauki harami ga yara nan ko wanne yayi ado mai kyau, ga maza manya wasu suna tafe a ƙafa da iyalanshi, wasu na cikin mota. A ƙafa muka isa babban masallaci wanda yake mafi kusa damu, minti talatinne ya kaimu muna zuwa tara nayi aka tayar da Sallah. Al'umma birjik kamar ba'a mutuwa.

Ana idarwa muka kawo hanyar gida, muna tafe yara na jin daɗi. Na danyi musu siye_siyen kayan zaƙi.

Muna shigowa na shiga rabon abincin sallah.

Na ba Mardiyya na Hamida, na ba Aminu na Maman Safara'u nace su kai musu harda zoɓo da nayi da ɗan soyayyen nama a leda.

Na gidan su Babangida na zuba da yawa tunda nasan suna da yawa ga almajirai ma, kaza kusan ɗaya na saka musu, zoɓo kuma na saka musu manyan roban faro huɗu. Ni da kaina na raka yaran har titi saida suka hau abun hawa kana na dawo, acan suke sallarsu sai in na je jibi sai mu dawo tare washegari kuma mu tafi wunin namu gidan.

Ina dawowa naci masa nayi ƙet sai bacci.

Hayaniyar ƴan gidanmu ce ta tasheni daman Maigogul ya saba aiko Uzairu zuchiyata karɓo abincin Sallah.

Wannan karon harda Gaza da Labbai aka tawo.

Tare na zuba mana abinci muna ci ana hira a haka yaran Adama da Rahama suka zo suma karɓan abincin Sallah sauri kuma suke yi Labbai nasa ta zuba musu na basu dubu ɗaɗɗaya kuɗin mota da goron Sallah.

Ni dai a haka aka kare sallar babu wani armashi.

Ranar wunin gidansu Babangida na saka wannan atampa da lace na matan Senegal gani da karamin ciki saina sake wani kyau da murjewa.

Edit with WPS Office

Karfe tara muka saba zuwa wannan karon sai sha biyu saura na sauka a ƙofar layinsu.

Abokan Babangida suna zaune a dadduma sun baza idanu sai gulma suke yi tare da ƙarema matan mutane kallo, ga kulolin abinci nan iri da kala a gabansu, da yanzu muma akwai tamu kular

Ina shiga tun daga zaure na tadda almajirai na cin tuwon shinkafa miyar taushe da tantakwashi, abinka da mai ciki take raina ya biya.

Cikin gidannan an cika an batsa ƴaƴa da jikoki, matan ƴaƴa ire_irenmu duk gasu nan gayyar munafukai ba.

Ina shiga na tadda mata an haɗa kai wata mai tallen turarukan wuta da magungunan mata ta shigo anata siya.

Sannunku ina wuninku?"

Daga cikin matan ƙannen Babangida na ɗakinsu Alawiyya da ita Alawiyyanne kaɗai suka amsa, sauran matan yayye, da ƴan ɗakin su Babangida babu wanda na isa kallon arziki sai dai kallon munafurci basui zaton zan fito haka fes dani ba. Gashi dama a kayan da Baba Malam ya siyo mana na kayan sallah harda takalmi da jaka su na saka.

MRS BUKHARI

Ina manyan mata masu capacityn  suke?  ku fito lambarku ce ta fito.

Ƴar uwa turaren wuta kike nema nau'ika daban_daban masu musulmin ƙamshi da kama muhallu? Ba itacen banza masu sanya gida ƙauri da hayaki kamar an kunna taohuwar bespa ba.

Matso gasu MRS  BUKHARI B4B GIDAN KAMSHI nazo miki da duk abinda kike buƙata na ƙamshi. Kama daga turarukan wuta irin na gidan alfarma. Zuwa humrori iri daban daban masu musulmin ƙamshi da riƙe jiki.

Bugu da ƙari muna da turarukan kaya, na fesawa dana turarar kaya.

Muna da kulaccam nau'i daban daban masu gyara jiki da lausasa  fata mata, ga kuma ƙamshi mai inganci.

Muna da turarukan tsugunno na musamman masu sirri Hajiyata

Muna da room freshener iri_iri

Muna da mopping mix masu kama waje.

Edit with WPS Office

Akwai turarukan kafet dana kujeru.

Sannan akwai box _ box  setika na Hajiyoyi masu ƙyallin goshi.

Muna da Amarya package.

Muna da uwargida package

Muna da maijego package

Muna bayar da sari ko a ƙasar waje kike, muna tura kaya

Saudiyya

Nijar

Ghana

Camaron

A duk ƙasar da kike kayanmu zai iso miki cikin aminci da yardar Allah.

Hajiya akwai Humrar matan aure wannan ta musamman ce.

Duk wani abu da kika sani na ƙamshi babu irin wanda bamu dashi a kamfaninmu.

Muna da turaruka designer na maza da mata wanda kamfaninmu ke bugawa Hajiya babu inda zaki je ki ci karo da mai irin ƙamshinki.

MRS BUKHARI B4B GIDAN KAMSHI TAZO MUKU DA DUK ABINDA KUKE SO NA KAMSHI HAJIYA.

KUNSAN KANURI MUNE KAMSHI DAMU AKE KOYI

SIYAN NAGARI MAIDA KUDI

MUNA MARABA DA MASU SIYAN ƊAYA KO SARI.

LAMBAR DA ZA'A SAMENI KAI TSAYE ITACE.

Wa.me/2348179523215

SAI NA JIKU

IDAN KAYA YA GAJI...

GAMMO MA YA GAJI

Edit with WPS Office

BADIAT IBRAHIM MRS BUKHARI B4B GIDAN KAMSHI

SHAFI NA ASHIRIN DA HUƊU

Bincike ya nuna sama da mutune  miliyon goma sha biyar ke shan muyagun ƙwayoyi a najeriya.

Hakan kuma ya jawo asarar rayuka, taɓarɓarewar tarbiyya. Ya haɓɓaka fitinu da manyan lefuka a arewacin najeriya dama ƙasar baki ɗaya.

Tun kafin zama ya gagaremu mu koma bacci da ido ɗaya a buɗe. Lokaci yayi da zamu haɗa ƙarfi da ƙarfe domin mu taimaka ma hukumar yaƙi da sha da fataucin miyagun ƙwayoyi.

Dan ganin mun kawar da wannan ta'asa dake shirin zame mana ruwan dare.

Shaye_shaye annobace ga al'umma.

Wannan saƙone daga hukumar yaƙi da sha da fataucin miyagun ƙwayoyi wato ( NDLEA)

Sanya kuɗin karatun a cikin wannan lambar asusun

0044442984

Buhari Ibrahim Ladan Gt bank

Lambar da zaku turo shaidar biya gasu kamar haka

08022059556

Ko kuma

08105932041

Masu son magana da marubuciyar kai tsaye kuma ga lambata

Wa.me/2348179523215

Edit with WPS Office

Subuwa:.

Harna shige ɓarayin Malama Babba ina jin idanu na kallona yu. Sauban babban yaron Sa'a naci karo dashi a tsaye da Mardiyya yana bata abu a leda. Ganina yasa yayi saurin gaisheni ya fice.

Hmm ajjiyar zuchiya kawai na sauke ina roƙon Allah kar yasa  Sauban  ya auri  Mardiyya kamar yadda Baba malam yace ya haɗa aurensu dan uwarshi ba yarda zata yi ba, nima Allah yana gani bazan yadda ba.

Inaji ina gani ba zan jefa ƴata cikin kunci ba. Shiga da sallama nayi ɗakin Malama Babba ƴan uwanta cike da ɗakin ƙanne da yayye dukka na sansu amman cikinsu babu wacce ta taɓa shiga ɗakina suna dai zuwa wajen matan Babangida. Yarana kab dana haifa ko barka bare suna.

Ina wuninku anyi Sallah lafiya?"

Na gaishe da matan ɗakin nai musu jam'u banda Sirikata dana gaisheta da ban

Su dai sun amsa amman ita cewa tayi dani.

"Sai yanzu ne kika ga damar zuwa kusan azahar kishiyarki tun bakwai take gidannan amman dake dodon naki baya nan shine sai yanzu kika ga damar zuwa. Ga ƴan aiki kin ajjiye da zasu girka miki ko"

Carab Yar Malama Babba tace.

"To Babba ai dole tazo war haka tana baƙin cikin mijinta ya auri aminiyarta sun tafi umara."

Murmusawa kawai nayi wannan ya faɗa ya cika wannan ta caɓe haka sukaita dai ƙananun maganganunmu na mata.

Ni dai dama na basu suka yi suka gama na sa kai na fita.

Wannan karon gefe guda na keɓe muka zauna ni da yarana babu wanda yai mun tayin abinci nima bansa akaba wallahi.

Sallar azahar da la'asar a ɗakin Malama ƙarama nayi anata hirar biki da irin malaman da za'a

Edit with WPS Office

gayyato.

Biyar nayi na haɗa kan yarana muka yi ma jama'ar gidan sallama muka tafi ni da ada sai bayan isha muke komawa gida. Na gaji da sarama kare ciyawa na dena tsoron kowa duk hukuncin da zasu ɗauka a kaina sun daɗe basu ɗauka ba a shirye nake da komai.

Bamu haɗu da Baba Malam da sauran mazan gidan ba sun tafi garinsu Ringim suma rana irin ta yau suke tafiya a gaggaisa da  dangi da ƴan uwa da abokan arziki basu suke dawowa ba sai dare. Mu kuma kaf surukan gidan Yaƴa da jikoki acan muke yin wunin babbar Sallah.

Washegari muka rankaya gida ni da yaran a tsakar gida muka tarar da kowa da kowa banda mazan gidan Maigogul ma baya nan wai suna biki a Abuja.

Dama ni duk Sallah da komai na girki nake tawowa sai muyi girkin iyaka ƴan ɗakinmu suma ƴan ɗakinsu Hauwa suyi girkinsu isu_isu.

Muna kan girkin anan aketa hirar biki da irin shagalin da zamu yi. Mun riga mun bada ɗinkunan lace da zamu yi ankonshi da ankon bikin duka dan harma ta kusan gamawa.

"Kinga Lolo ga fenti Gaza ya kawo mun wai in fenta a ɗakina gudunmawarshi kenan"

Dariya muka yi dukkanmu harda Rakiyan dake tsaye tana duba wasu tukwanen siyarwa da aka kawo mata.

Allah yasa bana sata bane, ina Gaza zai samo fenti?"

Baki Rakiya ta taɓe tace.

"Na satar ne ma. Ai bai ɓoye mun ba kinsan Gaza babu ruwanshi da ƙarya"

Buɗar bakin Hauwa dake zaune a kan kujerar tsugunno tana nenke ma yaranta kayansu tace.

"Dama ai ke kika lalatashi shi yasa yake kawo miki kayan sata ki saka hannu ki karɓa. Yara daga ƴan shaye_shaye sai ɗan daba sai ɓarawo, ga namamajo. Matan kuwa ba'a ma maganarsu"

Ai ina wuta Rakiya ta tsoma Hauwa ƙaramar magana tuni ta zama babba su Adama da Rahama suka haɗu dasu Layuza akaita gasar zagin juna da tone_tonen da ni banga amfaninsu ba.

Ina juya shinkafa data tsotse ina kallonsu. Sama da ƙasa Allah bai bani ikon cewa komai ba. Nadai san Hauwa akwaita da neman rigimar Rakiya ita ke takalota dan bata kaunar taga anyi zaman lafiya.

Sai da maƙota suka shigo raba wannan rikici ciki kuwa harda mahaifiyar ƴar shuwa.

Baƙin ciki goma da ashirin.

"Wai ku Rakiya sai yaushe zaku girma sai kace wasu karnuka kullum kuna cikin haushi?"

Edit with WPS Office

Adama tace.

"A_a MamaTala bari kar in miki rashin mutunci wallahi "

Rakiya tace.

"Adama ja gefe kiyi shiru. Ke Tala uwar gulma mai kutunguilar tsiya makira wacce ta hana mijinta sakat.

Wato kin shigone har gida ki yaɓa mun magana bayan wacce kike yowa tana shigowa har ciki gidannan?

Wallahi na sake ganin ƙafarki a gidannan kinga karnukan can?"

Ta nuna mata su da yatsa suna keji.

"To wallahi su zansa Gaza ya sakar miki su yagalgala miki agara.

Aurene ƴan Shuwa ta auri mijin Lolo hankalinku ya kwanta sai kisa mijinki kema ya sakeki kiyi zawarcin uban Babangidan tunda ku bakwa ramin kanku"

Naji daɗin abinda Rakiya tayi ma Mama Tala sosai. Babu shiri ta fita cikin naɗe tabarmar kunyarta da hauka.

Maƙota dai suka sasanta lamarin suka fita suna girgiza kai.

A tsakar gida muka ci abinci damu da yaran dukka.

Mata matan ƙananu aka haɗe musu. Yan matan Adama da Rahama ma aka haɗe musu, sai yara mazan ma suma a haɗe aka saka musu.

Sai bayan isha muka shigo gida duk a wahale ga laulayi dake addabata ga Khalid da yake damuna lallau sai mun haɗu ni kuma naƙi fur.

Washegari tun safe muka shiga wanki a tsakar gida bikin yarinyar Adama za'a soma tsirarsu sati dana Aisha, ga na gidansu Babangida  shi yasa muka soma rage aiyukanmu tun wuri dan da an soma biki babu zama.

Muna wankinnan Hamida ma tana tsakar gida a baranda tana yanka kayan ganye tana yi tana tashi tana shiga ɗaki ta dawo.

Hmmm ashe Babangida ne zasu dawo muna ɗaurayar wankin ƙarshe sai gashi Abokinshi Mustapha ya kawosu a motarshi da tarin tulin tsaraba rigi_rigi.

Kallonsu nayi na watsar naci gaba da shanyata suka zo suka wuce ni. Mustapha dai ya dakata mun gaisa kafin yabi bayansu zuwa part ɗin Yar Shuwa.

Ajjiyar zuchiya na sauke kawai na matse kayan dake hannuna ina shanya ina zancen zuchi.

Edit with WPS Office

Mun gama shanyar kenan Mardiyya na wanke wajen Aminu na wanke bokatan sai ga ƙannen Yar Shuwa da mahaifiyarsu  Mama Tala sun shigo. Suma suka wuce ni ƙannenta sai ɗaga hanci suke yi.

Oh duniya ƙawayenmu da mukai makaranta ma duk suka zo yima Yar shuwa sannu da dawowa washegari kenan.

Ni ko ina ɓarayina bana cikin sabgar kowa da yamma sai ga Babangida ya tako tinkis_ tinkis ya ɗaga labule ya dubeni na dubeshi na watsar.

Ya jima sosai yana kallona kafin naji yaja wata wawuyar ajjiyar zuchiya  to ta uban meye oho. yace.

"Kizo ki sameni a turakata yanzu Sabuwa ina da magana daku"

Kai kawai na gyaɗa halamar to, daman ni kaɗaice a falon ina zaune a ƙasa gama wayata da Rahama kenan tana sanar mun gobe za'a tafi jere.

Miƙewa nayi mayafin doguwar rigar dake jikina na warware na yana na fito.

Tun a bakin ƙofa naga takalma biyu. Da sallama na shiga na nemi ƙasa na zauna su du suna kujera ɗaya kaina na ƙasa bance uffan ba.

"To Alhamdulillah munje mun dawo. Ke Sabuwa bari in soma dake babu abunda zance miki sai godiya gantalinki kike fita son ranki da bananan. Shikenan ke har gobe kin kasa nutsuwa ki tsare kanki kenan ko me kike son kice mun. Yanzu har lalacewar tawa takai saidai kisa ƙafa ki fice ba zaki sanarmun ba ko me kike nufi ne?"

Cikin zuzutawa yake maganar yana bubbuga hannun kujera.

Kallon Hamida nayi nayi gajeren murmushi. Ba shiri tayi ƙasa da kanta. Saida na nutsa na saisaita kalamina kafin nace.

Ina sanarma Baba Malam in zan fita tunda dama zamanshi nake yi kuma naga shike ɗawainiyar ciyar damu da tufatar damu"

Babu hayaniya ko hargowa a muryata sam. Sai Babangida yayi tsam ya rasa mai zaice kuma. Kuma babu wani faɗama Baba Malam da nake yi gaban kaina nake yi kuma na faɗane dan nima in gasa mishi.

"Lallai Lolo so kike kice Sirikin naki kike aure ko me? Jannaty kana fa jin abinda take faɗa ai wannan maganar da girma take"

Kallonta nayi tsab itama ta kalleni tayi mun murmushin mugunta.

Babangida yafi minti talatin wallahi yana faɗa da zage_zage kamar zai dokeni. Wai har wani yinƙurowa yayi fa zai dira a wuyana su Hamida suka rirriƙeshi suna bashi haƙuri kamar wanda

Edit with WPS Office

jaki ya yar dashi.

Miƙewa nayi tsaye nace. Inajin bakina yana ciccijewa da kanshi. Nace dashi cikin muryar dabanci

Babangida kenan. Halan ka mance wacece Sabuwa ka kuma mance a yadda ka tsintoni ko? Kai sanin kanka ne kasan a doke bazan daku a wajenka ba. In ka dokeni na ƙyaleka ka tabbatar darajar aure kawai kaci ko ince darajar Yaƴanka amman in ba haka ba kasan zan iya saranka wallahi. Kai Allah wuya ta tafa wuya a manunfashi, wuya a gida, wuya a daji dan abu ta kazan.. Ku kuma tsofaffin makirai gaku ga rijalu akwai ranar ƙin dillanci. Kuma ku bini a hankali in ba haka ba na farɗe yarinya"

Tsaki na buga na fice ina  bonsin irin na ƴan iska. hawayen baƙin cikin wannan ƙaddararren auren nake zubarwa.

Ina tafe na jiyo gudu tib_tib_tib daga bayana ban aune ba Babangida ya rarumeni muka tafi taga_taga muka faɗi rib a daidai bakin part ɗina gefen cikina ya daki wayar data raba part ɗina sai jini. Shi kuma Babangida kanshi ya doki gini rib take wajen yayi ƙulu.

Matanshi suka rufu a kanshi, ni kuma da dabara na rarrafa da rarrafe na shiga part ɗina dan na kasa miƙewa tsaye marata kamar zata tsage. Allah ne ya sosu da ace na miƙe wallahi ranar da sai kowa yasan wacece Sabuwa.

Har yamma jikina babu daɗi har rawa yake yi mun, jinin dai kaɗanne ya zuba.

Da taimakon Mardiyya muka tafi asibiti cikin dai da nake murnar ya zube likitoci sun tabbatarmun bai zube ba yananan daram na dai bugu ne da yawa.

Magunguna suka bani da kuma umarnin kwanciya kar in yi aikin komai na tsawon satika ( bed rest).

Na dai wuni ranar a kwance.

Da daddare ina shan tea sai ga Malama Babba ta shigo babu ko sallama Sa'a uwar maras mutunci na biye da'ita a baya.

Zazzaunawa suka yi yara suka gaishesu a cunkushe suka amsa musu.

"Kuje ciki ku bamu waje maza"

Malama Babba ta kora yaran ciki.

"Sa'a kira Babangida yazo shi da Yar Shuwa ki sanar musu mun iso. Yau zaki ga yadda uwa take rama ma ɗanta duka dan ubanki wannan kawalin maras kamun kai da rashin dattaku"

Sa'a ta ɗaga wayarta ta kira Babangida.

Edit with WPS Office

"Kaci kari gamu a falon  fara da kiyashi kazo ka sakemu. Ka tawo da anty SHUWA."

Ni dai ina zaune, ban dena shan tea na ba dan tunsa na dawo asibity banci komai ba. Duk abinda naci sai ya dawo mun. Sama da ƙasa Allah bai bani ikon ko gaishesu ba.

Basu fi minty biyar ba sai gasu sun shigo.

Makirar a gaban Malama Babba ta gurfana tana gaishesu da wani irin ladabin da ko uwarta da ubanta bata taɓa yima irinsu ba.

Malama Babba harda rungumeta tanata shi mata albarka wai taga tsarabar Umara akwati guda.

Sa'a tayi mata godiya sosai dan suma tace tayi ma yaranta kab tsaraba.

Ni dai ina zaune ina ganin bariki.

"To bari muyi abinda ya kawo mu dan malam da ƙyar ya yadda muka tawo.

Ke Sabuwa wato har rashin mutuncin naki da rashin tarbiyyarki takai ki saka hannu ki daki Babangida. Banda kwara musu miya da kika yi? Sannan shi malam ya zama sa'anki kenan dan ubanki da zaki dinga kama sunan shi a maganarki, ko dan kinga Malam yayi rantsuwar sai Babangida ya zauna dake ne, koko a_a dai sabida kinga shi bai fiye ganin lefinki bane? Yau sai kin faɗa mun"

Carab Babangida yace.

"Rakiya ma fa suna dambe da Maigogul har waje wallahi ga Shuwa ita take faɗa mini Malama. Ni dai dan Allah ki roƙi Malam Baba ya taimakeni in yada kwallon mangwaro in huta da ƙuda rayuwar dabancin da tayi abaya take son ta dawo dashi ta gurɓatamun kan iyali.

Wallahi albarkacin Malam Baba take ci yau da irin dukan da zanyi mata ai bana wasa bane." Kuma kunsan Allah tsorata yayi fa.

Yana yi yana zazzare idanu Irinna cikakkun baduniyawa.

"Ai Kaci kari mu da kanmu zamu jibgeta taje mu ta kai ƙararmu wajen Malam Baban."

Cewar Sa'a data miƙe.

Nima miƙewa nayi tsaye nace. Ina jijjigewa idanuna na juyawa.

Wallahi kar ku sake wata ta matso inda nake dan zan basu mamaki. Wallahi Allah Babangida ka faɗa musu. Yanzu na dena yadda ku taka ni. Tunda rashin kunyar kuke so kun samu. Idan kaya ya gaji gammo ma ya gaji. Auren ƙaddara kawai dame ake so inji.

Wannan abun ai Babangida yafi kowa lefi kuma zanje in sanarma Malam Baba yai mun tsakani daku na gaji.

Edit with WPS Office

Ya isheni baƙin cikin da kuke cunkusamun tsawon shekaru fin goma sha. A yanzu wallahi bazan ɗauka ba duk wanda ya nuna mun hannu saina karya yatsan. Duk wanda yayi mun maganar banza zan mayar mishi kamar yadda madubi yake nuno hoton fuska. Dani kuke wasa. Zan nuna muku babu tarbiyya a gidanmu in tabbatar muku daga jikin kawali na fito, kuma duk yadda kuka kai ga aibantashi kun haihu da tsatsanshi. Ke Sa'a kin san karona dake wallahi. Dan in saka kanki gabas in yanka nifa ba komai bane ihe Batun saki da kuke yi ai ni a shirye nake inyi zawarci musamman inna tuno bani kaɗai zan yi zawarcin ba harda Saratu a zawarcin" Na ambaci sunan Malama Babba na asali.

Ina gamawa na wuce ɗakina  na saki kukan baƙin ciki. Jikina yana ta rawa zuchiyata tana ta tunzurani akan in rarumo wuka ko sanda in rakasu har waje.

Su Malama Babba yaya suka yi, ya suka ƙare tun ina jiyo tijarar Babangida har na dena jiyowa.

Lamo na kwanta na kira Khalid ya ɗebe mun kewar baƙin cikin da nake ciki. Mun fi ƙarfe ɗayan dare muna chart na sakin layi ni dashi baccine ya sureni wayar ta sulale a hannuna a lokacin bidiyo call muke yi dashi.

Washegari na tashi jikina ba ƙarfi hawan jinina ya tashi nice jiri nice ciwon kai, ga marata sai mintsinina take yi. Wanka kawai nayi, Mardiyya ita tai musu kayan kari goma nayi nai musu sallama na fito."

A tsakar gida na tadda Babangida yana wankin mota Usama na tsaye a wajenshi da biskit a hannunshi. A tunaninshi zanje inda yake harma in faɗa mishi inda zani. Ni kuma nayi alƙawarin na dena tambayar unguwa a wajenshi.

"Ke Sabuwa ina zaki je haka gaba gaɗi babu neman izini?"

A lokacin harna buɗe get zan fice.

Ko juyowa banyi ba, sai gashi fuu kamar kububuwa yazo ya sha gabana.

"Wai ina zaki nace Sabuwa?"

"Gidan Rahama zani"

"Da izinin wa, sannan me akeyi a gidan Rahaman da zaki je?"

Da izinin Malam Baba kasan zamanshi nake yi Aurar da ƴarta zata yi"

Duk na game na bashi amsar fuskata a murtuke. Dariya yayi yace.

"Hmmm Allah sarki wani zai ɗebi kara da kiyashi ɗaukar marar sani. Wata ƙila azal ce ma ta haushi kamar dai ni."

Kawai kuwa ai yama ɗauka sai dai kada a kuma. Bani hanya ko?"

Edit with WPS Office

Na firfito mishi da asalin idanuna ya gansu.

A wajen na tafi na barshi sama da ƙasa ban tanka mishi ba. Yanata kiran sunana

"Lolo sissss_sisss Lolo Baby my love ji mana ƴan mata minti ɗaya"

Yana yi yana dariya da halama daɗine yai mishi yawa dai. A haka na lallaɓa zuwa gidan Rahama. A tsakar gida na tadda matan gidan da tarkacen yaransu. Ga wasu gun_gun mata dangin mijinsu da suka tawo daga ƙauye dasu da ƴaƴansu sai gidan ya sake kacamewa ga tarkacen butoci, gwanduna, bokatai da shanyar tsummokinsu a bishiya.

Gaggaisawa akayi na faɗa ɗakin Rahama. Hanhai labulenta na saman ƙofa an ratayeshi su Adama anata bayani.

Salaha yaushe kika zo babu ko labari?"

Na tambayeta ina ture kaya a kujera dan in samu inda zan tsugunna nima.

"Jiya kusan goman dare na iso. Mota ce ta lalace mana a hanya."

Nan muka shiga gaggaisawa dai.

Waye a kwance a gado Rahama ta juya baya?"

Na tambayi Rahama. Baki ta taɓe tace.

"Waye kuwa in ba zahiya ba. Kin ganta yarinya sai son kwanan waje. Inta dawo da safe bata da wani aiki sai bacci data tashi ta aika a soyo mata ƙwai da taliyar ƴan yara a teburin me shayi. To kwana biyunnan dai zazzaɓi tace mun tana yi"

Ohh ni Sabuwa Allah ka kawo mana ɗoki ka kawo wata silar shiriyar kowa ta hanyar da zato bai zata ba.

Adama ce ta katse shiruna da cewa.

"Lolo tunda dai kinzo inaga mu kama hanya muje titi mu nemo motar ɗiban kaya kawai kayan suna gida can wajen Rakiya.

Rankayawa muka yi muka nemo mota, saida ta kwashe kayayyakin kitchen da Amarya ta tara a maƙota da ɗan tarkacen wajen Rahama kafin muka kama hanya. Kishiyoyin Rahama da dangin mijinsu kuma suka shiga ƙaramar motar da abokan ango suka kawo suka wuce can gidan Amarya, mu kuma muna gaba a abin hawa motar kaya na bayanmu har zuwa gida.

Gaskiya yarinyar taci sa'ar kujeru manya sosai gasu basu sha jiki ba dan sunyi sabunta fiye da na Aisha ma. Ga gadon ma babu laifi sib ɗince dai mai ƙofa biyu ƙaramace sosai.

Rakiya ga wata sib mai huɗu ai da ita aka bayar zaifi wannan tayi ƙanƙanta."

Edit with WPS Office

Rakiya ta harareni tace.

"Iyakar kuɗinsu fa kenan wannan in ita suke so sai sunyi cikon kusan dubu goma fa"

To Rakiya a bata wannan ɗin zan cika musu"

Hakan kuwa akayi muka tattare kaya harda Hauwa muka nufi gidan Amarya.

A tsakar gidan muka tarar da su Maman Tsalha a tsaitsaye cirko_cirko. Adama tace.

"Kuma lafiya ku kai tsaye haka?"

"Maman Tsalha tace ɗakinne zafi yayi yawa, amman tunda kunzo ai saimu shiga mu duka ko?"

Maza ne suka soma dire kujeru a tsakar gidan, ai nan take suka tsure basu yi tunanin haka ba sam. Leda muka soma shinfiɗawa a uwar ɗakin muka kafa gado, tuni na nemi waje na zauna dan jiri da amai na soma ji warin fentin ɗakin Amarya ya dinga hawa kaina.

MRS BUKHARI.

Ina manyan mata masu capacityn suke? ku fito lambarku ce ta fito.

Yar uwa turaren wuta kike nema nau'ika daban_daban masu musulmin ƙamshi da kama muhallu? Ba itacen banza masu sanya gida ƙauri da hayaki kamar an kunna taohuwar bespa ba.

Matso gasu MRS BUKHARI B4B GIDAN KAMSHI nazo miki da duk abinda kike buƙata na ƙamshi. Kama daga turarukan wuta irin na gidan alfarma. Zuwa humrori iri daban daban masu musulmin ƙamshi da riƙe jiki.

Bugu da ƙari muna da turarukan kaya, na fesawa dana turara kaya.

Muna da kulaccam nau'i daban daban masu gyara jiki da lausasa fata mata, ga kuma ƙamshi mai inganci.

Muna da turarukan tsugunno na musamman masu sirri Hajiyata

Muna da room freshener iri_iri

Muna da mopping mix masu kama waje.

Akwai turarukan kafet dana kujeru.

Sannan akwai box _ box setika na Hajiyoyi masu ƙyallin goshi.

Muna da Amarya package.

Muna da uwargida package

Edit with WPS Office

Muna da maijego package

Muna bayar da sari ko a ƙasar waje kike, muna tura kaya

Saudiyya

Nijar

Ghana

Camaron

A duk ƙasar da kike kayanmu zai iso miki cikin aminci da yardar Allah.

Hajiya akwai Humrar matan aure wannan ta musamman ce.

Duk wani abu da kika sani na ƙamshi babu irin wanda bamu dashi a kamfaninmu.

Muna da turaruka designer na maza da mata wanda kamfaninmu ke bugawa Hajiya babu inda zaki je ki ci karo da mai irin ƙamshinki.

MRS BUKHARI B4B GIDAN KAMSHI TAZO MUKU DA DUK ABINDA KUKE SO NA KAMSHI HAJIYA.

KUNSAN KANURI MUNE KAMSHI DAMU AKE KOYI

SIYAN NAGARI MAIDA KUDI

MUNA MARABA DA MASU SIYAN ƊAYA KO SARI.

LAMBAR DA ZA'A SAMENI KAI TSAYE ITACE.

Wa.me/2348179523215

SAI NA JIKU

IDAN KAYA YA GAJI...

GAMMO MA YA GAJI

BADIAT IBRAHIM MRS BUKHARI B4B GIDAN KAMSHI

SHAFI NA ASHIRIN DA BIYAR

Edit with WPS Office

TSOKACI

WANNAN LABARIN LABARINE DAYA FARU A GASKE BA KIRKIRARREN LABARI BANE.

MASU CEWA KAR SABUWA TA HAIHU, KO KUMA IN SA CIKIN YA ZAMA NA BABANGIDA. BANI DA IKON JUYA KOMAI.

ABINDA NAKE SO KU FAHIMTA SHI LABARI DARASIN CIKI SHINE ABUN KALLO BAWAI DOLE SAI LABARI YAZO DAI_DAI DA RA'AYOYINMU BA. BA KUMA DOLE SAI TAURARUWAR LABARIN TA ZAMA YADDA KUKE BUKATA BA. SAKONE AKESO A ISAR RUBUTU BA ZALLAN NISHAƊI BANE, FAƊAKARWANE GAMI DA HANNUNKA MAI SANDA, HARMA DA GYARA KAYANKA.

NAGODE DA FATAN KUN FAHIMTA?"

*LABARIN SABUWA YAJE INDA KAFAFUNA BASU ISA SU TAKA BA. INA SAMUN KIRA DAGA GARI_GARI JIYA DAGA CANADA WATA TA KIRANI A LITTAFINA TA ƊAUKI NUMBER NA HAR ALKHAIRI TAYI MUN MAI GWAƁI NAJI DAƊI SOSAI. HAJIYA INA GODIYA MARAR ADADI.

MASOYAN ALKALAMINA MASU BIBIYAR AIKINA SON SO⚔⚔🗡🗡🤺CAU CAU WUYA A GIDA WUYA A DAJI  WUYA A TYPING 😆

Bincike ya nuna sama da mutune   miliyon goma sha biyar ke shan muyagun ƙwayoyi a najeriya.

Hakan kuma ya jawo asarar rayuka, taɓarɓarewar tarbiyya. Ya haɓɓaka fitinu da manyan lefuka a arewacin najeriya dama ƙasar baki ɗaya.

Tun kafin zama ya gagaremu mu koma bacci da ido ɗaya a buɗe. Lokaci yayi da zamu haɗa ƙarfi da ƙarfe domin mu taimaka ma hukumar yaƙi da sha da fataucin miyagun ƙwayoyi.

Dan ganin mun kawar da wannan ta'asa dake shirin zame mana ruwan dare.

Shaye_shaye annobace ga al'umma.

Wannan saƙone daga hukumar yaki da sha da fataucin miyagun ƙwayoyi wato ( NDLEA)

Sanya kuɗin karatun a cikin wannan lambar asusun

Edit with WPS Office

0044442984

Buhari Ibrahim Ladan Gt bank

Lambar da zaku turo shaidar biya gasu kamar haka

08022059556

Ko kuma

08105932041

Masu son magana da marubuciyar kai tsaye kuma ga lambata

Wa.me/2348179523215

Babangida:.

Yana kwance a gado yanata baccinshi hankali kwance.

Yar Shuwa ta shigo da sallamarta taci kwalliya ta ɗakko wannan kwalli ta zirara a idanunta, magani ɗan matsi ma ta yi matsin dashi, yau take son ta tatsi kuɗin kasuwancinta. Tana cikin group ɗin manyan HAJIYOYI tana jin yadda suke wasa da kuɗi abun na burgeta. Gashi ɗazu yana tsakar gida yana wankin mota bayan Sabuwa ta fita Yar Shuwa  ta fito ta taddashi yana waya da halama kuɗi ya samu dan so yake ya ɗaura sama a gidanshi. Bayan ya gama wayar ne yake sanar mata so yake ya saka kuɗi sosai ya gyara gidanshi. Shine itama take son ta kwashi rabonta.

"Jannaty wai har yanzu bacci kake yi ne? Kaga fa wayarka Mustapha yana ta faman kiranka."

Edit with WPS Office

A zabure ya miƙe zaune yayi saurin karɓe wayar daga hannunta ya ɗaga tare da karawa a kunnenshi.

"Abokina Yaya akayine in kaji kira ta samu"

Mustapha daga cikin wayar ya amsa mishi da cewar.

"Kai dai mu haɗu da yamma a majalisa akwai labari mai zafi dolenka ka bani tukuici Allah"

Kur Yar Shuwa tayi mishi da idanu. Shima idanunta yake kallo yana waya yana murza yatsunta yana lumshe idanushi.

Maganin data saka tana din yadda yake matseta yana sauke wayar yace.

"Kinyi kyau sosai. Kin ganki kamar wata hamshaƙiyar ƴar kasuwa mai kuɗi shaƙe a asusu"

Tana jin haka ta faɗa jikinshi, dama dai shi abinda yake da muradi kenan masauki lafiyayye ya bata yana shafar sumar kanta. A hankali har abinda zai gudana ya gudana fiye da yadda tayi zaton maganin haka ta gani. Babangida birkice mata yayi ya kuma liƙe mata sosai da ƙyar ta yakiceshi dan ba ƙaramin gajiyar da'ita yayi ba.

"Jannaty kuɗi nake so ka bani in soma jujjuyawa rashin sana'arnan ya isheni wallahi.

Take yace.

"To kamar nawa kike ganin zai isheki ki soma sana'ar Habibaty?"

Idanu ta zare tare da buɗe baki. A ranta take jinjina ma wannan kwalli. A shagwaɓe tace.

"Inaga ko miliyan uku ai zata isa"

Kwarewa yayi babu shiri ya ɗagata a jikinshi ya shiga tari.

"Bani ruwa maza. Zan mutu"

A guje ta nufi kitchen ta ɗebo mishi ruwa.

"Hmm ai wallahi sai sai ka mutu amman wannan kuɗi sai ka fito dasu, ko arone sai kayi Allah.

Da sauri ta iso inda yake ta bashi ruwan ya sha sosai.

"Kin ko san yawa da girman miliyan uku kuwa? To ni Habibaty sai in ɗauki miliyan uku wai in baki kiyi kasuwanci. Me ma zaki siya haka ne?"

Rai ta haɗe ta harɗe hannayenta a ƙirjinta.

"Dubai nake so muje ni da matar abokin ka  Hajiya Turai in soma siyo dogayen riguna Jannaty. Nifa na ɗauka nafi ƙarfin hakan a wajenka. Wallahi ni harna faɗa mata dan dama saura sati biyu ta koma nace mata tare zamu je"

Edit with WPS Office

Zufa ce ta shiga karyo mishi miliyan uku fa ba ƙananun kuɗaɗe bane kuma ba nan kusa suke ba. Lissafi ya shiga yi in ƙarafai ko robobi ya siya na miliyan ukunnan zai samu ribar kusan milliyan ɗaya da ɗoriya.

Cikin ƙudurar Allah sai ya samu kanshi da amincewa akan zai tura mata kuɗin. Zazzaɓi ne ma ya lulluɓeshi babu shiri ya shiga bargo yana rawar ɗari tsabar yawan kuɗin

Haka dai dole ya tura mata wannan kuɗaɗe a account bayan ya tura ne kuma yaji kamar ya doki kanshi. Gashi shi ba abun yace ta dawo mishi da kuɗin ba kimarshi ta zube ba.

Babu shiri ya shiga bayi ya tsabtace jikinshi ya fice cikin haushi.

A cikin mota ta sameshi dafe da ƙirjinshi.

"Jannaty fita zaka yi ne wai?"

Ba tare daya kalleta ba yace.

"Fita zanyi"

Ita kuma sai wani murmushi take yi mishi.

"To me zan girka da daddare?"

Haɗe rai ya sake yi kana yace.

"Ai yau a kamfani zan kwana akwai mota biyu da za'a loda ma kaya na miliyoyin kuɗi gobe asussuba zasu wuce ikko to Dole in kasance a wajen"

A ranta tace.

"Ko kuma zata tafi wajen ƴan matanka kaje ka kwana kana aikin da bai dace ba dai. Maza kenan basu da aiki sai sharara ƙarya. To ni ina ma ruwana wallahi yabi duk karuwan garin.

A fili kuma tace.

"To Shikenan Allah ya kaimu goben. Ka kula mun da kan ka Jannaty"

Har sai da motarshi ta ɓace kafin ta dena mishi adabo.

Tana shiga ɗaki ta shiga waya da Hajiya Turai tana bata labarin aikin kwalli.

Dariyar manyan mata tayi tace.

"In banda abinki me miliyan uku zata yi miki Yar Shuwa. Ke da zaki karɓi manyan kuɗi a hannunshi kamar miliyan ashirin ko goma sha biyar. To ai ko kwallin da maganin kuɗinsu yafi kuɗin da kika karɓa, kin dai mun asarar magani kawai. Miliyan ukun ce har sai kin saka kwalli?"

"Hmmm Hajiya Turai da yaya na ɓamɓaro wannan ɗinma. Yanzu ma fishi yasa ya fice a gidan fa

Edit with WPS Office

ya nufi kamfani."

Dariya suka saka harda shewa. Hajiya Turai tace to zata arama Yar Shuwan miliyan uku ya zama miliyan shida shine zata samu kaya masu yawa. Daga ƙarshe bayan sun gama tsara yadda zasu yi tafiyar sai sukai ma juna sallama."

Babangida daya fita gidan Sumy ya wuce kai tsaye.

Acan ya ƙarashe wuninshi. Da yamma ya sha wanka ya nufi majalisarsu.

Mustapha na hango Babangida ya soma dariya. Shima dariyar dai yake yi mishi.

"Wai wanne albishirine wannan Mustapha. Ko dai aure zaka yi ne?"

Musbahu yace.

"Ko kuma kaine zaka cika she ta huɗun ba"

Dariya suka yi Babangida ya ba Musbahu hannu suka tafa.

"Kasan yau wai wa na gani ne Babangida a cikin gari?"

Muskutawa yayi ya gyara zamanshi.

"Wa ka gani to na tambayeka"

Hahaha abokina nutsu naga duk ka tsagu. Ramatu na gani. Tsohuwar budurwarka ɗiyan tsohon alƙali daya hana ka auren ƴarshi lokacin kana mitsiyacinka"

Kai Babangida ya girgiza fuskarshi ta canja yace.

"Uhm uhm hum Ramatu Alƙali zaka ce mun Hala sai mai hali. Wato Mustapha har gaba da abada bazan iya dena son Hala ba. Wato yarinyar ta haɗu ne me zafi ce sosai. Babanta ya kwabsa mun. Duk da dai tun farko ba da aure nake nemanta ba, zafi dai ake ragewa da'ita. Gata da biyayya duk hotel ɗin da nace tazo ta same ni sai yarinyarnan ta zo."

Musbahu yace.

"Kai mugu. Ya yarinya da aurenta zaka dinga tuno baya kuma. Wai Mustapha menene hikimar ma sanar mishi kaga Hala ne? Ka fa san irin holewar da suka yi tare, kuma yanzu da aurenta"

Mustapha yace.

"Sabida ta zama bazawara aurenta wata biyar da mutuwarshi. Kai Babangida kai kaga yadda Ramatu Hala ta haɓaka ta haɗa kayan Atata kuwa? Da gani daga hannun mai arziki ta fito, tayi

Edit with WPS Office

kyau ta sake haske"

Ai miƙewa Babangida yayi cak.

"In ce dai ka amshi lambarta ba gaisawa kawai kuka yi ka wuce ba dan nasan halinka sarai?

Jikin Babangida har ɓari yake yi. Mustapha da ragowar abokansu nan suka shiga aikin ƙyaƙyata dariya.

Shima Babangidan dariyar yake yi.

"Dan Allah bar ja mun rai Mustapha ka karɓo mun lambarta ne?"

"Na karɓo kaima kasan bazan yi wasa da damar ba.

Amman yanzu jira aurenta zaka yi, ko kuma waccan rayuwar zaku kuma afkawa?"

Babangida yana daga tsaye yace.

"Ina irin su Ramatu basu da yawa sam a duniya. Wuff zanyi da'ita gaskiya, in kaita gida in killaceta ya fiye mun?"

Nan Mustapha ya ba Babangida lambar wayar Ramatu. Take ya kirata ya sakata a hans free.

Ai kuwa ya samu tarba me kyau. Harma sun yi alƙawarin zuwa taran dare su haɗu a gidan wani cin abinci.

Ai kuwa dai hakan akayi.

A wannan haɗuwar tasu Babangida ya tsara Ramatu iyakar tsaruwa harta amince mishi a karo na biyu. Tare da sharaɗin ita ko sun yi Aure tana da gidanta sai dai ta zauna a ciki ranar kwananta ya dinga zuwar mata."

"Ai girmanki Hala ya fi hakan a wajena. Ko a baya na soki sosai mahaifinki ne yai mana tsakani. Ina fatan bazai zame mana matsala ba a tafiyarmu ta biyu ba ko?"

Dariyar manyan mata tayi kawai.

"Baba Allah yayi mishi rasuwa. Ko yana raye ai ka mallaki abinda akan shi a baya ya hana ka aurena. Sannan kai ka mance ni bazawarace ina da ƴancin zaɓarma kaina miji"

Jus ya kurɓa yace.

"Hakane. Allah ya jiƙan Baba. Yanzu dai bani labarin yaranki nawa, sannan yaya akayi aurenki ya mutu?"

Sai da tayi dariya sosai. Shi kuma Babangida shagaltuwa yayi da fararen haƙoranta.

"Babu laifin tsaye bare na zaune. Ni mijina yana kuka ya sake ni. Mahaifiyarshi ce ta matsa ya

Edit with WPS Office

sake ni sabida bana haihuwa" take sai idanunta ya kawo ruwa.

"Da fatan kai zaka juri zama da marar haihuwa tunda kana da wasu matan?"

Kai ya gyaɗa mata.

"Sosai kuwa ai ni hakan bai da matsala asalima naji daɗin hakan. Yaushe kike ganin za'ai auren?"

"Kai B House sai kace wani gwauro irin wannan zumuɗin"

Murmusawa yayi yace.

"To me za'a jira. Ko dai baki gaji da karɓe ma zawarawa kuɗinsu bane kina maganar gwauranci, marabata da gwauraye ai kaɗanne ka tara mata babu fasali babu hankali basu iya komai ba fa."

Sai da ta harareshi irin na soyayya kana tace.

"Nan da sati biyu ma a ɗaura in ka shirya"

Teburin gabansu ya doka tare da ƙanƙance idanu yace.

"Na shirya Allah ya nuna mana."

Da wannan matsayar sukai sallama wajajen sha ɗayan dare.

Babangida yana murza mota zuchiyarshi fal tunanin yaya zai tunkari gida da batun aurenshi. Sannan in Sumy taji ya cike gurbin da yake ta ƙaryar nata ne yaya zai yi da ita. Kuma yasan sarai ƴar hau ce sai ta sakar mishi ɓera a yayi.

Da wannan tunane tunanen ya isa wajen Sumy.

Washegari ya nufi gida cike da ɓacin rai. Ganin irin kwalliyar da irin tarbar daya samu tuni ya mance kanshi ma."

SABUWA:.

kafin azahar sai ga dangin maza niki_ niki da tuwonsu na shinkafa miyar kuɓewa bushasshiya babu kifi balle nama sai ruwa pure water leda biyu.

Ni da su Adama dai sai kallon_kallo na mamaki. Kishiyoyin Rahama kuwa ransu fes har suna shewa.

Edit with WPS Office

To ni dai abinka da mai juna Adama na zuzzuba tuwonnan raina ya biya. Ai kuwa naci sosai dan har guzirinshi ma nace zanyi.

Wajajen bayan la'asar muka kammala jera komai. Kujera 1 sitter guda ɗaya bata samu shiga ba. Mun so ajjiyewa ma a uwar ɗaki ta zauna dai amman ta cike ɗakin.

"Lolo ni ina ganin a saka kujerar a haka a falon. Kar a raba kujerar da ƴan uwanta, kinsan dai aka kai ɗakin Rahama yaranta ne zasu lahanta a banza"

Cewar Saliha kenan. Adama tace.

"Ato ko a sata ta wajen ƙofar shiga uwar ɗakin. Siririyar hanya ce dai zatai ragowa in aka girketa anan. Amman ayi hakan kawai mu samu mu tafi, gobe ma akwai fa karɓan masu kawo kayan akwati."

Mayar da kujerar da har mun fito da'ita tsakar gida muka yi, aka ajjiyeta a falo ta sake takure falon, ga takura in za'a shiga uwar ɗakin.

Sallama mu kai ma bataliyar matan gidan. Ni bamma koma gidan Rahama ba a hanya muka rabu akan sai zuwa goben.

Ina shiga gida ko zama bam ba sai ga yara sun shigo.

Taliya na ɓararraka musu, ni kuma na ɗumame tuwona na cinye tas, kafin na wuce ɗaki nayi Sallah.

Washegari dai sai na kira  Baba Malam a waya bayan mun gaisa sai nake shaida mishi an shiga bikin yarinyar Rahama kuma zan dinga zuwa, ana gamawa ma zamu shiga bikin A'isha.

"To Shikenan Sabuwa zan kira Babangida yanzu in sanar dashi. Kema kuma ki sanar mishi. Ni dai nayi miki izini kije. Sannan ki yi haquri ki gaiyaci abokan zamanki suje miki bikin na ƙanwar taki. Muma Maigogul ya kawo mana alawa da katin gaiyata, dani za'a ɗaura auren su Malama da su Sa'a ma duk zasu zo"

Ni dama nasan  abinda zaice kenan. Duk da banso na gaiyaci wasu Hamida ba gayyar gulma. Amman babu damuwa zan gaiyacesu albarkacin Baba Malam.

Godiya nayi mishi na ajjiye wayata.

Yau sai sha ɗayan rana na fice, Babangida dai bai kwana a gidan ba, ko tafiya yayi oho dai.

Haka dai mukaita sha'anin biki. Masu kawo akwati sun kawo akwatin su guda ɗaya babu laifi ta samu kaya daidai gwargwado.

Ranar sakun lalle gida ya ɗinke da jama'a sosai. Dangin maigogul da dangin Rakiya duk sun zo. Dama sun tawo bikin A'isha ne, kasancewar sati ɗaya ne a tsakaninsu yasa suka zo da wuri.

Edit with WPS Office

Haka dai aka gama wannan hidimar biki aka kai Amarya gidanta. Su Mardiyya har dasu a cikin ƙawayen Amarya."

Bayan mun gama wannan kuma muka shiga tsara yadda zamu soma bikin A'isha dan za'ayi shagulgula masu yawa.

Ranar laraba aka soma biki duk da dai na ƙawayenta ne kuma a nan falona suke son yi kasancewar yana da girma.

Baba Malam na kira a waya na shaida mishi.

Shima Babangidan duk da bana ganin motarshi nayi mishi text akan za'ayi bikin a nan gidana.

Tun safe mu dasu Adama muke yanka kayan marmari da Aisha ta kawo mana. Dukka ƴan ɗakinmu muna tare, a maza kuma Uzairu zuchiyata ne kawai yazo yana tare damu yanata yankan kankana. Bakinshi kuwa duk sanda zan kalleshi zanga a cike da kankana

Saliha da Rahama kuma suna kitchen suna ta tuyar kayan fulawa da naman kaza. Maman Safarau tun safe ta shigo taya mu aiki.

Hamida dai ta leƙo da sallamarta.

"Ah umman Aminu biki za'ayi a gidanne?"

Ta tambaya tana yashe bakinta.

Adama ce tace.

"Wallahi kuwa biki zamu yi na ƙanwarmu. Kinga ga katinku ma ke da Amaryarku dama jira nake inna gaggama aikina in leƙa in baku.

Muna gaiyatarku biki, ga shagulgulan bikin ma in zaku zo mana muna so"

Da murnarta ta sa hannu ta karɓa tana dubawa.

"Ahh ai damu za'ayi komai in sha Allah. Wanda za'ayi yau ma naga adireshin gidannan ne zamu leƙo. Umman Aminu Allah ya sanya alkhairi. Ina za'a kai amaryar?"

Ɗan guntun murmushi nayi mai ɗauke da fassarori nace.

Kaduna zamu kaiita"

Baki ta buɗe tace.

"Ahh ashe nisa zata yi. Kuma zaki je kema kai Amaryar naga kamar baki da lafiya ma"

Hamida uwar gulma kenan.

Lafiya ta ƙalau. Dani za'a kaita in sha Allah "

Edit with WPS Office

Ina gama fadar haka nayi wucewata kitchen na barta a tsaye. Da gulmar ma bata isheta ba sai ta shigo ta shiga taya Maman Safarau jera yankakkun kayan marmarinnan a babban firjina dake gefen ƙofar shigowa kitchen ɗina.

"Maman Aminu sauran zamu saka a firizata nan ɗin ya cika kuma ko rabi ba'a saka ba"

Cewar Maman Safarau. Tana da manyan firiza har biyu a tsakar gida, tana sana'ar sai da kayan ruwa da lokacin zafi.

To Maman Safarau babu damuwa. Salaha ke da Labbai kuje ku tayata aje a jejjera Uzairu zuchiyata ma ya tayaku"

Hamida tayi carab tace.

"To muje mana nima in taya ku"

Ai kuwa da itan aka rankaya aka tafi. Adama ce ta same ni a kitchen ina zuzzuba kayan fulawa a cikin robibin ci ka yar masu murfi.

"Ke Lolo haka kishiyarki tayi kos a munafurci wai? Ai bari kiga da kaina zanje in sanar ma Yar Shuwa bikin dan kar taki faɗa mata. Ko babu komai an fita ko babu soso da sabulu."

A_a Adama da kin bari ni wallahi banyi niyyar sanar musu da wani biki ba. Ita Hamida munafurcine zaisa dole zata je biki. Ita kuma waccan nasan ba zuwa zata yi ba. Nifa dan Baba Malam  yace in sanar musu ne ma"

"Nima sabida shi ɗinne. Kinga uban mijinku yana sonki kuma ya fifita soyayyarki akan soyayyar sauran surukan gidan. Kema kinsan da babu abinda zaisa in tsaya ina kula ƴar shuwa "

Ni dai ajjiyar zuchiya na sauke, shigowar su Hamida yasa dole nayi shiru.

"Hamida bani katin Amaryarku inje in kai mata kawai"

Cewar Adama. Hamida ta ciro katin data soka a zaninta. Adama ta amsa ta fita taje ta kai mata ta dawo.

Kafin azahar muka gama komai har gyaran gida da duk abinda ya dace.

Ana yin bayan azahar su Adama suka soma wanka dan ƙarfe huɗu daidai za'a soma yanzu kuma biyu saura.

Ina zaune ina shan tea da samosa Labbai na bakin madubi tana ƙyanƙyasa ado, kanta yasha kitson ƙari an mata su yis_yis masu tsayin gaske.

Labbai waya biya miki kuɗin kitsonnan haka?"

Na tambayeta ina dariya. Dariya ta kwashe dashi tana goga jan baki tace.

Edit with WPS Office

"Waye zai biya in ba Malam Habu ba. Dubu arba'in ya bani na hidimar bikinnan fa"

Idanu na zaro ni da Rahama wacce fitowarta wanka kenan muka ce.

"Dama malam Habu na da kuɗi haka?"

Dariya muka saka dukkanmu.

Labbai ta ciro ƙananun kayanta sababbi na ankon bikin. Baƙin wando da jar riga polo. Saida ta saka ta sake bazo kitsonta tace.

"In ma bashi dashi ni dai ya bani. Wai kunga yadda yake ɓare_ɓare a kaina kuwa? Wallahi har roƙona Allah annabi yayi akan kar in ba wani damar da zai matsi rayuwata yasan za'a shiga biki za'a tara mutane"

Adama data shigo yanzu a ban ɗakin yara tayi nata wankan tace.

"Kuma ke  kin amince da roƙon nashi? Maza yaita lallameki ki yarda ki aureshi su Rakiya sa dinga shiga ƙwatarki, ƙila ma Badaru da matarshi suma su shiga tunda duk maƙotane"

Rai Labbai ta haɗe tana fesa turare. Fara shigowar tawagar ƙawayen Amarya ne ya katse mana hirar. Nice ƙarshen wanka dan sanda suka soma kiɗe_kiɗensu da raye_rayensu kafin na fito. Dukkanmu har su Adama bakin siket muka siya mu da farar polo tunda mu yayyene. Su Qamriyya da su Layuza duk an hallara. Layuza ita kam wandonta taci itama kitsonta har gadon bayanta har gashin idanu naga ta saka an tuno baya kenan.

Ni a kujera ma na zauna kusa da Uzairu zuchiyata dake ta ɗaukar su Adama bidiyo suna rausaya. Shima baƙin wandone gajere a jikinshi da rigarshi amles ja

Amarya kuwa tasha kyau an ɗau kwalliya.

Ina zaune Maman Safarau ta shigo doguwar baƙar rigarta tsukakkiya ta saka da jan mayafi.

Ta zauna kenan Hamida ta shigo itama taci riga da wando. Tana shigowa ta faɗa cikin masu rawa harda ihunta. Murmushi nayi kawai dan rawar da take yi ya tabbatarmun da Hamida ƴar club ce. Ni da Maman Safarau dai muna zaune muna kallon kowa.

Uzairu zuchiyata ka koma ɗakin yara kaga bare sun soma shigowa kar kaja mana abun faɗe. Hararata yayi tare da miƙewa a tunanina shigewa cikin zaiyi sai kawai ya faɗa cikin masu rawa ya soma rawar gwatsile.

Biyar nayi muka soma rabon abun sha da abun ci, ƙawayen Amarya sai sake tuttuɗowa suke yi, dole na koma ɗaki, na bar Hamida da Maman Safara'u da rabo.

Ina kwance kamar a mafarki sai ga Babangida a kaina.

A zabure na miƙe ina mamakin dalilin da   yasa ya ratso cikin ƙawayen Amarya ya shigo har nan.

Edit with WPS Office

Shi da ba shigo mun yake yi ba.

"Ke Sabuwa gidan nawa kika maida mun club dan kinga duk Abinda kika roƙi  Baba  Malam yana yi miki ko? Ko shi da yasa irin matan da zaki haɗa tsula_ tsula kenan a gidan suna rawa suna jijjiga jiki komai nasu yana rawa masha Allah da bazai amince miki ba.

Da mutuncina da komai zaki tara mun mutane ana rawa a gidana?".

Tuno a inda muka haɗu yasa na saki murmushi kawai. Babangida irin rawar makel jeksin yake yi in akaje club ya mugun iyawa fili ake bashi yanayi ana ihu fa. Cikin raini nace

To kayi haƙuri ai bansan zaka shigo ba. Naga ko ɓarayin nawa sai da dalili kake shigowa. Sannan ai ba'a hana kiɗa da rawa a tsakankanin zallan mata ba."

"Naji uwar tsaro zance."

Ya dakatar dani da hannu.

"Ki kawo mun abincina ina ɗaki"

Ya fita fu ya barni da sakakken baki.

Abinci fa yace in kai mishi yana ɗaki.

Tabb lallai Babangida ya tabbata na mamajo.

Ohh to Allah ya shirya.

Miƙewa nayi kaina babu ko ɗankwali na fita na nufi falo.

Babangida na gani yana sintiri a tsakanin ɗakinshi da ɗakin yaran. Uzairu zuchiyata ƙila ganin Babangida yasa ya shiga ɗakin yara. A tsakiyar falon na tsaya na ƙare mishi kallo. Ya koma ya shiga ɗakinshi wallahi ya kasa yana tsaye yana kallonsu yana lashe bakinshi. Su basu san me ake ciki ba, shima kuma bai ganni ba.

Kitchen na shiga ina mai takaicin Auren mayen mata.

Tuwon dare da muka yi dasu Adama na saka mishi biyu a kula na zuba mishi miyar lalo taji bushasshen kifi. Sai na samu plate na zuba mishi samosa da soyayyen nama na buɗe firji na ɗakko fruit salad kofi ɗaya na dora mishi.

Ina fitowa falo da tiran Yar Shuwa na shigowa falon.

Idanu muka haɗa da'ita a kullum inna kalleta sai gubar data shayar dani ta nemi ɗauke numfashina.

Ashe zaki shigo?"

Edit with WPS Office

Na tambayeta ina dariya kamar babu komai"

"Uhm Wallahi "

Iyakar abinda tace dani kenan.

Bari in sallami Oga in dawo ko?"

A razane ta ɗago ta kalleni, ni ko ina murmushi na nufi ɗakin Babangida.

A jikin window na sameshi yana kallon mata. Ganina yasa ya matse harda sakin dogon tsaki.

"Dake bikine ji yadda kika tyi kwalliya kika tsuke. Amman ni da nake mijinki kafin ki barma ƙawarki ni baki ɗaya yaushe rabon da ki yi mun wannan kwalliyar?"

Ajjiye tiran nayi kawai nayi. Babangida yayi saurin riƙoni yana ƙokarin mannani da jikinshi. Hankaɗeshi nayi ya faɗa gadonshi yana dariya. Na fice ba tare da nace mishi uffan ba"

Yar Shuwa kuwa idanunta a kaina har na fito. Ɗaki nayi komawata dan kaina da ƙirjina ciwo yake yi mun kuma bana ƙaunar abinda zai dinga haɗani da Yar Shuwa a inuwa ɗaya.

Ana kiran magriba aka kashe waƙa taro ya ƙare kenan kuma.

Sai lokacin na samu na fito na tarar babu Yar Shuwa babu Hamida.

Adama an ba su Hamida kayan fulawa ko?"

Adama tana maida numfashi duk ta haɗa zufa tace.

"Roba bibbiyu na basu na ƙara musu da salat ɗin kofi bibbuyu ma. Kawarki kuma a leda ma na zuba mata jingin, ragowar salad kusan kofi shidda nace ta barshi.

Babangida ne ya fito ya fice.

Daga nan ƙawayen Amarya suka soma haɗa komatsansu, amman gidan bai gama watsewa da jama'a ba sai wajajen tara da rabi na dare.

Su Adama da su Labbai duk na roƙesu mu kwana in yaso gobe ma tafi gida aassafe. Dan ba ƙaramin hargitsa mun gidan akayi ba. Kujeruna ma duk sai da aka marmatsar dasu dan  fitina. Uzairu zuchiyata dai ayarin ƙawayen amarya ya bi. Naga wata farar yarinya ya manne ma.

Basu suka gama gyaran gidan ba sai sha biyun dare dan har wanke wanke sai da su kai mun.

Kulolin abincin da na kaima Babangida abinci naje na ɗakko babu komai a ciki ya cinye komai tas.

Bakina na taɓe kawai.

Duk a ɗakina muka haɗu a kan gado muka kwanta.

Edit with WPS Office

Khalid daya dame ni da kira dole na tashi na koma falo muka soma wayar da ni kaina ta zame mun jiki. Dan in ma bai kira ba, to ni zan kirashi mu raba dare muna hirarmu me daɗi, shaƙuwace mai ƙarfi a tsakankaninmu, Khalid yana kula dani sosai, duk abinda nake so naya mun, kuɗi kuwa yana yawan tura mun.

Washegari sassafe muka shiga batun abin kari. Tea aka dafa na ba Labbai kuɗi ta siyo mana biredi, Rahama ta soya mana kwai guda goma.

Ni da son cin waina ko alala na tashi. Dan haka tean kawai nasha na ɗumama cikina, Labbai da Salaha suka wanke kayan da muka ɓata, duk mu kai wanka ƙarfe takwas muka fito.

Hamida na tsakar gida tana shara tana ganinmu ta shiga washe baki tana gaishemu.

"Umman Aminu zaku tafi gidan bikin ba? Muma zamu zo in sha Allah zuwa yamma naga event ɗin na yamma ne."

To Shikenan sai kun zo"

Na bata amsa a taƙaice.

"Ni ko banji ɗuriyar su Mardiyya ba ko ba'a gidan suka kwana bane?"

Adama ce tace.

"Suna can gidan kakanninsu acan suka kwana. Zasu zauna acan har sai an gama biki sabida uwarsu ba zama zata yi ba"

Dariya kawai tayi, na lura mamaki take yi ko na meye tsohuwar kimunar ita ta baiwa kanta sani.

MRS BUKHARI

Ina manyan mata masu capacityn  suke?  ku fito lambarku ce ta fito.

Ƴar uwa turaren wuta kike nema nau'ika daban_daban masu musulmin ƙamshi da kama muhallu? Ba itacen banza masu sanya gida ƙauri da hayaki kamar an kunna taohuwar bespa ba.

Matso gasu MRS  BUKHARI B4B GIDAN KAMSHI nazo miki da duk abinda kike buƙata na ƙamshi. Kama daga turarukan wuta irin na gidan alfarma. Zuwa humrori iri daban daban masu musulmin ƙamshi da riƙe jiki.

Bugu da ƙari muna da turarukan kaya, na fesawa dana turara kaya.

Muna da kulaccam nau'i daban daban masu gyara jiki da lausasa  fata mata, ga kuma ƙamshi mai inganci.

Edit with WPS Office

Muna da turarukan tsugunno na musamman masu sirri Hajiyata

Muna da room freshener iri_iri

Muna da mopping mix masu kama waje.

Akwai turarukan kafet dana kujeru.

Sannan akwai box _ box  setika na Hajiyoyi masu ƙyallin goshi.

Muna da Amarya package.

Muna da uwargida package

Muna da maijego package

Muna bayar da sari ko a ƙasar waje kike, muna tura kaya

Saudiyya

Nijar

Ghana

Camaron

A duk ƙasar da kike kayanmu zai iso miki cikin aminci da yardar Allah.

Hajiya akwai Humrar matan aure wannan ta musamman ce.

Duk wani abu da kika sani na ƙamshi babu irin wanda bamu dashi a kamfaninmu.

Muna da turaruka designer na maza da mata wanda kamfaninmu ke bugawa Hajiya babu inda zaki je ki ci karo da mai irin ƙamshinki.

MRS BUKHARI B4B GIDAN KAMSHI TAZO MUKU DA DUK ABINDA KUKE SO NA KAMSHI HAJIYA.

KUNSAN KANURI MUNE KAMSHI DAMU AKE KOYI

SIYAN NAGARI MAIDA KUDI

MUNA MARABA DA MASU SIYAN ƊAYA KO SARI.

LAMBAR DA ZA'A SAMENI KAI TSAYE ITACE.

Wa.me/2348179523215

SAI NA JIKU

Edit with WPS Office

IDAN KAYA YA GAJI...

GAMMO MA YA GAJI

BADIAT IBRAHIM MRS BUKHARI B4B GIDAN KAMSHI

SHAFI NA ASHIRIN DA SHIDA:.

Bincike ya nuna sama da mutune miliyon goma sha biyar ke shan muyagun ƙwayoyi a najeriya.

Hakan kuma ya jawo asarar rayuka, taɓarɓarewar tarbiyya. Ya haɓɓaka fitinu da manyan lefuka a arewacin najeriya dama ƙasar baki ɗaya.

Tun kafin zama ya gagaremu mu koma bacci da ido ɗaya a buɗe. Lokaci yayi da zamu haɗa ƙarfi da ƙarfe domin mu taimaka ma hukumar yaƙi da sha da fataucin miyagun ƙwayoyi.

Dan ganin mun kawar da wannan ta'asa dake shirin zame mana ruwan dare.

Shaye_shaye annobace ga al'umma.

Wannan saƙone daga hukumar yaƙi da sha da fataucin miyagun ƙwayoyi wato ( NDLEA)

Sanya kuɗin karatun a cikin wannan lambar asusun

0044442984

Buhari Ibrahim Ladan Gt bank

Lambar da zaku turo shaidar biya gasu kamar haka

08022059556

Ko kuma

08105932041

Edit with WPS Office

Masu son magana da marubuciyar kai tsaye kuma ga lambata

Wa.me/2348179523215

A ƙofar gida muka tadda su Gaza da tawagarshi kusan rai ashirin duk saye da kayan saƙi na farauta. Ga karnukansu kewaye dasu. Sunata ɗaura guru da layu.

Yau abun na kanshi dan ko kallonmu bai yi ba, sai wani ciccijewa yake yi yana muzurai.

Salaha ce ta tsaya kulashi, ai kuwa ya lailayo ashariya ya lailaya mata.

Babu shiri ta biyo bayanmu muka kwashe da dariya.

Tsakar gidan cike da dangi anata cin ɗumamen tuwo da ruwan kokko.

Nan aka shiga gaggaisawa duk suna tsakar gida Rakiya dai bata ma gidan, Amarya dasu Sadiya duk basa gidan.

Mu kaɗai muka shiga ɗakin.

Ah ɗaki yasha fenti, harda kafet da doguwar kujera, da labule.

"Ahh lallai Rakiya uwar Amarya tasha gyara babu laifi. Ji ɗaki shar da fenti."

Ni dai kwanciya nayi a kujerar ina dariya kawai.

Tsahare ce ta shigo da tuwo da kokko a hannunta.

Yarinyar ƙanwar Rakiya ce Tabawa.

"Tsahare ashe kun zo, yaushe kuka zo, ina Baba Fa?"

Edit with WPS Office

Salaha ta tambayeta tana fara'a su sukai ma Tsahare ƙawancen bikinta, amman sa'ar Labbai ce.

"E ai munzo jiya wajen goman dare muka shigo. Da Baba muka tawo, harda ma Saude duk sun fita da Baba Rakiya sunje aro tukunya a maƙota"

Muka gaggaisa.

"Ashe aurenki ya kuma mutu Tsahare?"

Murmusawa tayi saida ta saka lomar tuwonta a baki kana tace.

"Wallahi aure ya mutu kinsan Aure raine dashi. Ko idda ban kammala ba. Baba tace in tattaro kayana mu tawo, zan zauna tare da Baba Rakiya in na samu miji sai in yi Aure na anan.

Kai na girgiza dan har cikin raina ban jima Tsahare daɗin dawowarta wannan gida ba. Nayi imanin tarbiyyarta lalacewa zata yi tsab. Su Sadiya ne zasu kama hannunta su sakata a yawo. Dolenta ma tayi yawo ko yinwa ta kasheta. Da zai yiwu dana ɗauketa  ai ta dinga taimaka mun.

Tsorona Allah tsorona Babangida nasan bazai yadda ba duniya ya tsani yaga wani nawa ya raɓeni.

Nima kuma ina tsoron kada Babangida ya saka ma Tsahare idanu dan ƙirjinta shaƙe yake da nono, dan suci amana a cikin gidan ma ba komai bane. Tunda Yar Shuwa taci amata uban kowa ma zai iya.

Rakiya ce ta leƙo ɗakin.

"Rahama kun shigo?

Ga nan shinkafa a fito a tsince, Labbai ke da Tsahare kuzo ku siyo itace. Uzairu zuchiyata tun safe nake nemanshi. Gaza kuwa nayi juyin duniya akan ya karɓo mana itace yaƙi fur. Wai ina son in kunyata shi a gaban yaranshi. Naga yau iskanci yake ji ja a kanshi. Magana zasu je ɗakkowa duk yadda akayi yadda naga ya tara yara da karnuka baƙaƙe"

Tsakar gida muka fito dukka, shinkafa muka shiga aikin tsincewa, anata hira da dangi, har wajen mu Baba ta karaso muka gaisa tare da tambayar bayan rabuwa, kafin kuma ta koma bakin aikinta. Tukunya take shafewa da toka. Sai ga Maigogul da kayan miya cikin bakko ya dire.

Nera dubu uku ya miƙa ma Rakiya.

"Kwa sai mai da Maggi iyakar abinda ya rage a hannuna kenan."

"Amman Maigogul batun abincin masu kawo kaya fa da tukuici yaya kake son inyi ni Rakiya"

Da hannu maigogul ya yafito ni. Babu shiri na miƙe na isa wajensu.

"Lolo ga Rakiya ki bata wani abu za'ayi girkin abincin masu kawo kaya. Ni dai ko tasi bani dashi. Ga batun tukuici. Sabida Allah gida fal ƴaƴa ace ni bazan huta ba. Sai yaushe haihuwa zatai mun

Edit with WPS Office

rana ne wai? Ita Aishan da tunda akasa bikinta ta dena kwanan gidannan ai na zaci nauyin komai zata ɗauka. Yanzu kayan miyannan da ƙyar na samu Alhaji na wajena ya bani dubu goma shine na siyo, ragowar canjin gashi na baki"

Adama ce ta ƙaraso tace.

"Rakiya ana fa jinku. Da ɗaki kuka shiga ai zaifi gidan cike yake da baƙi fa. Ga maƙota ma sun soma shigowa"

Ficewarshi yayi fuu yana zazzare idanu.

"Ohh ni Rakiya wannan wacce iriyar rayuwace ace miji bashi da zuchiyar tallafa ma iyalinshi da an magana yace bashi dashi. Jibi tsadaddun kayan dake jikinshi. Kayan biki ma kala uku yayi masu mugun tsada,ko yari bai iya sai mana ba"

Rakiya kiyi haƙuri duk abinda ya dace zamu je mu yo cefanen azo ayi ma masu kawo kayan abinci. Kuɗin tukuici kuma su Adama sa gagganɗa ayi."

Da haka na kashe bakin Rakiya.

Ai kuwa haka akayi ni da Salaha muka je kasuwa muka yo cefanenmu tsab.

Maƙota gidan da Labbai ta zauna Aure da Badaru anan muka shiga aikin girkin wajen ƙawar Labbai Lami. Itama lami zagewa tayi ta saka mana hannu a aikin girkin muka haɗu mu uku kowa da abinda yake yi. Hayaniyar biki kuwa har cikin gidan.

Azahar nayi jama'a suka soma shigowa yin Sallah Adama ce ta shigo duba mu.

"Ah kaji haka Lolo. Lallai yanzu kuwa Aisha ta kira wai masu kawo kayan suna hanya kafin la'asar zasu iso. Batun kamu tace tana gidan ƙawarta Fa'iza acan suke girkin abinda za'a raba a wajen kamun. Yarinyar tayi dabara gara data kama hol aje can ayi kamun ai yafi, tunda dangin mijin bamu san mota nawa suka tawo ba, gida ga ba yalwar ɗakuna"

Wallahi kuwa hakan yayi bayan la'asar za'a tafi kamun kenan?"

Salaha tace.

"E haka suka rubuta a jikin katin. Su kuma dangin miji ai sai wajajen bayan magriba zasu je wajen da an saka lalle shikenan taro ya watse.

Mu dai dab la'asar muka gama komai Lami ta ara mana kulolinya manya muka zuba dafadukan shinkafar a ciki, soyayyun kajin ma muka zuba a kula, sai salad kuma a ƙaton langa, matan gidan da lami duk mun ɗiba musu. Harda matar Badaru.

Sai da mu kai Sallah ma na samu na saka kayana. Shadda na saka ɗinkin riga da siket yaji surfani mai kyau irinna matan Senegal kunsan akwaisu da iya tsara kaya. Takalmina da mayafina kalarsu sak da surfanin gaban kayan, sai ɗan ɗankunnena da sarka mai ruwan zuma

Edit with WPS Office

dana saka.

Muna shiga gidan na tadda Hamida, da Maman Safarau, harda Sa'a da Alawiyya. Suna zaune a tabarma suna cin abinci amman banda Sa'a.

Wajensu na ƙarasa ina fara'a, da Hamida da Sa'a sai ƙarema kwalliyata kallo suke yi, suma fa sunyi kyau abinsu Sa'a da Alawiyya su masu hijab da niƙabi ne dama. Hamida kuwa ta ci sabon lace ja mai tsada amman hankalinta yana kan shaddar da na saka. Ba wata mai tsada bace can can. Dinkin dai da akayi mata ne mai tsadan hakan sai ya daraja shaddar.

Sannunku da zuwa ashe kunzo shine ba'a kirani ba. Ina maƙota muna girkin masu kawo akwati"

Na faɗa ina dariya tare da gaishesu dukka.

Sa'a dai da ƙyar tace

"Yaya taro?"

Alhamdulillah" Nima na faɗa da ƙyar

Alawiyya tace.

"Ai Rakiya tace ma za'a aika a kiraki to sai muka dai ce a barki tunda aiki kuke yi"

Abincin gabansu na kalla naga shinkafar fara fat tayi washar_washar babu kayan miyan kirki, babu man kirki.

Ina zuwa bari in kawo muku abinci'

Na yinƙura da sauri ina kiran Sadiya dana hangota tayi kyau da'ita.

"Da kin barshi ga abincin bikinnan a gabanmu ko baki gani bane?"

Cewar Hamida dake nuna mun abincin harda ruwa ɗan kamface a ƙaton kofi duk tsatsa.

Maman Safarau ce ta miƙe tace.

"Uwargida ran gida bari in taya ki ɗakko abincin."

Tare muka wuce harda Sadiya Lami nasa ta zuba abincin da kaza, naba Sadiya kuɗi ta soyo lemu da ruwan leda muka kai musu sai lokacin ne naga Sa'a an zuba mata ta karɓa.

Gobe dole in yi abinci na musamman ko dan dangin Babangida da su Hamida.

Masu kawo akwatine suka shigo da sallamarsu rigi_rigi da akwatunansu guda biyu da kit.

Ganin kalar mutanen ya kashe ma kowa jiki ruwan ƴan ƙauye garesu sosai, wasusunsu babu ko mayafi ma a jikinsu. Gasu sai da su kai Bus guda da ƙaramar mota.

Edit with WPS Office

Rakiya ce ta haɗo kanmu muka shiga ɗakinmu domin tarbar baƙi duk suna zazzaune.Dattijan, yaran matan kuma ɗakin Hauwa aka shigar dasu, duk ɗajunan saida suka cika. Baba Tabawa tace.

"Sannunku baƙi kun shawo hanya maraba lale da zuwa"

Wata dattijuwa da tafi kowa tsufa tace.

"An sha hanya kam. Ni sunana Alkeri ni Yar mahaifiyar Moses ce."

Kallon_ kallo ne ya shiga wakana a tsakankanimu jin sunan wannan dattijuwar dama sunan data kira Musa dashi. Kenan ba musulmi bane shi ɗin ko yaya ake nufi?

Nasan wannan tambayar duk itace a zukatanmu amman babu wanda dai ya tanka.

Abinci aka aika maƙota aka shigo musu dashi, aka basu waje.

Ina fitowa Sa'a da Alawiyya suna tashi.

"Anty Sabuwa mu kam zamu koma, gobe zamu zo ɗaurin auren tun da wuri in sha Allah. Allah ya sanya Alkhairi."

Allah ya kaimu nagode sosai Allah ya bar zumunci."

Har ƙofar gida na rakasa kana na dawo wajen su Hamida na zauna.

Anata shirin tafiya kamu wasu har sun tafi ma.

Mu tare da tawagar dangin mijin zamu je ayi kamu mu tarkato mu dawo.

Bayan sun gama cin abinci sun yi Sallah sai kuma aka sake tattaro kanmu muka shiga ɗakin Rakiya har sun buɗe akwatunan. Shaƙe da wasu irin atampopi ruwan kwara_kwara, ni dai jikina duk a mace shikenan ya tabbata ƙauye za'a kai Aisha. Kunga wani lace mai manyan huju da aka jima da dena yayinshi kuwa. Ga rigunan maman marasa ƙoƙo shafal_shafal dasu, komai dai irinna ƴan ƙauye. Takalma da jakar wallahi da aka ɗaga wata jaka mai kama da jirgin ruwa saida nayi dariya ni kam. Ajjiyar zuchiya Adama ta sauke tace.

"Munga kaya Allah yasa albarka Allah ya basu zaman lafiya kuma"

Wannan dattijuwar mai suna Alkhairi tace.

"Za'a bamu tukuicin cingam, alawa, biskit, da goro, ko dabino sai kuɗin masu ɗakko akwati nera dubu biyar da kuɗin silifas. Haka al'adarmu take da fatan Moses ya sanar muku?"

"Wai shi angon sunanshi Moses ne, naji sunan yafi mun kama dana ƙabila?"

Cewar Baba Tabawa. Rakiya dai tayi carab tace.

Edit with WPS Office

"Tawaba kiyi shiru. Yaro dai shi zai auri Aisha gobe, in ma ƙabila ne ai babu damuwa itama ƙabilar ce tunda bahausa ce"

Dole haka aka bar wannan maganar.

Mu kuma muka harhaɗa kuɗaɗe aka siyo duk abinda ake da buƙatarshi aka basu, tare da wannan kuɗi dubu biyar.

Nan kuma aka fito da kaya tsakar gida jama'a suka tawo kallo. Hamida sai kaɗa kai take yi duk atampar data ɗaga. Hmm wata sarƙa da Hamida ta ɗaga kamar ta matar dakacin ƙauye ohh Aure mai haɗe haɗe koma yaya ne Auren yafi mata akan wannan yawon ta zubas ɗin da take yi. Yau a kwana a gida gobe a kwana a hotel ko ges house.

Muna yin magriba muka ɗunguma zuwa wajen kamu. Dangin ango dai sai waran waɗanda suka dace akayi sabida yawansu.

Hamida fa uwar gulma muna tare sai taga ƙwal uwar daka.

A cikin hol ɗin akayi kamun Amarya, Amarya tayi kyau sosai dangin miji sun yaba da hasken fatarta sosai. Wajen yayi kyau ƙawayen Amarya sun ƙawata wajen.

Lalle suka shirɓuna mata bayan sun biya nera dubu biyar ma ƙawayen Amarya na sakun lallen.

Abinci aka raba mana, na ba Hamida da Maman Safarau.

Karfe taran dare taro ya watse, kowa ya kama gabanshi. Su Maman Safarau nabi muka dawo gida tare da su Labbai da Amarya da ƙawayenta dukka muka yo zuga.

Muna shiga suka buɗe sabon babin hira, ni dai ina cire kayan jikina na hau gado ko wanka na kasa, duk mun yi tulus ga laulayi a daddafe nake yin komai.

Washegari asubar fari muka shiga aikin tuyar ƙwai, muka ciccika filas ɗin shayina guda biyu masu lita uku uku, mummuƙi guda biyar manyan gaske, wanda za'a kaima dangin ango.

Muma mummuƙi da ƙwan da shayi muka ci, tun kafin sallar asuba akaita wanka da shiryawa, sabuwar atampar anko muka sassaka dan kafin ɗaurin auren zamu saka ankon da muka yi iyakar ƴan ɗakinmu kafin mu wuce Kaduna dan ɗaurin auren na karfe taran safiya ne.

Karfe bakwai da rabi muka fito dukkanmu harda Amarya da ƙawayenta. Itama ta saka ankon bikin tayi kyau.

A tsakar gida muka samu Hamida tana shanya. Gaggaisawa akayi sai wani fara'a take faman yi.

"Uhm sai kika ji ashe Amarya ta tafi Dubai saro kaya. Baban Aminu ya bata jari. Nima daya dawo jiya ne yake shaidamun"

Turus nayi ina mamaki Dubai sari, kuma Babangida ne ya bata jarin? Hukunci sai mai tsaga

Edit with WPS Office

idanu. Yar Shuwa an samu duniya.

Ayya Allah ya dawo da'ita lafiya"

"Sari fa kika ce, to sarin me?".

Cewar Adama, dama mu biyu ne muka tsaya su Labbai da ƙawayen Amarya duk sun riga sun fice ana gama gaggaisawa"

"Sarin wai dogayen riguna yace mun. Akwai matar abokinshi da take Abuja ita zatai mata ido acan. Mu muna zaune gaho an barmu kamar banzaye. Ya dai yi alƙawarin"

Sai taja bakinta tayi shiru.

Ai nasan yadai ɗau alƙawarin itama zai bata jarin take so tace. Munafurci yasa ta kasa ƙarashewa

Sune kuɗin Babangida ya tsone ma idanu. Baki na taɓe nace.

Bari muje sauri muke yi sai kun zo, zuwa sha ɗaya zamu wuce mu kam"

"To to bazan daɗe ba zan tawo nima in sha Allah "

Nan muka fice muka barta.

"Ahh yar shuwa ta cika tsinanniya yar abu ta kazan.... Dubai fa, ga mota ta mallaka, ga umara taje, ga gidan ubanta da aketa ƙishin ƙishin ɗin wai zata gyara musu, kinsan uwarta sai surutu da son fariya sai yaɗa labarai take yi"

Hmmmm"

Shikenan iya abinda na iya cewa, idanuna suka kaɗa sukai jawur dasu.

Mun shiga gidan mun tarar anata mulmular tuwon shinkafa. Maza ƴan ɗaurin auren har sun soma halarta.

Maigogul yana tsaye a tsakar gida shi da Hauwa. Yaci adon farar shadda sai waiƙiya yake yi surfanin gaban malum malum ɗinshi kuwa ko hakimi wallahi albarka,ga agogo, ga gogul da dama kullum yana manne dashi da yayi Magana ga haƙoran makanshi  sama da ƙasa reras a suke bayyana. Kamshin turarenshi ya cika tsakar gidan. Ko ango ƙaryarshi

Mata anata hada hada.

"Ke Lolo surukanki suna cikin ɗakin Rakiya maza kije ku gaisa, kuje tare da Amaryar.  Baba malam ma yace yana hanya shida Babangida"

Cewar Maigogul kenan yana tsaye riƙe da ƙugunshi. Kafin in shiga ɗakin Gaza ya shigo gidan saye da kayan saki sai warin layu yake yi idanunshi cike da farin kwalli.

Edit with WPS Office

"Ke Lolo eh ina Rakiya take dallah kwaɗo mata kira ko in danno kai in shiga eh wallahi"

To ka tsaya zan kira maka ita"

Na faɗa da saurina.

"Kai Gaza maza fice a gidannan ".

Wani kallo da Gaza ya watsa ma Maigogul babu shiri ya tsuke bakinshi.

"Hattara wallahi Dattijo bar ganin gida da mata yanzu sai inyi maka fitsari aka"

Ni dai da idanu na bi Maigogul haƙuri dan nasan ba ƙaramin aiki bane Maigogul ya ruƙunkume Gaza su subar mana da abin faɗe ba.

Da sallamata na shiga ɗakin Rakiya na tarar da su Malama ƙarama.

Rakiya Gaza na waje yana nemanki"

Kirji ta dafe tace.

"Wai ni Rakiya Gaza fa?

Miƙewa tayi ta tace.

"Malama ina zuwa dan Allah bari in dawo yanzu"

Ta fice da saurinta..

Malama ina kwana?"

A wulaƙance dai Malama Babba ta amsa mun. Malama ƙarama kuma ta amsa mun kadaran kadahan.

Leda me zane Malama ƙarama ta miƙo mun.

"Ga wannan Malam yace a kawo."

Nasa hannu na karɓa kofunane na tankaran a cikin kwali guda shida. Da kula mai biyu masu tsada.

Godiya nayi musu, ina zaune Baba Tabawa ta shigo musu da tuwo.

"Ai da kin tafi dashi a ƙoshe muke kinga muna karyawa muka fito"

Baba Tabawa tace.

"A_a Hajiya da dai kun sa albarka ko, bari a kawo ruwa"

Baba gashi sun kawo"

Edit with WPS Office

Na miƙa mata ina haɗiyar yawu kawai.

Karɓa tayi ta dinga godiya kafin ta fita ta aiko da ruwa.

Abincinnan dai basu ci shi ba, muna wannan zaman kuramen sai ga su Hamida da Maman Safarau sun shigo da sallamarsu ko wacce da leda a hannunta.

Mardiyya ce ta shigo riƙe da Usama a hannunta"

Mardiyya dama ashe kunzo, wa ya kawo ku?

"Tare da  Baba malam  muka tawo a motar Baba. Su Aminu da Aɗɗa'u suna wajen ɗaurin auren, Malama tana wajen Labbai"

Kai kawai na gyaɗa mata.

Sai da Hamida ta gaishe dasu Malama naga fara'arsu.

"Sakko yarinyar bari a taimaka miki ki huta"

Cewar Malama Babba.

Leda Maman Safarau ta bani.

"Gashi dan Allah babu yawa"

Ah mai yawan kenan an gode"

Hamida ta sakko yarinyarta daga baya ta ajjiyeta a cinyar Malama Babba. Tunda nake haihuwa Malama Babba bata taɓa ɗaukan goyona ba. Amman naga har wasa take da jinjirar Hamida.

Ledar hannunta ta miƙo mun na karɓa ina godiya.

Labbai ce ta shigo da abinci, masa da miya da nasa Lami tayi mun shi aka dure musu harda lemun kwalba.

"Lolo ki tashi ki sake kaya kinga har an ɗaura auren ma"

Kafin in bata amsa Rakiya ta leƙo.

"Lolo kizo kibi motar kaya a ɗebo kayan da suke gidanki motar kaya zata yi gaba tare da Uzairu zuchiyata"

Malama Babba na kalla, itama ni take kallo.

"Babu shakka"

Haka tace.

Edit with WPS Office

Miƙewa nayi nace

Zanje mu ɗebo kaya bazan daɗe ba yanzu zan dawo"

Malama ƙarama tace.

"Muma da zaran maza sun watse a waje zamu wuce bama zaki dawo ki tadda mu ba"

Godiya nayi musu nace da su Maman Safarau ina dawowa.

Ina fita na tadda Maigogul tare da abokinshi Chicib suna tsaye suna gaisawa da  Baba Malam da Babangida. Maigogul na ganina ya kirani. A gurguje na ƙarasa na gaishe da Baba Malam cikin nutsuwa. Babangida kuwa sai wani ƙaremun kallo yake yi dan ƙaramin ciki yasa na sake haske da wani irin fires.

 Baba Malam yace"

"Tafiyar ta taso ne Sabuwa?"

A_a tukunna zamu can gidane acan suka kai na ajjiye musu kayan ɗakin shine zamu je mu kwaso a dawo nan a harhaɗa"

Kafe ni da idanu Babangida yayi yana bina da wani irin kallo dana kasa gane na menene. Sosai hankalinshi yake kaina. Har wani ɓoyayyen ajjiyar zuchiya naga yana ta wani saukewa.

"To Shikenan maza jeki. Hamida zata tafi da yaran na riga nayi magana da Babangida su zauna a wajenta kafin ki dawo"

"Ke Lolo dan abu ta kazanki kina gani munata jiranki, kin tsaya a wajen daƙiƙin mijinki al kinkimi. Eh kizo dallah."

Cewar magazin da bansan yana cikin motar kayan ba. Baba Malam ya girgiza kanshi kawai.

Wucewa nayi ina takaici na shige gaban mota direba yaja muka wuce.

Mazagin da Uzairu zuchiyata suna bayan mota.

Buɗe musu garejin nayi aka ɗebe kayan muka dawo muka tarar anata loda mutane a mota, su Adama sun saka ankonmu  na lace, mun ƙara da shadda akayi mana na matan Senegal dake sunga nawa na shadda da atampa na Sallah.

Babu shiri nima na shiga ciki wuf na sake kayan nima na fito cikin anko lokaci bai bani damar yin kwalliya ba.

Hamida da Maman Safarau na ba cincin cikin leda nayi musu godiya, yara sunata ɗaga mana hannu ni dai na buɗe ƙofar mota na faɗa da ƴar jakata da kaya kala biyu.

Motar kaya kuwa tuni an gama loda sauran tarkacen har sun wuce, tare da su Uzairu zuchiyata

Edit with WPS Office

mu kuma anata shiga mota bus bus gasunan dake ashe angon wai direban motane sai aka kawo wadatattun motoci maƙota masu farin ciki da masu son ganin gulma duk suka shiga mota.

Fita zanyi a motar in dakatar da abun haka na jiyo Adama daga waje tana baloƙoƙo.

"Zo ki fice a motarnan dan abu ta kazan kaga yar kaza_kazan uba. Duk wanda ma ba'a gayyataba su fice"

Ina sakkowa naga ashe ƙanwar Yar Shuwa ce ta shiga mota zata bimu ganin gulma.

Nan mukaita fito da maƙotanmu da muka sam babu wata kyakkyawan alaƙa a tsakankaninmu. Muka ba abokan ango umarnin su rurrufe motoci jama'ar sun isa haka ragowar motocin da basu samu mutane ba su koma a haka kawai.

Cikin mota na koma, tsabar zafin kai ashe ina kusa da Baba Tabawa da Rahama da Tsahare nice cikon ta huɗun set ɗin bayan. Bamma sani ba sai yanzu na gansu.

Sha ɗaya da ashirin motocinmu suka soma fita a cikin layin, ragowar tsofaffi da mutanen unguwa sai aikin ɗaga mana hannu suke ta tayi har muka fita a cikin layin muka ɗauki titi samɓal, sai wani layi akeyi, mata na cewa in babu layi a bamu kuɗin mu.

Mu dake motarmu akwai tsofaffi sai muka auna arziki tsofaffi sun roƙi direba da kar yayi layi.

To dake ni ba ishasshiyar lafiya gareni ba, ai tun kafin a fita a dutse na soma gabga amai duk na ɓata kayana. Babu shiri aka tsaya na sauka aka siyo mun ruwa na wanke jikina, na siyo ledodi baƙaƙe.

Amai dai nake babu ƙaƙƙautawa gaskiya. Direba sai gudu yake yi a titi, niko na galabaita tun kafin aje ma ko'ina. Baccine ya kwasheni shine sauƙin dana samu nako yi bacci har na kusan awa biyu me kyau kafin na buɗe idanuna muka ci gaba da kallon ƙauyuka da gonakai. Surutu kuwa yinshi akeyi dake motar duk ƴan uwan Rakiya ne da suka tawo daga ƙauye.

Zamu shiga Kaduna yaune gobe ne abu har mukai azahar ga la'asar ta kawo kai. Tun ana tafe a konboi har aka warwatse ana dai haɗuwa da ɗaya biyu a hanya. Gamu a birnin Kaduna dai aman ba cikin ƙwaryar Kaduna ba, kuma a wani kwanar hanya muka haɗu da dukkan motocin Amarya a tsaye ana jiranmu dan sunce mune na ƙarshe.

Cikin konboi mukka sake tafiya,tun muna tafe a hanya kan kwalta sai gamu muna tafe cikin rairayi da jar kala"

"Ni kam ɗannan ba Kaduna zamu je bane, ni naga sai wuce ƙauyuka muke yi?"

A lokacin mun iso wani ƙauye da suke cin kasuwarsu yau, ga masu tallar gyaɗa dafaffiya, soyayya, rogo, awara, gurasa da ganda, ruwa, lemo, harda soyayyar kaza mai ƙyau. Abubbuwa dai iri iri"

"Baba Kaduna mun wuce ta nan inda muke tafe ƙaramar hukumar Zangon kataf zamu je. Angon

Edit with WPS Office

naku bakatafe ne ai"

Direba ya ba Baba Tabawa amsa.

A mugun galabaice na kalli Rahama itama ta kalleni. Illar rashin bincike kenan. Shi yazo ya sharara mata ƙarya yace a Kaduna zai ajjiyeta ashe a ƙauye zai kaita ya barota. Gashi yana da yare, ga shi ruwa biyu ne musulmi da kirista duk danginshi ne. Ohhh duk wannan ya farune a sakamakon rashin nutsuwa"

A gidan man wannan ƙauyen duk muka tsaya domin gabatar da sallar la'asar. Kafafunmu duk a kumbure suke kowa ya gaji ga yinwa da ƙishirwa.

Wasu suka wuce Sallah wasu kuma suka tsaya siyan abinci.

Labbai da Aisha na yafito suka iso inda muke tsaye ni  da Rahama.

"Ke Aisha wai kinsan dama a zangon kataf zaku zauna, sannan kinsan mijinki yana da dangi kirista?"

Rahama ta tambayeta tare da kakkafeta da idanu.

Kafin tayi magana kab ƴan ɗakinmu suka ƙaraso. Duk muka kafeta da idanu muna jiran ta bakinta.

MRS BUKHARI

Ina godiya sosai masoyana saƙwanninku suna ta shigowa na jinjina. Ina gani haƙiƙa ina jin daɗi sosai.

Wannan shafi na masoyan wannan labarinne na gida Najeriya da mutanen ƙetare ba.

Nagode sosai nace cau cau nisa'u na karya muku ɗankwali 🤺

Ina manyan mata masu capacityn  suke?  ku fito lambarku ce ta fito.

Ƴar uwa turaren wuta kike nema nau'ika daban_daban masu musulmin ƙamshi da kama muhallu? Ba itacen banza masu sanya gida ƙauri da hayaki kamar an kunna taohuwar bespa ba.

Matso gasu MRS  BUKHARI B4B GIDAN KAMSHI nazo miki da duk abinda kike buƙata na ƙamshi. Kama daga turarukan wuta irin na gidan alfarma. Zuwa humrori iri daban daban masu musulmin ƙamshi da riƙe jiki.

Edit with WPS Office

Bugu da ƙari muna da turarukan kaya, na fesawa dana turara kaya.

Muna da kulaccam nau'i daban daban masu gyara jiki da lausasa  fata mata, ga kuma ƙamshi mai inganci.

Muna da turarukan tsugunno na musamman masu sirri Hajiyata

Muna da room freshener iri_iri

Muna da mopping mix masu kama waje.

Akwai turarukan kafet dana kujeru.

Sannan akwai box _ box  setika na Hajiyoyi masu ƙyallin goshi.

Muna da Amarya package.

Muna da uwargida package

Muna da maijego package

Muna bayar da sari ko a ƙasar waje kike, muna tura kaya

Saudiyya

Nijar

Ghana

Camaron

A duk ƙasar da kike kayanmu zai iso miki cikin aminci da yardar Allah.

Hajiya akwai Humrar matan aure wannan ta musamman ce.

Duk wani abu da kika sani na ƙamshi babu irin wanda bamu dashi a kamfaninmu.

Muna da turaruka designer na maza da mata wanda kamfaninmu ke bugawa Hajiya babu inda zaki je ki ci karo da mai irin ƙamshinki.

MRS BUKHARI B4B GIDAN KAMSHI TAZO MUKU DA DUK ABINDA KUKE SO NA KAMSHI HAJIYA.

KUNSAN KANURI MUNE KAMSHI DAMU AKE KOYI

SIYAN NAGARI MAIDA KUDI

MUNA MARABA DA MASU SIYAN ƊAYA KO SARI.

LAMBAR DA ZA'A SAMENI KAI TSAYE ITACE.

Edit with WPS Office

Wa.me/2348179523215

SAI NA JIKU

IDAN KAYA YA GAJI...

GAMMO MA YA GAJI

BADIAT IBRAHIM MRS BUKHARI B4B GIDAN KAMSHI

SHAFI NA ASHIRIN DA BAKWAI

https://chat.whatsapp.com/E3bH5OKBh9jH2aYygj0ArA

Kina bukatar kaya masu kyau da inganci??

Kina bukatar kayan kitchen wnd suke available ba order ba??

Kina bukatar adashin gata wnd zaki dauki kaya kamar kyauta??

Kiyi joining wnn group din namu insha Allah xakiji dadin kasancewa a ciki.

Muna da kaya available masu kyau da rahusa💃🏾💃🏾

Ko kimin mgn ta👇🏾👇🏽

Edit with WPS Office

08093932955

Sanya kuɗin karatun a cikin wannan lambar asusun

0044442984

Buhari Ibrahim Ladan Gt bank

Lambar da zaku turo shaidar biya gasu kamar haka

08022059556

Ko kuma

08105932041

Masu son magana da marubuciyar kai tsaye kuma ga lambata

Wa.me/2348179523215

Adama tace.

"Hmm nifa kaina a ɗaure yake. Dangin mijin Aisha fa na cikin motarmu kusan duk rabinsu kirista ne. Sannan naga mun durfafi ƙauye garin su kare, kare ma da aka tambayeshi cewa yayi kaishi akayi"

Muma tutsiyen da muka yi mata anan kenan tayi ma mutane shiru" na ƙarashe maganar ina tsaki.

"Mahaifiyarshi ce kirista da duk abinda ya shafi danginta ɓangaren uwa da uba. Mahaifinshi

Edit with WPS Office

kuma bakatafe ne musulmi gaba da baya, sai wasu ƴan dangin kakanni da basa musulunci. Amman batun zama a Zango wallahi bai faɗa mun ba, duk da ko ma ya faɗa mun dole zan amince matsawar auren nake so in yi. Shekarata nawa a jibge a gida ina yawo kwararo_kwararo ƴan birni sunki suzo su auremu, irinsu Musa dukkanmu muka aura in banda Lolo data yi aure a gidan malunta gidan daraja"

Dole haka muka tsuke bakinmu mukai shiru. Gaskiya ne da ci gaba da yawon iskanci, gara rayuwar aure a ƙungurmun jeji ko babu komai zaka rabauta. Yin nisa da inda baka da daraja yafi alkhairi kaje wani waje can ka gina rayuwarka akan hanya me kyau.

Watsewa muka yi, kowa yayi Sallah muka koma mota da ɗan cimar da muka siya. Gashasshen balango me ruwa_ruwa na siya da gurasata mai yawa harda lemun kwalba. Bismillah nayi ma ƴan motar, su Baba dai sun saka albarka, niko zama na gyara ana tafe kowa na cin abinda ya siyo. Rahama me jego kuwa tuwonta ta siya miyar bushasshiyar kuɓewa da nama manya taci ta sha ruwa abinda da me shayarwa ga jegon ɗanyene bata juri yinwa ba.

Saida muka sake tafiyar sama da awa biyu muka iso Zango a lokacin duhu harya rufa.

Kofar gidan ango gungun maza ne zazzaune a fararen kujera suna ta aikin hira sun sha wankan shadda ko wanne da kalar tashi.

Isowar motocinmu yasa matan garin duk suka fito anata yiriri_yiriri tare da waƙoƙin al'adunsu.

Wallahi da ƙyar na sakko a mota saida Rahama ta cabkeni dan jiri ne ya kusan dokani da ƙasa ma.

"Yi a hankali Lolo. Ni dama kin sani baki zo ba. Irin wannan tafiyar azaba saiya zubar da ƙaramin ciki irin wannan. Ga Babangida ba haƙuri in da cikinnan zubewa zaiyi zai iya cewa bazai Yadda ba. Sannu bari in riƙe ki zuwa ciki"

Ta riƙeni gam muka bi ayarin mata da dangi da muka tawo tare zuwa cikin gidan lakan da suke ta shiga.

Rigiji gabji.

Gidane mai girman da saidai a barku da hasashenku dan ina irin wannan gidajen ƙauye wanda ake haɗe kan kab family hatta jika yana zaune da iyalinshi? To irin wannan gida Allah ya kawo Aisha. Ginin dai lakane jawur dashi ga ɗakunanan wasu a jejjere, wasu kuma a kewaye suke kamar ɓarayi kenan. Ɓarayi_ɓarayin sunfi yawa a gidan.ko katanga babu a gidan sai wani ɗan gini da akayi a ƙofar shigowa wanda wannan gini shi ya riƙe ƙofar shigowan. Duk da banga wata hikima a saka ƙofa a gidan ba in akayi la'akari da babu katanga a gidan.

"Maraba lale Amaryar Moses lalenku da zuwa baƙi ku shiga wancan ɓarayin acan zaku zauna kafin a ƙarashe gyaran ɗakin Amaryar tamu. Bari a kira Ruda tayi muku jagora. Ruda_Ruda".

Wannan mata ta shiga doka ma Ruda kira. Sai ga Ruda ta iso anci hular gashi irin me yayyeme

Edit with WPS Office

goshinnan gata baƙa ga jan janbaki ta rambaɗa kamar babanin Akuya.

Ita ta kaimu wani ɓarayi da babu kowa a ciki ɗakunane falle_falle guda uku a jere, sai banɗaki, da wani ɗan madafi da aka kewaye da kara. Ko'ina tsab.

Ni dai muna shiga na faɗa kan kujera  numfashina ya shiga sama da ƙasa, na daɗe sosai idanuna a rufe kawai jiri ne daga zaunannen yake hajijiya dani.

Ni ba suma bayi ba, amman bana cikin hayyacina ina jiyo muryoyi da yawa a kaina anata sannu_ sannu.

Sai can tsawon mintocin da bansan nawa bane sai naji na dawo daidai.

A hankali na buɗe idanuna na shiga ƙare ma jama'a kallo.

"Lolo sannu, ni wallahi da kinsani baki zo ba kinyi zamanki, kinji jikinki yadda ya ɗauki zafi kuwa, ga garinnan babu halamar wuta ga zafi"

Ni dai bana ko iya magana kwanciya nayi lawai bani na farka ba sai wajajen sha biyun dare.

Su Adama suna zaune dafa'an anata hira kowacce da mafici a hannunta kuma babu riga daga su sai ɗaurin kirji, Labbai kuwa ko ɗaurin kirji batai ba. Nunawa gasu dukwui

"Lolo kin tashi? Sannu da jiki"

Wata iriyar yinwace ta ƙulle mun cikina babu shiri na dafe cikin nawa.

Yinwa nake ji ku bani abinci inci dan Allah "

"Ga abincin can a gefenki, ai dole kiji yinwa sha biyun dare ne fa yanzu. Yanzunnan aka gama kiɗa a waje muma muka shigo ciki"

Langa na jawo na buɗe. Da shinkafa da miya naci karo da ƙatuwar cinyar kaza. Cokali nasa na dinga kamfata ina afawa a cikina, saida naci fin rabi na dawo daidai, sai a lokacin naji irin gishirin dake cikin miyar kau idanuna a runtse na haɗiye naman bakina na kora da ruwa"

Miyar ba dai tsami da gishiri ba wai. Saida na ƙoshi naji gishirin ga mai"

Dariya mu ka yi dukkanmu. Alwala nayi na rama sallolin da ake bina ina jiyo muryoyin su Baba suma daga ɗakin dake kusa da namu.

Wai Aisha an kaita ɗakinta kuwa, yaya aka ƙare ku bani labari dan na  fahimci bamu isa muyi bacci a wannan zafin ba da dukkan halamu basa samun wuta gashi harda firji naga ta siya. Sannan inasu Layuza?

Adama tace.

"Tana can ɗakinta ita da ƙawayenta anci rawa da dangin miji. Ke kinga dangin Maman Musa

Edit with WPS Office

yadda suke tiƙar rawa kan jiki kan ƙarfi?"

Rahama tace.

"To ai sun saba da rawar choci ba dole ba. Ji fa wani wai baffanshi ne ke kinga rawar gwatsilen da ya dinga yi, giya ce sukaita rabawa a ƙoƙo"

Labbai tace.

"Nifa duk ba wannan bane a gabana ba. Ba kuma shi yafi damuna ba. Domin A'isha ita a hakam ma Allah ne ya sota. Ciki sau nawa nawa tana zubarwa? Ko wata huɗu anyi ne data zubar da ciki ta dinga ciwonnan kamar zata mutu Lokacin ina gidan Badaru"

Na dubeta nace.

To menene damuwar taki?"

"Damuwata yadda Yar Shuwa ta samu dama ta mimmiƙe ƙafafunta a gidanki, taje umara yanzu ta tafi Dubai wai kasuwanci, ga mota an siya maya, ga gidansu an gyara musu. Wannan abu da ciwo yake. Wallahi ni wannan abun na ƙullata na saka shi a raina"

Hmmm ni kaina duk motsina tare yake yi da tunain ƴar shuwa da irin cin Amanar da tayi mun. Da irin yadda ta shafa ma idanunta toka ta shure duk wani aminci da yaddar dake tsakanin mu. Shi kuma Babangida dake burinshi yaga ya jani a ƙasa dole zai aureta ko da baya sonta. Balle babu namijin da zai ganta ya ji batai mai ba gaskiya."

"Lolo duniyar tunani kika faɗa ko? Nifa na ɗauka abun baya damunki ne?"

Cewar Rahama data dawo dani daga dogon tunanin dana lula. Sai da na sauke ajjiyar zuchiya mai nauyi ƙirjina wani abu ya tokareni kafin da ƙyar nace.

Ba damuna bane bayayi ba. Nanata maganar babu abinda zai haifar face ɓacin rai. Yadda ƴar shuwa ta shigo rayuwarmu bana so ko a mafarki Babangida ya saketa. Kunsan Allah in dai ana kwana ana tashi, dare na rufawa gari na wayewa, duk tsawon zamani sai Yar Shuwa tayi ɗan daka ce bata san Babangida ba ma. Nima lokaci na nan yana zuwa da zanyi abinda kowa sai ya gigita a lokacin da bana buƙatar shawarar kowa"

Hawayen baƙin ciki na share zuchiyata na soya mun da zafi. Mun daɗe muna hirarmu sai zuwa daf asuba aka kawo wuta, shine fa muka kunna fanka har muka ɗan kwanta. Ni baccinma nayi nayi yazo yaƙi zuwa. Kawai sai nayi alwala na yi raka'atanil fajir. Sannan na tashi su Adama, wayoyinmu duk muka jojjona chaji mu kai Sallah duk muka yi bacci.

Wajajen taran safe suka ɗauke wutarsu babu shiri muka tashi sabida zafi.

"Muje a gaggaisa da matan gida kar aga rashin kanmu kuma"

Cewar Adama data miƙe tana zira riga.

Edit with WPS Office

BABANGIDA:.

Gabaki ɗaya Hamida ta kasa gane kanshi a cikin kwanaki biyunnan da soyayyarshi da Ramatu ta sake kafa sabuwar Gwamnati, ga sama ana aikin ɗora musu sai gini ma'aikata suke yi.Ita  Yar Shuwa har lokacin gishiri bai fice akan kaza ba ita yana taka tsantsan duk ranar da yake ɗakinta. Sannan maganar barinta ƙasa yafi komai mahimmanci a gabanta. Dan ta shiga Kano ma mahaifiyarta ta rakata sun yi paspo kwanansu biyu suka samu suka dawo.

Nan ta shiga shirye_shiryen tafiyarta duk randa Babangida yake ɗakinta batun tafiyarne. Kuma gashi an sata a sabon group inda take ganin sababbin dogayen riguna kai tsaye daga kamfani.

Shi kuma ta ɓangaren goga a ranar da ya rage saura kwana bakwai wa'adin da Ramatu ta gindaya mishi ya cika ya shiga majalisarsu jikinshi a mace.

Musbahu yana basu labarin irin cin mutuncin da sirikanshi suka yi mishi.

"Wallahi dattijonnan ina kwance ya wani kirani ta inda ya shiga ba tanan yake fita ba. Wai yarinya ta wuni a asibity banje na dubata ba.

Nace to Baba ni likita ne da ni zan dubata na bata wadataccen kuɗi, kuma nasa an girko abinci harda naman kaza me akeso kuma ko dan dai nine uban ƴan lefi?"

Dattijonnan mukaita faɗi in faɗa da ƙyar dai muka sasanta. Ai da naje asibitin sai wani kumbura take yi sabida danginta sun gama zugeta. To danta haihu haihuwa nawa akayi mun za'ayi mun wata sabuwane."

Dariya suka saka. Jamilu yace.

"Aini shi yasa yara shida nace muku sun isheni. Sunje ma duk nasa sunyi family planning Zainab ce ma uwar ƙorafi take taimun ƙorafin ita jini na zubo mata ita wai tana ƙarni haka dai."

Lura sukai da Babangida baya magana kuma irin maudu'in da yafi zagewa akai ake tattaunawa. Mustapha ya zungureshi tare da kurɓar shayinshi na maganin maza da basu da aiki sai shan shi.

"Kaci kari ko matanne suka doka maka kaine? Kai amman Yar shuwa ta yankeka da yawa. Million uku ka ɗauka kaba mace tana gidanka? Nasan bazai wuce abinda ya dameka ba kenan"

Iska ya furzar yace.

"Wallahi ko ɗaya. Wannan babin tuni na rufeshi. Naje wajen Kawu Manga ne da batun ƙarin aurena shine ya koroni yace ko zan sake aure sai nan da wasu shekaru. To saura sati ɗaya

Edit with WPS Office

wa,adin da Ramatu ta bani ya cika fa. Sannan ita kanta a gida ganin yadda zawarawa sukai mata yawa akan wa'adi take. Jiya kasa yin mu'amular aure da Hamida nayi, duk da dama sha'awarta ta gama ƙarewa a kaina. Jikinta duk ya saki. To menene mafita ni yanzu?"

Wannan yace wannan, wannan yace wancan.

"Ina da mafita. Me zai hana muje mu samu Babanmu ai shima zai iya shige maka gaba ayi komai. In yaso daga baya ka sanar ma shi kawun. Amman Babangida kaci gari nifa nafi jiye maka Sumy wallahi yarinyarnan Yar balaja'uce zata iya fasa maka taya kasan dai ƴar yaga rigace"

Ajjiyar zuchiya Babangida Kaci gari ya sauke tare da lumshe idanunshi ya buɗe a hankali.

"Tun jiya da wani abu ya tokareni a maƙoshina sai yau yanzu ya sauka. Mustapha wannan shawarar taka tayi. Batun Sumy tureshi a gefe da badan ina tsoron Baba Malam ba da tuni na yaga mata riga. Daduro bai yi ba wallahi."

Khalifa yace.

"Gashi jiya_jiyannan na dawo da Rose garinnan harna kama mata gida komai an zuba a gidan. Acan na kwana hankalina kwance, kace na taro mach?"

Harara Babangida kaci gari ya doka mishi yace.

"In iskancinta ya tashi sau nawa Sumy tasha zuwa nan majalisar tai mun yaga riga a gabanku? A hakanma ni jan wuya ne kai ka sani. Gashi ta zamemun ƙarfen ƙafa kullum barazana.

Auren sirri nake so muyi da Ramatu tunda bama haihuwa take yi ba.  Duk kana gani sabida Sumy ne, zata iya kasheni ma in taji labari fa, In komai ya tabbata zan sanarma da Malama dan ita ko mutum na kashe dole in sanar mata. Baba Malam kuwa harya koma ga mahalicci bazai san da zaman Ramatu ba.

Yaushe ake samun Baba na shago a gida?"

Ya miƙe a zabure. Musbahu yana dariya yace.

"Kai Kaci gari baka da dama mutumin. Wallahi ko yanzu naga wacce tayi mun, nima aurenta zanyi. In kaga mun dena auren mata da sakin su to wallahi tsufane ya riske mu.:

Babangida yace.

"Tsufanma irin wanda injina suka dena aiki ba?"

Shi dai Khalifa haka aka barshi da tunani.

(Wai ina maza suke son shiga ne wuta? Wannan wacce iriyar rayuwace haka. Karfa kuyi tunanin rubutawa akeyi dan raha. A_a wannan da gasken _gaske yake faruwa. Kuma kema ba zaki kasa

Edit with WPS Office

sanin maza masu ɗabi'ar Babangida kacigari da abokanshi ba. Zaman majalisa masifa ne, matan da mazajensu suke zaman majalisa wallahi abun a jajanta musu ne. A majalisa babu irin abinda maza basa yi, da sannu suke juyarma da kansu tunaninsu suita ziga junansu suna ma juna ingiza mai kantu ruwa, gami da bama juna guraguran shawarwari)

Su huɗu suka kama hanya suka je gidan iyayen Mustapha. Babangida ɗane shima a gidan yana shiga duk inda yake so kasancewar Mustapha da Babangida abotarsu bata yau bace.

"Wai wa nake gani haka kamar Babangida kaci gari?"

Cewar Hajiyan Falo mahaifiyar Mustapha."

Shiga sukai da sallama ai kuwa uwargidan Mustapha tana falon Hajiya a gaban wasu akwatuna"

"Wallahi Hajiya nine dai naki guda ɗaya. Me zuwa shan zoɓo da Alala"

Dariya tayi mishi. Suka zauna aka gaggaisa. Matar Mustapha ta gaishesu.

"Kayan auren waye wannan Hajiya?"

Cewar Babangida da yake ƙarema kayan da matar Mustapha kallo"

"Kayan Auren ƴarku ce Fari'atu ka gansu ɗazunnan aka kawo. Yanzunnan su Sauma'iyya basu jima da barin gidannan ba. Yaya iyalin naka mai kala_kala dan uwargidanka ce kaɗai mai dauwamammen wajen zama. Kai da abokin naka an rasa gane me kuke nema"

Babangida dai sosa kai yayi. Mustapha kuma ya doka ma matarshi uwar harara, babu shiri tace.

"Hajiya nima zan wuce zanje in ƙarashe girki sai da safe"

Ta saka kanta ta fice.

"Hajiya Baba na shago yana shagone ban hango takalminshi ba?"

"Yananan kuje ku sameshi. An rikito wata rigimar kenan tunda dama shike biye muku"

Suna dariya dai suka fice dab magriba ne hakan yasa bayan sun gaishe da farin dattijon Mustapha ya rabtaɓo mishi bayani da abinda suke neman alfarmar ya shige musu gaba.

Baba na shago ya jinjina lamarin ainun kafin yace.

"A_a fa gaskiya wannan lamarin yana da girma. Me yasa ba zaka sake gwada tuntubar Kawun naku ba, ko kuma dai ka haƙura matanka uku a sanina. Wannan Auren zai iya zamema matsala kuma zai sake farraƙa tsakaninka da mahaifinka, kasan dai shekarun baya yadda aka kwashe da wannan kawalin da abokinshi ɗan daudunnan."

Babangida da ya jarabtu da son Ramatu yake ganin tamkar numfashinshi tsaiwa zaiyi in bai aureta ba. Kasa cewa komai yayi, ko baiyi auren sirrin dan kowa ba dolenshi yayi domin ɓoye ma

Edit with WPS Office

Sumy, to ko dai ya sallami Hamida ne kawai ya damu Kawu Manga da magiya? Kar kuma lokaci ya ƙure mishi dan mugun taurin kai garesu shi yasa Baba Malam har yanzu yake fishi dashi.

"Baba na shago ayi haƙuri daga baya zasu sani. Sannan ai kai me iya ɗaura mun aurene ba dole sai Baba Malam ko kawu manga ba. A duba lamarinnan nafi buƙatar sirrin a halin yanzu"

Bayan dogon nazari Baba na shago yayi na'am da buƙatar yaran nashi. Take Babangida ya ajjiye mishi sadaki, da lambar ƙanin mahaifin Ramatu.

"Zan kirashi zuwa gobe ma in yana gida zan ɗauki Alhaji Gali nawa, sai Mustapha ya kaimu muje.

Amman fa ga nasiha zanyi muku. Yawan aure da saki bashi da wani fa'ida. Wallahi ina guje muku ranar da zaku yi nadama. Munyi fishin, munyi faɗan har mun gaji mun zuba muku idanu. To amman ina jiye muku ranar da zaku zubama naku yaran idanu sakamakon sunƙi jin maganarku. Ko kuma ranar da zaku kasa bacci a sakamakon wata rigimar da yara zasu kwaso muku na zubewar daraja. A wannan shekarun kuma duk inda daraja take nemanta kukeyi ko dan samun kwanciyar hankalan ƴaƴayenku mata da suke gidan aure.

Kai Babangida kafi Mustapha sani tunda kai malamine ɗan malamai gaba da baya.

To Allah dai yayi albarka"

Da 'Ameen"

Suka amsa suka fito.

Kai tsaye masallaci suka wuce.

Washegari Baba na shago suka tafi gidansu Rahama. Allah cikin ikonshi da amincewarshi ba'ai wata_wata ba akace a ɗaura auren kawai tunda waliyai sun hallara in yaso zuwa sati me zuwa amarya ta tare.

Hakan akayi kuwa Mustapha ya zo ma Babangida da kyakkyawan labari me daɗi. Tun a majalisa ya kira Hala shi yana farin ciki,itama tana yi.

Washegari yaje ya bata dubu ɗari biyu da hamsin na kaya da hidimar da zata yi.

"A_a gaskiya sunyi mun kaɗan wannan ai ko iya gyaran jikina ba lallai ya isaba Sokoto zanje aimun gyara zan haɗa miji da Shuwa a matsayina na basakkwata nima dole in fitar da jihata kunya." ( Mamanmu Hajara Aliyu ana magana 😆)

Murmusawa Babangida yayi yace.

"To abinda za'ayi shine su ki riƙesu na gyaran jikin kawai. Zan turo miki na lefen ta banki kafin ki dawo daga Sokoton. In kin lamince ai sai in miki rakiya ko?"

Dariyar manyan mata tayi tace.

Edit with WPS Office

"A_a ka dai bari in tare tukunna. Yanzu dai kaji da matanka kafin in zama ɗaya daga cikinsu. Nasan da ace sun san da batun auren da yanzu sunanan suna kishi dani ko?'

"Ke mance dasu, su sunma isa kishi dake? Kowacce dai ta biya allonta saita wanke. Bar batunsu mu dawo batun tarewa nifa a matse nike, kuma nayi nayi mu ɗan zagaya hotel kinki yadda yanzu ma da kike mallakina kinata jana a ƙasa"

Kallonshi tayi tana wani jin farin ciki. Tun a baya soyayyarta ta nunka ta Babangida ninkin ba ninkin, shi sha'awarta kawai yake ji, kuma a baya ƙarya yake yi ba wani aurenta da zaiyi. Ita kuma sonshi take yi soyayya ta gasken gaske bata san zaɓen tumun dare tayi ba.

"Haba B House me kake ci na baka na zuba? Kai dai bari in tare zamu yi amarcinmu yadda ya kamata. Sai dai kayi haƙuri tunda an ɗaura zankai sati uku ban tare ba gaskiya." A razane Babangida ya dubeta yace.

"Amman wasa kike yi ko? Dan Allah kar kisa zuchiyata ta buga"

Kafin ta bashi amsa mahaifiyarta ta shigo falon da sallama. Babangida ya saisaita nutsuwarshi waje guda suka gaisa da Umma sosai.

"Dama abinda yasa na shigo dan mu gana da junane in ganka ka ganni, sannan an ɗaura aure ya kamata ace iyayenka mata su kawo lefe domin aga juna ko?"

Yawu Babangida ya haɗiye yace.

"Hakane umma zasu zo in sha Allah in za'a kai Amarya. Amman batun lefe da kuɗin zan bayar"

Murmushi tayi tace.

"A_a Babangida zaifi kyau a kawo lefen dan mu toshe bakin dangin ubanta. Gabaki ɗaya basa son auren dan dai kawai Ramatu Bazawarace musulunci ya bata cikakken ƴancin zaɓan miji da kanta. To ƙanin ubanta yace za'ayi duk abinda akeyi su kuɗin gaisuwa duk za'a kawo. Sannan batu na gaba zamu je Sokoto ni da'ita wajen dangina a ƙalla zamu kai wata guda kayi haƙuri da mun dawo sai ta tare kaji da fatan babu damuwa ko?"

Zufa na keto ma Babangida yace babu Matsala.

Da haka suka yi sallama. Babangida ya zama babu Amarya, babu Sabuwa, Babu Yar Shuwa sai Hamida da yaran. Babangida kacokam ya suri jakarshi ya koma gidan Sumy.

WANNAN KENAN"

Hamida"

Edit with WPS Office

Tana kitchen sai tsaki take dokawa sakwara Babangida ya kirata yace tayi mishi yana hanya zai dawo. A lokacin da yake wayar tare da'ita Sumy na ƙanƙame a jikinshi.  Garinsu zata je mahaifinta babu lafiya shine yake so ya koma gida.

"Shikenan ita ta tafi anzo an jibgemun yara ƴan iska marasa ji. An haɗani da aiki ko wanne irin so Malam Baba yake ma Sabuwa oho shegiya mai nacin tsiya"

Harta gama dakan sakwararnan tana mitar tsiya, a gurguje tayo wanka ta kintsa, miyar ɗanyen kifinta na wuta bata dahu ba su Mardiyya suka shigo da sallama.

Harara ta doka musu bata ko amsa gaisuwarsu ba.

"Dallah ku shige ciki ki sako kaya kizo kiyi wanke_wanke yananan tun safe yana jiranki"

Malama tace.

"Umman Usama ni yinwa nake ji"

Da harara ta bita.

"Ba nace ku dinga tsayawa kuci abinci acan gidansu Babanku ba me yasa baku ci ba?"

Aminu yace.

"Sanda muka shiga gidan ba'a gama abincin ba. Shine  Baba Malam yace mu tawo kar muyi dare a hanya"

"Ba shakka. To ke ba kin iya girki ba Mardiyya? Sai ki shiga ki girka muku abinda zaku ci. Ni abinci daga ni sai ƴaƴana sai mijina nayi shi. Na gaji da wannan sarama kare ciyawan gaskiya"

Jin kamar miyarta na ƙauri yasa ta shiga kitchen ɗin a guje. Ai kuwa ilai miyar duk ta kama.

Tsaki tayi ta kashe gas ɗin ta juye miyar a haka a kula ta jera komai a dainig.

Mardiyya kuma ƙannenta taja suka shiga ciki

Suna cire kayan makarantarsu Aminu yace.

"Zan wanke mana uniform ɗin kije Adda ki dafa mana abinci yinwa nake ji"

Da sauri Mardiyya ta fice a lokacin Malama harta soma kuka Aɗɗa'u kuwa acici mala'ikun tauna ko magana baya iyayi sabida baya jurar yinwa.

A gurguje Mardiyya ta shigo kitchen bayan ta tsayar da sanwar jallof ɗin makaroni saita shiga wanke tarin kwanukan dake kitchen ɗin tun na abincin safe da suka yi breakfast. Kafin ta gama abincinta ya dahu ta kashe gas ɗin. A lokacin ana kiraye_kirayen Sallah su Aminu sun leƙo sun mata sallamar zasu masallaci.

Edit with WPS Office

MRS BUKHARI

Ina manyan mata masu capacityn  suke?  ku fito lambarku ce ta fito.

Yar uwa turaren wuta kike nema nau'ika daban_daban masu musulmin ƙamshi da kama muhallu? Ba itacen banza masu sanya gida ƙauri da hayaki kamar an kunna taohuwar bespa ba.

Matso gasu MRS  BUKHARI B4B GIDAN KAMSHI nazo miki da duk abinda kike buƙata na ƙamshi. Kama daga turarukan wuta irin na gidan alfarma. Zuwa humrori iri daban daban masu musulmin ƙamshi da riƙe jiki.

Bugu da ƙari muna da turarukan kaya, na fesawa dana turara kaya.

Muna da kulaccam nau'i daban daban masu gyara jiki da lausasa  fata mata, ga kuma ƙamshi mai inganci.

Muna da turarukan tsugunno na musamman masu sirri Hajiyata

Muna da room freshener iri_iri

Muna da mopping mix masu kama waje.

Akwai turarukan kafet dana kujeru.

Sannan akwai box _ box  setika na Hajiyoyi masu ƙyallin goshi.

Muna da Amarya package.

Muna da uwargida package

Muna da maijego package

Muna bayar da sari ko a ƙasar waje kike, muna tura kaya

Saudiyya

Nijar

Edit with WPS Office

Ghana

Camaron

A duk ƙasar da kike kayanmu zai iso miki cikin aminci da yardar Allah.

Hajiya akwai Humrar matan aure wannan ta musamman ce.

Duk wani abu da kika sani na ƙamshi babu irin wanda bamu dashi a kamfaninmu.

Muna da turaruka designer na maza da mata wanda kamfaninmu ke bugawa Hajiya babu inda zaki je ki ci karo da mai irin ƙamshinki.

MRS BUKHARI B4B GIDAN KAMSHI TAZO MUKU DA DUK ABINDA KUKE SO NA KAMSHI HAJIYA.

KUNSAN KANURI MUNE KAMSHI DAMU AKE KOYI

SIYAN NAGARI MAIDA KUDI

MUNA MARABA DA MASU SIYAN ƊAYA KO SARI.

LAMBAR DA ZA'A SAMENI KAI TSAYE ITACE.

Wa.me/2348179523215

SAI NA JIKU

IDAN KAYA YA GAJI..

GAMMO MA YA GAJI

BADIAT IBRAHIM MRS BUKHARI B4B GIDAN KAMSHI

SHAFI NA ASHIRIN DA TAKWAS.

SADAUKARWA.:

NA SADAUKAR DA WANNAN SHAFI A GAREKI ( MAMANMU MAI KAFACITI. BABBAR MACE, FARA MAI FARAR ZUCHIYA SARAUNIYA A ZUCHIYAR BABANMU HABIBINKI HAJARA ALIYU SOKOTO SHAFIN NAKI NE KIYI YADDA KIKE SO DASHI)

Edit with WPS Office

https://chat.whatsapp.com/E3bH5OKBh9jH2aYygj0ArA

Kina bukatar kaya masu kyau da inganci??

Kina bukatar kayan kitchen wnd suke available ba order ba??

Kina bukatar adashin gata wnd zaki dauki kaya kamar kyauta??

Kiyi joining wnn group din namu insha Allah xakiji dadin kasancewa a ciki.

Muna da kaya available masu kyau da rahusa 💃🏾💃🏾

Ko kimin mgn ta👇🏽👇🏽

08093932955

Babangida ya shigo a lokacin Hamida tana falo a zaune yarinya ta tusata gaba da kuka kwana biyunnan da zaran duhu ya rufa zata tsiri kukan da ko rarrasuwa bata yi. Nono wannan in aka

Edit with WPS Office

bata ba zata karɓa ba.

Tana kan jijjigata tana rusa ihu ya shigo. Jin kukan yarinyar ya kuma tunzura fushinsa dan a mota yayi waya da Ramatu yana mata ƙorafin wata guda yayi mishi yawa. To da wannan suka ɗan samu hatsaniya har tana cewa ta fasa auren yayo mata text na saki dan ita ba'a takurata.

"Meya sameta take irin wannan masifar kukan kinsan zan shigo da gajiya ba zaki  rarrasheta ba sabida wulaƙanci?"

Da jaraba yake mata maganar hakan yasa duk ta sake ruɗewa. Ga mamaki daya cikata ta lura itama kamar fa ta zama bora a gidan.

"Wallahi babu abinda ya sameta kwana biyu kullum haka take wannan kukan. Kuma cikinta da kunnenta duk lafiya suke"

Tsaki yayi ya nemi kujera ya haye yana huci.

A baya ta saɓa yarinyar tazo tayi mishi sannu da zuwa.

"Kinga zan shiga ciki in watsa ruwa kafinnan yarinyarnan ta dena kukan. Ki kawo mun abincina can"

Idanunshi a lumshe yake maganar dan sha'awar Ramatu ce ke kaɗa mishi hanji. Mikewa yayi tare da shafar sumar kan Usama yayi ficewarshi.

Ajjiyar zuchiya ta sauke kawai, kwana biyu ta kasa kane kai da ƙafafuwan Babangida sam, ko da yake tunda dai Yar Shuwa ta shigo gidan komai ya rincaɓe a madadin Sabuwa ce zatai ta fama da ƙunci sai ƙunci ya dawo kan Hamida ( dama nace in zaka gina ramin mugunta ka ginashi daidai kai ƙila kai zaka faɗa. In ma da zurfi ka gina ka cuci kanka )

Miƙewa tayi ta gabatar da sallah kafin ta sauke yarinyar a baya ta kira Mardiyya ta bata ita. Tana kuka har harshenta na kaɗawa amman sabida son miji ta mikama Mardiyya yarinyar babu ko tausayi

"Ko goyata kita jijjigata har sai tayi bacci"

"To"  Kawai Mardiyya ta iya cewa ta goya mufida ɗan a bayanta ta shiga aikin jijjiga yarinya, ita kuwa kamar sake turata akeyi.

Kayan abinci Hamida ta shiga kaiwa ɓarayin Babangida. Tana jin saukan ruwan wankanshi a bayan gida. Ga wayarshi a gado anata kira. Lamba ce babu suna Hamida ta taɓe bakinta ta fice.

Ragowar kayayyakin ta ƙarasa kawowa lokacin data shiga Babangida ya fito harya zura jallabiyarshi anata kiraye_kirayen sallar isha. Ficewa yayi ba tare daya ce da'ita uffan ba. Waldrop ɗinshi ta buɗe inda take ajjiye ƴan rigunan bacci, zanin gado, da hijabin Sallah. Wanda su waɗannan kaya a ɗakin suke da'iman. Taga duk an wargaza mata su ba dai yadda ta ajjiyesu ba. Ranta yai mummunan ɓaci ainun hijabin ta zaro tayi Sallar isha dashi. Daga tsakar gida ta

Edit with WPS Office

jiyo Babangida nayi mata wulaƙantaccen tozartaccen kira ba shiri ta fita gabanta na dokawa.

"Sabida baki da hankali kina fa ji yarinyarnan sai kuka take yi amman kinyi biris. Wannan wanne irin shirme da shashanci ne haka Hamida, anya baki samu taɓuwar kaiba kuwa?"

A fusace tace.

"To me zan mata? Bata karɓar nono, bata rarrasuwa kashe kaina kake so in yi?"

Da yatsa ya nuna kanshi yana ƙanƙance idanu irin na maza baduniyawa.

"Ni Babangida kike faɗa ma to me zaki mata, kike faɗi in faɗe dani Hamida? Ke baki san zaman haƙuri nake yi dake bane ko? To wallahi ki shiga hankalinki tun kafin kizo kina kukan nadama"

Rabon za'ayi yasa Hamida cikin ɗaga murya tace.

"Nifa na gaji dama da irin rashin adalcin da kake yi a gidannan. Ya'isheka haka tunda ka shigo kake wani fishi fishi dake wacce take sanyaya makan bata nan ko?"

Tas ya zuba mata mari tare da kai mata naushi da ƙafa tayi saurin kaucewa. Duk da haka saida ya kuma zuba mata dundu saida yawu ya zubo a bakinta. Abinda bai taɓa yi mata ba kenan

"Kije ji huta a gidanku. Tunda daɗine yayi miki yawa. Gobe sassafe ki fice mun a gida, tunda ba'a koya miki tarbiyya ba ƴar iska maras mutunci "

Tsaki yaja yayi shigewarshi cikin ɗaki.

Hamida ma ta shige ciki a guje tana kuka. A daren ta haɗa kan kayanta a ƙaramin akwati da shirin gobe sassafe zata wuce Gombe.

Shi kuma gogan naku yana shiga ya zauna danya kwashi girki. Yana saka nomar farko a baki yaji ɗacin ƙonewa ga ƙauri da miyar take yi.

"Hmmm yarinyarnan zanyi maganinta ina jin mun  gama ni da ita. Ji yadda tai mun asarar abinci waye zaici  wannan abincin"

Miƙewa yayi ya shirya ranshi a ɓace ya fice fuuu a gidan megadi na ɗaga mishi hannu. Gidan cin abinci yaje yayi odar lafiyayyen farfesun jelar saniya yaci yayi hani'an ya fice. Haka siddan yaji yana da sha'awar yaita yawo a gari sabida kaɗaici yayi mishi yawa sosai, club ya kewaya ya cashe ya rungume mata kala_kala. Sai biyun dare ya shigo cikin gidan.

Hamida ta ɗaga labulen wandonta tana hango Babangida yana tafe yana waya.

Sauke labulen tati tare da sauke ajjiyar zuchiya taci gaba da kewaye ɗakin zuchiyarta cike da dana sanin rikicinsu da Babangida. Yanzu ita da ake ganinta cikin rufin asiri, gashi anyi mata alƙawarin zuwa umara harda bada jari yaya zata koma gidansu alhalin tasan Babangida baya zuwa bikon mace. Tasan data fita sai dai ya aiko mata da takaddar sakinta.

Edit with WPS Office

Shawarar da Na'ila ta bata kawai tana ga zata ɗauka. Da wannan shawarar ta kwanta tayi baccinta harda minshari.

Sassafe ta sallami su Mardiyya da ruwan bunu da tsurar mummuki kamar dai jiya.

Suna fita ta fito da akwati da goyo Usama na biye da'ita ta kulle ɓarayin nata ta saka kai ta fice.

Gidansu Na'ila ta faɗa. Da Maman Safarau taci karo a tsakar gidan tana ɗumamen abincin kari. Sama_sama suka gaisa ta shige ɗakin Na'ila.

"Kece sassafe haka, yaya ince dai ba can garin naku zaki wuce ba dai ko?"

Cewar Na'ila kenan.

Zama tayi a kujera tace.

"Gidansu Babangidan zanje kamar yadda kika bani shawara. Ko zai rabu dani wallahi nima saina tatsi rabona tunda dai juninshi ne auri saki"

"Koke fa. Balle ma babu fa inda zaki sai kin so. Inata miki tayi malamai bakya yadda. Ta ɓangaren magungunanan mata dai nasan kina ƙoƙari. Ga wata mata da aka bani labarinta wallahi daga Chadi tazo ance akwaita da magungunan mata gobe ki tanadi kuɗi Hajiya muje mu siyo ki gigita Abban Usama.

Nima jiya ƙawata Murja ta kawo mun wata gumba ƴar kaɗan a leda na cinye a haka. Wai ke kinga sambatu sato hanya yayi cikin dare ya faɗo, amman saida taji ihunshi yaji daɗi"

Tafawa suka yi babu shiri Hamida ta saki dariya tace.

"Kice akwai harka? Ke gara magungunan matan sunfi tasiri. Asirinnan faɗa miki ne bam ba mun ɗan taɓa a baya kafin ya aureni da yake shirin zai rabu dani. To a gaskiya asiri baya wani tasiri a jikinshi. Saida muka siyar da gonarmu kuɗin ya ƙare tas kafin fa mu ka ɗan samu canji shima ba wani na azo gani ba. Damma a jikinshi mun mayar da filin, harma gona na siya a garinmu.

Gara in sha magungunana ko banza maji daɗin tare kuma suma babban makamine na kama miji ram a hannu. Ke ba gashi satar kwana akeyi miki ba. Kishiyarki da lusarar ƙawarta babu fus a gado sai aikin ƙafafar su iyayen gidane kiga suna zuba doron iskanci, a tunaninsu sune kan gida yaransu ma sune manya" Tafawa suka yi tabb suna dariyar iskanci.

"Bari inje da wuri dana dawo zan san duk yadda nayi na tatsi kuɗi a hannunshi gobe sai muje. Dan ka haɗa miji da Shuwa dole ka zage damtse. Kinsan Allah ai na rakaki ɗakinta kinga falonta ko?

Hmm matarnan wani akwatine da'ita na gargajiya shake da magungunan mata na gargajiya da ƙwayoyin bature. Tana jina tayi wuf ta rufe, sai waɗanda ta daddama da nono na gani, ranar ita ke da girki."

Edit with WPS Office

Da kyar Hamida ta yakice dai ta tafi gidansu Babangida.

A ƙofar gida ta tarar da  Baba malam  tare da almajirai. Irin kallon daya watsa mata yasa tayi saurin tsugunnawa ta gaisheshi.

"Lafiya lau da fatan kuna lafiya?"

Dama jira take yi, nan ta shiga zaiyano mishi abinda ya faru. Bai hanata magana ba, kuma bai ƙi saurare ba har sai da ta dasa aya kafin yace.

"Kinsan gidan ƙanina ai ko Manga?"

Kai ta gyaɗa mishi.

"E na sani "

"Yauwa daga yau duk abinda ya haɗaki da shi Babangida can zaki nufa Babangida ɗan can gidanne kuma shi ya karɓi aurenki. Kije duk hukuncin daya yanke daidaine. Sabuwa ce kaɗai a cikin matanshi na ɗaura auren da kaina."

Ba ƙaramin mamaki tayi ba. Tunda take bata taɓa kawo mishi ƙaraba, saidai tasan duk ƙarar da Sabuwa ta kawo mishi yana ɗaukar mataki da kanshi. Ko labari yaji anyi mata wani abun da ba daidai ba yana ɗaukar mataki, kana ko abinci da Babangida ya dena basu taga ai shi ya ɗauki nauyin komansu.

Miƙewa tayi a sanyaye tace.

"Zan shiga in gaishesu"

Murmusawa yayi yace.

"To madallah "

Yaci gaba da biya ma gaddi karatu. Ita kuma tana shiga tayi kaciɓus da babban wansu Babangida shi da Malama Babba suna tattaunawa.

Hamida nan take ta hau tsiyayar hawayen munafurci.

"Ke lafiya menene ba dai sakin ki Babangida yayi ba? Wai Malama Babba so Babangida yake yi ya ƙarashe buga zuchiyar Baba Malam ne kafin hankalinshi zai kwanta?

Kinga ya saketa dan Allah da goyo, ga Farida can ya saketa da ciki sai ɗaukar ɗawainiyarsu Malam Baba yake yi"

Cewar wansu Babangida yana maganar da ɓacin rai.

"Wannan yaron kayi shiru ka rufa mun asiri kar a jiyo mu a cikin gida. Kasan kullum idanu suke zubawa suga ta ina da kuma me Babangida zai zo. Hamida saki nawa yayi miki. Da fatan

Edit with WPS Office

iyayenki basu sani ba tukunna ko?"

"Ba sakina yayi ba. Cewa yayi in tafi garinmu har sai ya neme ni"

Ajjiyar zuchiya du su biyun suka sauke. Wawo yace.

"To me kika yi mishi da zafi shi da bashi da haƙuri ana faɗa mishi ya rage wannan zuchiyar tashi?"

Nan ta labarta musu komai.

"Yanzu dai Wawo maza jeka ka mayar mishi da matarshi zai kuma zo wallahi ya same ni saina saɓa mishi. Kai bari ma muje tare kawai"

Ai kuwa taren suka fito Malama Babba ta je ta samu Malam.

"Malam dama zanje in mayar ma da Babangida matarshi ne ya korota. Izini nake nema"

Kur yayi yana kallon waje guda yaji kamar baiji ba. Sai can yace.

"Adawo lafiya"

"Malam"....

Yayi saurin ɗaga mata hannunshi babu shiri ya miƙe ya shiga rarratsa almajirai yana zungurarsu da sanda wadanda basa ɗaga murya.

Da ƙyar ta miƙe sabida rashin guiwa ta faɗa mota suka tafi.

Tunda suka tawo take tunane _tunanen baya zuchiyarta na suya mata.

"Sabuwa Allah ya isa tsakanina dake. Har abada kema kinbar samun farin ciki a haka zaki dauwama"

Ta faɗa a hankali tana sake tuno yadda a baya Malam ya fifita Babangida sama da duk yaran daya haifa, har takai ta kawo Malam baya son Babangida ya matsa kusa dashi, ga tsananin kamanninsu komansu iri ɗaya tamkar ƴan biyu girmane da furfura kaɗai suka bambancesu, wani murya, zati, ƙasumba, wushirya, tabon sallah, tafiya, tsayuwa, zama ku babu ta inda Babangida ya bar Malam fa.

"Malama mun iso fa. Dan Allah ki dinga sassautama kanki akan tunaninnan ke da Malam ɗin duk ba ishasshiyar lafiya bace daku ba. Ai yaci ace yanzu kunyi fatali da damuwar Babangida "

Ajjiyar zuchiya ta sauke tare da goge hawayen da bata san suna zuba mata ba.

Ashe har a farfajiyar gidan suke bata san sanda aka shigo ba.

Babangida yana goge motarshi ya bubbuɗe murafan dai-dai dasu Malama ta fito, ganin fitowar

Edit with WPS Office

Hamida yasa yazo a fusace yace.

"Wai ba cewa nayi ki kama hanya ki wuce garinku ba. Dan jar masifa shine kika je gidanmu. Ohh kema kin zama Lolo kenan ko? Malama Babba wannan yarinyar da kike ganinta ba mutunci bane da'ita ba. Ni na gaji ta wuce garinsu kawai...."

"Kai ka rufe mana baki a wajannan daga zuwa babu maraba balle gaisuwa ka hau jarabar daka saba. Wannan ɓakar zuchiyar taka dai tananan. Dallah kazo ka same mu a ciki"

Cewar Wawo kenan. Malama batace komai ba tabi bayansu zuwa ɗakin Hamida duk suka nemi waje sauka zauna harda Babangida dake zaune kafaɗa da kafaɗa da wanshi suna fuskantar Malama, Hamida kuma tana gefe can tana fuskantar ƙofar uwarɗakinta.

"To babu wani tashin tashina yarinyarnan kada ka kuma korarta kayi haƙuri koma me tayi maka ta zauna. Allah ya sani bana son yawan aure da sakin mata da kake yi Babangida. Yanzu jibi yaranka biyu basa gabanka, gana uku a cikin Farida shin daɗinka kenan? Ni in so samu ne kaje ka ɗebo yaranka kazo ka zube ma matanka su riƙe ma yara ko banza zasu taso a gidan ubansu kuma tare da ƴan uwansu"

Wawo yace.

"Tabbbas hakane. Amman Malama kin mance ne? Ai iyayen yarannan ba zasu taɓa danƙamai yarannan ba ko zai yi yayane. Ni nafi goyon da bayan iyayensu su riƙesu kawai shi dai a matsayinshi na mai sani yayi ƙoƙarin sauke nauyin yaran daya rataya a wuyanshi ba wai yabar Bana malam da ɗawainiyar da ba tashi ba, tunda shi yake yi musu duk wata ɗawainiya. Baba Malam abin a tausayama ne, kuma ya fi ku gaskiya. Son wannan ɗan banzan yaron mara ji ne ya rufe miki idanu."

Malama tace.

"Hakane Wawo shikenan. Babangida ka yafe ma Hamida taci gaba da zamanta akan ƴaƴanta. Ke kuma ki kiyaye abinda zaki yi mishi ya ɓata mishi ranshi ku zauna lafiya"

"Shikenan Malama taci sa'a amman wallahi da saita shekara tim a gidansu. Matane basu iya komai ba sai raini da kishin banza da wofi."

Nan dai Malama ta miƙe tace.

"Wawo muje maza ka mayar dani gida"

Tare suka fita dukkansu har saida motar su Malama ta fita Hamida ta koma ciki ta shiga aikace aikace a ranta tana aiyana Allah ne ya sota Na'ila ta bata wannan shawarar.

"Lallai ko nawa ne yau saina kashe na gigita kan baban Usama nasanshi da santi. Bari dai in gama aikina"

Nan ta shiga shara da goge_goge. Labule Babangida ya buɗe yayi ƙerere a waje.

Edit with WPS Office

"Zan fita da daddare kiyi shinkafa da wake da miya, waken ki dafa daban irin dahuwar yarbawa"

Harya sake labulen tace.

"Baban Usama sai dai babu kaza sai jan nama kai kuma ba cin jan nama kake yi ba"

Rai a ɗaure yace.

"Nifa bani da kuɗi babu kayan ciki, ko jelar saniya ne?"

A sanyaye cikin hadiye fishi tace.

"Akwai du biyun naga ne in miya za'ayi kafi son kaza su kuma kafi son ayi farfesu da..."

"Ji yadda kike tsara magana kamar an rubuta miki.

To kiyi farfesun jelar saniya da alkubus."

Kafin tayi magana yayi ficewarshi.

Ai gyaran ɗakin da bata kammala ba kenan ta zari mayafi ta ja hannun Usama sai gidan Na'ila tare da wasu manyan atampopinta.

"Kinga Waɗannan rakani zaki yi mu siyar in samo magunguna na tashin kai. Kwana biyunnan nayi sanyi da yawa da nayi magana sai faɗa sai hantara.

A gurguje Na'ila ta shirya nan tsakar gida suka bar yaran suka yi tafiyarsu.

Ai kuwa a gidan wannan mata yar Chadi anan Hamida ta sake gamuwa da mata ƴan a mutu ma maganin mata. Ƴan a sai da rai a nemo suna a wajen rijalu.

Kayan mata na dubu hamsin ta jida na cusawa ne, na sha ne, na shafawane duk gasunan.

Ai kuwa kafin dare tayi ɗib da maganguna ita kanta zamzam take jin kanta tun yamma.

Tana gama girkinta ta harɗe a falo taci ƙananun kaya ƙirjinnan nata rabi a waje suke, ta lallaɓa yarinya anata ɗirka mata mama har saida tayi amai kafin tayi baccin. Su Mardiyya kuwa suna ɗofane a cikin ɗaki tare da Usama.

Hmm a wannan daren dai Babangida yayi linƙaya sosai ya samu wadatacciyar gamsuwa ta musamman. Cikin farin ciki da nishaɗi suka kwana da asuba ma saida ya ƙara ace warshi babu karin kumallon daya wuce wannan. Kafi ɗumame😆

Edit with WPS Office

SABUWA:.

Da ɗakin su Baba Tabawa muka soma. Du suna zazzaune suma babu riga. Ni kam in banda jiri da ciwon kai babu abinda ke damuna.

"Adama yanzu dama kuna ciki baku je kun taya su aikin ba? Tun asuba su Tsahare suke cikin gidan fa. Lolo ke kam kar kiyi aiki kije dai ɗakin Aisha kiyi zamanki"

To Baba ina kwananku?"

Na gaishesu murya a sanyaye. Duk aka gaggaisa kana muka nufi tsakar gidan babban gidan me shashe shashe. Ni dai bayan tsaiwar gaisuwa na wajen mintina goma cikin ɗakin Aisha na shige nan na bar su Adama har sun kama aiki anata hira.

Akan gado na tadda Aisha a uwarɗakinta tana kwance lamo babu kowa a ɗakin an dai gyareshi.

Ɗagowa tayi ta dubeni sai naga damuwa dankare da ranta. Bakin gadon na samu na zauna.

Lafiya amarya da tunani, ina ƙawayen naki suka tafi?"

"Hmm sun tafi wanka gidan matar abokin Musa. Lolo kinsan Allah tun jiya nake tubka da warwara anya zan iya rayuwar gidannan kuwa?"

Harararta nayi nace.

Sai zaman gidan Maigogul da bashi da maraba da zaman kai shi zaki iya? Naga ai Zango ba ƙauye bane irin ƙayau ɗinnan ba. Ga wuta, ga makarantu, kuma naga matan garin babu laifi sai dai fa budewar idanu meye to matsalarki? Bayan kinsan shekaru huɗu kika kwashe kina zawarci ko zawarcin kika fi sone. Duk da kuke ganinmu a zaune a gidajen mazajen namu ba zaman dai akeyi ba.  Kufa kuke dankwafar dani in nace zan kaso aurena. Ai sai nake ganin rayuwar Zango tafi sau dubu akan rayuwar gidan Badaru. Ba a haka Labbai ta zauna har saida ya saketa da kanshi ba? Haka rayuwar Zango tafi rayuwar gidan Malam Habu amman a hakan Labbai tace zata shiga sabida gudun fadawa gararamba."

Ajjiyar zuchiya mai nutsuwa Aisha ta sauke tace.

"To Shikenan in sha Allah zan zauna Lolo. Kuma ina fatan in iya zaman"

Zaki iya in baki nuna mishi halinki ba. Ki dai kula kinga gidanku gidan yawa ne, duk abinda zaku yi kuyi a ɗaki ba'a tsakar gida ba. Banda cewa za'ayi dambe, ko a biyo miji da wuƙa a guje"

Dariya tayi ta jijjiga kai tace.

"Tabb wallahi sai dai in bata kama ba. Ai sanda namiji zai kuntuka maka wani du da gwa ɗin baka sanin ka dira ma a wuyanshi fa. In kika tsaya ke zai mayar bola kamar yadda kuka zama tsamaye ke da su Adama. Nifa da nice mijinki da tuni na tsinke mishi abinda yake bin mata dashi uban kowa ya huta"

Edit with WPS Office

Duka na kai mata muna dariya.

Shigowar Labbai da Layuza ne ya katse mana hirarmu.

Labbai na riƙe da robar fenti babba shaƙe da kokko, Layuza na ɗauke da katuwar kwalla lamba wan shaƙe da ƙosai, sai fanke cikin leda mai zane. Sai wani taɓe baki take yi tana wani mun mugun kallo.

"Aisha kije kiyi wanka wai an kai miki ruwan wanka, za'a zagaya dake wajan dangin surukarki, ashe bata aure anan gidan Musa kaɗai ma ta haifa anan."

Cewar fa Layuza tana yi tana yatsina aikinta kenan ƴar iska.

Aisha taje tayo wanka mu kuma muka shiga raba kayan abinci

Naci ƙosannan sosai kokkon dai babu sikari amman ni naji daɗinshi, su Adama kuwa sai aikawa sukayi akaita siyo musu sikari

Wanka muka yi dukkanmu na ɗakko atamfar ankon bikin yar shuwa na saka dan ɗinkinta yayi kyau kuma babbar atampa ce. Takalmina jakata kalar atampar,. Duk wanda ya kalleka sai yaga ka bambanta da ƴan uwanka, abinda yake sake cusama ƴan ɗakin su Layuza ƙiyayyata kenan suna ganina cikin rufin asiri a zahiri, a baɗini kuma sun fini kwanciyar hankali. Mota ango ya turo da ni, da Adama, da Baba Tabawa da Hauwane muka shiga mu biyar kenan, mu huɗu a baya Adama dake ƙatuwace saita zauna a gaba da direba.

Ango da ragowar mata danginshi suma suka cika ƙaramar mota muka wuce ɗan wani ƙauye nesa kaɗan da zango.

Acanma ashe bikine gagarumin gaske mahaifiyar Musa ta haɗa mun samu tarbar arziki sosai. Wasa_wasa mune har bayan isha a gidannan sai wajajen taran dare abokan ango suka zo suka mayar damu. Uwar ango ta haɗomu da kayan arziki cikin bokiti atampopine masu tsada banda kuɗi da aka taru akaba A'isha bokiti ta dinga zaga mutanen biki suna saka mata kuɗinnan. Manyan kuɗi domin nuna bajinta fa akaita sawa haka al'adarsu  yarensu take., amman uwar ango ko Hausa ta kirki babu a bakinta.

A tsakar gida muka tadda jama'ar biki, muma muka baje daga mu har Aishan a waje muka kwana.

Washegari kuma tun wuri muka shirya aka raka mu kasuwa, biki dai akeyi yau kuma dangin ango na wajen uba suke nasu wunin.

Mu dai muna kasuwa wajen kashe ƙwarƙwatar idanunmu da siyan ɗan tsaraba dai.

Da misalin ukun rana. ina kwance a kujera a falon Aisha ina karanta dadaɗan saƙonnin Khalid daya tura mun ta WhatsApp inata murmushi. Hotunan da muka yi a biki na tuttura mishi na haɗa mishi da kalaman soyayya harma na faɗa mishi yanayin jikina.

Edit with WPS Office

"Hawan jininki ne ya tashi. Bakya ji shi yasa nace karki tafi amman kika shagwaɓe mun akan ke kina so kije ga irinta nan kinsan ciki ma na ɗaga hawan jini."

Dariya nayi tare da lumshe idanuna, haƙiƙa ina jin daɗin yadda Khalid yake nuna tsantsar kulawarshi gareni.

To kasan fa bikin ƴar dakinmu akeyi shi yasa. Amman gobe sassafe zamu dawo inaso kuma in ganka kafin in koma gida"

Na rubuta na tura mishi, baije ba ma sabida network. Saƙwanni na ɗan dudduba  na ajjiye wayar.

"Lolo Adama yanzu yarinyarnan waɗannan uban kuɗi da aka tara mata kuɗi kusan dubu ɗari biyu me kuke ganin zata yi dasu gudun kada su salwanta?"

Cewar Rahama. Wannan tace fili, wannan tace tasai awaki, wannan tace ta kama sana'a.

To ni ina ganin ta raba kuɗinta biyu cib rabi ta kawo a siya mata zinare ta samu na shiga taro, rabin kuma ta zauna ta nutsu inma kiwon zata yi. Ni da Labbai zamu iya shiga gari yanzu a siyo mata ta adana abinta kudin lalacewar kuɗaɗenta"

Nan akayi na'am da shawarata, Rahama tace.

"Kirgo kuɗin ki bayar suje a sirrance a siyo miki Lolo tayi kyan kai"

A lokacin gram na zinare nera dubu hudu ne, Allah sarki rayuwa.

Haka muka shiga gari kasuwar ƴan gwala-gwalai  muka sai mata ɗan kunne da sarƙa babba, har nima na sai ɗan kunne da sarƙa ƙarami na dubu hamsin daga cikin kuɗin da Khalid yake yawan turomunne, daman a baya ma na sai ɗankunnena mai kyau yana adane.

Washegari sassafe mukai sallama da matan gidan, Aisha na kukanta haka dai muka rabu. Ta bada turmin atampa, sabulun wanka, da man shafawa a kawo ma Rakiya. Uzairu zuchiyata fa shiga gari yayi bamu ganshi ba ma ashe tuni ya dawo gida garin babu daɗi kuma matan garinne basu yi mishi ba dama sabida su yaje.

Zuwa bayan la'asar sai gamu a ƙofar gidanmu.

Nan aka kacame da hira, dole haka na kuma kwana dan zazzaɓine sosai a jikina. Munyi da khalid gobe zai zo muje ya kaini asibity dan ba ƙaramar damuwa ya shiga ba.

MRS BUKHARI

Sanya kuɗin karatun a cikin wannan lambar asusun

Edit with WPS Office

0044442984

Buhari Ibrahim Ladan Gt bank

Lambar da zaku turo shaidar biya gasu kamar haka

08022059556

Ko kuma

08105932041

Masu son magana da marubuciyar kai tsaye kuma ga lambata

Wa.me/2348179523215

IDAN KAYA YA GAJI..

GAMMO MA YA GAJI

BADIAT IBRAHIM MRS BUKHARI B4B GIDAN KAMSHI

SHAFI NA ASHIRIN DA TARA.

https://chat.whatsapp.com/E3bH5OKBh9jH2aYygj0ArA

Kina bukatar kaya masu kyau da inganci??

Edit with WPS Office

Kina bukatar kayan kitchen wnd suke available ba order ba??

Kina bukatar adashin gata wnd zaki dauki kaya kamar kyauta??

Kiyi joining wnn group din namu insha Allah xakiji dadin kasancewa a ciki.

Muna da kaya available masu kyau da rahusa 💃🏾💃🏾

Ko kimin mgn ta👇🏽👇🏽

08093932955

Tun safe muka soma shirin komawa gidajenmu, Adama kam tun jiya da daddare tsohuwar soyayya ta tashi mijinta ya durfafi kiran wayarta. A lokacin muna mayar ma da Rakiya yadda akayi. Rakiya dai cewa tayi.

"Ai koma ina aka kaita yafi mata, Zango ai ba ƙauye bane ma babu dai wayewa kamar birni. Fatanmu shine Allah yasa ta yadda ta zauna mitsiyaciyar kar taje ta daka ɗan mutane"

Akwatin kayana na ɗauka nace.

To ni kam zan tafi asibiti ma zan wuce daga nan jikin nawa yaƙi"

Rakiya tace.

"Zuwa gobe in Allah yasa muna cikin rayayyu zan kawo miki su Tabawa Tsahare zata ɗan zo tayi miki kwana biyu kafin ta dawo"

To Rakiya Allah ya kaimu. Baba sai kun zo.

Sallama nayi musu na fito. Khalid na bayan layinmu yana jirana a mota. Da Maigogul naci karo zai shigo. Yana ganina ya washe bakinshi.

Edit with WPS Office

"Lolona tafisu tafi sauran mata ashe kun dawo dake sabida baƙi bana kwana a gidan.

Maigogul ina kwana?"

"Ah baki da lafiya ne Lolo naji miryarki irinta marasa lafiya?'

Ya tambayeni cike da kulawa"

E bani da lafiya asibiti ma zanje yanzu haka daga nan kuma sai in koma gida inje in kwanta"

Maimakon ya damu da halin daya gani a ciki a_a burinshi kawai in bashi kuɗi. Dubu uku na zaro na bashi ya dinga godiya ni dai a wajen na tafi na barshi, na ɓille ta lungu nayi sauri na faɗa motar Khalid.

Yana zaune yana sauraren waƙar 2 Baba wanda akafi sani da 2 face a cikin waƙarshi mai taken Sarauniyar Afirka (African Queen). Idanuna na lumshe ƙamshi da sanyin motar ne yake ratsani ga ɗumin zazzaɓi da nake jiyo turirinshi a hancina.

Hannun Khalid naji a jikina yana aikin tattaɓani tare da raɗamun wasu kalamai a kunnuwana masu rikitani.

A hankali na tureshi nace.

Bana son ƙamshin turaren jikinka tayar mun da zuchiya yake yi sosai"

Dariya yayi cikin kulawa yace.

"Wannan Babyn nifa ya takura mun. Dana sani ban saka ƙamshin ba ai kuma wannan kwalliyar musamman taki ce"

A haka yaita jana da hira har muka isa wani asibityn kuɗi dake bayan gari haka.

Likitannan ya gama duk aune aunen da zaiyi da tambayoyin da zaiyi mun. Khalid na gefe riƙe da jakata.

"Alhaji gara da Allah yasa kai da kan ka ka kawo Madam asibiti. A zahirin gaskiya ina bada shawarar in da hali da kun haƙura da wannan cikin inaga zaifi. Jininta ya hau sosai hakanma zai iya taɓa lafiyar abinda ke cikin nata, ita kanta tana cikin haɗari mai girma, ga deepretion da yayi mata yawa ya kamata a duba ita lafiyarta a farko tukunna. Bana bada shawarar taci gaba da renon cikinnan gaskiya. Barazanane ga lafiyarta, yanzu haka akwai buƙatar dole a bata gado"

Ni dai ina zaune babu yadda nake jikinma kuma tsananta yake, marata sai riƙewa take yi tanai mun wani irin damƙa da juyi. Likita yace a cire ciki, ni kuma akwai sharaɗi a kaina. To ƙila wannan dake cirewa zasu yi da kansu oho dai. Juyowa Khalid yayi ya dubeni.

"Baby ya kike gani, in barki a wannan asibityn ko in mayar dake janaral asibity sabida gudun matsala uhm Babyna?"

Edit with WPS Office

Ya tambayeni cike da kulawa dan duk hankalinshi a tashe yake, ni kaina hankalina yayi mugun tashi hawayene suka zubo a kan kumatuna. Idanunshi ya runtse ya miƙar dani tsaye.

"Dr ina zuwa dan Allah "

Fita yayi dani ya sani a mota. Ya suka ƙare da likita Allah masani ni dai ya tuƙani zuwa asibiti babba.

Muna isa cikin gaggawa aka tarbeni aka bani gado.

Labbai da Baba Malam kawai na ba Dr lambarsu ta kirasu, ban bi ta kan wani Babangida ba.

"Dr dan Allah ina neman alfarma"

Na faɗa ina cije baki.

Drn ta dubeni tace.

"Ina jinki Sabuwa menene?"

Dan Allah bana so ƴan uwana su san ina da hawan jini, ko wani ciwo na daban."

Murmusawa tayi tace.

"To ai Sabuwa dole ne fa su sani sabida dole sai mun faɗa musu dalilin cire cikin, ba haka kawai ake cire ciki ba fa. Amman ke me yasa kike ɓoye cutar da take damunki?"

Kuka na rushe mata dashi mai tsanani ina roƙonta.

Tare da jaddada mata ciwon ƴa mace na ƴa mace ne.  Bawai dan na yarda da kalmar ba.

"Shikenan ki dena kuka Sabuwa, nasan me zance musu nasan dole kina da naki dalilin. Amman ba zamu tsaya jiran ƴan uwanki ba zamu shigar dake kawai ayi gaggawar cire miki cikin sabida kina cikin mawuyacin hali ni nayi mamakin da kike iya magana ma.

Jinine ya ɓallemun ina daga kwance har zuba yake yi wallahi a ƙasa kamar fitsari tsi_tsi.

Ni daga nan banma sake sanin halin da nake ciki ba na sume.

Baba Malam:.

Yana zaune a ƙofar gida yana karatun wasu littattai kira daga asibiti ya isheshi cewar Sabuwa surukarshi babu lafiya. Babu shiri ya miƙe ya shiga cikin gidan.

Edit with WPS Office

Ɓarayin Malama Babba ya wuce, tana zaune tare da ɗalibanta mata a falonta Baba Malam yayo gyaran murya.

"Babba ki fito muje asibiti matar Babangida babu lafiya daga asibitin ma aka kirani"

Babu shiri Malama Babba ta miƙe duk tabi ta ruɗe ita a hasashenta Hamida ce.

Umarni Malam ya bayar akan a biyo su da ruwan zafi da abinci.

Suna fitowa suka ci karo da Wawo shigowarshi kenan.

"Juya ka kaimu asibiti Wawo"

Baba Malam ya faɗa murya ba ƙarfi.

Har suka isa asibity babu wanda ya kula kowa. Kiran lambar da aka kirashi da'ita Baba Malam yayi, take aka ɗauka.

"Yarinya gani a asibitin a wanne ward take ne?"

Daga wayar tace.

"Tana ɓangaren ƴan haihuwa Baba yanzunnan aka shiga da'ita ɗakin tiyata ma"

Duk suna jin abinda likitan take cewa.

Kan Malam ya ɗaure sosai duk da hakan bai yi musu ba, suka nufi ward ɗin masu haihuwa. A wata ƙofa suka tarar da Rakiya a zaune tare da Labbai. Nan take Malama Babba ta haɗe girar sama data ƙasa"

"Sannunku Rakiya yanzu kuke tafe ne?"

Cewar Baba Malam

Da dariya Rakiya ta gaishesu, Baba malam ne kaɗai ya amsa, Wawo kuma ya gaisheta ta amsa da fara'arta. Malam yana lure da Malama bata amsa gaisuwar Rakiya ba.

"Bamu daɗe da zuwa ba kuka iso. Lolon fa bata daɗe da fitowa daga gida ba. Dama jiya da suka dawo jikin babu daɗi sam, acan ma ance a kwance aka ƙarashe bikin da'ita sai kuma ga kira. Bamu samu ganinta ba ma"

A wulaƙance Malama Babba tace.

"Dama ita Sabuwan ciki ne da'ita. Dan naga nan ɓangaren ƴan haihuwane. Wannan ɗakin da take ciki kuma, ɗakine na wankin ciki, nan aka taɓa kawo Sa,a ɓarin da ta taɓa yi"

Kallon da Baba Malam yayi mata ne yasa ta gane tayi ɓaranɓarama idanta ma rufewa yayi ta mance shab Malam yana wajen.

Edit with WPS Office

"Cikine da'ita yama kwana biyu ai"

Labbai ta bata amsa  a fitsarance.

"Wawo kira Babangida maza yazo "

Baba Malam ya faɗa tare da zama a kujerar dake fuskantar su. Carab Malama Babba tace.

"Ai da an barshi yana wajen aikinshi Malam. Duk abinda ya kama ga ka ga Wawo zaku yi ai ko? Dan Allah kabar yaro ya yi aikinshi."

Rakiya tace.

"Hakane malam daka barshi ai, kuma da kuka zo wallahi naji daɗi sosai Allah ya saka da Alkhairi"

Kai Malam ya girgiza kawai ya ciro wayarshi ya daddanna lambar Babangida ya kirashi.

Da sallamarshi ya amsa yana wani larabci kamar gaske.

"Kazo babban asibiti ɓangaren ƴan haihuwa ka same mu yanzunnan. In zaka tawo kazo da kayan tea, kasa matarka ta dafo ruwan zafi ka tawo dashi, kana ka umarceta da yin girki"

Kit ya datse wayarshi. Maigogul ne ya ƙaraso wajen, tun kafin ya iso ƙamshinshi ya iso, yana cikin shadda wagambari mai ruwan toka, komai nashi fes kamar wani ɗan majalisar jaha, ko wani hamshaƙin ɗan kasuwa. A kusa da malam ya zauna ya miƙa mishi hannu aka gaisa, hannayenshi cike da zobunan azurfa masu tsada har uku.

"Malama ina wuni, ya kuma me jikin dai?"

Ya faɗa yana kallon Malama.

"Jiki bama ce ba tunda bamu samu ganinta ba"

Kai ya girgiza yace.

"Wallahi ina can wajen sana'ata nayi baƙin manyan mutane mata nine mai masaukinsu kuma maji daɗinsu, sai ga kira Rakiya ta yo mun kira Ɗaxunnan muka rabu da'ita harma ta bani dubu uku, a ciki na ba mata kuɗin cefane na ɗan soke ragowar a aljihuna. Allah dai ya ba Lolo lafiya"

Malam wani ƙududun baƙin ciki da takaicine ya turniƙeshi da ƙyar ya haɗiye. Wai shine mai siriki kawali, kuma har yake faɗan daga wajen sana'arshi yake, kuma shine ma maji daɗinsu ya dace ya faɗa mishi haka kenan ?

yace dashi.

"Ameen ya Allah"

Edit with WPS Office

Iyakar abinda yace kenan duk akai shiru. Maigogul dai yaita amsa waya kamar wani babban ɗan kasuwa"

"Maigogul ka saka wayarnan a silent ko ka kashe baki ɗaya, a asibiti muke fa"

Cewar Rakiya da ranta ya ɓaci, su Malama Babba ko ba'a magana.

"To azagwaigwai a masallaci muke ko a makabarta da bazan amsa waya ba?  Kasuwa ta buɗe mun ina neman na rufin asirin ku amma kina in kashe waya?'

Da faɗa yake maganar ya dubi  Baba malam  yace.

"Dan Allah kaji abinda fa take faɗa mun malam"

Ya ƙura mishi idanu yana jiran amsarshi.

"Kayi haƙuri abinda ta faɗa ba laifi bane. Inma zaka amsa wayar sai ka je gefe ba nan cikin mutane ba"

Sai kuma ya sassauta yayi shiru.

Kofar ɗakin da suke tsaye aka buɗe sai ga Lolo a kan gadon marasa lafiya an tuƙota tana kwance samɓal tana bacci, wani irin muguwar rama na farad ɗaya ta ƙara gashi tayi wani irin mugun haske sosai."

Miƙewa suka yi suka bi bayan ma'aikatan jinyar har zuwa ɗakin masu haihuwa.

A gado suka ɗaurata Dr khadija maidoki tace.

"Waye mijin nata a cikinku?" Ta ƙure Wawo da idanunta.

"Ni wan mijinta ne, wannan iyayenmu ne, mijin nata yana hanya"

"To dan Allah inason ganinka domin in maka bayani.

Baba zaku iya jira a waje, ɗakin matane ba'a fiye barin maza su jima ba. Su matan zasu iya zama tare da'ita karsu wuce mutum biyu kuyi haƙuri '

Cike da ladabi da biyayya take magana dasu.

Fita tayi hannunta na cikin lab kot ɗin data ɗaura akan jar atamparta.

Malam da Maigogul suka bi bayan wawo. Tsulum Malama Babba ta miƙe.

"Ina daga waje"

Ta faɗa a kausashe. Labbai tace.

"Rakiya kayi nayi kije waje kema ki zauna ki huta zan zauna da'ita"

Edit with WPS Office

Rakiya ta miƙe tabi bayan Malama Babba, su suka zauna a wata baranda matan, mazan kuma suka zauna a benci. Suna zama Babangida na isowa hannunshi niƙi_niƙi da ledojin kayan tea harda biredi me kwakwa da ƙaton filas na ruwan tea Hamida na biye dashi.

Shi ko Wawo yana ofishin Dr khadija maidoki tana yi mishi bayanin bogi domin rufa ma Sabuwa asiri dan bata san uzurinta ba, amman tabbas tasan tana cikin damuwa mai yawa.

"Sakamakon tafiya da tayi da ƙaramin ciki a jikinta hakan ya jigatata sosai ya taɓa lafiyar cikin kasancewar cikin ƙaramine. To cikin ya fita da kanshi sai muka wanke mata cikin nata sakamakon ragowar da bai gama fita ba. Ta yi asarar jini masu yawa tana buƙatar ishasshen bacci da hutu, sannan tana buƙatar ƙarin jini kamar leda huɗu haka, muna buƙatar jinin inda hali yau, kar dai ya wuce gobe ko da zai wuce yau ɗin. Sannan dan Allah mutum ɗaya muke buƙatar ta zauna da'ita dan gudun hayaniya a kanta. Daga yanzu dai zata yi bacci har na tsawon awa ashirin da huɗu allurar baccin da mukai mata tana da ƙarfi sosai." Dr Khalid kafin ya bar Sabuwa a asibiti yayi Magana da abokinshi Dr Jamilu akan a kula sosai da Sabuwa wannan dalilinne yasa har akayi mata komai ba tare da sun ajjiye kuɗi, ko wani nata yazo ba.

Wawo ya yi kasaƙe yana tunanin irin illar da Babangida yayi musu na gayyato zuriyar maigogul cikin tasu zuriyar amman ƙaddarallah.

"To Shikenan Dr mun gode Allah ya saka da Alkhairi. Bari in ƙanina yazo zamu zo a ɗebi jikinshi in yayi daidai da nata, mun gode"

Wawo ya fito yana tafe yana karkaɗa kai har ya iso inda su Malama da  su  Baba Malam suke zaune

Ga Babangida ya haɗe ranshi tamkar an aiko mishi da saƙon mutuwa bayan an gama bashi labarin Sabuwa ce babu lafiya, yana kamfani yana wata harkar arziki  Baba malam  ya harziƙoshi a tunaninshi ma ko Malama Babba ce babu lafiya shi yasa ya tulo uban kayan tea ko madara nido ya siyo ta babban gongoni, ga bombita, ga siga, ga bota da biredi, ga tea yasa an dafo harda ɗan farfesun kifi da akayi mishi yasa aka ɗebo Hamida ta riƙo.

"Wawo yaya ake ciki ka fito, ya kukai da likita?"

Cewar  Baba  malam daya ɗauke kallonshi daga kan Babangida da tunda aka faɗa mishi Sabuwa ce babu lafiya yake ta ƙunƙunni, shi kuma yana karance yanayinshi.

"Cikin dake jikinta ne ya samu matsala, shine akai mata wankin ciki, kuma sakamakon jinin data zubar ana bukatar jini da za'a ƙara mata. Likitan dai tace kada ya wuce yau, ko kuma gobe, na dai ce bari mijinta ya ƙaraso, ashe yazo sai yaje ya samu Drn da kanshi. Baba Malam zan mayar dakai gidane? Dan ance sai zuwa gobe uwar haka ma zata farka sabida allurar da akayi mata da ƙarfi"

Ajjiyar zuchiya ya sauke. Babangida ya shiga mamakin ciki da akace Sabuwa na dashi. Hamida kuma a ranta tace.

Edit with WPS Office

"Namiji kenan ɗan babanshi a cikin kaso ɗari na zantukan rijalu kaso casa'in du karyace da labarin ƙanzon kurege. Shi da yace yafi shekara bai kasance ta ba, ashe ƙarya yake yi har tayi ciki ya zube ciki kuma ƙarami.

Maganar  Baba Malam ce ta katse ma Hamida tunanin da take yi mai zurfi.

Sallama yayi musu, ya zaro kuɗi ya danƙama maigogul yako yi carab ya dafe kuɗin tare da hannunshi.

"Angode Allah ya saka da Alkhairi Allah ya ƙara buɗi"

Haka suka kama hanya suka wuce Hamida kuma Babangida yace ta jirashi, tana zaune a kusa da Rakiya"

"Ka dafe kuɗi ai sai ka bani kaso na ko kafin inji kiɗa a magwan"

Cewar Rakiya kenan harda buga cinya"

"Kai kayi nayi akwaiki da tsinannen son kuɗi, yanzu sai an raba wannan kuɗi ku da zanma hidima da kuɗin. Babu ko ƙwayar hatsi ke kin sani a gidan. Naga ku da zaku kwana anan jibi kayan alatu rigi_rigi da yaronnan ya kawo"

Yana magana yana zazzare idanu.

"Ai kuwa baka isaba kasan Allah sai ka bamu wani abun tunda ko ka kai abincin bana gidan ba ci zanyi ba. Yarana nasan babu wacce zata zauna a gidan balle kace zaka basu su dafa, Hauwa ce dai makirar matarka ba dafawa zata yi ta basu ba. Suma ba isasrsu zaiyi ba. Inma fa kakai ɗin kenan. Kila ma ai tela zaka kaima"

Kwafa yayi ya zaro dubu biyu ya miƙa mata ta fisge kuɗin tana ci gaba da maganganu. Hamida kuwa sai naɗewa take yi a fakaice saida tayi musu vidiyo ba tare da sun sani ba, data ga sunata haɗa idanu da Labbai ne tasha jinin jikinta ta ajjiye wayar."

BABANGIDA:.

Da sallama ya shiga office ɗin Dr bayan ya raka su Malama bakin motarsu.

"Dr nine mijin Sabuwa, wana ya faɗamun ana buƙatar jini, ni kuma ba ishasshiyar lafiya bace dani. Shine nace ko akwai jini na siyarwa?"

Saida ta gama rubuta abinda take rubutawa a laptop ɗin dake gabanta tace.

"Bama rasa jini a asibiti, akwai bayin Allah da suke zuwa a ɗebi jininsu kyauta a ajjiye a lap domin a taimaki mabuƙata dashi. Amman a cikin ƴan uwa ko dangi ba za'a samu waɗanda zasu...

Edit with WPS Office

"Dan Allah Dr a bamu jini na siyarwa kawai."

Ya katseta a fusace har yana wani dafe kai gami da lumshe idanununshi. Yar Shuwa da Ramatu sai garashi suke yi. Ramatu sai tatsan manyan kuɗi take yi a hannunshi gashi taki dawowa.

"Ok Shikenan za'a duba wanda yayi daidai da nata jinin, zuwa anjima kaɗan sai ka dawo aje a biya kuɗin jinin"

Da sauri ya zabura ya fice, sai a bakin ƙofa yayi godiya. Da harara Dr khadija maidoki ta bi bayanshi harda ɗan guntun tsakinta.

"Duk yadda akayi wannan miji na sabuwa shine matsalarta. Da ganinshi bashi da daɗi kamar kashi, gashi da faɗa da saurin fishi."

Baki ta taɓe ta miƙe a tsanake ta nufi lap domin samo jinin da za'a ɗaurama Sabuwa..

Shi kuma gogan a gaggauce ya fito.

"Ke taso mu tafi maza ana jirana a kamfani "

Kuɗaɗe ya zaro a ajjihunshi ya miƙa ma Rakiya.

"Dr zata buƙaci ku biya kuɗi sai a zara a biya in bai isaba sai ku kirani a waya a sanar mun."

Dam Rakiya ta riƙe kuɗin.

Maigogul yace.

"Amman naga baka buƙaci ganin Sabuwan ba ko?"

Ko juyowa bai ba yace.

"Gobe in nazo na ganta "

Suka sha kwana abinsu.

"To nima dai gaskiya inaso zan tafi ina da baƙi, gobe zan dawo dam ba a gida zan kwana ba.

Rakiya zuba mun abinda ke kular inci sai in wuce, ki haɗa mun tea mai kauri"

Labbai ta miƙe ta shiga duba Sabuwa, tanata baccinta hankalinta a kwance.

Maigogul yana cin farfesun kifinnan sai ga tuwo daga gidan Malam Baba ƙanin Babangida ya kawo, da kafet harda filo"

"Kaga kuwa dama inata zuchi_zuchi ince maka ka sa yarannan su kawo mana ko da tabarmane, sai gashi sun kawo"

"Uhm Rakiya Allah yaba wannan yarinya lafiya ni kinga tafiyata"

Edit with WPS Office

Haka su Rakiya suka zauna su biyu da Labbai, Labbai sai suntirin shiga dubo Sabuwa take yi, ko motai bata yi, Dr tazo ta daura mata jini a hannunta.

Labbai ce ta je ta biya ta dawo a cikin kuɗin da Babangida ya bayar nera dubu goma da ɗari biyar ce tayi rara Rakiya kuwa ta soke.

Washegari tun sassafe su Adama suka zo asibiti duba Lolo, zuwa hantsi su Tabawa Uzairu zuchiyata ya kawosu suma suka dubata.

Sai wajen azahar aka aiko abinci daga gidan Babangida amman babu wanda yazo asibitin da sunan dubiya har yamma.

Da misalin ƙarfe biyar da arba'in Sabuwa ta farka"

SABUWA:.

a hankali na buɗe idanuna da sukaimun nauyi sosai. Hannuna na kalla naga ƙarin jini akeyi mun, jikina da ƙasana na mun wani irin ciwo. Idanuna na lumshe wasu hawaye suka gangaro mun a hankali.

"Ah Lolo ta tashi Rakiya "

Cewar Labbai data shigo ɗakin yanzu"

Bani ruwa in sha Labbai ƙishi nake ji"

"Labbai kira likita, bari in bata tea tasha ta warware hanji ance kar a bata ruwan sanyi"

Cewar Rakiya kenan.

Kakkauran tea ta haɗamun na samu na jingina bayana a jikin ƙarfen gadon ina shan tean a hankali. Ga wani irin jiri na ɗibata

"Sannu Lolo Allah ya baki lafiya. Salaha tana hanya nace tazo yau ta kwana, ni kuma inje gida sabida gobe sassafe baƙi zasu koma"

Ban bata amsaba sai ga Dr tare da Labbai.

Ƴan tambayoyi da aune_aune tayi mun.

Ta bani magungunan hawan jini tace in naci abinci sai in haɗiya.

Godiya nayi mata.

Tuwon shinkafa miyar yakuwa da nama Rakiya ta zuba mun, naci babu laifi na hadiyi magungunana sannan na rama sallolina ina daga zaune sabida jiri nake yi sosai. Ban jima ba na

Edit with WPS Office

sake komawa bacci. Babu inda baya yi mini ciwo

Bayan na tashi wajen taran darene su Salaha suke sanar dani Babangida yazo amman ko minti biyar baiyi ba ya kama hanya ya tafi.

Hmmm"

Shine abinda na iya cewa danni ta kaina nake.

Kwanana biyar a asibiti, amman Malama Babba bata sake zuwa ta duba ni ba. Sa'a da Kudidi dai sunzo, suma basu fi minti biyar ba suka koma. Hamida sau ɗaya tazo, ana dai kawo abincin dare, na rana daga gidansu Babangida ake kawowa. Khalid kuwa kullum saiya zo ya duba lafiyata cikin dare.Salaha na tura ta kawo mun yarana suka ganni. Sai naga har ramewa suka yi, kuma duk sun yi wani iri dasu.

Da safe aka sallamemu su Adama tare muka rankaya gidana harda Laraba.

Su sukai mun aikin komai ina kwance a doguwar kujera.

Maƙota sukaita shigowa dubiya, daga ƙarshe sai gudu nayi ciki nace duk wanda yazo ace nayi bacci kafin suka barni na huta.

Hamida kuwa ko leƙe bata shigo ba. Gidan naga aikin ɗora sama akeyi ga bulo jingim a tsakar gidan, da muke shigowa ma motar bulo muka gani shaƙe da bulo anata saukewa.

Da yamma lis su Adama sukai mun sallama Tsahare dai nace ta zauna ta taimaka mun.

Yara kuwa da suka dawo suka ga na dawo ai sai suka shiga murna Mardiyya harda sauke ajjiyar zuchiya.

Muna zaune ina shan tea ga magungunana a gabana. Yaran kuma abinci suke ci, Mardiyya na karatun qur'ani, sai Tsahare dake goge mun kayan yara Babangida ya shigo da sallamarshi.

Kir idanunshi akan Tsahare dake guga ta sunkuya ƙirjinta a baiyane sosai.

Sannu da dawowa"

Na faɗa da muryar ciwo. Amman baima san inayi ba.

"Ina wuni Alhaji mun sameku lafiya?"

Cewar Tsahare.

A dibibice ya amsa harda dariyarshi yana tambayar mutan gida"

Miƙewa tayi ta bar wajen, shiko yabi ƙirjinta dake rawa da kallo. Yara suka bi bayanta.

Gyaran murya nayi.

Edit with WPS Office

"Ehh me kike cewa Lolo?"

Ya faɗa a gigice.

Shiru yayi ya ƙurama waje ɗaya idanu

"Wow Kai kaga wata lafiyayyar yarinya?"

A hankali ya faɗa ni kuma naji sarai me yace.

Na riga na tsorata da sha'anin Babangida.

"Sabuwa me aiki kika samu ke?"

Ya tambayeni a sake"

Hmm a_a yarinyar ƙanwar Rakiya ce da suka zo biki"

"Ayya bata koma ba kenan?"

Gobe zata koma."

Na watsa magungunana na bisu da tea.

"Wai yaushe kika ɗauki cikin da harni bansan kina dashi ba, ko dai a yawon bin maza kika samoshi Sabuwa?"

Ji wata tambayar rainin wayo.

Ranar daka kwanta dani ranar cikin ya shiga"

Miƙewa yayi  ya nufi ɗakinshi.

"Kisa a kawo mun abincina yanzu. Wallahi dan dai cikinnan ya zube ne kawai bazan tsananta bincike ba."

Ya ƙule harda banko ƙofar.

Daddagewa nayi na miƙe na haɗa mishi komai a tire nakai mishi da kaina. Daga shi sai gajeren wando na shiga na sameshi.

Nadai ji yana waya kamar yana cewa an riƙe motocinsu a hanya shaƙe da kayan ƙarafai na miliyoyin kuɗaɗe. Tiran na ajjiye mishi nayi ficewata. Ɗakin yaran na shiga nace.

Tsahare taso muje ki kwana a ɗakina"

Miƙewa tayi tace.

"Gugar fa?'

Edit with WPS Office

Muje ɗakina kiyi tunda Babansu ya dawo.

Mardiyya in kuka gama ku kwanta ni nasha magani zanje in kwanta."

Sukai mun sallama, mu kuma muka tafi ɗakina.

Laraba na guga ni kuma ina ɗan duba chart haka dai da groups ɗinmu na littafi da muke zumunci sosai.

Mu ka ɗan taɓa chart da khalid bacci yai awon gaba dani jikina babu ƙarfi ko kaɗan ciwon ciki ya far mun sosai. Dama tun da akayi mun wankin cikin sai nake jin kamar wani dunƙulallen abune a cikin cikin nawa yake yi mini ciwo.

MRS BUKHARI.

Sanya kuɗin karatun a cikin wannan lambar asusun

0044442984

Buhari Ibrahim Ladan Gt bank

Lambar da zaku turo shaidar biya gasu kamar haka

08022059556

Ko kuma

08105932041

Masu son magana da marubuciyar kai tsaye kuma ga lambata

Wa.me/2348179523215

IDAN KAYA YA GAJI...

GAMMO MA YA GAJI

BADIAT IBRAHIM MRS BUKHARI B4B GIDAN KAMSHI

SHAFI NA TALATIN

Edit with WPS Office

https://chat.whatsapp.com/E3bH5OKBh9jH2aYygj0ArA

Kina bukatar kaya masu kyau da inganci??

Kina bukatar kayan kitchen wnd suke available ba order ba??

Kina bukatar adashin gata wnd zaki dauki kaya kamar kyauta??

Kiyi joining wnn group din namu insha Allah xakiji dadin kasancewa a ciki.

Muna da kaya available masu kyau da rahusa 💃🏾💃🏾

Ko kimin mgn ta👇🏽👇🏽

08093932955

Washegari yara na tafiya makaranta nace da Tsahare ta shirya ta tafi gida mai gidanne yace ta koma gida"

"Amma ko nayi wani abunne jiya? Ɗazu ma ya leƙo yasa na shigar mishi da abinci ɗakinshi, harma ya bani kuɗi"

A tsorace na dubeta nace.

"Ni ina ina akayi duk wannan aikin. Yasa fa kika kai mishi abinci ɗakinshi fa, shiga kika yi ko daga bakin ƙofa kika tsaya?"

"Shiga nayi, aradu shi yace in shiga in ajjiye mishi a kan gado"

Edit with WPS Office

Ajjiyar zuchiya na sauke. Tur da halin Babangida wlh tur tur tur.

Hannunta na jawo fuu muka shiga ɗaki, kwancen kaya kala uku na zakulo mata. Na bata kuɗin mota, na aunar musu shinkafa da wake, mangyaɗa harda maggi, na bata dubu biyu nace ta ba Rakiya.

Sai da ta tafi na sauke ajjiyar zuchiya mai nauyi.

Ina zaune a falo Babangida ya shigo da sauri ashe baya ciki. Bai daɗe ba ya fito hannunshi da takaddu ya fita a gaggauce yana waya."

Yana fita Hamida ta ɗaga labule, labulen na hannunta sannan tayi sallama sai fisga take yi"

"Yaya jikin naki? Jiya kun shigo bananan dake mune akan bikin yarinyar Yaya Sa'a muna can ana cincin. Yanzu ma jere zani nace bari in duba jikin naki"

Ta faɗa tare da dure mun ledar kayan yara.

Jiki Alhamdulillah. Ayya biki kam yazo, ni sai ranar sakun lalle zanje in sha Allah kya gaishesu"

Bata ko tanka ba tayi wucewarta.

Ina jiyota suna gaisawa da Maman Safarau tana tambayarta ashe an sallamoni"

"E an sallamota jiya nima sai ganinsu nayi"

Amsar data bata kenan tana kwakkwaɓe bakinnan nata. Da sallama Maman Safara'u ta shigo, hannuna riƙe da kaskon turaren wuta zan turara gidan. Carab ta amshe.

"Haba zauna ke da baki da ishasshiyar lafiya ina ke ina wani turara gida. Bari dai inyi miki. Kinsan tun safe naso shigowa in taimaka miki sai nai tunanin oga na wajenki kinji abinda ya hanani zuwa. Jiya sai wajen goman dare nasan an sallamoki naji Na'ila na faɗama mijinmu"

Ayya ai Yarinyar ƙanwar Rakiya bata daɗe ma da tafiya ba. Jiya kuma harda su Rahama muka dawo. Su suka yi gyare_gyaren komai har miya sukai mun data tuwo da ta tumaturi."

Zama tayi da kaskon a hannunta tace.

"Naji Hamida na bada labarin wai tayi mamaki da akace cikine dake, sabida wai ba'a mu'amular Aure dake. Sai kawai kwatsam akace kinyi ɓari. Kinsan ta kan hakan suke ta faɗa tun ranar da aka kwantar dake?"

Mamakine ya kamani ainun.

To ita Hamida yaya akayi tasan Babangida baya tarawa dani? Oh wato tasan duk abinda yake faruwa kenan ma. Duk da a gabanta nace na haƙura da mu'amalar aure da Babangida.? Amman halamu kamar sun nuna tuntuni tasan a jingine nake"

Edit with WPS Office

Duk a zuchiyata nake magana.

A zahiri sai nayi dariya nace da Maman Safara'u.

To mata da mijinta sai aji mamakin tana da ciki? In zai kwanta dani zuwa zaiyi ya sanar mata. Ga yara nan na haifa tun kafin tazo gidan. Halin annamimancine kawai na maza. Ta yiyu ya faɗa mata hakanne dan ya faranta mata. Ta yiyu kuma ƙazafi tayi mishi sabida halin kishi"

"Ai kuna bikinnan fa sunyi faɗa harya koreta, ita ƙawarta ce ta bata shawarar kada ta sake ta tafi"

Nan ta dinga bani labari. Daga haka itama ta shiga bani labarin yadda take fama da nata kishiyar da satan kwana da akeyi mata"

To ke bakya shan magungunan ne da akeyi miki satan kwana? Ai tunda maganin mata yana tasiri harda satan kwana kema sai ki dage kiyi ta sha"

Murmusawa tayi kawai.

"Kinsan Allah Maman Mardiyya kibar ɗa namiji kawai. Duk ranar da Allah ya kawoki zan nuna miki irin magungunan da nake sha bama ƴan ƙasarnan ba. Ga waɗanda nake dafawa da kaina firjina cike da tsumi_tsumi iri daban_daban, nafi Na'ila tsabta, nafita kyau, na fita komai da komai. Ni ina ganin suna son su haɗu su kasheni da baƙin cikine kawai.

Jiya da daddare muna bacci ya sulale ya fita. Yana fita na miƙe na biyo bayanshi, shi ya faɗa ɗakinta ni kuma na faɗa banɗaki na ɗauro alwala. Na shiga kai ƙararshi wajen Allah daga shi har itan.

Yana shigowa ya ganni inata Sallah. Duk sai ya tsargu yaƙi ya kwanta niko na dinga sallah dan bana son wata magana kuma.

Nayi alƙawarin bazan sake ƙorafi ko damuwa ba. Kuma in sha Allah na dena kuka koda kuwa ɗakinta sukutum zai tare. In turar ta ƙarashe kaini bango ma ni da kaina zan sallamar dashi ga ita Na'ilan mai ƙasan zinare"

Mun daɗe munata tattauna matsaloli, tare da'ita muka ci abincin rana jallof ɗin manja tayi mana, nace tayi mana tazarce har dare kawai kada in bata wahala.

Sai ukun rana ta tafi lokacin yara harsun dawo sun yi Sallah sunci abinci sunata shirin zuwa islamiyya"

Haka dai na kwana biyu ina jinyata ni kaɗai.

Khalid shi ya mayar dani asibiti domin a sake duba jikin nawa musamman ciwon cikin da yake addabata. Ranar sakun lallen gidan Sa'a sai azahar ni da Labbai muka shiga gidan. Naga Farida tsohuwar matar Babangida tazo da ɗan cikinta ƙurbibi. Nafisa ma tsohuwar matar Babangida tazo ita kam da goyonta a baya tayi aure kenan. Duk akayi gaisuwar mutunci, ni dai tunda na

Edit with WPS Office

leƙa ɗakin uwar bikin ta ganni na ganta, na gaishe da dangin miji da baƙin nesa dana kusa saina dawo waje ni da Labbai muka zauna akaita sha,anin biki.

Mun dai samu arzikin an turo mana da alala da lafiyayyen kunun gyaɗa alala leda biyu, sai kunun kuma kofi ɗaya.

Ki cinye alalan zan dai sha kunun'"

"Zan dai nemi baƙar leda in saka alalen in naje gida naci, gidan da yinwa aka tashi. Gaza fa yayi wata barna babba wallahi yana kulle mantawa nayi ban shaida miki ba. Har gida ƴan doka suka biyoshi da gudu suka kama shi."

Kai na girgiza nace.

Yayi saran daya saba ba? Yaushe ma damuwar su Gaza zata bar mutum ya samu lafiya? Wallahi ni babu inda zani, kuma a wannan karon sisina bazai yi ciwon kai ba "

"Ai ko kinje baki isa ganin Gaza ba

Rakiya ma tayi ta gama, maigogul kuwa baiko kula Rakiya ba da take bashi labarin ba balle asa ran zashi.

Kila ma sai yaci gidan ɗan kande fa, yaron da suka kusan cirema wuya yana asibiti rai ga Allah fa. Bari kiga ina zuwa in samo leda'

Ɗakin kishiyar Sa'a ta shiga ta samo leda, saina ganta da shinkafa cikin plate"

Saida ta saka alalan a leda ta jefa jaka tace.

"Ga shinkafa kishiyar Sa'a ta bani. Itama ɗakinta damƙam da jama'a"

Haka dai anayin magriba muka kama hanya.

Washegari ɗaurin aure, shima sai azahar na iso, gudunmawar jug ɗin tankaran me kofuna shida na miƙa ma Sa'a

"Angode"

Iyakar abinda tace kenan. Bata san darajar Baba Malam bane ya kawo ni bikinta ba. Matan ƙannen Babangida ko wacce sai kallon banza, anata shirin tafiya wajen walima ba dan raina yaso ba muka bi zugar motar dake jigilar kai jama'a ta kaimu.

An gaiyaci malamai Mata manya_manya sanannun da dana ambaci sunansu a ganesu, dan bidiyon walimar yana kan manhajar YouTube.

A wajen na hango Babangida shi da wata mace a bakin ƙofar shigowa hol ɗin sai murmushi yake yi mata.

Edit with WPS Office

An rarraba mana masa, cincin, da naman kaza sai ruwa da jus duk a leda. Labbai dai biyu ta amsa, na haɗa mata da nawa nace ta kaima Rakiya. Su Mardiyya naga suma duk sun samu.

Daga wajen walimar zuwa wajajen bayan isha masu ɗaukar amarya suka ƙaraso, har damu akai Amarya. Gidan amarya tubarkalla.

Bani na dawo gida ba sai wajen goman dare.

Ga zazzaɓi babu damar a ɗaga maka ƙafa abinka da dangin miji."

BABANGIDA:.

Abubuwa goma da ashirinne suka haɗu suka dame ma Babangida.

Na farko dai batun Ramatu ne. Bata da aiki a kullum sai batun kuɗi kuma manyan kuɗi ake tura mata, shi kuma lallaɓata yake yi kawai ta dai samu ta dawo ta tare.

Matsala ta biyu Ƴar Shuwa itama tunda ta tafi ya kasa gane kanta. Bata bashi hankalinta ya yayi ƙorafi sai tace suna kasuwane shi yasa.

Ana cikin haka kuma yaji batun kwantar da Sabuwa a asibiti.

Bai fita daga wannan kashe kuɗin asibiti ba aka kama mishi kayanshi a hanyar Lagos har mota biyu har direba ɗaya Allah yayi mishi rasuwa, ɗayan kuma an tsinceshi a hanya bayan faruwan abun da kwana ɗaya. Yana asibiti rai a hannun Allah. Ɓarayine da suke tare masu irin motocin ƙarafuna haka su kashe direbonin su jaye motar su tafi da motar da kayan sabida tsantsar zalunci, in suka tafi da kaya da motar shikenan magana ta ƙare, ita kanta motar yankata akeyi a sakata a kas a haɗa a siyar da'ita. gashi kaya na maƙudan kuɗaɗene a ciki

Ga gini ya rikito ya narka kaɗaɗe, ga babbar asara ta moliyoyi ta sameshi duk ya rasa inda zai tsoma ranshi.

Ya sanarma da Malama Babba halin da ake ciki bayan bikin ɗiyar Sa'a. Malama Babba ta sanarma  Baba Malam domin a saka Babangida a adda'a.

Abokan sana'arshi sai kira suke sunai mishi jaje, da ƙyar yake amsawa danma yanata ambaton Allah.

Yana zaune a ofishinshi ya tusa takaddar lissafin kuɗaɗen kamfani da adadin kayan da suke dashi a ƙasa, sai yaji hankalinshi ya sake tashi.

Kuɗin kamfani yayi ƙasa sosai gaskiya.

Idanu ya lumshe ya taso daga kujerar aikin ya zauna a kujera dogowa ya lumshe idanu kanshi da

Edit with WPS Office

zuchiyarshi na bugawa.

Kiran wayarshi ne yasa ya tuna Ƴar Shuwa yau zata dawo, duk yadda akayi ma itace ke kiransi. Idanunshi a lumshe ya ɗaga wayar ya kara a kunne"

"Hello Jannaty gamu a Abuja kaga harna yi wanka naci abinci dai nace bari in kiraka kayi mun buking jirgi in tawo"

Zan tura miki kuɗin Alhaji sai yayi miki buking."

Daga wayar tayi murmushi tace.

"To Shikenan Jannaty amman ya naji ka duk a birkice lafiya dai?"

Idanu ya lumshe yace.

"Lafiya kaina ke ciwo, ga lissafin kuɗi a office yayi mun yawa. Zan tura miki dubu talatin a account ɗinki'

Sallama suka yi ya tura mata kuɗin, ya kwanta a office ɗin kamar wasa bacci ya kwasheshi na tsawon awa uku. Da sauri ya tashi daya hango agogo lokacin Sallah ya kusa baiyi saura minti uku ba.

A gurguje ya ɗaura alwala ya fito gudu_gudu. Ya tarar yaranshi sunata auna ƙarafai da robibi da samari suke ta kawowa.

"Musa ku bar duk abinda kuke yi muje masallaci, in an gama a dawo"

Dama wannan ƙa'idarshi ce.

Sai da kuwa akayi sallar bayan sun dawo akaci gaba da kasuwanci. Babangida kuma ya aika yaro ya siyo mishi abinci. Tuwon semo da miyar taushe, da farfesun ƙafar saniya yace a siyo mishi.

Karfe biyar ya baro kamfani lokacin ƴar Shuwa ta iso Dutse tana ma gida dan har ta kira ta tambayeshi abinda zata girka.

Majalisa ya wuce a canne ya ɗan zazzage takaicin nashi ma sai goman dare ya shiga gidan.

Ɗakinshi ya wuce kai tsaye kawai. Bai jima da zama ba Ƴar Shuwa ta shigo riƙe da tiren abinci ɗauke da kyawawan kuloli. Tayi adonta da doguwar riga mai tsadar gaske. Tana dire tiran ta zauna a bakin gado tana shafo wuyan Babangida sai taji halamar da zafi.

"Jannaty naji jikinka da zafi zazzaɓi kake yi ne?'

Dake ɗan duniya ne sai cewa yayi.

"Zazzaɓin rashinki ba, ai tunda kika tafi nake zazzaɓi ke baki ga nayi rama ba? Gashi na kasa

Edit with WPS Office

samun hankali da nutsuwarki, ke kuma naki salon kasuwancin kenan da kasawa da siyarwa?"

Daɗine ya lullubeta dan ta yadda da maganganunshi. Data ma kalleshi sai taga yako yi ramar kamar yadda ya faɗa.

A baki ta dinga bashi abinci yana amshewa, Ramatu ta dinga kiran wayar Babangida. Yar Shuwa ta ɓata rai.

"Wai wake kiranka haka ne tun ɗazu ka ɗauka mana. Sannan me kalmar D S yake nufi ina buƙatar fassara"

"Bafa wata bace dan nasan duk a tunaninki mace ke kirana. D S yarone dake kula mun da motocina na surufi. Yanzu dai bari in kashe wayar ki bani labarin Dubai sannan a ɗebo mun kayan da aka saro in gansu "

Da wannan maganar ya hilaci Yar Shuwa harta mance da batun kiran waya dai.

A haka rayuwa taita tafiya Ramatu sai da tayi wats biyu cir kafin ta tare.

Ai kuwa Babangida murna kamar me, kaya ya tarkata ya koma gidanta da zama a zuwan baya garin baki ɗaya ma, anata ragargazan amarci Masha Allah.

Ta ɓangaren Yar Shuwa kuma ta tantsama harkar kasuwanci kaya basu fi wata ɗaya ba duk aka wawashesu. Sai dai wasu kuɗaɗen sun fito yayinda wasu suka dulmiya aka cinyesu tayi naci da sunturin ita kam harta gaji. Gashi wata biyu ta cika da zata koma sarin kaya ita da Hajiya Turai, kuɗinta bai kai yadda take tunani ba a madadin a kirga riba sai aka shiga ƙirga asara. Bata dai daddara ba ta tuntuɓi Babangida daya ara mata nera million ɗaya data dawo zata bashi in an siyar da kaya. Da ƙyar dubu ɗari biyar ta fito a aljihunshi shima fama yake yi tattalin arzikinshi sai ƙasa yake yi, yanzu ko motar surufi guda ɗaya ce a kamfaninshi kuma ta gaji kuɗin sabuwa yake son ya haɗa ya siya. Wani sa'in yana gani za'a kawo musu kaya na miliyoyin kuɗi ammam bashi da kuɗin siye, ga riba suna haɗa idanu dashi amma babu damar ci

A cikin watanni biyunnan abubbuwa suka haɗu suka caɓe ma Babangida, ga Ramatu da ciki ita da tace bata haihuwa, gashi har izuwa wannan lokacin bai sanar ma Malama Babba yayi Aure ba kasancewar kwana biyunnan ciwon sikari ya dameta anata sintirin zuwa asibiti ne.

Ga ƴar Shuwa itama ciki gareta yana lissafin hidindimun dake gabanshi, ga kuɗin ma babu na kirki da buguzun kawai yake ci. Ana haka Sumy itama ta kirashi take sanar dashi ciki gareta.

Ko da ya kaita asibiti dan a cire cikin kamar yadda suka saba Dr ya sanar musu a wannan karon komai zai iya faruwa da Sumy in suka matsa.

Sumy na jin haka ta daka tsalle tace ba za'a zubar mata da cikinta ba. Sun yi sunturin asibiti yafi uku maganar dai ɗaya ce, Sumy tace babu batun zubar da ciki kawai zata haifa data haihu ɗansu yayi wayo sai suyi aurensu kawai.

Edit with WPS Office

Haka rayuwar taita turawa tsakankanin Babangida da iyalanshi.

SABUWA:.

Haka rayuwar taci gaba da garawa yau fari gobe tsumma, Dama ni dai ƴar kallo ce a gidan Babangida, ginin daya kwaso naga a kwana biyunnan duk komai ya tsaya an dai kashe ginin.

Ta ɓangaren matanshi naga zaman gugar jigida suke yi da junansu, ranar ma ina jiyosu suna cacar baki a tsakar gida. Ita Yar Shuwa tana bakin cikin Babangida ya bama Hamida jari na nera dubu ɗari tana ɗan saida takalma da mayafai abinda ya kawo rigimar kenan.

Ta ɓangaren Khalid kuwa a kullum sake shaƙuwa muke yi da junanmu, kuma muna yawan haɗuwa akai_akai amman haɗuwar tamu tafi da rana ido na ganin ido, koma da safe haka. Yana biya mun dukkankin buƙatuna da zaran na faɗa mishi.

Gaga gaga al'amura sukaita tafiyar wahainiya.

A cikin ƴan watanni na fuskanci makirci, sharri, kazafi iri iri a wajen ƴar Shuwa. Har cewa tayi inta kwanta tana mafarkin zan kasheta da abinda yake cikinta.

Ha'a ni cikin dare Babangida ya shigo ina chart ni da Khalid wajajen biyun dare. Da sauri na miƙe.

"Ke Sabuwa ki sakarma Shuwa mara tayi fitsari na dai faɗa miki. Abunnan ya isheni ashe har maita yi kike yi kin hana Yar Shuwa kwanciyar hankali tunda kika ga cikinta ya tsufa."

Yaimun cin kashin da ko kare bazai ci ba ya fita.

Yanzu fa a unguwarmu ganina suke marar kirki dan basu taɓa jin labarin abu mai daɗi a kaina ba. Hamida tayi nata, Yar Shuwa ma tayi nata itama tayi ƙawaye kuma ko da yaushe ɗakinta cike da mata, ta zama uwar tattare matan unguwa duk wani gulma da makirci a ɗakinta ake haifanshi, kuma haka zatai ta girki anaci, amman Babangida baya gani. Yafi ganin wanda zan girka in kai gidanmu, ko ɗan wanda zan auna in kai musu, alhalin bashi yake ciyar damu ba, kuɗin makarantar yara tuni ya dawo wuyan Malam Baba, hatta kuɗin tara na yaran makaranta shike basu na duk sati.

Sassafe mahaifiyarta tazo ta tafi da'ita ai kuwa kwananta ɗaya a gidansu ta haifo diyarta mace.

Har akai suna, tayi arba'in ta dawo ɗakinta daga ita har ɗiyar ban sasu a idanuna ba. Nadai ji labarin irin tiƙa_tiƙan ragunan da aka yanka mata, da girke_girken da akayi. Ance har akwati Babangida yayi na Baby da Maman baby, dangin Babangida kuwa sun nuna mata kara sosai kwana bakwai suka yi suna sunturi. An raba abinci kab tsukukun layinmu, amman banda gidanmu da gidan Malam Habu sabida Labbai na aure a gidan. Duk wannan labaran a bakin Rakiya nake ji da naje na wuni a gida sati guda da sunan.

Edit with WPS Office

Yarana basu da ikon su shaƙata a tsakar gida zata kamasu da duka, tun ina kawaici na shiga tanka mata muna yi tunda abinda take so kenan.

In goga ya dawo ta kitsa mishi ƙarya da gaskiya ya hauni da faɗa da zagin iyayena. Allah ya sani na gaji da auren Babangida hakkina zan nema ya sakeni ko da tsiya ko da arziki. Ko a tsakar gida na haɗu da Yar shuwa sai gabana ya yanke ya faɗi. Sabida bana son rigima, kuma bana son zuchiya ta tunzurani in aikata mata abinda zan ƙarashe rayuwata a gidan yari. Ta kai ta kawo ko kashe mun yara zata yi bazan ko iya leƙawa tsakar gidan ba. Hana yaran nayi kawai fita, amman Mardiyya ita ke mata aiki harda wankinta ita ke yi.

A hakan munata cuɗawa har ƙara nakai wajen Malam Baba akan ya umarci Babangida ya sake ni. Ya dinga lallaɓani yana bani kalma. Rakiya da Maigogul da suka ji labari sukai mun tas wannan ya zaga ya cika ya ba wannan, a lokacin watan Labbai biyu da Auren Malam Habu auren da saida akayi dambarwar jaraba kafin aka yi shi, da har mun cire rai da auren ma to kana naka Allah na nashi. Duk da haka ban sare ba tunani nake ta faman yi tayaya zan rabu da wannan ƙaddararren auren? Idanuna ya rufe hawan jini da ciwon damuwa na shirin illatamun rayuwata. Yanzu ko magana akeyi mun ba kasafai na fiye ji ba, ni ba kurma ba bala'in Babangida na neman mayar dani nakashasshiya.

Ranar da bazan mance da'itaba itace ranar juma'ar dana samo hanya mafi sauƙi da zan rabu da auren Babangida, ko yaƙi uwarshi da ubanshi saiya tafa mun takaddata, daga inda naje ɗinma saida na biya asibity jinina kuwa ya hau sosai, gashi ko bacci bana samu. Da  rana Khalid ya dawo dani gida zan sauka a daidai layinmu kwatsam saiga Babangida shi kuma da Hamida a mota sunzo zasu wuce.

Wani irin wawan burki yaja da ƙarfin gaske, niko gabana ya tattake ya faɗi ni da Babangida muka shiga kallon kallo. Saina dake kamar banji tsoro ba.

Khalid ne ya sakko ya buɗe both ya ciro mun manyan ledojin da yayo mun siyayya ya zagayo ta gabana yana murmusawa. Cike da hulawar daya saba bani a kullum. Har mayafina ya gyara mun. Nima wani lafiyayyen murmushi nayi ma Khalid nice harda lankwashe wuyana.

Kur naga Babangida yayi yana dubanmu numfashinshi na fita da sauri da sauri, tamkar wani fusataccen zaki. Hamida kuma bakinta ta sake tana son ganin gulma.

KAKASARA KAKA

AKWAI KURA ME NEMAN MATAN BANZA YAU YA KAMA TASHI MATAR"

Shin ko ya zata kaya a tsakankanin Babangida da Khalid, dama Sabuwa?

MRS BUKHARI

Edit with WPS Office

Anan gabar na kawo karshen littafi na daya

Zan tafi hutu na kwana goma cir dan Allah aimun afuwa wani gagarumin uzurine ya same ni. Sannan ko babu uzirin ina yin hutu duk karshen littafi duk da baya kaiwa kwana goma

Amman kunsan babu wasa dana dawo zanci gaba da baku kullum.

Labarin yanzu ne zamu shigeshi gadan gadan.

Ku faɗi ra'ayoyinku

Da darrusan da kuka samu a iyakar littafi na ɗaya.?

Sannan wanne sako marubuciyar take son isarwa a cikin labarin?

Shin ya yanayin tasirin da labarin yayi miki?

Duka wannan amsar ina son jinta daga bakunan masoyana masu kamshin tufa.

Ni dai na tafi honeymood kuimun adda'ar dawowa lafiya domin jin ci gaban wannan cakwakiyar.

Son so cau_cau cau

⚔⚔⚔⚔⚔⚔🤺🤺🤺🤺🤺🤺🗡🗡🗡🗡🪚🪚🪚🔪🔪

Edit with WPS Office

Edit with WPS Office